# SHARHIN KA'IDOJI MASU BAYANI A KAN TAUHIDI DA KASHE-KASHENSA

(التَّقْسِيمُ وَالتَّقْعِيدُ لِلْقَوْلِ الْمُفِيدِ)

**WALLAFAR:**
**Sheikh Haisam dan Muhammad Jamil Sarhan**
Tsohon Mai karantarwa a Sakandaren Masallacin Annabi SAW
http//attasseel-alelmi.net
http//sahaan.net

**Allah Ya gafarta masa da iyayensa, da duk wanda ya taimaka wajen buga Littafin**

**FASSARAR:**
Murtala Yaqub Ibrahim

**Littafin Waqafi ne Domin Allah**
**Ba ya halatta a sayar da shi**

**TARJAMAR HAUSA**

Bugun Farko

Dukkan Hakokin Littafin abun kiyayewane
waɗanda suke sha'awar buga shi ko fassara shi don rabawa kyauta su tuntubi mawallafin ta Yanar gizo:

islamtorrent@gmail.com

بسم الله الرحمن الرحيم

Godiya ta tabbata ga Allah, muna gode masa, kuma muna neman taimakonsa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrin kawunanmu, da munanan aiyukanmu, wanda Allah Ya shiryar dashi, ba mai batar dashi, kuma duk wanda Ya batar dashi, ba wani mai shiryar dashi, kuma ina shaidawa babu abin bautawa bisa cancanta sai Allah Shi kadai, ba Shi da abokin tarayya, kuma ina shaidawa lallai Annabi Muhammadu BawanSa ne kuma ManzonSa.

Bayan haka:

## KA'IDOJI

## YA KAMATA A SANSU KAFIN KARANTA LITTAFIN

1. Ya dace dalibin ilimi ya haddace Matanin Kitabut tauhid kafin darasinsa. ( Kayi hadda, duk mahaddaci jagora ne ).
2. Sanin dalilin kafa hujja da kowace a'ya, da sababin zuwanta cikin ba'bin.
3. Sanin alakar kowani babi ga kitabut tauhid, da sababin kawo shi, domin dunkulewar manufar littafin waje guda.
4. Zamu takaita ne kan sharhi guda; " **Al-Qaulul Mufiid** ", Wallafar Shaikh Muhammad bin Shaleh Al-Uthaimin -Rahimahullah- idan muka gama da shi kuma sai mu dauko wani sharhin, domin kar a samu cin karo.

## ME YASA MUKE KARANTA WANNAN LITTAFIN?

1. Saboda Malamai na Allah sunyi wasiyci kan karanta shi.
2. Yana daga mafi kyayun abinda aka wallafa a wannan babin.
3. Mawallafin ya kyautata wajen mayar da martini da rusa hujjojin wadanda suka saba wa shari'a, da rusa shubuhohinsu, tareda da Ambaton dalilai.
4. Allah ya sanya wa littafin karbuwa a bayan kasa.
5. Malamai sunyi wasiyci da a haddace shi tareda fahimtarsa.
6. An Kyautata tsara babukan littafin da jeranta su yanda ya dace.
7. Malamai sun mayar da hankali wajen karantar dashi, da yawan masa sharhi.

8. Littafin cike yake da dalilai daga Al'kurani da Saunnah.
9. Saukin Lafuzzansa.
10. Shaidar Malamai ga mawallafin da tumbatsa cikin ilimi, da ingatacciyar aqida.
11. Littafin ya mayar da hankali sosai kan Tauhhidin ibada (Uluhiya), saboda kusakurai masu yawa da mutane suka auka ciki gameda wanna nau,i na tauhidi, sannan ya ambaci Tauhidin Rububiyya, da Tauhidin Asma'u was sifat.
12. Saboda mawallafin littafin (Allah Ya jikan sa) ya rubuta shi ne a bisa tafarkin Salaf (Magabata na kwarai), bai ambaci wani abu daga maganarsa ba, kamar Imamul Bukhari (Allah Ya jikansa) gameda littafinsa (Sahihul Bukhari).

## KITABUT TAUHID YA KUNSHI (BABUKA 67)

Kafin fara karatun kowani littafi, yakamata a fara karanta muqaddimar littafin da fihirisarsa don sanin abinda littafin ya kunsa, da fahimtar hanyar mawallafin, sa'annan fahimtar abinda littafin ya kunsa a dunkule, don haka, zamu iya kasa littafin zuwa kashi goma:

## [1]: GABATARWA (BABUKA: 5 )

**[1] Mawallafin bai sanya tarjama ma wannan babin ba; (BABIN WAJABCIN TAUHIDI).**

Mawallafin ya kawo shine don bayyanin cewar: Tauhidi shine farkon wajibai akan bayi, kuma mafi girman wajibai, domin shine hakikanin da'awar Annabawa, -Amincin Allah ya tabbata a gare su-.

**[2] BABIN FALALAR TAUHIDI DA YANDA YAKE KANKARE ZUNUBBAI.**

Mawallafin ya kulla wannan babin ne domin janyo hankula da kwadaitarwa, tare da bayanin cewa ambaton falalar wani abu baya nuni kan rashin wajabcisa, kuma domin akwai wasu da suke hana karatun Tauhidi da karantar da shi..

**[3] BABIN DUK WANDA YA TACE TAUHIDI ZAI SHIGA ALJANNA BA TARE DA HISABI BA.**

Ya kawo shine domin wajabcin tace Tauhidi daga shirka da bidi'oi, da aiyukan sabo, kulla wannan babin bayan babin wajabcin Tauhidi da falalarsa ya dace.

**[4] BABIN JIN TSORON AUKAWA CIKIN SHIRKA.**

Ya kawo shi ne saboda duk wanda yake son ya tace Tauhidi wajibibi ne a kansa yaji tsoron aukawa cikin shirka, kuma yaji tsoro ga waninsa, saboda zai iya zaton cewar ya tace Tauhidin alhali bai tace ba, sannan dukkan babukan da ya kawo su a bayan wannan babin bangare ne na tace Tauhidi;

Misali; ( Babin tsoron aukawa cikin shirka, bangare ne na tace Tauhidi ).

**[5] BABIN ( KIRA ZUWA GA KALMAR SHAIDAWA BABU ABIN BAUTAWA BISA CANCANTA SAI ALLAH ( LA'ILAHA ILLALLAHU ).**

Ya kawo shi ne -wallahu a'alam- saboda sabubba guda biyu:

1. Saboda duk wanda yake son ya tace Tauhidi to wajibi ne yayi kira zuwa gare shi, kamar yanda Annabi (sallallahu alaihi wa sallam) da mabiyansa sukayi.
2. Kuma domin mayar da martani ga wanda yace: farkon abin da za'ayi kira akai shine Sallah.

## [2]: TAFSIRIN TAUHIDI (BABUKA: 9

**[6] BABIN ( TAFSIRIN TAUHIDI DA SHAIDAWA BABU ABIN BAUTAWA BISA CANCANTA SAI ALLAH).**

Bayan ya ambata mana wajabcin Tauhidi, tareda kwadaitar da mu zuwa gareshi, da wajabcin tace shi, da tsoron kishiyarsa (abinda yake bata shi = **shirka**), da kuma kira zuwa gare shi, ya dace ya bayyana mana hakikanin wannan Tauhidin, daga wannan babin har zuwa karshen littafin .

**[7] BABIN ( YANA DAGA SHIRKA: SANYA ZOBE / KAMBU, KO ZARE DA MAKAMANTANSU DOMIN DAGE BALA'I KO TUNKUDE SHI )**

Wannan tafsirin Tauhidi ne, bayan sanin kishiyarsa.

**[8] BABIN ( ABINDA YA ZO NA DALILAI KAN HUKUNCIN TOFI DA LA'YU)**

Ya kawo shi ne don bayanin tofi da la'yu irin na shirka wanda suke kore Tauhidi.

**[9] BABIN ( HUKUNCIN WANDA YA NEMI ALBARKA DA WATA BISHIYA KO DUTSE DA MAKAMANTANSU ).**

Ya kawo shi ne domin bayanin Tabarruki (neman albarka) irin wanda aka hana, shine wanda yaci karo da Tauhidi.

**[10] BABIN ( ABINDA YAZO NA HUKUNCIN YANKA DON WANIN ALLAH).**

Yayi nufin bayanin cewa yin yanka domin wanin Allah saboda soyayya gareshi da girmama shi, yana warware Tauhidi ( yana lalatashi ).

**[11] BABIN ( BA YA HALATTA AYI YANKA DON ALLAH A WAJEN DA AKE YANKA DON WANINSA).**

Yayi nufin bayanin abin da wadansu jahilai ke aikatawa -wadanda suke kore Tauhidi- na kamanceceniya da mushirikai da tarayya dasu cikin idodinsu da wajajen ibadarsu.

**[12] BABIN (YANA DAGA SHIRKA YIN BAKANCE DON WANIN ALLAH).**

Ya kawo shi ne don bayanin irin bakancen da aka hana; wanda yake lalata Tauhidi.

**[13] BABIN (YANA DAGA SHIRKA NEMAN TSARI DA WANIN ALLAH ).**

Yayi nufin bayanin cewa; neman tsari da wanin Allah cikin abin da babu mai iko akai

Sai Allah, yana warware Tauhidi

**[14] BABIN (YANA DAGA SHIRKA; NEMAN AGAJI A WAJEN WANIN ALLAH KO ROKONSA).**

Yayi niyyar bayanin cewa, yana daga ayyukan shirka; neman agaji da rokon wanin Allah abinda babu mai iko akansa sai Allah.

## [3]: BACIN BAUTAR WANIN ALLAH ( BABUKA 4)

**[15] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: (SHIN SUNA SHIRKA NE DA ABIN DA BA YA HALITTAR KOMAI KUMA SU NE AKE HALITTAWA).** *(QS. Al-A'araf: 191).*

Ya kawo shi ne don kore bauta ga wanin Allah, sawa'un; Annabi ne ko wani gunki ko makamancisu.

**[16] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: ( HAR A LOKCIN DA AKA YAYE TSORO DAGA ZUKATANSU SAI SU CE: MENENE UBANGIJINKU YA CE? SUKA CE, GASKIYA , KUMA SHI NE MADAUKAKI MAIGIRMA)** *(QS. Saba'i: 23).*

Ya kawo shi ne don kore bauta ga Mala'iku Masu girma.

**[17] BABIN CETO.**

Ya kawo shi ne don bata abin da kafirai suke riyawa na ceton iyayen gijinsu.

**[18] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: ( HAKIKA KAI BA KA SHIRYAR DA WANDA KA SO, AMMA KUMA ALLAH YANA SHIRYAR DA WANDA YAKE SO ).** *(QS. Al-Qasas: 56).*

Ya kawo shi ne don bayanin Allah shi kadai ne yake da ikon shiryarwa ta gam da katar banda waninsa.

## [4]: SABABIN KAFIRCIN BANI ADAM (BABUKA:

Bayan ya fassara Tauhidi, kuma ya ba'ta bautar wanin Allah, to ya dace ya ambaci sabubban da suke sa a auka cikin kafirci, domin mu nisance su.

**[19] BABIN (ABIN DA YA ZO NA SABABIN KAFIRCEWAR BANI ADAM DA BARIN ADDININSU; SHINE: WUCE IYAKA CIKIN SALIHAN BAYI).**

Mafi girman hadari cikin sabubban kafircewar Bani Adam, kuma shine farkon shirka da ta faru a bayan kasa.

**[20] BABIN ABIN DA YA ZO NA KAUSASAWA A KAN WANDA YA BAUTA MA ALLAH A WAJEN KABARIN WANI SALIHI, TO YAYA KUMA IDAN YA BAUTA MA SA) .**

Hotuna da daukansu sabubba ne NA aukarwa shirka da Allah, da rikon kaburbura a matsayin masallatai.

**[21] BABI (ABINDA YAZO NA CEWAR: WUCE IYAKA CIKIN KABURBURAN SALIHAI YANA MAYAR DA SU GUMAKA DA AKE BAUTA MUSU BA ALLAH).**

Wuce iyaka cikin kaburburan salihan bayi sabubba ne na kafirci.

**[22] BABI (ABIN DA YA ZO NA TSAREWAR MANZON ALLAH -SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAM- JANABIN TAUHIDI, DA TOSHE DUK WATA HANYAR DA ZA TA KAI ZUWA GA SHIRKA).**

Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) ya toshe duk hanyoyin shirka a kuduri da aiyuka, Babi ya na tafe kan toshewarsa kan maganganun da su ke kaiwa ga shirka.

**NA BIYAR: LALATA HUJJAR WADANDA SU KE CEWA SHIRKA BA ZE AUKU CIKIN WANNAN AL'UMMAR BA, DA YANKIN LARABAWA (BABI GUDA NE).**

**[23] BABIN ( WANI SASHE NA WANNAN AL'UMMUR ZAI BAUTA WA GUMAKA).**

**[6] AIYUKAN SHAIDANU ( BABUKA 7)**

**[24] BABIN ( ABIN DA YA ZO KAN SIHIRI ).**

Ya kawo shi ne, don bayanin sihiri ba ya yiyuwa sai an kafirce wa Allah, sihiri ya na da cikin manyan hanyoin da suke kai mutane zuwa ga kafirci.

**[25] BABIN (BAYANIN WASU NAUUKA NA SIHIRI).**

Ya kawo shi ne don ya karantar da mu cewar sihiri ya na da nauuka, kuma wajibi ne a nisance su.

**[26] BABI (ABIN DA YA ZO KAN BOKAYE DA MAKAMANTANSU).**

Ya kawo shi ne don ya mana bayaninsu da hukuncin zuwa wajensu da ire iren zuwa wajen nasu.

**[27] BABI (ABIN DA YA ZO KAN AN-NUSHRA(WARWARE SIHIRI).**

Ya kawo shi ne don kawar da rikici da ambaton abin da aka hana daga gare shi da wanda akayi rangwame.

**[28] BABI (ABIN DA YA ZO KAN CAMFI).**

Ya kawo shi ne don kore abin da mutanen jahiliyya suke kai na camfi.

**[29] BABIN ( ABIN DA YA ZO NA ATTANJIM ( ILIMIN TAURARI ).**

Ya kawo shi ne don bata ilimin da ake raya shi na sanin gaibu.

**[30] BABIN ( ABIN DA YA ZO NA JINGINA SAUKAN RUWAN SAMA DA TAURARI ).**

Ya kawo shi ne domin lalata ratayuwa da sabubban shirka.

## [7] AIYUKAN ZUKATA (BABUKA: 9 )

**[31] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ KUMA AKWAI DAGA MUTANE WANDA YAKE RIKAN WASU KISHIYOYI BAICIN ALLAH ].** (QS. Al-Baqarah: 165).

Ya kawo shi ne don kore Tauhidi daga wanda ya so wani abin halitta kamar yanda yake son Allah ko fiye da yanda yake son Allah.

**[32] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ IYAKA DAI WANCANINKU SHAIDAN NE YAKE TSORATAR DA KU MASOYANSA ]** (QS. Al-Imran: 175).

Ya kawo shi ne don kore Tauhidi daga wanda yak e tsoron wani abin halitta kamar yanda yake tsoron Allah ko sama da haka.

**[33] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ KUMA GA ALLAH SHI KADAI SAI KU DOGARA IDAN KUN KASANCE MUMINAI]** (QS. Al-Maidah: 23).

Ya kawo shi ne don kore Tauhidi daga wanda ya dogara ga wanin Allah.

**[34] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ SHIN SUN AMINCE WA MAKARUN ALLAH ? ]** (QS. Al-A'araf: 99).

Ya kawo shi ne domin musulmi ya hada tsakanin tsoro da kwadayi cikin bautar Allah.

**[35] BABI ( YANA DAGA IMANI DA ALLAH HAKURI AKAN KADDARAR ALLAH).**

Ya kawo shi ne don bayanin halin mumini yayin jarabawa.

**[36] BABIN ABIN DA YA ZO KAN RIYA.**

Ya kawo shi ne domin bayanin girman hadarin riya ga musulmi, kuma itace abin da a kafi tsoro ga salihan bayi.

**[37] BABIN: YANA DAGA SHIRKA MUTUM YA NUFI DUNIYA DA AIKINSA ( KARAMAR SHIRKA CE ).**

Ya kawo shi ne don bayanin duk wanda ya nufi duniya da aikin lahira, to ya auka cikin shika, bayanin haka shine yardarsa da fushinsa duka kan duniya.

**[38] BABIN: DUK WANDA YA BI MALAMAI DA SHUWAGABANNI CIKIN HARAMTA ABIN DA YA HALATTA, KO HALATTA ABIN DA ALLAH YA HARAMTA TO HAKIKA YA RIKE SU IYAYEN GIJI (SHIRKAN DA'A).**

Ya kawo shi ne don bayanin abin da yake warware Tauhidi, sakamakon kaiwa hukunci zuwa ga wanin Allah.

**[39] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ SUNA SON SU KAI KARA ZUWAGA GA DAGUTU ]** (QS. An-Nisa: 60).

Ya kawo shi ne don taimakon musulmi, wajen fahimtar ma'anar: kafircewa wa dagutu, da banbancewa tsakakin imani na gaskiya da na karya.

## [8] TAUHIN SUNAYE DA SIFOFI (BABI GUDA)

[40] **BABI ( HUKUNCIN WANDA YA MUSANTA WANI ABU NA SUNAYEN ALLAH KO SIFONFINSA ).**

Ya kawo shi ne don kore Tauhidi daga wanda ya musanta wani suna ko sifar Allah.

## [9] LAFUZZAN DA AKA HANA, DA NA SHIRKA (BABUKA 29)

**[41] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ SUNA SANIN NI'IMAR ALLAH SA'ANNAN KUMA SUNA INKARINTA ]** (QS. An Nahl, 83).

Ya kawo shi ne don bayanin abin da ya wajaba kan mumini game da ni'imomin Allah.

**[42] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [SABODA HAKA KADA KU SANYA WA ALLAH WASU KISHIYOYI, ALHALIN KUWA KUNA SANE ]** **(QS. Al Baqarah, 22).**

Ya kawo shi ne don bayanin halin musulmi na rantsuwa da Allah ba da wanin sa ba, tare da bayanin banbanci tsakanin kalmar: ( و ) da ( ثم ) yayin rantsuwa.

**[43] BABIN ( HUKUNCI WANDA AKA MASA RANTSUWA DA ALLAH KAN WANI ABU YA KI GAMSUWA ).**

Ya kawo shi ne don bayanin girman Allah cikin zuciyar musulmi yayin da aka masa rantsuwa da Allah kan wani abu.

**[44] BABI HUKUNCIN CEWA: ( ABINDA ALLAH YA SO KAIMA KA SO).**

Ya kawo shi ne don tsawatar wa ga musulmi game da yin tarayya cikin kalmar Mashi'a (son kasantuwar wani abu).

**[45] BABI ( WANDA YA ZAGI ZAMANI HAKIKA YA CUTAR DA ALLAH MADAUKAKI ).**

Ya kawo shi ne don hana musulmi zagin wani abu na zamani, (Kamar: Iska, Zafi, Sanyi da sauransu) domin hakan zagin wanda ya umarce su ne kuma ya hore su .

**[46] BABIN ( HUKUNCIN KIRAN WANI DA: ALKALIN ALKALAI DA MAKAMANCINSA).** Ya kawo shi ne don tsawatar wa musulmi kar ya ketare iyakar Rububiyar Allah.

**[47] BABIN GIRMAMA SUNAYEN ALLAH MADAUKAKI DA CANZA SUNA KAN HAKA.**

Ya kawo shi ne don bayanin yanda ya kamata mumini ya girmama sunayen Allah da sifofinsa, da Addininsa da Annabawansa.

**[48] BABIN ( HUKUNCIN WANDA YA YI IZGILI DA WANI ABU NA ADDININ ALLAH KO ALKUR'ANI KO MANZON ALLAH SALLAL LAHU ALAIHI WA SALLAM).**

Ya kawo shi ne don bayanin kafircin me izgili da addinin Allah, da yanda za'a mua'malance shi, da wajabcin kiyaye harshe.

**[49] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ KUMA LALLAI IDAN MUKA DANDANA MASA WATA RAHAMA DAGA GARE MU BAYAN WATA CUTA DA TA SHAFE SHI LALLAI ZAI CE WANNAN -NIIMAR- TAWA CE ]** (QS. Fussilat, 50).
Ya kawo shi ne don bayanin abin da ya zamo wajibi akan musulmi yayin zuwar wata ni'ima gare shi da bayan samuwarta.

**[50] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ YAYIN DA YA BA SU SALIHI SAI SUKA SANYA MASA ABOKAN TARAYYA CIKIN ABINDA YA BA SU ]** (QS. Al a'araf, 190).

Ya kawo shi ne don bayanin yanayin mumini yayin wata ni,ima, da haramta duk wani sunan da aka bautar da shi ma wanin Allah.

**[51] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ KUMA ALLAH YA NA DA SUNAYE MASU KYAU SAI KU ROKE SHI DA SU ]** (QS. Al A'araf, 180).

Ya kawo shi ne don tsawatar wa mumini kan ilhadi cikin sunayen Allah da sifofinsa.

**[52] BABIN ( BA YA HALARTA ACE: ( ASSALAMU ALAL LAH ).**

Ya kawo shi ne don tsawatar wa mumini kan nisantar duk lafuzzan da suke kore ladubba tare da Allah.

**[53] BABI ( HUKUNCIN CEWA: ALLAH KA GAFARTA MINI IN KA SO ).**

Ya kawo shi ne domin tsawatar wa mumini kan sanya wa Allah sharadi cikin addu'a, -kamar cewarsa; Allah ka gafarta mini in ka so- da kuma kara fadakar da shi kan matsayin Allah.

**[54] BABI: [ KAR WANI YA CE: BAWANA KO BAIWATA ]**

Ya kawo shi ne domin fadakar da musulmi game da kyautata lafuzza.

**[55] BABI: [ BA A HANA WANDA YA ROKI WANI ABU DA SUNAN ALLAH ].**

Ya kawo shi ne domin bayanin halin musulmi yayin da aka roke shi da sunan Allah, sai ya amsa don girmama sunan Allah.

**[56] BABIN: [ BA A ROKON KOMAI DA FISKAR ALLAH SAI ALJANNAH ].**

Ya kawo shi ne domin bayanin halin muwahhidi game da girmama Allah, da cikakken ladabi tare da Allah.

**[57] BABIN: [ ABIN DA YA ZO CIKIN FADIN: BA DOMIN KAZA BA DA… ]**

Ya kawo shi ne domin bayanin ladabin musulmi wajen kyautata Magana, da haramcin hawan kawara wa shari'ar Allah ko kaddararsa.

**[58] BABI [ ANYI HANI KAN ZAGIN ISKA / GUGUWA ].**

Ya kawo shi ne don shiryar da musulmi zuwa ga Magana mai amfani yayin da ya ga wani abin da ba ya so.

**[59] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ SUNA ZATON ABIN DA BA SHI NE GASKIYA BA, A GAME DA ALKAH, IRIN ZATO JAHILIYYA ]** (QS. Al- Imran, 154).

Ya kawo shi ne don tsawatar da musulmi kar ya munana zato wa Allah, irin zaton jahiliyya.

**[60] BABIN [ ABIN DA YA ZO NA HUKUNCIN MASU INKARIN KADDARAR ALLAH ].**

Ya kawo shi ne don bayanin yanayin imanin mumini da abin da Allah Ya kaddara.

**[61] BABIN [ABIN DA YA ZO NA HUKUNCIN MASU DAUKAN HOTO].**

Ya kawo shi ne don ya fadakar da musulmi kan hadarin ketare iyakar Rububiyyar Allah.

**[62] BABIN [ ABIN DA YA ZO NA HUKUNCIN YAWAN RANTSUWA ].**

Ya kawo shi ne don wasiyya ga mumini kan tsare imaninsa, da girmama Allah yayin ta'amuli da mutane.

**[63] BABIN [ ABIN DA YA ZO NA ALKAWARIN ALLAH ].**

Ya kawo shi ne don mumini ya girmama alkawarin allah da alkawarin manzon Allah - Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- cikin yanayi na sauki ko tsanani.

**[64] BABIN [ABIN DA YA ZO NA RANTSUWA AKAN ALLAH].**

Ya kawo shi ne don tsawatar wa mumini kar ya ketare iyakan Rububiyyar Allah da rufe kofar Rahamar Allah kan bayinsa.

**[65] BABAIN [ BA'A NEMAN CETO DA ALLAH AKAN BAYINSA ].**

Ya kawo shi ne don tsawatarwa ga mumini, kada ya sanya matsayin wani halitta sama da matsayin Allah.

**[66] BABIN [ ABIN DA YA ZO NA CEWA: MANZON ALLAH SALLAL LAHU ALAIHI WA SALLAM YA TSARE SHINGEN TAUHIDI KUMA YA TOSHE HANYOYIN SHIRKA ]**

Ya kawo shi ne don mumini ya nisani duk wata maganar da zata bayu zuwa shirka.

**NA GOMA: CIKITAWA (BABI DAYA NE)**

**[67] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA: [ BASU GIRMAMA ALLAH MATUKAR GIRMAMARSA BA]** (QS. Az-Zumar 67).

Ya kawo shi ne don yayi wa mumini bayanin cewa mushirikai wadanda ba su kadaita Allah ba, to ba su girmama Allah hakikanin girmama shi ba; don haka ya kai mumini ka kiyayi tafarkinsu.

## NA FARKO: MUQADDIMAR KITABUT TAUHID (TA KUNSHI BABUKA BIYAR)

Me yasa mawallafin baiyi mukaddima ma wannan littafin ba?

[1] Ta fadi ne daga sashen makwafa littafin, domin an samu Basmala da Hamdala da Salati wa Annabi (Sallallahu Alaihi Wa Sallam) a wasu kwafi na littafin.
[2] Ya wadatu ne da tarjamar littafin, domin kasantuwanta lakanin abinda littafin ya kunsa [Tauhidi].

[3] Ya yi koyi ne da Imamul Bukhari (Allah Ya jikan sa), yanda shi ma bai yi mukaddima wa Littafinsa ba, domin ya alakanta mutane da Al kur'ani da Sunnah.
[4] Babuka biyar na farko su ne a matsayin mukaddima.

## MA'ANAR TAUHIDI

**A Larabce:** Tushe ne na **(ya kadaita wani abu)** idan ya mayar da shi abu guda.

**A Shari'ance:** Kadaita Allah da abin da Ya kebanta shi, n rububiyya da Uluhiyya da Asma'u was Sifat.

[1] Tauhidur Rububiyyah: Shi ne kadaita Allah Ta'ala da Halitta da Mulki da Juya al'amurra, ko kuma: kadaita Allah da Ta'ala da Aiyukansa.

[2] Tauhidul Uluhiyyah (Al Ubudiyyah): Shi ne kadaita Allah Ta'ala da Bauta, ko kuma: Kadaita Allah Ta'ala da aiyukan bayi.

[3] Tauhidul Asma'i was Sifat: Shi ne kadaita Allah Ta'ala da abin da Ya Kira kanSa da shi, ko Ya sifanta KanSa da shi, a cikin Littafinsa ko bisa Harshen Manzonsa (Sallallahu Alaihi Wa Sallam), A tabbatar da abin da Ya Tabbattar wa KanSa, sa'annan a kore abin da ya kore wa KanSa. ba tare da jirkitawa ba, ko korewa, kuma ba tare d yin bayanin yanayin Sifar ba ko misalta ta.

Ba'a karban aiyuka sai da Tauhidi, kuma an halitta mu domin mu kaita Allah ne, babu mai shiga Aljannah sai mai Tauhidi, kuma Tauhidi shi ne da'awar dukkan Annabawa, Kuma tabbatar da Tauhidi da tace shi ya na hana aukawa cikin shirka, Tauhidi sababi ne na yawaitan kyawawan aiyuka.

## IBADA: TA KUNSHI ABUBUWA BIYU:

[1] **MAI AIKIN**: Aikata bauta, na nufin Kankan da kai wa Allah da aikata abubuwan da Ya yi umarni da su, da nisantar abubuwan da ya yi hani a kansu; soyayya gare shi da girmama shi.

[2] **AIKIN**: Abin da ake bauta wa Allah da shi: Suna ce da ta tara dukkan abin da Allah Yake so kuma Ya Yarda da shi, na maganganu da aiyukan fili da na boye. ( Ibn Taimiyya ne ya fada. رحمه الله).

## [1] BABIN WAJABCIN TAUHIDI

Mawallafin Allah Ya jikansa bai yi tarjama ma wannan babin ba, don ya alakanta mutane da Al kur' ani da Hadisi, dalilan da ya ambata suna nuni akan wajabcin Tauhidi, don haka za mu iya kiran sa **( BABIN WAJABCIN TAUHIDI )** ”.

### DALILI NA FARKO:

Da fadin Allah Ta'ala:

(وَمَا خَلَقْتُ الْجِنَّ وَالْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ)

*“Ban halicci mutum da Aljan ba se don su bauta mi ni.” (QS. Az Zariyat, 56).*

● Ma'ana (لِيَعْبُدُونِ): *Su kadita ni da bauta*, su kankan da kai gare ni da yin da'a, su aikata abin da aka umare su, kuma su bar abin da aka hane su. ( Abdullahi dan Abbas Allah Ya kara yarda a gare su ya ce: (Duk lafazin: **" عبادة bauta "** a cikin Alqur’ani, ma'anarta **Tauhid**.

● Ma'anan ayar**:** Ban halicci mutum da aljan sabo da wani abu bu face bauta.

### DALILI NA BIYU:

Da fadin Allah Ta'ala::

(وَلَقَدْ بَعَثْنَا فِي كُلِّ أُمَّةٍ رَّسُولاً أَنِ اعْبُدُواْ اللّهَ وَاجْتَنِبُواْ الطَّاغُوتَ)

*“Hakika mun aika Manzo cikin, kowace al'umma (kuma ya na fada mu su cewa): ku bauta wa Allah kuma ku nisanci Da'gut ” (QS. An-Nahl, 36).*

● **wannan ayar An karfafe ta da abubuwa guda uku:** [1] Rantsuwa "ana kaddara ta" [2] Harafin **" Lam "** (اللام) [3] Harafin **" kad "** [قد]. (dukkan su haruffa ne na karfafa zance).

● Ijma'in Manzanni kan kira zuwa ga Tauhidi, kuma lallai saboda haka Allah Ya aika su.

## KALMAR AL' UMMA A CIKIN KUR'ANI: TA NA DA MAANONI HUDU:

**[1] JAMA'A**

Kamar yanda tazo cikin wannan ayar.

**[2] IMAM**

إِنَّ إِبْرَاهِيمَ كَانَ أُمَّةً قَانِتاً لِلَّهِ حَنِيفاً

*" Lallai ne Ibrahim ya kasance Shugaba mai da'a ga Allah mai karkata zuwa gaskiya ".* (QS. An-Nahl: 120).

**[3] ADDINI**

بَلْ قَالُوا إِنَّا وَجَدْنَا آبَاءنَا عَلَى أُمَّةٍ

*" Bari dai, sunce lallai ne mun samu ubannin mu a kan wani addini "*(QS. Az-Zukhruf: 22).

**[4] ZAMANI**

وَقَالَ الَّذِي نَجَا مِنْهُمَا وَادَّكَرَ بَعْدَ أُمَّةٍ

*" Kuma wannan da ya kubuta cikin mutum biyun ya ce, abayan ya yi tunani bayan a lokaci mai tsawo " (QS. Yusuf: 45).*

● ***(Ku nisanci Da'gut)*:** Ma'ana ku yi nesa da shi, ku kasance a wani bangare shima ya na wani bangaren.

● Mafi cikan Ta'arifin da'gut shine Ta'arifin: Ibnul Qayyim ( Rahimahullah): **" Duk abin da bawa ya ketare iyakansa; na wani abin biyayya, ko wani abin bauta, ko wani wanda ake ma sa da'a** ". (Ma'ana: idan ya yarda da hakan).

[1] **Wanda ake ma sa biyayya:** kaman bokaye da masu sihiri, da miyagun maluma.

[2] **Wanda ake bauta ma sa**: Kaman gumaka.

[3] **Wanda ake yi ma sa da'a:** Kaman jagorori da wadan da suka fice daga da'a wa allah.

● Nunin ayar a kan Tauhidi shi ne: gumaka da'gutai ne da ake bauta musu ba Allah ba.

● **Tauhidi ba ya cika sai da rukunnai biyu: korewa da tabbatarwa:** sabo da tsantsan korewa shi kadai; ba ya tabbatar da komai, kuma tsantsan tabbatarwa kadai ba ya hana tarayya, misali ka ce: ( Zaidu ya ya na tsaye), ya tabbatar da tsayuwa wa Zaidu, amma hakan ba ya nuni a kan kadaituwan Zaidu da tsayuwa, ( Ba wanda ya tsaya), wannan korewa ne tsantsa, Amma idan ka ce: (Babu wan da ya tashi se Zaidu), to hakika ka kadaita shi da tsayuwa, sabo da jumlar ta kunshi tabbatarwa da korewa.

● Hikimar aika Manzanni.

**[1] TSAYAR DA HUJJAH:** Allah Ya ce:

( رُّسُلاً مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلاَّ يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى اللّهِ حُجَّةٌ بَعْدَ الرُّسُلِ ).

*(Manzanni masu bayar da bushara kuma masu gargadi, domin kada wata hujja ta kasance ga mutane akan Allah bayan manzannin ) (QS. An-Nisa: 165).*

**[2] RAHAMA GA BAYI.** Allah Ya ce:

( وَمَا أَرْسَلْنَاكَ إِلَّا رَحْمَةً لِّلْعَالَمِينَ ).

( Kuma ba Mu aike ka ba face domin jinkai ga talikai ) *(QS. Al-Anbiya: 107).*

**[3] BAYANIN HANYAR DA TAKE KAIWA ZUWA GA ALLAH.**

**DALIL NA UKU:**

Da fadin Allah Ta'alah:

(وَقَضَى رَبُّكَ أَلاَّ تَعْبُدُواْ إِلاَّ إِيَّاهُ وَبِالْوَالِدَيْنِ إِحْسَاناً إِمَّا يَبْلُغَنَّ عِندَكَ الْكِبَرَ أَحَدُهُمَا أَوْ كِلاَهُمَا فَلاَ تَقُل لَّهُمَا أُفٍّ وَلاَ تَنْهَرْهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوْلاً كَرِيماً)

*"." (QS. Al-Isra'i: 23).*

*• ( Kada ku bauta wa kowa face Allah )*: Wannan shi ne Tauhidi sabo da ya kunshi korewa da tabbatarwa.

HUKUNCIN ALLAH IRI BIYU NE:

[1] Hukunci irin na Shari,a:

● Ba ya kasantuwa se cikin abiin da Allah Ya ke so.

● Ana iya samun sa ko a rasa shi.

Allah ta'ala Ya ce:

وَقَضَى رَبُّكَ أَلاَّ تَعْبُدُواْ إِلاَّ إِيَّاهُ

***" Kuma Ubangijinka Ya hukunta kar ku bauta wa kowa face Shi ".***

Ma'anar **Qadhaa** a nan: Ya shar'anta ko Ya yi wasiyci.

[2] Hukunci na kaunu (halitta):

● Yana kasancewa cikin abin da Allah Yake so da wanda ba Ya so.

● Babu makawa ga aukuwarsa:

Allah Ta'ala Ya ce:

وَقَضَيْنَا إِلَى بَنِي إِسْرَائِيلَ فِي الْكِتَابِ لَتُفْسِدُنَّ فِي الأَرْضِ

***" Kuma Mun hukunta zuwa ga Bani Isra ila a cikin littafi cewa lallai ne kuna yin barna a cikin kasa ".***

## ME YA SA ALLAH YA HUKUNTA ABIN DA BA YA SO?

Abin da ake so sabo da wanin sa, shi abin ki ne a zatinsa, se dai akan so shi ne sabo da hikima da maslahar da suke alaka da shi; se ya kasance abin so ne ta wata fiskar, abin ki ta wata fiskar

**misali:** yin barna a ban kasa cikin bani israila abin ki ne a wajen Allah, sabo da Allah ba ya son barna da mabarnata, amma lura da hikimar da ta kunsa, Allah Yana son ta **(Barnar)** ta wannan fiskar.

**Misali na biyu:** Fari, rashin ruwa, rashin lafiya, talauci.

### ABUBUWAN SO IRI BIYU NE:

Wanda ake sonsa domin zatinsa; shine: Allah

Wanda ake sonsa domin waninsa, kamar magani ana son sa domin neman sauki /

### *BAUTA TA KASU KASHI UKU*:

Gmammiya: itace bauta irin ta Rububiyya, (Bautar galaba): kowa ya na yin wannan bautar, Allah Ta'ala Ya ce:

إِن كُلُّ مَن فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ إِلَّا آتِي الرَّحْمَنِ عَبْداً

***" Dukkan wanda yake a cikin sammai da kasa bai zama ba face mai jewa ne ga Mai rahama yana bawa".*** *(QS. Maryam: 93).*

Kafiri ma ya shiga cikin wannan maganar.

Kebantacciya : *Itace bautar da'a wa Allah (gamammiya), Allah Ta'ala Ya ce*:

وَعِبَادُ الرَّحْمَنِ الَّذِينَ يَمْشُونَ عَلَى الْأَرْضِ هَوْناً

***" Kuma bayin Mai rahama, su ne wadanda suke tafiya a kayin kasa cikin natsuwa ".*** *(QS. Alfurqan: 63).*

Wannan ta game duk wanda ya bauta wa Allah da shari'arsa.

Mafi kebanta: itace bauta irin ta Manzannin Allah (Alaihimus salam): itace mafi cikar bauta. Allah Ta'ala Ya ce:

تَبَارَكَ الَّذِي نَزَّلَ الْفُرْقَانَ عَلَى عَبْدِهِ

**" Albarka ta tabbata ga wanda Ya Saukar da (littafi ) mai rarrabewa ma BawanSa "** *(QS. Alfurqaan: 1).*

Babu wani wanda zaiyi kusa da wadannan Mnzannin cikin ibada.

### DALILI NA HUDU:

Da Fadinsa:

(وَاعْبُدُواْ اللّهَ وَلاَ تُشْرِكُواْ بِهِ شَيْئاً) الآيَةَ.

*" Kuma ku bauta wa Allah kar ku tara shi da komai " (QS. An-Niisa : 36).*

● شَيْئاً ( Komai ): Nakira a siyakin hani ta na game komai, Annabi ne ko mala'iki ko waliyyi, ko wani abu na duniya, don haka kar ka sanya duniya tare da Allah cikin bauta.

**DALILI NA BIYAR:**

Da fadinsa:

(قُلْ تَعَالَوْاْ أَتْلُ مَا حَرَّمَ رَبُّكُمْ عَلَيْكُمْ أَلاَّ تُشْرِكُواْ بِهِ شَيْئاً) الآيَةَ.

*" Kace ku zo in karata abin da ubanginku Ya haramta a kanku, kar ku tara shi da komai "* (QS. Al-An’am : 151).

**DALILI NA SHIDA:**

قَالَ ابْنُ مَسْعُودٍ ﵁ : «مَنْ أَرَادَ أَنْ يَنْظُرَ إِلَى وَصِيَّةِ مُحَمَّدٍ ﷺ الَّتِي عَلَيْهَا خَاتَمُهُ؛ فَلْيَقْرَأْ قَوْلَهُ تَعَالَى (قُلْ تَعَالَوْاْ أَتْلُ مَا حَرَّمَ رَبُّكُمْ عَلَيْكُمْ أَلاَّ تُشْرِكُواْ بِهِ شَيْئاً) إِلَى قَوْلِهِ: (وَأَنَّ هَذَا صِرَاطِي مُسْتَقِيماً فَاتَّبِعُوهُ...)

Ibnu Mas’ud ya ce; ( wanda yakeso ya yi dubi zuwa ga wasiyyar Annabi Muhammad (sallallahu alaihi wasallam) wanda akanta akwai hatiminsa, to sai ya karanta fadin Allah Ta'ala: ***" Kace ku zo in karata abin da ubanginku Ya haramta a kanku, kar ku tara shi da komai*** "), *har zuwa fadinsa: " kuma lallai ne wannan itace hanyata mikakka don haka sai ku bita"*

**ASSIRA'D**: TAFARKI / HANYA: ana jinginata ga:

1. **Allah;** domin ta na kaiwa zuwa gare shi, kuma domin shine wanda Ya shimfida ta ga bayinsa.
2. **Masu tafiya akan hanyar:** domin sune kadai wadanda su ka shige ta, kuma hanyar tsira daya ce, amma hanyoyin bata sunada yawa.

**WADANNAN AYOYIN SUN KUNSHI WASIYYOYI GOMA:**

**Ayar farko (wasiyyoyi biyar):**

1. Kadaita Allah (Tauhid).
2. Biyayya ga iyaye biyu.
3. Kar mu kasha yayanmu.
4. Kar mu kusanci alfahasha ( zina ).
5. Kar mu kasha ran da bai halatta ba sai da hakki.

**Aya ta biyu (wasiyyo hudu)**

6. Kar mu kusanci dukiyan maraya saida abin da yak e mafi kyawu. **Maraya:** shi ne wanda babansa ya mutu bai balaga ba
7. Muyi adalci wajen magana.
8. Mu cika mudu da sikeli da adalci.
9. Mu cika alkawarin Allah.

10. Aya ta goma ( wasiya guda ) (**Kuma lallai** ***Wannan ne tafarkina madaidaici*** ). Ya zo a hadisi " Manzon allah (sallallahu Alihi wa sallam) Ya zana layi mikakke, ya ce: wannan itace hanyar Allah, sa'annan ya zana wasu layin ta damansa wasu kuma ta hagunansa, sai y ace: wadannan hanyoyin, akwai shaidani kan kowacce ya na kira zuwa gare shi .

**MUHIMMAN FA'IDODI:**

**Ran da Allah Ya haramta ( tsararriya):**

1. Musulmi.
2. **Azzimmiy:** Kadon amana.
3. **Al-Mu'ahad** (wanda akayi alkawarin zaman lafiya da su ).
4. **Al-Musta'min** (wanda muka ba shi aminci).

Fadin Allah: (Mu muke azurta ku (iyayen) kuma muke azurta su ). (QS. Al-An'am: 151) sai ya fara ambaton arzikin iyayen biyu domin talaucin ta shafe su.

Acikin surat (Al-Isra'i: 31) kuma Allah ya ce: (Mu muke azurta su (yayan) kuma muke azurta ku) sai ya fara da arzikin yayan kafin na iyayen, domin su mawadata ne amma sun a tsoron talauci.

Fadin Allah ( se da hakki ) shari'a ta tabbatar d:
1. Idan rai ta kashe a kashe ta.
2. Wanda ya taba yin aure kuma ya yi zina.
3. Wanda ya yi ridda ya bar jama'ar musulmi.

**Isa girman da ake balaga da shi:**
1. Cikan shekaru goma sha biyar.
2. Fitan gashin gaba.
3. Fitan maniyyi.
4. Mace ta na karawa da haila.

**Al-Wasiyyah**: da maanan alkawari, kuma alkawari baya zama wasiyya sai idan ya kasance cikin wani lamari muhimmi.

**ME YA SA BN MAS'UD YA CE, WANNAN AYAR WASIYYAR MANZON ALLAH NE SALLALAHU ALAIHI WA SALLAM, ALHALI ANNABI BAIYI WASIYCIN BA?**

[1] Sabo da ya ga wadannan ayoyin sun kunshi dukkan ma'anonin addini, ayoyi ne masu girman gaske.

[2] Sabo da wasiyyar Allah ce, (Wannan Allah Ya yi muku wasiyci da shi), kuma Annabi Sallallahu Alaihi wa sallam jakadan Allah ne.

**DALILI NA BAKWAI:**

وَعَنْ مُعَاذِ بْنِ جَبَلٍ ۏ قَالَ: كُنْتُ رَدِيفَ النَّبِيِّ صلى الله عليه وسلم عَلَى حِمَارٍ، فَقَالَ لِي: «**يَا مُعَاذُ أَتَدْرِي مَا حَقُّ اللهِ عَلَى الْعِبَادِ؟، وَمَا حَقُّ الْعِبَادِ عَلَى اللهِ؟**»، قُلْتُ: اللهُ وَرَسُولُهُ أَعْلَمُ، قَالَ: «**حَقُّ اللهِ عَلَى الْعِبَادِ: أَنْ يَعْبُدُوهُ وَلَا يُشْرِكُوا بِهِ شَيْئًا، وَحَقُّ الْعِبَادِ عَلَى اللهِ: أَنْ لَا يُعَذِّبَ مَنْ لَا يُشْرِكُ بِهِ شَيْئًا**»، قُلْتُ: يَا رَسُولَ اللهِ؛ أَفَلَا أُبَشِّرُ النَّاسَ؟ قَالَ: «**لا تُبَشِّرْهُمْ فَيَتَّكِلُوا**». أَخْرَجَاهُ [فِي «الصَّحِيحَيْنِ»].

Daga Mu'azu dan Jabal Allah Ya kara yarda a gare shi yace: na kasance a bayan Manzon Allah Sallallahu Alaihi wa Sallam a kan jaki, sai ya ce da ni " **Ya Muaz, ko kasan hakkin Allah akan bayinsa, da hakkin bayi akan Allah**, se nace: Allah da Manzon sa su suka fi sani, sai ya ce: " **hakkin Allah a kan bayinsa: su bauta masa kar su hada shi da kowa**, hakkin bayi kuma akan Allah: Ba zai azabtar da wanda baya shirka ba, sai nace: ya Manzon Allah: ba na yi bushara wa mutane ba? Sai yace " A'a, kar ka mu su bushara domin za su dogara ” ( Bukhari, Muslim).

- ( Ko kasan): Tambaya ce ta kwadaitarwa, da janyo hankalin abokin magana, wannan salo ne me kyau a wajen karantarwa.
- ( Hakkin bayi akan Allah ): Bayi ba su cancanci wani wajibi akan Allah ba sai abin da Allah Ya wajabta wa kansa domin falala daga gare shi.
- ( أُبَشِّرُ ) Bushara itace: ba da labarin abu mai faranta rai, ana iya amfani da ita wajen ba da labara kan abu mara kyau ( amma amfi amfani da ita kan abu mai kyau ).
- **( لا تُبَشِّرْهُمْ ):** Ma'ana: kar ka ba su labara..
- Hadisin na nuni kan falalar Tauhidi, kuma Tauhidi ya na hana azaba.
- Kuma Allah ba ya azabtar da wanda bai tara shi da komai ba, kuma Tauhidi sababi ne na gafarta zunubai, manzon Allah ya hana a ba wa mutane labari don kar su dogara kan wannan busharar su gaza wajen tabbatar da Tauhidin yanda ya kamata, domin tabbaar da Tauhidi na lizimta nisantan sabon Allah, domin sabon Allah daga son zuciya ne, wannan daya ne cikin nau'uka na shirka.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

( Wadannan mas'alolin ba sa cikin kitab Tauhid, mawallafin ya ya rubuta su ne domin sharhi wa littafinsa, shi ne mafificin wanda zaiyi wa littafin sharhi, domin shi ya fi kowa sanin maqasudin abin da ya rubuta, ya kamata a kula da su sosai ).

1. Hikimar halittan Aljanu da Mutune: ( Don su kadaita Allah da bauta, ba don su shagaltu da abinci ko aurarraki ba ).

2. Ibadah itace Tauhidi domin a kansa ake husuma. (tsakanin Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam da kuraishawa, sabo da haka duk Ibadan da ba'a gina ta akan Tauhidi ba to lalatacciya ce ).

3. Duk wanda baizo da Tauhidi ba to bai bauta wa Allah ba, dalilin haka fadin Allah:

( وَلَا أَنتُمْ عَابِدُونَ مَا أَعْبُدُ ).

*" **Kuma ku, ba ku zama masu bauta wa abin da na ke bauta wa ba".***

4. Hikimar aiko Manzanni: ( A kadaita Allah da bauta, kuma a nisanci bautan da'gut ).

5. Sakon Allah ya game dukkan al'ummah.

6. Addinin dukkan Annabawa daya ne. (Asalin Addini Allah daya ne, amma shari'oin annabawa sukan sha bam bam, lura da yanayin al'ummomin da wajaje da zamunna ).

7. Mas'ala babba: bautar Allah ba ta cika har se in an kafirce wa dagut *"Allah ta'ala Ya ce: " duk waanda ya kafirce wa dagut "* (QS. Al Baqarah, 256). (ya kira ta babba ce sabo da, da yawan mutane sun jahilce ta, ba shi halatta a kira wanda ya aikata wani abu bisa jahilci da mushiriki ko fasiki ko tsinanne ba, sabo da hukunci kan irin wadannan mas'alolin ya na da sharudda da abubuwan da suke hana hukuncin ).

8. Dagutu ya game duk abin da aka bauta masa wanda ba Allah ba.

9. Girman sha'anin ayoyi uku bayyanannu na suratul " An' am" a wajen Salaf, a cikinsu akwai mas'aloli goma, mas'alar ta farko: hani akan shirka.

10. Ayoyi bayyanannu na suratul isra'i: cikinsu akwai mas'aloli goma sha takwas, Allah Ya fara su da fadinsa:

لاَّ تَجْعَل مَعَ اللّهِ إِلَـهاً آخَرَ فَتَقْعُدَ مَذْمُوماً مَّخْذُولاً

*"**Kar ka sanya wani ain bautawa na dabam tare da Allah, har ka zauna kana abin zargi tababbe**" (QS. Al Isra'i: 22).*

Kuma Ya cika su da fadinsa:

وَلاَ تَجْعَلْ مَعَ اللّهِ إِلَهاً آخَرَ فَتُلْقَى فِي جَهَنَّمَ مَلُوماً مَّدْحُوراً

*"**Kuma kada ka sanya wani abin bautawa na dabam tare da Allah, har a jefa ka a cikin Jahannama kana abin zargi abin tunkudewa** )" (QS. Al Isra'i: 39).*

Allah mai tsarki Ya fadakar da mu girman wadannan ayoyin cikin fadinsa:

ذَلِكَ مِمَّا أَوْحَى إِلَيْكَ رَبُّكَ مِنَ الْحِكْمَةِ

*"**Wannan na daga abin da ubangijinka Ya yi wahayi zuwa gare ka na hikima**" (QS. Al Isra'i: 39).*

11. Ayoyin surstun Nisa'i, wadanda ake kiransu ayoyin hakkoki goma Allah ta'ala Ya fare su da fadinsa:

وَاعْبُدُواْ اللّهَ وَلاَ تُشْرِكُواْ بِهِ شَيْئاً

*" Kuma ku bauta wa Allah kada ku hada shi da komai " (QS. An-Nisa : 36).*

( Hakkin Allah shi ne mafi girman hakkoki ).

12. Fadakarwa game da wasiyyar Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam lokacin mutuwansa: ( hakika be kebe wadannan ayoyin da wasiyya ba, sedai ya yi isharan cewa: idan mukayi riko da littafin Allah to har abada ba za mu bace ba ).

13. Sanin hakkin Allah a kanmu: ( Shi ne mu bauta masa kar mu hada shi da komai).

14. Sanin hakkin bayi a kan Allah idan suka ba da hakkinsa. ( Hakki ne na falala).

15. Mafi yawan Sahabbai ba su san wannan mas'alar ba. ( Domin Muazu ya sanar da ita yayin mutuwarsa domin kubuta daga laifin boye ilimi, bayan rasuwan adadi mai yawa na sahabbai, Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya ji tsoron kar su dogara ne, ba wai yana nufin boye ta ne sake ba, domin da ya na nufin haka da be sanar da Mu'azu ba bare waninsa.

16. Halaccin boye ilimi sabo da maslaha, ( Tare da sharuddan boyewan ).

17. Ana son yin bishara ga musulmi game da abin da zai faranta ma sa rai. ( wannan ya na daga mafi kyawun fa'idodin ).

18. Tsoron dogara da sakankancewa kan yalwar rahamar Allah ( Haka nan bai halatta a debe tsammani daga Rahamar Allah ).

19. Wanda aka tambaye shi idan be san amsar ba, sai ya ce: Allah da manzonsa su suka fi sani ( Ana fadan haka ne lokacin da manzon Allah sallallahu alaihi wasallam yake da rai, kan al'amura na Shari'a wadanda Allah Ya sanar da shi su ).

20. Ya halatta a kebe sahin mutane da ilimi banda wani sashen.

21. Tawaliun Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallam na hawa jaki tare da goyo akayi.

22. Halaccin yin goyo akan dabba. ( Da sharadin kar a cutar ita ).

23. Girman sha'ani wannan matsalar (Tauhidi).

24. Falalan Muazu dan Jabal.

## [2] BABIN FALALAR TAUHIDI DA YANDA YAKE KANKARE ZUNUBBAI

Mawallafin ya kawo shi ne domin kwadaitarwa da jawo hankula, sabanin abin da shaidan ya ke jefawa cikin zukatan wasu, sa'annan tabbatar falala ga wani abu ba ya hana wannan abun ya zamo wajibi, falalan ya na daga sakamako da fa'idodi na nasa.

### DALILI NA FARKO

الَّذِينَ آمَنُواْ وَلَمْ يَلْبِسُواْ إِيمَانَهُم بِظُلْمٍ أُوْلَـئِكَ لَهُمُ الأَمْنُ وَهُم مُّهْتَدُونَ

*" Wadanda suka yi imani kuma ba su garwaya imaninsu ba da zalunci, to wadannan suna da amintuwa kuma sune shiryyayu ". (QS. Al-An'am: 82).*

● { وَلَمْ يَلْبِسُواْ }: Basu garwaya shi ba. {بِظُلْمٍ} (Da zalunci ), Ma,anar zalunci anan: kishiyan imani, shi ne: shirka.

● { مُّهْتَدُونَ }: (Shiryayyu) [1] A Duniya; kan Shari'ar Allah da ilimi da aikin kwarai. [2] A Lahira; zuwa ga Aljanna.

● Tabbatuwar aminci duniya da lahira ya na daga falalar Tauhidi.

### DALILI NA BIYU:

وَعَنْ عُبَادَةَ بْنِ الصَّامِتِ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ صلى الله عليه وسلم: «مَنْ شَهِدَ أَنْ لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ، وَحْدَهُ لَا شَرِيكَ لَهُ، وَأَنَّ مُحَمَّدًا عَبْدُهُ وَرَسُولُهُ، وَأَنَّ عِيسَى عَبْدُ اللهِ وَرَسُولُهُ، وَكَلِمَتُهُ أَلْقَاهَا إِلَى مَرْيَمَ، وَرُوحٌ مِنْهُ، وَالْـجَنَّةَ حَقٌّ، وَالنَّارَ حَقٌّ، أَدْخَلَهُ اللهُ الْـجَنَّةَ عَلَى مَا كَانَ مِنَ الْعَمَلِ»، أَخْرَجَاهُ.

Daga Ubadah bin Samit Radhiallahu'anhu, ya ce: Manzon Allah Sallallahu'alaihi wasallam ya ce: " wanda ya shaida ba bu abin bautawa bisa cancanta sai Allah, shi kadai, ba shi da abokin tarayya, kuma ya shaida Annabi Muhammad bawansa ne kuma manzonsa, kuma ya shaida Annabi Isa bawan Allah, ne kuma manzonsa, kuma kalmarsa ce da ya fiskantar ta ita zuwa ga Maryam, kuma wani ruhi ne daga Allah, kuma Aljannah gaskiya ce, kuma wuta gaskiya ce, Allah Zai Shigar da shi Aljannan gwargwadon abinda da ya kasance akai na aiki ". ( Bukhari da Muslim)

### DALILI NA UKU:

وَلَهُمَا فِي حَدِيثِ عِتْبَانَ: «فَإِنَّ اللهَ حَرَّمَ عَلَى النَّارِ مَنْ قَالَ: (لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ)؛ يَبْتَغِي بِذَلِكَ وَجْهَ اللهِ».

Daga Bukhari da Muslim cikin hadisin itban dan Malik , "Allah ya haramta wa wuta

duk wanda ya fadi: ( la'ilaha illal lah ) ya na me neman yardar Allah da haka"

● شَهِدَ (Ya shaida ): الشَّهادة (Shaidawa): Yin furuci da harshe, da kudurin zuci, da gasgatawan (ayyukan) gabbai.

● أَنْ لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ: Ba bu abin bautawa bisa cancanta sai Allah.

● وَحْدَهُ (Shi kadai): karfafawa ce kan tabbatar da kadaitakan Allah. لَا شَرِيكَ لَهُ (Ba shi da abokin tarayya): karfafawa ce wajan kore tarayya da Allah cikin duk abin da ya kebanta da shi.

● وَأَنَّ مُحَمَّدًا (Annabi Muhammad): Dan Abdullah dan Abdul Mutdalib dan kabilar quraishawa dangin Hashim.

● (عبده): Bawansa ne [1] Ba abokin tarayyan Allah ba ne. [2] Ya dara kowa wajen bauta.

● (ورسوله): Wanda Allah Ya aike shi da wahayi, baiyi karya ba wa Allah. Abubuwan da suke tauye wanna shahadar: [1] Zunubbai. [2] ( **Bidio'i** ) kirkire kirkire a cikin addini.

● **Zunubbai**, a gamammiyar ma'anarta, za mu iya daukar ta da ma'anar Shirka, Amma bisa ga kebantacciyar ma'anarta, tana zuwa da ma'anar: [1] Bbban shirka. [2] Karamar shirka. [3] Babban zunubi. [4] Karamin zunubi.

● (Annabi Isah bawan Allah ne): Wannan martini ne kan Nasara. (Kuma Manzonsa ne): Martani ne kan Yahudawa, mu (musulmai ) munyi imani da manzancinsa, amma binsa cikin wani abu na shariarsa da ta saba wa shari'armu ba wajibi ba ne a kanmu, hukuncin Shario'in Annabawa gabanninmu, na da matsaya uku:

[1] Idan ta saba wa shari'armu, bai halatta muyi aiki da ita.

[2] Idan ta dace da shari'armu, to sai mu yi aiki da Shari'armu.

[3] Idan Shiria'armu ba ta yi magana a kai ba, to shariarmu ce.

● Mutane sun kasu bangare biyu da na tsakiya gameda Annabi Isah (alaihis salam).

[1] **Wadanda su ka yi jafa'i:** kamar Yahudawa, sun karyata shi, kuma sun soke shi da mahaifiyarsa, sun muzanta annabcinsa kuma suka yanke hukuncin kisan kai a kansa.

[2] **Wadanda suku zurfafa:** kamar Nasara, suka ce: shi dan Allah ne, dayan abu uku, kuma suka rike shi abin bautawa.

[3] **Tsaka tsaki:** (Musulmai) Mun shaida cewa shi bawan Allah ne kuma manzonsa, kuma mahaifiyarsa mai yawan gaskiya ce, kamammiya wacce ta tsare farjinta, kuma misalinsa a wajen Allah kamar misalin Annabi adam ne, Allah Ya halicce shi daga turbaya sa'annan Yace da shi, kasance, sai ya kasance.

● (( Kalmarsa )): Saboda shi an halitta shi ne da Kalmar Allah, Isah bai kasance kalmar Allah ba, domin **( KALMA ),** Magana: sifar Allah ce.

● (( Ruhi daga gare shi )): Halitta ne daga halittunsa, anjingina shi zuwaga Allah madaukaki, domin girmamawa ne da karramawa.

● (Allah zai shigar da shi Aljannah): shigarwa Aljannah iri biyu:

1. **Cikakken shigarwa:** wanda bai dandani azaba ba, sune wadanda aikinsu ya cika.
2. **Wanda ya ke da tawaya:** Za'a dandana masa azaba, wadanda suke da nakasu.

● (Wanda ya fadi: ***laa ilaaha illallah***): da sharadin ikhlasi, dalili: " **yana mai neman yardan Allah** ".

● Cikin wannan hadisi akwai martini ga kungiyoyi biyu:

1. **Murji'ah:** Sune suka ce: fadin **(laa ilaaha illallah)** kadai zai wadatar wajen shiga Aljannan ko da ba a yi aiki ba ko ikhlasi.
2. **Khawaarijawa:** Sune suke cewa duk wanda ya aikata babban laifi kafiri ne, zai dauwama a cikin wuta.

ABUBUWAN DA ALLAH YAJINGINA WA KANSA:

Jingina abubuwan da suke tsaye da kansu: kamar **(Taguwar Allah)**, wannan jingina halitta ce zuwa ga mahaliccinta, duk wani abin da yake tsayuwa da zatinsa wanda bai da sila da zatin Allah to wannan abun halitta ce.

Jingina sifofin da ba su sadu da wani halitta ba. kamar fadin Allah: **(Wanda na halitta da hanu na biyu)** to wannan ya na shiga babi ne na jingina sifa zuwaga wanda ya siffantu da ita.

Gamammiya jinginawa Allah Ya ce:

( إِنَّ أَرْضِي وَاسِعَةٌ )

*" Lallai kasaTa mai yalwa ce"*

Jinginawa irinta girmamawa, kamar fadin Allah:

( وَرُوحٌ مِنْهُ )

*" Kuma wani Ruhi ne daga gare shi "*

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنْ أَبِي سَعِيدٍ الْـخُدْرِيِّ رضي الله عنه عَنْ رَسُولِ اللهِ صلى الله عليه وسلم قَالَ: «**قَالَ مُوسَى غ: يَا رَبِّ عَلِّمْنِي شَيْئًا أَذْكُرُكَ وَأَدْعُوكَ بِهِ، قَالَ: قُلْ يَا مُوسَى: لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ، قَالَ: كُلُّ عِبَادِكَ يَقُولُونَ هٰذا؟ قَالَ: يَا مُوسَى؛ لَوْ أَنَّ السَّمٰوَاتِ السَّبْعَ وَعَامِرَهُنَّ - غَيْرِي - وَالْأَرْضِينَ السَّبْعَ فِي كِفَّةٍ، وَ(لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ) فِي كِفَّةٍ، مَالَتْ بِهِنَّ لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ**»، رَوَاهُ ابْنُ حِبَّانَ وَالْـحَاكِمُ وَصَحَّحَهُ.

Daga Abu Said Al-Khudri radhiallahu'anhu daga Manzon Allah Sallallahu'alaihi wasallam ya ce: " Musa (Alaihis salam): ya ce: ya Ubangij ka sanar da ni wani abu da zan ambace ka kuma in roke ka da shi, se Allah Ya ce: ya Musa kace: ***laa ilaaha illallahu,*** se Annabi Musa ya ce: ai dukkan bayinka suna fadin wannann, sai Yace: ya Musa " Da Sammai bakwai da abinda ke cikinsu -banda ni- da kasa bakwai da abin da ke cikinsu -banda ni- da za a sanya su a tafin ma'auni, kuma a sanya ***laa ilaaha illallahu*** a dayan tafin, to sai ***laa ilaaha illallahu*** ta rinjaye su ". ( Ibn Hibban da Hakim ne suka rawaito shi, kuma Hakim ya inganta shi ).

**DALILI NA BIYAR:**

وَلِلتِّرْمِذِيِّ - وَحَسَّنَهُ - عَنْ أَنَسٍ، سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ صلى الله عليه وسلم يَقُولُ: «**قَالَ اللهُ تَعَالَى: يَا ابْنَ آدَمَ، إِنَّكَ لَوْ أَتَيْتَنِي بِقُرَابِ الأَرْضِ خَطَايَا، ثُمَّ لَقِيتَنِي لَا تُشْرِكُ بِي شَيْئًا، لَأَتَيْتُكَ بِقُرَابِهَا مَغْفِرَةً**».

Daga Imam Tirmidzi –kuma yace: hadisi ne mai kyaw- daga Anas, yace: na ji Manzon Allah ( sallallahu alaihi wasallam ) yana cewa: Allah Ta'ala ya ce: " Ya kai dan Adam da za ka zo mi ni da zunubbai cikin kasa sa'annan ka hadu da ni ba ka hada ni da komai **-shirka-** da na zo ma ka da cikin ta na gafara".

● لَا إِلَٰهَ إِلَّا اللهُ : ***Laa ilaaha illallahu:*** wannan jumlar zikiri ne wanda ya kunshi addu'a, saboda mai ambaton allah ya na neman yardan Allah ne, se dai duk wanda yazo mabudin da ba shi da hakware ba zai bude masa kofa ba, sharuddanta sune wadannan hakwaren.

● بِقُرَابِهَا مَغْفِرَةً **( Da cikinta na gafara )**: Tauhidi ya na da sakamako maigirma, ya na kankare dukkan zunubbai, idan bawa ya hadu da Allah ba ya hada shi da kowa **(shirka)**, **Gafartawa:** boye zunubi da yafe shi.

**MATSALOLI:**

1. Yalwan Falalar Allah.
2. Yawan ladan Tauhidi a wajen Allah.
3. Tauhidi kuma ya na kankare zunubi.
4. Tafsirin ayar suratul An'am *" Wadanda suka yi imani kuma ba su garwaya imaninsu ba da zalunci, ". (QS. Al-An'am: 82).*
5. Ka kula da abubuwa guda biyar na cikin Hadisin Ubada bn Samit.
6. Idan ka hada shi da Hadisin Itban da na bayansa, z aka fahimci ma'anar " Laa'ilaha illallah", kuma za ka fahimci kuskuren rudaddu ( saboda dole ya nemi yardan allah cikn ayyukansa, to wannan zai taime ke shi wajen kyautata aiki.

7. Fadakarwa kan sharadin da ke cikin Hadisin Itban. (furuci kadai ba ya wadatar wa).

8. Kasantuwar Annanabawa kansu an fadakar da su falalar *laa ilaaha illallah.* ( wadanda ba su ba sun fi bukatar a fadakar da su game da falalarta ).

9. Fadakarwa kan rinjayen *laa ilaaha illallah* a kan dukkan halittu, tare da cewa da yawan masu fadanta mizaninsu zai yi kasa ( to wannan matsalar daga mai fadin kalmal ne ba daga Kalmar ba, saboda barin wani sharadi daga sharuddanta ).

10.Nassi ya tabbatar da cewa adadin kasa guda bakwai ne, kamar sammai. (misali game da adadinsu ).

11. Akwai halittu a cikinsu. ( Mala'iku su ne halittun cikin sammai ).

12 Tabbatar da sifofin Allah, sabanin yan mazhabin Asha'ira, da sauran masu kore siffofin Allah, ( Akwai tabbatar da sifar fiska wa Allah ).

13. Idan ka fahimci hadisin Anas, to lallai ka fahimci fadinsa cikin hadisin Itban cewa: " Lallai ne Allah ya haramta ma wuta dukkan wanda ya ce: ( la'ilaha illal lah ya na neman fuskar Allah da haka ". kuma lallai barranta daga shirka ba da maganar baki ba ne kadai (dole ne a samu kudirin zuci ).

14. Ka kula da cewa Annabi Isah da Annabi Muhammad dukansu bayin Allah ne kuma manzanninsa.

15. Sanin cewa Annabi Isah an kebance shi da cewa shi **Kalmar Allah ne**. (maana an halicce shi da kalmar Allah ba tare da uba ba).

16. Kasantuwar shi **Ruhi** ne daga Allah. ( cikin rayuka halittatu).

17. Sanin falalar yin imani da Aljannah da Wuta. ( kuma hakan daya ne daga sabubban shiga Aljannah).

18. Fahimtar fadinsa: " **gwargwadon abinda ya kasance akai na aiki** ".

19. Sanin cewa Mizanin lahira ya na da tafuka guda biyu.

20. Sanin ambaton Fiska. ( Sifa ce cikin sifofin Allah).

## [3] BABIN WANDA YA TACE TAUHIDI ZAI SHIGA ALJANNAH BA TARE DA HISABI BA

Ya kulla wannan babin ne domin mu tace tauhidi wanda Allah Ya wajabta shi a kanmum kuma ya kwadaitar da mu a kayi, **Tace shi**: shine tsarkake shi daga shirka, da bidi'a da zunubbai, kuma hakan ya na kasantuwa ne ta hanyar; ilimi, kuduri, da jayuwa.

Tace Tauhidi a wajen mawallafin ( Allah Ya jikansa) zai kasance ne bayan fahimtar wannan babin da aiki da shi, a dunkule, sa'annan daki daki kamar haka:

1. Yin koyi da Annabi Ibrahim ‘alaihis salam.
2. Koyi da shuwagabannin waliyyai ( Sahabbai ).
3. Ka wanzu a kan Tauhidi ko da kai daya ne.
4. Dogaro da Allah, da barin; tofi da sakiya da chamfi.

**Dalili na farko:**

**Allah ta’ala Yce:**

إِنَّ إِبْرَاهِيمَ كَانَ أُمَّةً قَانِتاً لِلّهِ حَنِيفاً وَلَمْ يَكُ مِنَ الْمُشْرِكِينَ

*“Lallai Ibrahim ya kasance jagora ne, mai da'a wa Allah, hanifan (wanda ya kafirce wa shirka ya karkata ga Tauhidi ), kuma bai kasance cikin mushirikai ba ”. (QS, An-Nahl, 120)*

Allah Ya yabi Annabi Ibrahim alaihis salam cikin wannan ayar, ya zamo wajibi akanmu mu so shi sa'annan muyi koyi da shi, kuma muna cancantar yabo gwargwadon koyinmu da shi, Annabi Ibrahim Ya tace Tauhidi ne da abubuwa guda shida kamar yanda yazo cikin ayar:

1. **{أُمَّةً} :** Shugaba wanda ake koyi da shi, cikin aiyukansa da jihadinsa tare da dogaro a kan Allah.
2. **{قَانِتاً}:** Mai da'a ga Allah a cikin kowani yanayi, ( mai dawwama ne a kan da'a ).
3. **{لِلّهِ}:** Sabada Allah, wannan yana nuni akan ikhlasi.
4. **{حَنِيفاً} :** Wanda ya fiskanci Allah ya juya baya wa shirka, kuma ya nisanci dukkan abin da ya saba wa da'a .
5. *(Bai kasance cikin masu shirka ba)*: Barranta daga shirka da mushikai (Da zuciyz da halshe, da gabbai ).
6. *(Ya kasance mai godiya kan ni'imomin Allah), (QS. An-Nahl : 121).* Domin ni'ima jarabawa ce, tana bukakar godiya.

**Fa'idodi:**

1. Baban Ibrahim alaihis salam Azara ya mutu bai musulunta ba, Allah ya ce: ( Yayin da ya bayyana masa cewa shi abokin gaban Allah ne sai ya barranta daga gare shi ). *(QS. At-Taubah: 129).*

2. Iyayen Annabi Nuhu su biyun muminai ne, yace: (Ya Ubangiji ka gafarta mini da ni da iyaye na guda biyu) *(QS. Nuh : 28).*

3. Imam Ahmad ya ce: ( Abubuwa uku ba su da tushe, yakukuwa, fitintinu, tafsiri, galibi ana rawaito su ba isnadi, ba bu wanda ya san wani abu na labarin al'ummomin da suka shude se ta hanyar wahayi, na Maganar Allah da Sunnar Annabi sallallah alaihi wasallam ).

**DALILI NA BIYU:**

Allah ta'ala Ya ce:

وَالَّذِينَ هُم بِرَبِّهِمْ لَا يُشْرِكُونَ

*( Wadanda suke gameda ubangijinsu ba su yin shirka ). (QS. Al-Mu'minun : 59).*

●{Ba sa yin shirka }: Shirka da gamammiyar ma'anarta; domin tace tauhidi ba zai yiyu ba har sai an nisanci shirka gaba daya, ba a na nufin ba za su aikata sabo ba, domin duk wani dan Adam mai sabo ne, sedai idan suka saba, sukan tuba a lokacinta ba sa dorewa a kan sabo.

**DALILI NA UKU:**

وَعَنْ حُصَيْنِ بْنِ عَبْدِ الرَّحْمٰن قَالَ: كُنْتُ عِنْدَ سَعِيدِ بْنِ جُبَيْرٍ، فَقَالَ: أَيُّكُمْ رَأَى الْكَوْكَبَ الَّذِي انْقَضَّ الْبَارِحَةَ؟ فَقُلْتُ: أَنَا، ثُمَّ قُلْتُ: أَمَا إِنِّي لَمْ أَكُنْ فِي صَلَاةٍ؛ وَلَكِنِّي لُدِغْتُ، قَالَ: فَمَا صَنَعْتَ؟ قُلْتُ: ارْتَقَيْتُ، قَالَ: فَمَا حَمَلَكَ عَلَى ذَلِكَ؟ قُلْتُ: حَدِيثٌ حَدَّثَنَاهُ الشَّعْبِيُّ، قَالَ: وَمَا حَدَّثَكُمْ؟ قُلْتُ: حَدَّثَنَا عَنْ بُرَيْدَةَ بْنِ الْحُصَيْبِ؛ أَنَّهُ قَالَ: «لَا رُقْيَةَ إِلَّا مِنْ عَيْنٍ أَوْ حُمَةٍ»، قَالَ: قَدْ أَحْسَنَ مَنِ انْتَهَى إِلَى مَا سَمِعَ؛ وَلَكِنْ حَدَّثَنَا ابْنُ عَبَّاسٍ ﭬ، عَنِ النَّبِيِّ □ أَنَّهُ قَالَ: «**عُرِضَتْ عَلَيَّ الأُمَمُ، فَرَأَيْتُ النَّبِيَّ وَمَعَهُ الرَّهْطُ، وَالنَّبِيَّ وَمَعَهُ الرَّجُلُ وَالرَّجُلَانِ، وَالنَّبِيَّ وَلَيْسَ مَعَهُ أَحَدٌ، إِذْ رُفِعَ لِي سَوَادٌ عَظِيمٌ، فَظَنَنْتُ أَنَّهُمْ أُمَّتِي، فَقِيلَ لِي: هٰذا مُوسَى وَقَوْمُهُ، فَنَظَرْتُ فَإِذَا سَوَادٌ عَظِيمٌ، فَقِيلَ لِي: هٰذه أُمَّتُكَ، وَمَعَهُمْ سَبْعُونَ أَلْفًا يَدْخُلُونَ الْجَنَّةَ بِغَيْرِ حِسَابٍ وَلَا عَذَابٍ**»، ثُمَّ نَهَضَ فَدَخَلَ مَنْزِلَهُ، فَخَاضَ النَّاسُ فِي أُولَئِكَ، فَقَالَ بَعْضُهُمْ: فَلَعَلَّهُمُ الَّذِينَ صَحِبُوا رَسُولَ اللهِ □، وَقَالَ بَعْضُهُمْ: فَلَعَلَّهُمُ الَّذِينَ وُلِدُوا فِي الإِسْلَامِ فَلَمْ

يُشْرِكُوا بِاللهِ شَيْئًا، وَذَكَرُوا أَشْيَاءَ، فَخَرَجَ عَلَيْهِمِ رَسُولُ اللهِ  فَأَخْبَرُوهُ، فَقَالَ: «**هُمُ الَّذِينَ لَا يَسْتَرْقُونَ، وَلَا يَكْتَوُونَ، وَلَا يَتَطَيَّرُونَ، وَعَلَى رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ**»، فَقَامَ عُكَّاشَةُ بْنُ مِحْصَنٍ؛ فَقَالَ: يَا رَسُولَ اللهِ، ادْعُ اللهَ أَنْ يَجْعَلَنِي مِنْهُمْ، فَقَالَ: «**أَنْتَ مِنْهُمْ**»، ثُمَّ قَامَ رَجُلٌ آخَرُ، فَقَالَ: ادْعُ اللهَ أَنْ يَجْعَلَنِي مِنْهُمْ، فَقَالَ: «**سَبَقَكَ بِهَا عُكَّاشَةُ**».

Daga Husaini dan Abdurrahman ya ce: " na kasance a wajen Saidu dan Jubair sai ya ce: waye a cikinku ya ga tauraron da ya fadi a daren jiya? Sai n ace: ni ne, amma dai ba sallah na keyi a lokacin ba, sedai an cije ni ne -saran majici ko kunama- sai ya ce: to me ka yi? Na ce: na yi ruqyah ne, sai y ace: meye dalilin hakan: n ace: hadisin, da Sha'abi ya ba mu labara, ya ce, me ya ba ku labari? Na ce: daga Buraida dan Husaib; ya ce: " ba bu ruqyah sai a kammun baka, da cizon ma'abocin dafi (Maciji, kunama da sauransu ), sai ya ce: hakikia duk wanda ya tsaya kan abinda ya sani to ya kyautata, sedai Abdullahi dan Abbas -Allah Ya kara yarda a gare su- ya ba mu labari, daga Annabi -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: **" An bijiro mini da wadansu al'ummomi sai naga wani Annabi tare da shi akwai wasu jama'a, sa'annan wani Annabin shi kuma akwai mutum guda tare da shi, sa'annan wani kuma da mutane biyu, sa'annan wani annabi ba bu kowa a tare da shi, sai aka nuna mini wani dandazo na jama'a masu yawa sai na zaci ko al'ummata ce, sai aka ce da ni, wannan Musa ne da mutanensa, se na sake ganin wani dandazon na jama'a masu yawan gaske, se akace da ni, wannan itace: al'ummarka, <u>cikinsu akwai mutum dubu saba'in wadanda za su shiga Aljanna ba tare da hisabi ba, kuma ba tare da azaba ba"</u>**, sa'annan ya mike ya shiga gidansa, sai sahabbai suka yi dikaken ko su wanene wadannan? Wasu su kace: kila sahabban Annabi sallallahu alaihi wasallam ne, wasu kuma su ka ce: kila sune wadanda aka Haifa cikin musulunci wadanda ba su taba yin shirka ba? sukayi ta ambaton abubuwa, sai Manzon Allah -sallallahu alai wasallama- ya fito sai suka ba shi labarin hirarsu, sai yace musu: "Sune wadanda ba sa neman ayi musu tofi, kuma ba sa yin sakiya, ba sa yin chamfi, kuma ga Ubangijinsu suka dogara " sai Ukkasha dan Mihsan ya mike sai ya ce: ya Manzon Allah ka roka mini Allah ya sanya ni cikinsu, sai ya ce ka na cikinsu, sa'annan wani mutum ya mike ya ce: ka roka mini Allah ya sanya ni cikinsu, sai ya ce: "Ukkasha ya rigaye ka da ita". ( Bukhari & Muslim).

● انْقَضَّ : Ya fa'di.
● ارْتَقَيْتُ : Na yi ruqyah ( Addu'a tare da tofi ).
● عَيْنٍ : ( Kammun baka ).
● ( Me ya kaika ga yin hakan?) wannan dalili ne akan neman hujjah, cikin ladabi.
● ( Ba'a ruqyah sai a kammun baka da cizon ma'abucin dafi ): Ma'ana: ba maganin da ya fi amfani kan cutar kammun baka, da cizon abubuwa masu guba, fiye da ruqyah irinta shari'a (Addu'oin da suka tabbata a kur'ani da Sunnah) tare da kiyaye sharuddansu, ana iya yin magani ta hanyar da ba ruqyah ba (wanda be saba wa shari'a ba).
● حُمَة: cizon ma'abucin dafi (Maciji, kunama da sauransu), amma Kalmar: ( الحمَّة ): ma'anarta: Zazzabi.
● الرَّهْطُ : Mutum uku zuwa goma.
● لا يسترقون: Ba su neman ruqyah wajen wani yayin rashin lafiya, saboda:
1. Karfin dogaronsu da Allah.
2. Guje wa kankan da kai ma wanin Allah.
3. Don kar su rataya zukatansu da wanin Allah.
● Riwayar "**وَلَا يُرْقَوْنَ** (ba su yin ruqyah))", kuskure ne kamar yanda sheikhul Islam Ibnu Taimiyah ya fada, saboda Manzon Allah sallallahu Alaihi wasallam ya na yin ruqyah, kuma ya tabbata Mala'ika Jibril da Aisha sunyi masa ruqyah, hakazalika sahabbai ma sun kasance suna yin ruqyah.
● Kashe kashen mutane dangane da ruqyah:
1. Wanda ya ke neman ayi masa ruqyah, to wannan, kamalar tauhidi ta kubuce masa (ba ze shiga cikin mutane dubu saba'in ba).
2. Ba ya hanawa idan wani ya yi masa ruqyah, to wannan ba ze rasa kamalar ba, domin shi baiyi ba kuma bai hana ayi masa ba.
3. Ya hana wanda zaiyi masa ruqyah, wannan sabanin sunnah ne, domin Annabi sallallahu alaihi wasallam be hana Aisha ta yi masa ruqyah ba.
● وَلَا يَكْتَوُونَ : Ba su neman wani ya yi musu sakiya.
● وَلَا يَتَطَيَّرُونَ : ***At-Tadayyur***; shi ne chamfi da wani abin gani ko abin ji na kukan tsuntsu, ko wani sanannen abu, a wani wuri ko zamani, **Hukuncinsa**: karamin shirka ne.
● Wasun wadannan abubuwa ukun -na magungunan da shari'a ta yarda da su- ba sa hana shiga Aljannah ba tare da hisabi ko azaba ba, saboda dalilai da suka kan halaccin yin magani, da yabon wasu magungunan, kamar zuma da habbatus saudah.

## AL'UMMA IRI BIYU

***Ummatu al-ijaabah*:** Su ne suka amsa kiran Allah, da Manzonsa (sallallahu alaihi wasallam). **(Muminai)**

***Ummatu ad- da'wah*:** Sun kunshi wadanda suka amsa kiran Allah, da Manzonsa (sallallahu alaihi wasallam). Da wadanda ba su amsa ba. **(kafirai)**

### *MATSALOLIN BABIN:*

1. Sanin martabobin mutane cikin Tauhidi.
2. Ma'anar tace Tauhidi: ( tace shi daga shirka da bidi'a da zunubbai ).
3. Yabon Allah Subhanahu ga Annabi Ibrahima cewa bai kasance cikin mushrikai ba.
4. Allah Ya yabi manyan waliyyai, saboda kubutansu daga shirka..
5. Barin neman ruqyah daga wani, da sakiya su na cikin tace Tauhidi
6. Tawakkali da Allah shine ginshikin wadannan abubuwan. ( saboda bawa ya bar wadannan abubuwan saboda karfin tawakkalinsa ne).
7. Zurfin ilimin sahabbai, sun fahimci cewa ba za su samu wannan matsayin ba sai da aiki, ( wanda aka tsarkake niyyah ).
8. Kwadayinsu kan alkhairi. ( su na son isa ga gaskiya domin aiki da ida ).
9. Falalar wannan al'ummar ta fiskar yawanta, da kyawun aiki.
10. Falalar Sahabban Annabi Musa alaihis salam ( mabiyansa ).
11. An bijiro ma Annabi sallallahu alaihi wasallama da al'ummomi. ([1] Domin rarrashi a gare shi. [2] Bayani akan falalarsa da darajarsa ).
12. Kowace al'ummah za'a tayar da ita tare da Annabinta..
13. Karancin wadanda su ka yi imani da Annabawa.
14. Annabin da ba wanda ya amsa masa zai zo shi kadai.
15. Daga cikin amfanin wannan ilimin: [1] kada yawan mutane ya rude mu ( don kar mu halaka tare). [2] kuma kada karancin mabiya ya dame mu ( mutane kadan za su iya fin masu yawa alheri ).
16. Anyi rangwami cikin ruqyah ( ta shari'a ) a kammun baka da cizon ma'abota dafi (macijiya, kunama) ( da sauransu ).

17. Zurfin ilimin Salaf, saboda fadin Said bin jubair: (hakikia duk wanda ya tsaya kan abinda ya sani to ya kyautata), wannan ya ke nuni cewar babu cin karo tsakanin hadisi na farko da na biyu.

18. Nisantar salaf yabon wani da abinda bai cancanta ba.

19. Fadin Annabi wa Ukkashah: ( ka na daga cikinsu ), alama ce cikin alamomin annabta.

20. Falalar Ukkashah. (ya na cikin wadanda za su shiga Aljannah ba tare da hisabi ba).

21. Ana iya amfani da kinaya a wajen da ya dace. [1] kodai saboda wannan mutumin munafiki ne (wanda akace masa Ukkasha ya riga ka ). [2] Ko kuma tsoron kar a bude kofar da kowa zai tambayi wannan matsayin, har wanda bai cancance shi ba.

22. Kyawawan dabi'un Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam.

## [4] BABI NA HUDU: TSORON YIN SHIRKA

**Me yasa mawallafin ya kawo wannan babin bayan babin tace Tauhidi?**

Saboda duk babukan da suka zo a bayan babin tace Tauhidi bangare ne nasa, tsoron aukawa cikin shirka bangare ne na tace Tauhidi, hakanan kira zuwa ga Tauhidin shima bangare ne na tace shi, haka abun ya ke har karshen littafin.

Saboda kar mutum ya rudu da cewa shi ya tace Tauhidi alhali bai tace ba, kada ya rudu da kansa.

**DALILI NA FARKO:**

إِنَّ اللّهَ لاَ يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَلِكَ لِمَن يَشَاءُ

***" Lallai ne Allah ba ya gafartawa idan akayi tarayya da Shi, Kuma Yana gafarta abinda be kai shirka ba ga wanda Ya so "*** *(QS. An-Nisa: 48).*

**DALILI NA BIYU:**

وَاجْنُبْنِي وَبَنِيَّ أَن نَّعْبُدَ الأَصْنَامَ

***" Kuma Ka nisanta ni da diyana daga bautar gumaka "***. *(QS. Ibrahim: 35).*

**YAYA ZAMU KAUCE MA SHIRKA?**

- Koyon Tauhidi, Aiki da shi Kira zuwa gare shi, Hakuri a kan haka.
- Sanin shirka da sabubban da suke iya kaiwa gareta, domin nisantarta.
- Rokon Allah, da neman taimakonsa domin Ya tsaremu daga aukawa cikin shirka.
- Barranta daga shirka da ma'abotansa, da nisantar su domin kar ya zamo cikin su.

● Allah ba Ya Gafarta shirka idan aka mutu a kayi, domin laifi ne maigirma kan hakkin Allah kebantacce, shine Tauhidi, duk wanda ya mutu kan babban shirka, to zai dawwama cikin wuta har abada, amma idan ya mutu kan karamar shirka to za ayi masa azaba gwargwadon shirkarsa sa'annan ya shiga Aljannah, ba zai dawwama a wuta ba.

Saboda ya na daga cikin ma'abota imani. ( ya mutu da wani sashe na Tauhidi ).

● {*Ka nisanta ni* }: Ka sanya ni a gefe, Ka sanya masu bautar gumaka a wani gefen, har kowa ya nisanci kowa.

● { *Gumaka* }: ***Assanam*** (gunki ) shine abin da aka sanya shi a surar mutum ko surar wani abu daban, kuma ake bauta ma sa koma bayan Allah, ***al-wasan***: shine duk abin da aka bauta masa ba Allah ba, ko yaya ya ke. ***al-wasan*** *ya fi fadin ma'ana sama da* ***assanam.***.

● Ibrahim -alaihis salam ya na jin tsoro shirka wa kansa tare da cewa shi badadin Allah ne, kuma shugaban masu kadaita Allah, to yaya namu halin zai kasance?.

Kar ka amince wa kanka daga aukawa cikin shirka ko munafurci, domin babu wanda ya ke aminta daga munafurci sai munafuki.

**DALILI NA UKU:**

وَفِي الحَدِيثِ: «أَخْوَفُ مَا أَخَافُ عَلَيْكُمْ: الشِّرْكُ الأَصْغَرُ، فَسُئِلَ عَنْهُ؟ فَقَالَ: الرِّيَاءُ».

[3] Ya tabbata cikin hadisi: "**mafi girman abin da na fi ji muku tsoro: karamar shirka**, sai aka tambaye shi mecece karamar shirka? Sai ya ce: **riya** "

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ ؓ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «مَنْ مَاتَ وَهُوَ يَدْعُو لِلهِ نِدًّا؛ دَخَلَ النَّارَ». رَوَاهُ الْبُخَارِيُّ.

[4] Daga dan Mas'ud Allah Ya kara yarda a gare shi, Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: " Duk wanda ya mutu ya na sanya wa Allah kishiya **to zai shiga wuta**". ( Bukhari)

**DALILI NA BIYAR:**

وَلِمُسْلِمٍ عَنْ جَابِرٍ ؓ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «مَنْ لَقِيَ اللهَ لَا يُشْرِكُ بِهِ شَيْئًا دَخَلَ الْجَنَّةَ، وَمَنْ لَقِيَهُ يُشْرِكُ بِهِ شَيْئًا دَخَلَ النَّارَ».

[5] Daga Jabir Allah Ya kara yarda agare shi, Manzon Allah sallallahu alai wasallam ya ce: "wanda duk ya hadu da Allah ba ya shirka zai shiga Aljannah, wanda ya hadu da shi ya na hada shi da wani abu **to zai shiga wuta** ".

● Riya: itace mutum ya yi wata ibada ma Allah domin mutane su ganshi ko suji shi su yabe shi a kan wannan ibadar, ba ya nufin sanya wannan ibadar wa mutanen, idan ya sanya ta garesu to ya zamo babban shirka, amma idan yayi wata ibada da nufin mutane suyi koyi da shi, to wannan ba riya ba ce, wannan daya ne daga hanyoyin kira zuwaga Allah ( Da'awa ).

**Hanyoyin magance matsalar riya:**

1. Karatun Tauhidi, domin da shi ne bawa ya ke ganin girman Allah, ba ya damuwa da wani cikin addinin Allah.
2. Yawan Addu'a.
3. Mutum ya yi kokarin boye ayyukansa na alheri tsakninsa da Ubangijinsa .
4. Kar mutum ya ki yin aikin alheri da hujjar kaucewa aukawa cikin riya.
5. Yawaita kyawawan aiyuka wadanda suke tunasar da bawa lahira, kamar ziyaran makabarta da sharuddanta.

**ME YA SA ANNABI SALLAL LAHU ALAIHI WASALAM YA KE TSORACE WA AL'UMMARSA RIYA SAMA DA TSORON MASIHUD DAJJAL?**

Saboda fitinar Dajjal a fili ta ke, amma fitinar riya a boye ta ke.

Fitinar Dajjal tanada kebantaccen lokaci (karshen zamani), sabanin riya da take iya akuwa a kowani lokaci.

**KASHE KASHEN RIYA**

**Daga asalin ibadar:** Ibadar da aka ginata akan riya, To wannan ibadar batacciya ce.

**Wanda ya auku:** Ibadar don Allah aka fare ta, amma riya ta auka cikinta.

**Bayan ya kare ibadar:** Ba ya tasiri sedai idan akwai ketare iyaka ciki, kaman gori da cutarwa bayan sadaka.
.

**Ya tunkude shi,** to wannan ba zai cutar da shi ba, saboda ya yi kokarin tunkude shi, ibadarsa ta inganta.

**Riyar ta rinjaye shi,** to wannan yanada kashe kashe:

Idan farkon ibadar ya na saduwa da karshenta, kamar SAllah, to wannan ibadar ta lalace gaba daya.

Idan farkon ibadar bata sadu da karshenta ba, kamar zakkah: to kadai bangaren da riyar ta shiga ne ya baci.

- نِدًّا : **Anniddu**: shine kishiya da makamanci.
- **(Zai shiga wuta ):** wannan shine ukubar rikan kishiyoyi ma Allah.
- شَيْئًا **( kowani abu):** ya game kowani irin shirka, ko da mafificin halitta mutum ya tara shi da Allah, to zai shiga wuta.

● (Duk wanda ya hadu da shi, ya na mai hada shi da wani abu to zai shiga wuta): idan shirkar karama ce to, ba ta lizimta tabbata a cikin wuta, amma idan babban shirka ce to, tana lizimta tabbata a cikin wuta.

● **(Shirka):** Hada Allah da wani cikin bauta ba abu ne mai sauki ba, sedai kuma Allah Ya na yassare wa bawansa ikhlasi, sai ya zamo kamar yana ganin Allah a gaba gare shi, sai ya nemi yardan Allah da aiyukansa, ba neman yabon mutane ko guje wa zarginsu ba, domin har abada mutane ba za su iya amfanar da shi da komai ba.

● Hakanan kuma, yanada muhimmanci kar mutum ya yi farin ciki idan mutane suka karbi maganarsa, a'a, yayi farin ciki idan suka karbi maganarsa domin dacewarta da gaskiya, ba domin kasancewarta maganarsaba, hakanan akasin hakan, ikhlasi abune mai wahala, amma idan mutum ya fiskanci Ubangijinsa fiskanta ta gaskiya kan mikakkiyar hanya; to wannan Allah zai taimake shi a kan ikhlasi, kuma ya sauwake masa.

**Addu'a ya kasu kashi biyu:**

**Dua'u ibadah** (Addu'a ta ibada): kamar wanda ya yi sallah ko hajji ko azumi ma wanin allah to wannan kafiri ne babban kafirci.

**Dua'u mas'alah** (Adduar roko): Ya kasu kasha biyu:

**Abin da ba mai iko akai sai Allah:** wannan yinsa ma wanin Allah shirka ce babba, Kaman wanda ya nemi da, ko saukar da ruwan sama a wajen wanin Allah.

**Cikin abin da halitta suke da iko akai:** Wannan ya na halatta idan ya cika sharudda hudu: wanda za'a roka din ya zamo; rayayye, kuma yana wajen, kuma ya na da iko, kuma shi sababi ne kadai.

**BANBANCIN BABBAR SHIRKA DA KARAMA:**

**Babban Shirka:**
- Ya na fitar da mutum daga Addini.
- Ya na bata dukkan aiyuka.
- Ma'abocinsa zai dawwama cikin wuta har abada.

**Karamar Shirka:**
- Ba ya fitar da mutum daga Addini.
- Yan a bata aikin da riya ta shiga ciki.
- Ba 'a dawwama cikin wuta saboda shi.
- Ba ya halatta jinni da dukiya.

● Ya na halatta jini da dukiya, daga mahukumta.
● Dalili ya na nunin cewa baban shirka ne.
● Ya yi kudirin cewa wanin Allah ya na da wani tasarrufi boyayye cikin halittu, kuma ya na iya jawo amfani ko tunkude cuta.

● Dalili ya na nuni kan shi karami ne.
● Ya sanya abin da Allah bai sanya shi sababi ba sababi.
● Duk wata hanyar da zata kai zuwaga babban shirka, to karamar shirka ce.
● duk abin da shari'a ta kira shi shirka ko kafirci, amma Kalmar ba ta zo da (ال), to ga ka'ida, sai a dauke shi karamin shirka.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tsoron aukawa cikin shirka.
2. Riya nau'i ne na shirka.
3. Riya karamir shirka ce. ( wato kankani riya).
4. Riya itace mafi girman abin tsoro ga salihai, (saboda za ta iya aukawa cikin zuciyar mutum ba tare da ya sani ba, saboda buyarta da yanda zuciya take neman auka wa cikinta, domin da yawan zukata su na son a yabe su kan ibada.
5. Kusancin Aljanna da wuta.
6. Magana a kan kusancinsu ya zo cikin hadisi guda.
7. Wanda ya hadu da Allah ya na shirka to zai shiga wuta koda ya fi kowa bautan Allah. (idan shirkar babba ce to ba zai shiga Aljannah ba, idan kuma karama ce to za'a yi masa azaba gwargwadon zunubinsa sa'annan ya shiga Aljannah ).
8. Matsala maigirma; tambayar Annabi Ibrahim Khalil Allah Ya tsare shi da yayansa daga bautan gumaka.
9. Annabi Ibrahi ya kula da cewa gumaka sun batar da mutane masu yawa:

رب إنهن أضللن كثيرا من الناس

*“ **Ya Ubangijina lallai su sun batar da mutane masu yawa** ” (QS. Ibrahim, 36).*

*10* Ckin wannan babin akwai tafsirin " **la'ilaha illalliah** " kaman yanda imamul Bukhari ya ambata.

11. Falalar wanda ya kubuta daga shirka. (zai shiga Aljannah).

## [5] BABIN KIRA ZUWAGA KALMAR SHAHADA

**Me yasa mawallafin ya kawo wannan babin?**

1. Yayin da ya ambaci Tauhidin mutum, sai ya ambaci kiran waninsa zuwaga hakan; saboda imani ba zai cika ba har sai ya yi kira zuwaga Tauhidi, wajibi ne bayan mutum ya tabbatar da Tauhidi ya yi kira zuwa gare shi.
2. Domin mayar da martini akan wadanda suke cewa fakon abin da mutum zai fara da shi shi ne Sallah ba Tauhidi ba.

**DALILI NA FARKO:**

Da Fadin Allah Ta'ala:

قُلْ هَـذِهِ سَبِيلِي أَدْعُو إِلَى اللّهِ عَلَى بَصِيرَةٍ أَنَاْ وَمَنِ اتَّبَعَنِي

*((Kafada musu cewa wannan itace hanyata ina kira zuwaga Allah Ta'ala akan basira ni da wanda ya bi ni)) (QS. Yusuf :108).*

● ***{Hanyata}***: Ya kunshi abin da Annabi sallallahu Alaihi wasallam ya zo da shi, na shari'a, ( ibada da da'awa zuwaga Allah ).

● ***{Zuwaga Allah}***: masu da'awa sun kasu gida biyu: [1] mai kira zuwaga Allah. [2] mai kira zuwaga wanin Allah.

● ***{Akan basira}***: ya kunshi: [1] ilimin shari'a. [2] sanin halin wanda ake kira zuwaga Allah. [3] Hikimah.

● **Sharuddan kira zuwaga Allah (Da'awa):**

1. Iklasi.
2. Ilimin shari'a..
3. Hikimah.
4. sanin halin wanda ake kira zuwaga Allah.
5. Hakuri.

**DALILI NA BIYU:**

**عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ۞؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ لَـمَّا بَعَثَ مُعَاذًا إِلَى الْيَمَنِ قَالَ لَهُ: «إِنَّكَ تَأْتِي قَوْمًا مِنْ أَهْلِ الْكِتَابِ، فَلْيَكُنْ أَوَّلَ مَا تَدْعُوهُمْ إِلَيْهِ شَهَادَةُ أَنْ لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ - وَفِي رِوَايَةٍ: إِلَى أَنْ يُوَحِّدُوا اللهَ - فَإِنْ هُمْ أَطَاعُوكَ لِذَلِكَ؛ فَأَعْلِمْهُمْ أَنَّ اللهَ افْتَرَضَ عَلَيْهِمْ خَمْسَ صَلَوَاتٍ فِي كُلِّ يَوْمٍ وَلَيْلَةٍ، فَإِنْ هُمْ أَطَاعُوكَ لِذَلِكَ، فَأَعْلِمْهُمْ أَنَّ اللهَ افْتَرَضَ عَلَيْهِمْ صَدَقَةً تُؤْخَذُ مِنْ أَغْنِيَائِهِمْ فَتُرَدُّ عَلَى فُقَرَائِهِمْ، فَإِنْ هُمْ أَطَاعُوكَ لِذَلِكَ، فَإِيَّاكَ وَكَرَائِمَ أَمْوَالِهِمْ، وَاتَّقِ دَعْوَةَ الْـمَظْلُومِ؛ فَإِنَّهُ لَيْسَ بَيْنَهَا وَبَيْنَ اللهِ حِجَابٌ»، أَخْرَجَاهُ.**

Daga dan Abbas Allah Ya kara yarda a gare shi: yayin da Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya aiki Mu'azu zuwa Yaman, ya ce ma sa " Lallai ne zaka je ga wadansu mutane daga ahlul kitabi, **farkon abin da zaka kira su akai;** su shaida babu abin bautawa bisa cancata sai Allah, -a cikin wata riwayar: kayi kiran su zuwa ga su kadaita Allah- idan suka yi maka biyayya kan haka; ka sanar da su Allah Ya farlanta a kansu salloli guda biyar, cikin kowani yini da dare, idan sun maka biyayayya kan haka, to ka sanar da su Allah Ya farlanta sadaka a kansu, ana karba daga mawadatansu a mayar da ita zuwaga mabukatansu, to idan sukayi maka biyayya akan haka, to ka kiyayi masu daraja daga dukiyoyinsu, kuma ka kiyayi addu'ar wanda aka zalunta, domin babu shamaki tsakaninta da Allah". (Bukhari da Muslim).

**Cikin wannan hadisin akwai:**

1. Shar'ancin aika masu kira zuwaga Allah, da karantar da su yanda za siyi da'awar .
2. Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya aika mutum guda, wannan dalili ne akan halaccin karbar riwayar mmutum guda, koda kuwa a bangaren aqida ce.
3. ba a shardanta wa yin da'awa wasu kwanaki kididdigaggu ba, mai da'awa yana zama ne cikin wadanda ya ke musu da'awar gwargwadon bukatar su.
4. Salon kiran wadanda ake da sabani da su, kuma hanya mafi sauki itace a kirayesu zuwaga Tauhidi (kadaita Allah ), ba muhawara ba.
5. Kira zuwaga musulunci shi kadai ba zai wadatar ba, dole ya sanar da su wajiban da suke kansu a musuluncin har su gamsu, kuma su aikata, sedai anaso ya zamo bisa tartibin da yazo cikin hadisin Mu'azu Allah Ya kara yarda a gareshi.

**DALILI NA UKU:**

وَلَهُمَا عَنْ سَهْلِ بْنِ سَعْدٍ ﭬ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ يَوْمَ خَيْبَرَ: «**لَأُعْطِيَنَّ الرَّايَةَ غَدًا رَجُلًا يُحِبُّ اللهَ وَرَسُولَهُ، وَيُحِبُّهُ اللهُ وَرَسُولُهُ، يَفْتَحُ اللهُ عَلَى يَدَيْهِ**»، فَبَاتَ النَّاسُ يَدُوكُونَ لَيْلَتَهُمْ، أَيُّهُمْ يُعْطَاهَا، فَلَمَّا أَصْبَحُوا غَدَوْا عَلَى رَسُولِ اللهِ ﷺ، كُلُّهُمْ يَرْجُو أَنْ يُعْطَاهَا، فَقَالَ: «**أَيْنَ عَلِيُّ بْنُ أَبِي طَالِبٍ؟**»، فَقِيلَ: هُوَ يَشْتَكِي عَيْنَيْهِ، فَأَرْسَلُوا إِلَيْهِ فَأُتِيَ بِهِ، فَبَصَقَ فِي عَيْنَيْهِ وَدَعَا لَهُ؛ فَبَرَأَ كَأَنْ لَمْ يَكُنْ بِهِ وَجَعٌ، فَأَعْطَاهُ الرَّايَةَ، فَقَالَ: «**انْفُذْ عَلَى رِسْلِكَ حَتَّى تَنْزِلَ بِسَاحَتِهِمْ، ثُمَّ ادْعُهُمْ إِلَى الإِسْلَامِ، وَأَخْبِرْهُمْ بِمَا يَجِبُ عَلَيْهِمْ مِنْ حَقِّ اللهِ تَعَالَى فِيهِ، فَوَاللهِ لَأَنْ يَهْدِيَ اللهُ بِكَ رَجُلًا وَاحِدًا خَيْرٌ لَكَ مِنْ حُمْرِ النَّعَمِ**».

«**يَدُوكُونَ**»؛ أَيْ: يَخُوضُونَ.

Daga Bukhari da Muslim, daga Sahal dan Sa'ad Allah Ya kara yarda a gare shi, cewa Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya fada a ranan yakin khaibar: " Wallahi lallai ne zan bayar da tuta gobe, ga wani mutum, wanda ya ke son Allah da manzonsa, kuma Allah da Manzonsa suke son sa, Allah zai bude khaibar a hannunsa",

sai sahabbai suka kwana, suna tattaunawa a cikin darensu, ma waye za'a ba shi wannan tutar cikinsu?, yayin da suka wayi gari, sai sukayi sammako zuwaga Manzon Allah salallahu alaihi wasallallam kowansu ya na fatan aba shi, sai ya ce: " ina Aliyu dan Abi-dalib?" sai aka ce: idonsa yana ciwo, sai akayi aike zuwa gare shi aka tafo da shi, sai ya yi tofi a idonsa kuma ya yi masa addu'a, sai ya warke kamar baiyi ciwon ba, sai ya ba shi tutar, ya ce masa: " **ka tafi cikin natsuwa har ka sauka a farfajiyarsu, <u>sa'annan ka kira su zuwaga Musulunci, ka sanar da su abin da ya wajaba akansu na hakkin Allah,</u>** Wallahi! mutum daya ya shiriya sanadinka, yafi maka alheri sama da jajayen rakuma".

**(Suna kutsawa)**, ma'ana suna tattaunawa da tunani a wannan daren mawa za'a bayar da tutar.

**Wannan hadisin ya kunshi:**:

1. Tabbatar wa Allah da sifar soyayya, Allah Ya na so, kuma ana son sa, sedai soyayyar Allah ba irin ta mutane ba ce.
2. Tabbaar falala ta musamman ba ta lizimta falala ta gaba daya, kamar fadin Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam gama da Abu ubaida Allah Ya kara yarda a gare shi, cewa shi ne: "**Aminin wannan al'ummar**" wannan baya nufin cewa yafi dukkan sahabbai falala, hakanan Mu'azu Allah Ya kara yarda a gare shi.
3. **حُمْرِ النَّعَمِ:** Jajayen rakuma, ya ambace su ne saboda larabawa suna tsananin son su.

***Khawariqul 'Aada't:*** (abubuwan da suka saba wa al'ada hudu ne, suna zuwa sabanin yanda mutane suka saba; kaman mutum ya tashi sama ko yayi tafiya a kan ruwa:

1. **Aayah:** Ta Annabawa ce, ba'a kiranta mu'ujizah; A'ya ce tazo cikin Al-kur'ani ba, mu'ujizah ba, Mu'ujiza zata iya gagaran wasu, kuma zata iya kasantuwa ga wasun Annabawa, amma ba zai taba yiyuwa, wani mutum yayi da'awar a'ya bayan mutuwar Annabi sallallahu alaihi wasallam ba.

2. **Karamah:** Ta waliyyai ce, sune wadanda suka siffantu da imani da takawa, misalinta shine abinda ya faru da ashubul kahfi (ma'abota kogo).

3. Mu'ujiza ko fitinah: Tana kasancewa ne tare da waliyyan shedan, muna iya gane ta ne da sanin halin mutum, ba imani ba takawa, misali kan haka: abinda ya ke faruwa a hannun Dajjal.

`4. Fadhihah: Tozarci: duk wanda ya karyata Allah, to zai kunyata shi a duniya kafin lahira' misalin fadiha shine abinda ya faru da Musailimah Al-kazzab; yayi tofi a idon wani maras lafiya sai ya makance.

**MATSALOLIN BABIN:**

1. Yin kira zuwa ga Allah hanyar mabiya Manzon Allah ne Sallallahu alaihi wasalam (hanyar Manzanni da mabiyansu).

2. Fadakarwa a kan ikhlasi, saboda da yawan mutane ko ya yi kira zuwa ga gaskiya to zaka sumu yana kirane zuwa ga kansa.

3. Basira (ilimi) yana cikin farillai ( Da'awa farillah ce, don haka ilimin yin da'awar shima ya zama farillah).

4. Daga dalilan kyautatuwar Tauhidi, kasancewarsa tsarkake Allah Ta'ala ne daga zagi.

5. Daga munin shirka, kasancewar shirka zagin Allah ne. ( Mumin yana tsarkake Allah ne daga tawaya).

6. Daga mafi muhimmancinsu, muslulmi ya nisanci masu shirka don kar ya zamo daga cikinsu, ko da baiyi shirka ba.

7. Tauhidi shine farkon wajibi akan mutum.

8. Wajibi ne mutum ya fara da Tauhidi kafin komai, hatta sallah.

9. Ma'anar ((**su kadaita Allah**)) shine ma'anar: *shaidawa ba bu abin bautawa bisa cancanta sai Allah*.

10. Mutum zai iya zamowa daga ma'abota littafi amma bai san ma'anar lailaha illallahu ba, ko yasan ma'anarta amma ba ya aiki da ita.

11. Fadakarwa kan karantarwa bisa mataki mataki.

12. Farawa da mafi muhimmanci, sai mai bi masa. (a fara da Tauhidi sai Sallah, sai Zakkah).

13. Yanda ake sarrafa zakkah. (ana ba da zakkah wa sinfi takwas na mutane ne).

14. Yayewar Malami shubuha daga mai neman ililmi a wajensa. (ta hanyar karantar da shi da dage jahilci daga gare shi).

15. Hani kan taba manyan dukiyoyin mutanen da ake karbar zakkah a wajensu .

16. kiyayar addu'ar wanda aka zalunta.

17. Labartawa kan cewar ba ta da hijabi. (ya hada tsakanin kwadaitarwa da tsoratarwa).

18. Daga dalilan Tauhidi, abin da ya gudana wa shugaban manzanni, da shuabannin waliyyai, na wahala, da yunwa, da annoba (za'a fahimci haka cikin kisser yakin khaibar).

19. Fadinsa: (lallai ne zan ba da tuta…), alama ce daga cikin alamomin annabta.

20. Tofin Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam a idanun Aliyu radiyallahu anhu, shima yana daga alamomin annabta.

**21.** Falalar Aliyu bn Abi-dalib radiyallahu anhu .

22. Falalar Sahabbai, yanda suka kwana suna tattaunawa cikin wannan daren, da shagaltuwarsu daga busharar cin nasara. (saboda kowa na fatan a ba shi tutar, domin samun tabbacin son Allah da manzonsa).

23. Imani da kaddara, domin an bada tutar ga wanda baiyi yunkurin samun ta ba, da hana ta ga wanda ya yi yunkurin samunta.

24. Kyakkyawar ladabi cikin fadinsa: " **cikn natsuwarka** ",(umurninsa kan bi ahankali banda gaugawa).

25. Kira zuwa ga Musulunci kafin yaki.

26. Shar'ancin yakar wadanda aka taba kiran su amma ba su amsa kirar ba.

27. Da'awa da hikima saboda fadinsa, " **ka ba su labarin abin da ya zamo wajibi a kansu** ". (mutum zai iya lizimtar aiki da musulunci, ko yaki aiki da shi, to dole a cigaba da lallashisa domin kar ya koma cikin kafirci ).

28. Sanin hakkin Allah a musulunci.

29. Ladar wanda mutum guda ya shiriya a hannunsa, (shine mafi alhairi gareka daga duk wani abin da ake ganin kyawunsa aduniya ).

30. Rantsuwa a kan fatawa (bai dace ba yin rantsuwa akan fatawa sai dan saboda wata maslaha da fa'ida).

## Jarabawa kashi na farko ( babi

### [1] Ambaci babuka biyar na farkon kitabut tauhid, da munasabarko kowani babi ga kitabut tauhid

| No | Unwanin babin | Sababin kulla babin |
|---|---|---|
| 1 | | |
| 2 | | |
| 3 | | |
| 4 | | |
| 5 | | |

### [2] Cika iba'ran da abin da ya dace da ita:

1. Muna karanta kitab attauhid ne saboda sabubba kamar haka?
a. ……………………………………………………………………………………………
b. ……………………………………………………………………………………………
c. ……………………………………………………………………………………………
d.……………………………………………………………………………………………
e.……………………………………………………………………………………………
2. Mawallafin bai ambaci mukaddima ba wa kitabut tauhid saboda:
a.……………………………………………………………………………………………
b.……………………………………………………………………………………………
c.……………………………………………………………………………………………
3. Zamu iya kasa kitabut tauhi zuwa:
a. ……………………………………………………………………………………………
b. ……………………………………………………………………………………………
c. ……………………………………………………………………………………………
d.……………………………………………………………………………………………
e.……………………………………………………………………………………………
f. ……………………………………………………………………………………………
g. ……………………………………………………………………………………………
h. ……………………………………………………………………………………………
i.……………………………………………………………………………………………
j.……………………………………………………………………………………………
4. Mayar da martani ga wanda yace kitabut tauhid ya kunshi uluhiya ne kadai: da :
a. Babin ………………………………………………………………………………
b. Babin ………………………………………………………………………………
c. Babin ………………………………………………………………………………

5. Ubudiyyah (Bauta) ta kasu zuwa:
a. Bauta irin ta……………………………………Tana nufin…………………………… Dalili kan haka:………………………………………………………………………………
b. Bauta irin ta…………………………………… Tana nufin …………………………… Dalili kan haka………………………………………………………………………………
c. Bauta irin ta…………………………………… Tana nufin ……………………………
Dalili kan haka ……………………………………………………………………………………
6. Rayuka da Allah ya haramta a kashe su hudu ne:
a. …………………………………………...b. ……………………………………………………
c. ………………………………………….. d. ……………………………………………………
7. Ibnu Mas'ud radiyallahu anhu ya ambaci ayar (Al-An'am : 151-153) wasiyyar Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam domin ita: ……………………………………………………
8. Ma'nar al'umma (الأمة) cikin Alqur'ani na nufin:……………………………………ko …………………………ko……………………………ko…………………………………..
9. Ma'anar tace Tauhidi:……………………………… daga………………………………..
da………………………………………da………………………………………………
10. Wannan al'ummar itace mafi yawan al'ummomi cikin:
……………………………………da……………………………………………………….
11. Tabbatuwar falala ta musamman ba ta lizimta gamammiyar falala:
……………………………………………………………………………………………………
12. (Ba'a rukya se a kammun baka), ma'ana?
……………………………………………………………………………………………………
13. Hani ya zo kan neman rukya da sakiya, banda zuwa wajen likita, saboda?.......................
.........................................................................................................
14. *{Allah ba ya gafartawa idan akayi tarayya da shi}, ma'ana:* ……………………………
*{Yana gafarta abin da bai kai shirka ba}, ma'ana:* ………………………………………......
15. Ma'nar *{wani ruhi ne daga gare shi}?*……………………………………………………. *Ma'anar {Kalmarsa ce}:*…………………………………………………………………………………….
16. Abubuwan da Allah ya jingina su zuwa gare shi sun kasu zuwa:
[1] Jingina……………………wannan jinginawa ce irin ta:…………………………………….
[2] Jingina……………………wannan jinginawa ce irin ta…………………………………….
17. Fadinsa: "Ukkasha ya riga ka da ita", ya fada ne domin:…………………………………
ko kuma:………………..................................................................
18. Ma'anar: [basu garwaya imaninsu]? …………………………….[da zalunci]:……………...
19. Mu na jin tsoron shirka ne da:
1. ……………………………………………2……………………………………………………
3. ……………………………………………4.……………………………………………………
5……………………………………………………

20. Ma'anar (yana nemam fiskar Allah da hakan): …………………………………… ciki hadisin akwai tabbatar da sifar:……………………………………………………. …………
21. Sharuddan da'awa: [1] ……………………………………………………………
[2] ……………………………………………[3] …………………………………………………
[4] ……………………………………………[5] …………………………………………………
22. *Abubuwan da suka saba wa al'ada (خوارق العادات):*
1. ……………………………………ta na kasancewa ne ga:………………………………………
2. ……………………………………ta na kasancewa ne ga: …………………………………
3. ……………………………………ta na kasancewa ne ga:…………………...…………..
4. ……………………………………ta na kasancewa ne ga:……………………………………
23. Mawallafin ya ce: ( barin rukya da sakiya yana daga tace tauhidi), amma bai ambaci chamfi ba sabo da?……………………………………………………………………………….

[3] Cika guraben a jadawalin kashe kashen tauhidi masu zuwa:

Cikin asalin ibadah:
………………………
………………………
………………………
………………………

Wanda ya auku ciki:
……………………
……………………
……………………
……………………

Bayan an gama ibadah:
…………………………………………
…………………………………………
…………………………………………
………………………………………….

……………………………………………………………
wannan bay a cutarwa, kuma ibadah ta inganta.

……………………………...
wannan yana kasuwa:

…………………………………………………
……………………………………...……
Hukuncinsa…………………………………

…………………………………………
…………………………………………
Hukuncinsa……………………………

[4] Saka alamar: (☒) a wajen da ya dace, ko ka cika ibarar:

1. Mawallafin kitab tauhid shine: ☐ Ibnu Usaimin ☐ Muhammad bin Abdul wahhab at-Tamimi.
2. Nasihar maluma: ☐ hardace matani kafin darasinsa ☐ ba fa'ida cikin harda, fahimta shine muhimmi.
3. fadin Allah:

الَّذِينَ آتَيْنَاهُمُ الْكِتَابَ يَتْلُونَهُ حَقَّ تِلاَوَتِهِ

*[ **Wadanda muka bai wa littafi, suna karatunsa a kan hakkin karatunsa]*** *...(QS. Al-baqarah: 121).*

Za'a fa'idanta daga ayar: kada dalibin yabar wani ilimi har sai ya iya shi. ☐ haka ne ☐ kuskure ne.

4. Malamai sun bibiyi kitabut tauhid basu samu hadisai munkarai cikinsa ba. ☐ haka ne ☐ kuskure ne.

5. komai yalwar ilimin malamai, wannan ba ya nunin cewa su ma'asumai ne. ☐ haka ne. ☐ kuskure ne.

6. Akwai daga litattafan sheikh Muahammad bin Abdul Wahhab: ☐ Kashfush shubuhat. ☐ Masaailu Al-Jaahiliyyah. ☐ Mukhtasaru As-Sirah. ☐ Usulu Al-Iman. ☐ gaba daya.

7. Babukan Kitabut Tauhid: ☐ Babuka: 67. ☐ Babuka: 76. ☐ Babuka: 10.

8. Idan ka mallaki wani littafi to ba z aka yi saurin shigar da shi laburarenka ba har se bayan ka bibiye shi a gurguje ko ka karanta mukaddimarsa, da abubuwan da ya kunsa. ☐ haka ne. ☐ kuskure ne.

9. Za mu iya karkasa kitabut Tauhid zuwa kashi : ☐ kashi: 11 ☐ kashi: 9 ☐ kashi: 10.

10. Kitabut Tauhid na daga mafi fa'idar litattafan da aka wallafa ta hanyar kafa dalili, da sanin hikima da nitsawa cikin sirrin matsalolin shari'a. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

11. Ilimi: ya kunshi hadawa da rarrabawa. ☐ haka ne ☐ kuskure ne.

12. Wajibi ne a hardace lafuzzan malamai kan ma'anoni, da rabe rabensu da banbance banbance. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

13. Kason farko na kitab Tauhid: ☐ Mukaddimah. ☐ Tafsirin Tauhidi. ☐ Wajbcin tauhidi.

14. Mawallafin ya yi koyi ne da Imamul Bukhari wajen gabatarwa da cikawa. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

15. Mawallafin baiyi tarjama wa babin farko ba, za mu iya tarjama shi da: “Babin Mukaddimah”. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

16. kason farko na littafin ya kunshi: ☐ Babi: 5. ☐ Babi: 6. ☐ Babi 7.

17. Tauhid ya kasu zuwa: ☐ tauhidin rububiyyah, tauhid uluhiyyah, tauhidin asma'u wa sifat. ☐ tauhidin al-maa’rifah, wal-isbat, Wal, qasd wal-iradah ☐ gaba daya.

18. Wanda yayi imani da sashen tauhidi banda sashe wannan tauhidinsa bai cika ba. ☐ haka ne ☐ kuskure ne.

19. Karkasa tauhidi bidi'a ce saboda babu dalili kan haka?.
☐ haka ne ☐ kuskure ne.

20. Alakar tauhidi da imani shine: imani ya fi fadi, tauhidi bangare ne na imani. ☐ haka ne ☐ kuskure ne.

21. Kalmar shahada ( *laa ilaaha illallah)* tanada: ☐ rukunnai biyu. ☐ rukunnai takwas. ☐ rukunnai bakwai.

22. Kadaita Allah da jujjuya al'amura cikin halittu, da saukar da ruwa, wannan tauhidin: ☐ uluhiyyah ☐ rububiyyah ☐ al-asma'u wa sifat.

23. Yana daga abin da ke kore asalin tauhidi: ☐ babbar shirka. ☐ karamar shirka ☐ bid’ah.
24. Biyayya ga iyaye shine mafi girman wajibai. ☐ Haka ne ☐ kuskure.
25. Zina da kashe ran da allah ya haramta, sune mafi girman abin da Allah ya haramta. ☐ haka ne ☐ kuskure ne.
26. Ibada ta kunshi abubuwa: ☐ biyui ☐ daya.
27. Ma'anar ibada: (suna ce da ta kunshi duk…) wannan maganar? ☐ Ibnul Qayiim ☐ Ibnu Taimiyah.
28. Maganar daidai itace: ana tabbatar da sifar Allah: ba tare da… ☐ takyifi ba (bayanin yanayin sifar), ko misaltawa ba. ☐ takyifi ba (bayanin yanayin sifar), ko kamantawa ba. ☐ duka biyun ba banbanci.
29. Duk wata aya cikin Al kur'ani ta na nuni akan tauhidi. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
30. Hikimar halittan aljanu da mutane daidai yake da hikimar halittan dabbobi. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
31. Allah ya ce:

وَمَا خَلَقْتُ الْجِنَّ وَالْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ

“ ***Ban halitta Aljanu da mutane ba sai don su bauta mini***.” *(QS. Az-Zariyat: 56):*
Galibin rikicin da ke faruwa cikinta yana kasancewa ne a cikin ☐ fahimta. ☐ Aiki.
32. an kallafa wa Aljanu yin: ☐ Imani kadai. ☐ Iman da yin aiki da shari'oi.
33. الأمة Lafazin al'ummah cikin Alqur’ani na zuwa da ma'anar: ☐ imam ☐ addini ☐ zamani ☐ kungiya ☐ duka gaba daya.
34. Allah ya ce: *“Mun aika da manzo cikin dukkan al'umma…” (QS. An Nahl, 36).* Ma'ana tun daga zamanin (☐ Adam ☐ Nuh) har zuwa zamanin (☐ Isa ☐ Muhammad) alaihimussalam. Hikimar aika su itace: ☐ tsayar da hujjah ☐ jinkai ☐ bayanin hanya zuwa ga Allah ☐ duka gaba daya.
35. Gumaka suna daga dagutai wadada ake bautawa wanda ba Allah ba.
☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
36. Wanda ake masa biyayya daga dagutai shine kamar; shuwagabannin da suka fice daga da'a wa Allah. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
37. Wanda aka bauta masa wanda ba Allah ba, amma bai yarda da bautar ba ☐ daghutu ☐ ba daghutu ba ne.
38. Aya ta biyu cikin kitabut tauhid tana nuni kan haduwan manzanni waje kira zuwa ga tauhidi. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
39. Mawallafin ya ce: ( aya ko ayoyi ) ( mafi cikar aya ko ayoyi) . ☐ haka ne ☐ kuskure ne.
40.Kaddara da hukunci da irada sun kasu zuwa; ta shari'a da kauniyyah ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
41. Yana daga hukuncin (☐ kauni ☐ shar’i) abinda allah yake sonsa ta wata fiskar kuma yake kinsa ta wata fiskar.
42. Allah ya ce:

وَقَضَيْنَا إِلَى بَنِي إِسْرَائِيلَ فِي الْكِتَابِ لَتُفْسِدُنَّ فِي الأَرْضِ

**" mun hukumta zuwa ga Bani Isra'ila a cikin littafi cewa lallai ne kunayin barna a cikin kasa"**
Hukunci ne irin na ☐ kauni ☐ shar'i.
43. Dukkan dabbobi suna tsarkake Allah banda tsaka. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
44. Bauta ta kasu gida ☐ biyu. ☐ uku. Tasbihin tsuntsaye bauta ce irin ta: ☐ galaba (tilas). ☐ da'a.
45. Mushirikai suna bautar Allah ta wata fiskar.
☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
46. Ibadah tana tabbatuwa ne da harshe da gabbai: ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
47. Fadin Allah: {*Kar ku hada shi da komai},* *(QS. An-Niisa : 36),* ta game kowa da komai; Annabi ne, mala'ika ne, waliyyi ne, hakanan duk wani lamari ne cikin lamurran duniya. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
48. Bushara itace: bayar da labarin abin da yake faranta rai, banda abu mai cutarwa . ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
49. Rayin da Allah ya haramta a kashe ta, itace ran: :
☐ musulmi ☐ kadon amana ☐ wanda akayi alkawin zaman lafiya da shi ☐ wanda aka ba shi aminci ☐ gaba daya.
50. Shin Annabi sallallahu alaihi wasallam ya yi wasiyya? ☐ na'am ☐ A'a.
51. Fadin Ibnu Mas'ud radiyallahu anhu: (wasiyyar Annabi); domin ita: ☐ ta kunshi dukkan addini ☐ wasiyyar Allah ce ☐ duka biyun.
52. Hakkin bayi akan Allah: ☐ hakkine na wajibi ☐ haki ne na falala.
53. (Allah da Manzonsa su sukafi sani) ana fadan Haka ne: ☐ lokacin da Annabi sallallahu alaihi wasallam yake raye. ☐ ana iya fada a kowani lokaci.
54.●Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya hana Mu'azu ya yi musu albishir domin: ☐ kar suyi gasa. ☐ kar su sakankance. ☐ duk gaba daya.
● Mu'azu -Allah ya kara yarda a gare shi-, ya ba da labarin a karshen rayursa, don haka ya saba wa Annabi?
☐ na'am ☐ A'a, bai saba ba.
● Haramunne a boye ilimi cikin kowani yanayi: ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
55. Shin wannan hukuncin ya kebanci Mua'z bin Jabal ne? ☐ na'am ☐ A'a.
56. Tabbatar falalar wani abu na nuni kan wannan abun ba wajibi ba ne.
☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
57. Allah ya ce:
وَإِذَا ذُكِرَ اللَّهُ وَحْدَهُ اشْمَأَزَّتْ قُلُوبُ الَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِالْآخِرَةِ وَإِذَا ذُكِرَ الَّذِينَ مِن دُونِهِ إِذَا هُمْ يَسْتَبْشِرُونَ (٤٥)
*[ **Kuma idan aka ambaci Allah Shi kadai, sai zukatan wadanda ba su yi imani da ranan lahira ba, su kyamata, kuma idan aka ambaci waninsa sai suyi farin ciki** ]. (QS. Az-Zumar: 45 ).*
Wannan ayar ta dace sosai da babi na: ☐ biyu ☐ biyar ☐ hudu.
58. Abubuwan da Allah ya jingina su ga zatinsa sun kasha gida: ☐ biyu. ☐ uku.

59. Mafi girman zalunci shine mutum ya zalunci waninsa a ransa ko dukiyarsa ko mutuncinsa. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
60. Makomar wanda ya hadu da Allah alhalin ya mutu akan laifin da ba shirka ba, ☐ Azaba ☐ ya na karkashin ganin damar Allah.
61. *Kalmar (Laa ilaha illallahu)* zikiri ne ba addua ba. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
62. Akwai masu fadan (*laa ilaha illallahu)* Amma ba su da wata kima a wajen Allah. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
63.Ya na warware shaidawa da cewar: Annabi Muhammadu Manzon Allah ne?: ☐ sabon Allah ☐ bid'ah ☐ duk gaba daya.
64. Cewar: "Annabi Isa bawan Allah ne" raddi ne kan Yahudawa, Sa'annan cewar: "Annabi Isa Manzon Allah ne" martani ne kan Nasara. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
65. Fadin Allah: Annabi Isah {*Ruhi ne daga Allah*}, wannan jinginawa ce irin ta: ☐ abubuwa tsayayyu da zatinsu ☐ sifofi.
66. "Allah zai shigar da shi Aljannah": ☐ shigarwa cikakkiya. ☐ shigarwa tawayayyiya ☐ duka biyun.
67. Tace tauhidi shine reraye shi daga: ☐ shirka ☐ bid'ah ☐ sabon Allah ☐ duka biyun.
68. Fadin Allah: *{ **Lallai ne Ibrahim ya kasance shugaba** }:* ma'ana: ☐ abin koyi ☐ imam ☐ mai karantar da alkhairi ☐ duka ukun.
69. Ba'a yin rukyah saboda cutukan fili da na boye, sedai kadai kammun baka, ko saran ma'abocin dafi. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
70. Hadisin لَا يَسْتَرْقُونَ (ba sa neman ayi musu ruqyah), imam Muslim ya kara: وَلَا يُرْقَوْنَ (ba sa yin ruqyah), wannan karin: ☐ ta inganta ☐ bata inganta ba.
71. Babban shirka na halatta jini da dukiya, sedai in kadon amana ne (**Zimmiyyun**), ko wanda akayi alkawarin zaman lafiya da shi (**Mu'ahad**) . ☐ benar ☐ salah.
72. Banbancin mai ruqyah da mai neman ayi masa ruqya: shine: mai neman ayi masa mai roko ne, mai karkata zuwa ga wanin Allah da zuciyarsa, amma shi me yin rukyah, mai kyautatawa ne ga waninsa. ☐ haka ne ☐ kuskure ne.
73. Daidata Allah da waninsa cikin abin da Allah ya kebanta da su shirka ne: ☐ babba ☐ karama.
74. Abinda aka sassake shi bisa wata sura ana kiransa: ☐ Sanam ☐ Wasan ☐ duka biyun.
75. *Manyan dukiyoyi sune:* ☐ mafi tsadansu ☐ na tsakiya ☐ mafi kashi.
76. Bawa na samun kamala ne sakamakon ilimi da aiki da shi, kuma yana kamala waninsa ne ta hanya da'awa da hakuri. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
77. Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya na jin tsoron Dajjal wa al'ummarsa sama da yanda yake ji musu tsoron riya . ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
78. Idan bawa ya zamo mai gaskiya cikin kudirinsa; to dole ya zamo mai kira zuwa ga Allah. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
79. Al-Basirah shine: ☐ ilmmin shari'a ☐ hikimah ☐ sanin yanayin wanda ake kiransa ☐ duka gaba daya.

80. Sharuddan da'awa: ☐ biyar ne. ☐ hudu ne. ☐ uku ne.

81. Banbancin babban shirka da karama:

| Babban shirka | Karamar shirka |
|---|---|
| | |
| | |
| | |
| | |
| | |

Tambaya ta biyar: Sanya daga jerin (A) abin da yadace da shi daga jerin (B)

| No | (A) | (B) |
|---|---|---|
| 1 | Al'hummah | Kankan da kai wa Allah tare da bin umarninsa, da nisantar abinda ya hana; tareda soyayya da girmama shi. |
| 2 | Al-Uluhiyyah | Jajayen rakuma, ya ambancesu, larabawa na son su |
| 3 | Al-Ibadah | Camfi da tsuntsun da ake ganinsa, ko aka ji kukansa, ko wani sananne, a wani waje ko wani zamani. |
| 4 | Ad-Daghut | Makamanci da kwatankwaci da tsara. |
| 5 | Ar-Riya | Wanda aka bauta masa akan surar mutum ko waninsa. |
| 6 | At-Tadayyur | Abin da aka bauta masa ba Allah ba ko yaya yake. |
| 7 | An-Niddu | Duk abin da bawa ya ketare iyaka da shi, na wani abin bi, ko abin bauta ko wanda ake yi masa da'a. |
| 8 | As-Sanam | Ya na ibada domin mutane su ganshi ko suji shi su yabe shi. |
| 9 | At-Tauhid | Kadaita Allah da halitta, da mulki, da jujjuya al'amura. |
| 10 | Al-Ibadah | Kadaita Allah da bauta, ko da aiyukan bayi. |
| 11 | Al-Khawarij | Suna ne da ya hada duk abin da Allah ya ke so kuma ya yarda da shi, na zantuka da aiyuka. |
| 12 | Al-Wasan | Wadanda suke cewa; me aikata babban laifi, kafiri ne, kuma zai dauwama cikin wuta. |
| 13 | Ar-Rububiyyah | Kadaita Allah da rububiyyah, uluhiyya, asma'u wa sifat. |
| 14 | Humrun na’am | Ya fiskanci Allah, ya nisan ci shirka, da sabon Allah. |
| 15 | Hanifan | Cizon duk abu mai guba. |

NA BIYU: TAFSIRIN TAUHIDI BABI TARA

[6] Babin Tafsirin Tauhid (Shahadat an la ilaha iIlallah)

Bayan da magana ta gabata kan tauhidi, zuciya za ta yi kwadayin ta san menene hakikanin wannan tauhidin wanda aka kulla wadannan babuka saboda shi, ( wajabcin tauhidi, falalarsa, tace shi, tsoro daga kishiyarsa, kira zuwa gare shi). Wannan babin: (Tafsirin tauhidi zuwa karshen wannan littafi) amsa ne a kan haka.

DALILI NA FARKO:

Da fadin Allah ta,ala:

(أُوْلَـئِكَ الَّذِينَ يَدْعُونَ يَبْتَغُونَ إِلَى رَبِّهِمُ الْوَسِيلَةَ أَيُّهُمْ أَقْرَبُ ) الآيَةَ.

***Wadancan wadanda suke kiran, suna neman tsani zuwa ga Ubangijinsu, wadanne ne mafifita a kusanta**… (QS. Al-Isra : 57).*

يَدْعُونَ (*suke kira*): wadannan da ake rokon su, su da kansu suna neman kusanci ne zuwa ga Ubanginsu wanene daga cikinsu ya fi kusancin; to ta yaya zaku ringa rokon su alhalin suma mabukata ne zuwa ga wani? (Wannan shine shirkan roko).

DALILI NA BIYU:

Da fadinsa::

(وَإِذْ قَالَ إِبْرَاهِيمُ لِأَبِيهِ وَقَوْمِهِ إِنَّنِي بَرَاء مِّمَّا تَعْبُدُونَ (٢٦) إِلَّا الَّذِي فَطَرَنِي...) الآيَةَ.

***Kuma -katuna- yayinda Ibrahim ya fada wa babansa da mutanensa, lallai ne ni na barranta daga abin da kuke bautawa, face wannan da ya kake ni** …(QS. Az-Zukhruf : 26-27).*

● {***Face wannan da ya halicce ni***}, ya hada tsakanin korewa da tabbatarwa, be ce: (face Allah ba) saboda fa'idodi guda biyu:

1. Bayanin dalilin kadaita Allah da bauta; kamar yanda Allah -Maitsarki ya kadaita da halitta to ya wajaba a kadaita shi da bauta.

2. Saboda bayanin bacin bautar gumaka; domin ba su ne suka kage ku ba, ballantana ku bautata musu.

● Tauhidi ba ya tabbatuwa ta hanyar hada bautar Allah da waninsa, wajibi ne a tace tauhidi ga Allah shi kadai.

A wasu kasashen musulmai, zaka samu wadan su suna yin sallah, kuma suna fitar da zakkah, suna azumi da zuwa aikin hajji tareda haka, sunayin sujada wa kaburbura.

**DALILI NA UKU:**

Da fadinsa:

(اتَّخَذُواْ أَحْبَارَهُمْ وَرُهْبَانَهُمْ أَرْبَاباً مِّن دُونِ اللّهِ ) الآيَةَ.

***[ Sun riki malamansu -Yahudu- da masu bautansu -Nasara- iyayengiji koma bayan Allah ].*** *(QS. At-Taubah: 31).*

**DALILI NA HUDU:**

Da fadinsa:

(وَمِنَ النَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ اللّهِ أَندَاداً يُحِبُّونَهُمْ كَحُبِّ اللّهِ) الآيَةَ.

***[ Kuma akwai daga mutane wanda yake rikan kishiyoyi koma bayan Allah, suna son su kamar son Allah.].*** *(QS. Al-Baqarah : 165).*

- أَحْبَارَهُمْ: **Ahbarahum:**, ana ce wa mutum: (bahrun) saboda yawan iliminsa.
- وَرُهْبَانَهُمْ: **Ruhbanahum:** masu bauta cikinsu.
- أَرْبَاباً: **Arbaban:** (ababen bauta), sunyi da'a ga maluma cikin sabon Allah, kuma sun bauta wa ruhban daga cikinsu (wannan shirka ce irin ta da'a).
- {***Suna son su kamar son Allah***}: ma'ana: su na son kishiyoyin da suka sanya wa Allah irin son da sukeyi wa Allah ta'ala.

### Rabe Raben Soyayya

**Soyayya tareda Allah:** (Babbar shirka ce). Wannan ta na kore hakikanin son Allah. Kamar a so wanin Allah daidai da son Allah ko sama da son Allah.

**Soyayya domin Allah:** (Wajibi ne). (( **mafi amincin igiyar imani shine kauna domin Allah**..)) [hadis].

**Soyayya irin na dabi'a:** (Halal ne). da sharadin kar ya gabatar da ita akan son Allah. Kamar son daa, da mata.

So don Allah yana iya zamowa cikin; aiki, da me aikin, da wasu zamunna, ko wajaje..

**DALILI NA BIYAR:**

وَفِي الصَّحِيحِ عَنِ النَّبِيِّ □ أَنَّهُ قَالَ: «**مَنْ قَالَ: لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ** <u>**وَكَفَرَ بِمَا يُعْبَدُ مِنْ دُونِ اللهِ**</u> **حَرُمَ مَالُهُ وَدَمُهُ، وَحِسَابُهُ عَلَى اللهِ** ٥». وَشَرْحُ هٰذِهِ التَّرْجَمَةِ: مَا بَعْدَهَا مِنَ الأَبْوَابِ.

Ya zo cikin Sahihul Bukhari daga Annabi sallallahu alaihi wasallam ya ce: " Duk wanda ya ce: laa ilaha illallahu, sa'annan ya kafirce wa abinda ake bautawa wanda ba Allah ba, to, dukiyarsa da jininsa sun haramta, hisabinsa yana ga Allah maigirma da buwaya ". shar wannan tarjamar yana: babukan da za su zo a gaba.

" Kuma ya kafirce wa abin bautawa da ba Allah": wajibi ne ka kafirce wa bautar wani wanda ake bauta masa ba Allah ba, ka kafirce wa dukkan kafirci, hakanan duk wanda ya tabbatar da kalmar shahada, amma tare da haka yana ganin cewa addinin Yahudu da Nasara suke kai a yau gaskiya n
e, to lallai ne wannan ba musulmi ba ne, haka kuma duk wanda yake ganin cewa addinai tunani ne na muta ne kowa ya zabi wanda yaso, to wannan ba musulmi ba

***MATSALOLIN BABIN:***

Mafi girma da muhimmanci matsalolin babin sune; tafsirin tauhidi, tafsirin kalma

r shahada, kuma yayi bayani karara cewa: (babu makawa daga korewa da tabbatarwa) :

- Ayar suratul isra'i, ya bayyana raddin da ta kunsa a kan mushrikan da suke rokon salihan bayi, cikinta akwai dalilin cewar hakan shirka ce babba. (shirkan roko).
- Ayar surat At-Taubah: a ciki ya bayyana cewa lallai (Yahudu da Nasara) sun riki malamansu da masu bautansu a matsayin ababen bauta koma ba Allah ba, kuma ya bayyana cewa ba su umurce su da komai ba face su bauta wa Allah shi kadai, tareda cewar tafsirin ayar a sauwake shine: yin da'a ga malamai da masu bautansu cikin sabon allah, koda kuwa ba'a roke su ba to lallai: (shirka ce irin ta da'a )
- Fadin Annabi Ibrahim ga kafirai: **" lallai ne ni na barranta daga abin da kuke bautawa' face wanda ya kage ni "**, se ya togace ubangijinsa daga cikin ababen bautan, Allah maitsarki ya ambaci wannan barrantar da soyayyar sune: tafsirin Kalmar shahada, [laa ilaha illallah] Allah ya ce:

وَجَعَلَهَا كَلِمَةً بَاقِيَةً فِي عَقِبِهِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ (٢٨)

***" Kuma ya sanyata kalma wanzazziya a cikin zuriyarsa ko za su koma -daga batansu zuwa ga Allah- "*** *. (QS. Az-Zukhruf : 28).*

- Ayar suratul Baqarah kan kafirai wadanda Allah ya fada game da su

وَمَا هُم بِخَارِجِينَ مِنَ النَّارِ

***" Kuma ba su zama masu fita daga wuta ba ".*** *(QS. Al-Baqarah : 167).*

Ya ambaci cewa su suna son ababen bautarsu kamar yanda suke son Allah; wannan yana nuni kan cewa suna son Allah so mai yawa, amma hakan bai shigar da su cikin musulunci ba, to kuma yaya lamarin wanda ya so wani abin bauta sama da yanda yake son Allah? Sa'annan yaya lamarin wanda abin bautan kadai yaso ba Allah ba?
( Shirkar soyayya, ta kasu kashi hudu:

1. Yana son Allah sama da yanda yake son waninsa, wannan shine hakikanin tauhidi.
2. Yana son wanin Allah kamar yanda yakeson Allah, to wannan shirka ce.
3. Yana son wanin Allah sama da yanda yake son Allah, wannan yafi muni samada wanda ya gabata.
4. Ya so wanin Allah kadai, babu wani abu cikin zuciyarsa na son Allah ta'ala, wannan shine mafi munin kaso kuma mafi zamowa masifa.

- Daga ciki akwai fadin Annabi sallallahu alaihi wasallam:

**مَنْ قَالَ: لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ <u>وَكَفَرَ بِمَا يُعْبَدُ مِنْ دُونِ اللهِ</u> حَرُمَ مَالُهُ وَدَمُهُ، وَحِسَابُهُ عَلَى اللهِ**

"Duk wanda yace: laa ilaha illallahu, sa'annan ya kafirce wa abin da ake bautawa wanda ba Allah ba, to dukiyarsa da jininsa sun haramta, kuma hisabinsa yana ga Allah" wannan yana daga manyan abubuwan da suke bayyana ma'anar " laa ilaha illallahu", domin shi bai sanya yin furuci da ita kadai ba wajen tsare jini da d ukiya, ko sanin ma'anarta da lafazinta kadai, kuma bai sanya ikirari da ita kadai ba, ko kasancewarsa ba ya bautan kowa sai Allah shi kadai ba shi da abokin tarayya, A'a, dukiyarsa da jininsa bazasu haramta ba har sai ya kara a kan hakan, kafircewa wa abin da ake bauta masa wanda ba Allah ba, to idan har yayi kokonto ko yaki, to dukiyarsa da jininsa ba su haramta ba.

Menene mafi girman wannan matsalar! Kuma menene mafi bayyanar wannan magana! da hujjah wanda takai makura wajen yanke duk wani mai jayayya.

## [7] BABIN ( YANA DAGA SHIRKA: SANYA ZOBE KO ZARE DA MAKAMANTANSU DOMIN DAGE BALA'I KO TUNKUDE SHI )

- **(( Ya na daga shirka)):** ma'ana: sashe ne na shirka, daga cikinsa akwai babba kuma akwai karami, don haka ya saki zancen bai kaiyade shi ba.
- **(( Dauke bala'i )):** bayan saukansa.
- **(( Ko tunkude shi )):** kafin saukansa.

**Shin sanya kambu da zare da makamantansu, karamar shika ce ko babba?**

**Babbar shirka:**
Idan ya kudurta cewa wannan abin da ya rataya yana tasiri da kansa, kuma yana iya janyo wani amfani ko tunkude wata cuta.

**Karamar shirka:**
Idan ya kudurce cewa wannan abin da ya rayata din sababi ne, alhali Allah bai sanya shi sababi ba, a al'adance, ko a shari'ance.

Kashe kashen mutane (kudirinsu kan sabubba):

**Ya inganta:**
Wanda ya yarda da abin da allah ya sanya shi sababi kuma ya sanya shi sababi. Sabubba iri biyu ne: sabubba a al'adace; (Kaman magani), ko a shari'ance (kamar ruqyah).

**Karamar shirka:**
Wanda ya riki sababi daga abin da Allah bai sanya shi sababi ba, kamar rataya kayin saniya domin tunkude kammun baka, wannan ba sababi ba ne ingantacce.

**Babbar shirka:**
Wanda ya sanya wani sababi kuma yayi imani da cewa wannan sababin yanada tasiri da kansa wajen kawo amfani ko tunkude cuta.

**Mutane sun kasu bangare biyu da na tsakiya gameda halaccin riko da sabubba**

**Bai yarda da sabubba ba:**
wanda ya kore hikimar Allah, kamar yan kungiyar: Jabriyyah da Asha'irah.

**Ya zurfafa wajen riko da sabubba:**
Wanda ya sanya abin da ba sababiba sababi, kamar wasu daga sufaye.

**Tsaka tsakiya:**
Ya tabbatar da sabubba, a al'adance, kuma a shari'ance kadai.

**Hukuncin wanda ya rataya zare da makamancinsa, sun kasu kamar haka:**

| | |
|---|---|
| Wanda ya jahilci hukuncin ratayawar. | Wannan sai a ilimantar da shi. |
| Ya yi imani cewaratayawar sababi ne, alhali Allah Ta'ala bai sanya su sababi | karamar shirka ce. |
| Ya yi imani cewa sabubba sunada tasiri da kansu, kuma suna iya janyo amfani ko tunkude cuta. | Babbar shirka ce. |
| Ba shi da wani kudiri kan ratayawar, ya na sanyawa ne kadai saboda ado, kamar yanda wasu samari ke yi, -Allah ya shiyar da mu da su- duk wanda ya ga irin wannan zai zaci cewar hakan ya halatta, sai ya zamanto ya bude wa mutane kofar sharri da hakan, kuma cikin hakan akwai koyi da mata da kuma mushrikai. | Babban laifi ne. |

**DALILI NA FARKO:**

قُلْ أَفَرَأَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن دُونِ اللَّهِ إِنْ أَرَادَنِيَ اللَّهُ بِضُرٍّ هَلْ هُنَّ كَاشِفَاتُ ضُرِّهِ

***[ Ka ce: ku bani labarin abin da kuke kira wadanda ba Allah ba, idan Allah Ya nufe ni da wata cuta shin su zasu iya yaye cutarSa ].*** *(QS. Az-Zumar : 38).*

- Wadannan gumakan ba sa iya taimakon ma su bautan su da janyo wani amfani ko tunkude wata cutarwa, kuma su ba sabubba ba ne kan hakan, ana kiyasi kan haka ga duk wani abun da ba sababi bane a shari'ance ko a al'adance; don haka sanya shi sababi shirka ne da Allah madaukaki.
- [ **Kace Mai isata Allah ne** ]: *(QS. Az-Zumar : 38).*

Cikin wannan ayar akwai mayarda lamarin isarwa zuwaga Allah ba zuwaga wasu sabubba na dimuwa ba.

**DALILI NA BIYU:**

عَنْ عِمْرَانَ بْنِ حُصَيْنٍ؛ أَنَّ النَّبِيَّ ﷺ رأى رَجُلًا فِي يَدِهِ حَلْقَةٌ مِنْ صُفْرٍ، فَقَالَ: «مَا هٰذِهِ؟»، قَالَ: مِنَ الْوَاهِنَةِ، فَقَالَ: «انْزِعْهَا؛ فَإِنَّهَا لَا تَزِيدُكَ إِلَّا وَهْنًا، فَإِنَّكَ لَوْ مُتَّ وَهِيَ عَلَيْكَ مَا أَفْلَحْتَ أَبَدًا». رَوَاهُ أَحْمَدُ بِسَنَدٍ لَا بَأْسَ بِهِ.

Daga Imran dan Husain, Manzon Allah sallalahu alaihi wasallam ya ga wani mutum ya sanya zobe na tagulla a hannunsa, sai ya ce: " menene wannan? " sai yace: na sanya ne don kariya daga cutar (wahina), sai ya ce: " cire shi, domin ba abin da zai kara maka sai rauni, lallai ne za ka mutu wannan zoben yana hanunka to har abada ba zaka rabauta ba". (Imam Ahmad ne ya rawaito shi da isnadi ba laifi).

- "Zobe na tagulla" azurfa da makamantansa, ko da bakin karfe ne ko zare ya shiga.
- "menene wannan?": Samun tabbaci kafin inkari, don kar ya gina hukunci akan zato.
- "Al-wahinah": cuta ce a cikin kashin hanu kamar **(Rheumatism),** ya sanya kambin ne domin ya tsare shi daga wannan cutar.
- "Ba abin da zai kara maka sai rauni": ma'ana: rauni a jika da kudiri, sakamako yana kasancewa ne gwargwadon aiki.

**DALILI NA UKU:**

وَلَهُ عَنْ عُقْبَةَ بْنِ عَامِرٍ مَرْفُوعًا: «مَنْ تَعَلَّقَ تَمِيمَةً فَلَا أَتَمَّ اللهُ لَهُ، وَمَنْ تَعَلَّقَ وَدَعَةً فَلَا وَدَعَ اللهُ لَهُ».

وَفِي رِوَايَةٍ: «مَنْ تَعَلَّقَ تَمِيمَةً فَقَدْ أَشْرَكَ».

Daga Imam Ahmad, daga Uqbatu dan Amir, ya daga hadisin zuwaga Annabi sallallahu alaihi wasallam: " duk wanda ya rataya da wata laaya, to kar Allah Ya cika masa burinsa, kuma dukkan wanda ya rataya wuri, to kar Allah ya kwantar masa da hankalinsa". yazo cikin wata riwayar: "duk wanda ya rataya zuciyarsa da wata laaya to hakika yayi shirka".

- " duk wanda ya rataya da wata laaya": ya rataya ya rataya zuciyarsa da ita, don haka yace: (ya rataya da ita), bai ce: ya rataya ba.
- " Kar Allah ya cika masa burinsa ": wannan jumlar ko dai ta zamo addu'a ce a kan wanda ya rataya laaya, ko kuma labari ne tsantsa.
- " Duk wanda ya rataya wuri ": wani abu ne da ake cirowa daga kogi, kamar kwasfa.
- " Kar Allah ya kwantar masa da hankalinsa": kar Allah bar shi cikin natsuwa.
- "Hakika ya yi shirka" shirka ce babba in har ya kudirce cewa wannan laayar tanada tasiri da kanta ba tare da izinin Allah ba, idan bai kudirce hakan ba to ta zamo karamar shirka.

**DALILI NA HUDU:**

وَلابْنِ أَبِي حَاتِمٍ عَنْ حُذَيْفَةَ؛ أَنَّهُ رَأَى رَجُلًا فِي يَدِهِ خَيْطٌ مِنَ الْحُمَّى، فَقَطَعَهُ، وَتَلَا قَوْلَهُ: وَمَا يُؤْمِنُ أَكْثَرُهُمْ بِاللهِ إِلاَّ وَهُم مُّشْرِكُونَ

A riwayar Ibnu Abi Hatim daga Huzaifa; cewa shi yaga wani mutum ya sanya wani zare a hannunsa saboda mashashshara, sai ya tsinke shi, sa'annan ya karanta fadin Allah: [ Da yawa daga cikin mutane ba su yin imani da Allah face sai sun kasance masu tara Allah da wani] . *(QS. Yusuf, 106).*

● *Alhumma* (mashashshara): ya rataya shi ne domin ya samu sanyin jiki ko waraka daga wannan cutar.
● "Sai ya yanke shi": Domin kawar da munkari da hannunsa, wannan yana nuni akan karfin magabata wajen kawar da munkari.
● **Hukuncin ratayawar** : haramun ne duka; rataya zobe ne, ko zare ko ko wuri ko laayu ko idanuwan kerkece, ko kofaton dabba, ko tsohon takalmi, ko dan kwallo kore, ko tafi, ko tafin hannu, ko kan bijimi, ko mutum mutumin zaki, ko wani bangare na bishiya, ko tsummokara, da makamantansu.

***MATSALOLIN BABIN:***

1. Kausasawa kan sanya zobe da zare da makamantansu.
2. Da wannan sahabin ya mutu da wannan kambun a hanunsa ba zai rabauta ba, a ciki akwai dalili kan maganan sahabbai cewa karamar shirka tafi girman laifi sama da Al-kaba'ir (manyan laifukan da ba su kai shirka ba), (saboda ba'a gafarta shirka, koda karama ce; sabanin Al-kaba'ir ).
3. Kuma ba a yi masa uzuri da jahilci ba. ( Bayan manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya baiyana masa hukuncin hakan, jahilci iri biyu ne:
[1] Jahilcin da ba a uzuri a kansa, shine jahilcin da samu sakamakon sakaci da kawar da kai wajen neman ilimin shari'a tareda saukakar hanyoyin samun ilimin, to wannan ba uzuri a kansa; cikin aikin kafirci ko zunubbai. .
[2] Jahilcin da ake yin uzuri a kansa; shine sabanin abin da ya gabata, wanda baiyi sakaci ko kawar da kai ba, kuma hanyar samun ilimin ba ta sauwaka ba gareshi, kuma bai taba tunanin cewar wannan abun haramunne ba, to wannan yanada hanzari, idan musulmi ne to wannan ba zai cutar da shi ba, idan kuma yana nasabtuwa zuwaga kafirci ne, to wannan kafiri ne cikin hukuncin duniya, amma a lahira kuma, to hukuncinsa yana wajen Allah).

4. Wadannan abin ratayawar ba sa amfanar da komai a duniya sai cutarwa saboda fadin Annabi shallallahu'alaihi wasallam: " ba za ta kara maka komai ba face rauni ".

5. Yin inkari tareda kausasawa a kan wanda ya aikata irin wannan aikin.

6. Bayani karara cewa duk wanda ya rataya da laya, zai dogara da ita.

7. Bayani karara cewa duk wanda ya rataya da laya to yayi shirka.

8. Rataya zare saboda mashash,shara shima hukuncinsa kenan.

9. Ayar da Huzaifah ya karanta dalili ne cewar sahabbai suna kafa hujjah kan karamar shirka da ayoyin da suka sauka akan babbar shirka kamar yanda Abdullahi dan Abbas ya ambata gameda ayar surat Al Baqarah. (gameda soyya).

10. Rataya wuri saboda kammun baka, ya shiga ciki. (yana daga layoyi na shirka).

11. Yin mummunar addu'a kan wanda ya rataya laya kar Allah ya cika masa burinsa, da kuma wanda ya rataya wuri shima kar Allah ya bar shi cikin sukuni (ba zamu fadi hakan karara ga wanda muka ganshi ya saka laya, -ba za muce masa kar Allah ya cika maka burinka ba-, domin hakan zai iya fusata shi kuma ya sa guje wa gaskiya, sedai abin da yakamata muce masa shine: rataya laya da wuri ba su bai halatta, kuma sai mu karanta masa hadisai kan hakan).

## [8] BABIN ABIN DA YAZO KAN TOFI DA LAYU

Meyasa mawallafin yace: (babin abin da yazo)? Bai ce: (yana daga shika; yin Tofi ) kamar yanda ya fada a babin da ya gabata?

1. Saboda ruqyah ta kasu kasha biyu; (wanda aka shar'anta da wanda aka haramta).
2. Dukkan laya shirka ne, se layar da ta kasance da alkur'ani to wannan haramun ne.

**DALILI NA FARKO:**

فِي الصَّحِيحِ عَنْ أَبِي بَشِيرٍ الأَنْصَارِيِّ؛ أَنَّهُ كَانَ مَعَ النَّبِيِّ ﷺ فِي بَعْضِ أَسْفَارِهِ، فَأَرْسَلَ رَسُولًا: «أَنْ لَا يَبْقَيَنَّ فِي رَقَبَةِ بَعِيرٍ قِلَادَةٌ مِنْ وَتَرٍ - أَوْ: قِلَادَةٌ - إِلَّا قُطِعَتْ».

Ya zo cikin Sahihul Bukhari daga Abu Bashir Al-ansari; ya kasance tareda Annabi sallallahu alaihi wasallam cikin wani sashe na tafiye tafiyensa, sai manzon Allah ya aiki wani dan aike da cewa: " lallai ne kar a bar wata igiya na kittani, ko yace: - kowace irin igiya- a wuyar wani rakumi face sai an yanke shi ".

- "Sai ya aika": ya tura dan aika domin bibiyar halayesu gwargwadon shari'a.
- Igiya da ake ratayawa a wuyar dabba: suna imani da cewa hakan yana ba da kariya daga kammun baka.

**DALILI NA BIYU:**

وَعَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ ﵁ قَالَ: سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُولُ: «إِنَّ الرُّقَى وَالتَّمَائِمَ وَالتِّوَلَةَ شِرْكٌ». رَوَاهُ أَحْمَدُ وَأَبُو دَاوُدَ

Daga dan Mas'ud Allah ya kara yarda a gare shi yace: naji Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam yana cewa: "Lallai ne, tofi da layu da tiwala (Wuri-Mallakau) shirka ne " [Ahmad da Abu Dawud ne suka rawaito].

**DALILI NA UKU:**

وَعَنْ عَبْدِ اللهِ بْنِ عُكَيْمٍ مَرْفُوعًا: «مَنْ تَعَلَّقَ شَيْئًا وُكِلَ إِلَيْهِ». رَوَاهُ أَحْمَدُ وَالتِّرْمِذِيُّ.

Daga Abdullahi dan Ukaim ya daga hadisin zuwaga Annabi sallallahu alaihi wasallam: " duk wanda ya ratawa wani abu to za' a jingina shi zuwaga wannan abun' [ Ahmad da Tirmizi ne suka rawaito)

● “Lallai ne ruqyah” : ma'ana ruqyah sananniya a wajen larabawa ta shirka, wanda shari'a ba ta tabbatar da ita ba.

● “Duk wanda ya rataya da wani abu za a jingina shi zuwaga wannan abun”: bai ce: (duk wanda ya rataya ba kadai ), saboda bayan ya rataya kuma sai ya rataya zuciyarsa ga wannan abun, duk wanda ya rataya zuciyarsa da Allah to lallai ne Allah Ya isar masa, amma duk wanda ya rataya zuciyarsa da wanin Allah to hakika ya tabe.

● Bai kamata ba mutum ya rataya zuciyarsa da wani sababi, abin da ya wajaba a kansa shine ya rataya zuciyarsa da Allah, maaikacin da ya rataya zuciyarsa gaba da albashinsa, tareda mancewa da cewa Allah shine wanda ya kaddara masa samun wannan albashin, to hakika ya auka cikin shirka, amma idan ya yi da cewa wannan albashin nasa wani sababi ne wanda Allah Ya kaddara masa samunsa to wannan ba ya kore tawakkali.

**Sharuddan ruqyah a shari'a:**

- Dole ta zamo daga alkur'ani ko Sunnah, ko addua da sunayen Allah ko sifofinsa.
- Dole ta zamo da maganar da ake fahimta, ake ji, kuma aka san abin da ta kunsa a yare.
- A yi imani da cewa ruqyar sababi ne a shari'ance ba ta amfani face da izinin Allah.

Idan aka rasa daya cikin wadannan sharuddan, to ta zamo ba ruqyah ta shari'a ba ce, ruqyah anayin ta ne cikin harshen larabci sedai idan idan addua ce to babu laifi ayi ta da kowani irin yare da sharadin kada a canza sunayen Allah, saboda su ana fadan su ne gwargwadon yanda sukazo cikin dalilai (ana iya hikayar sunayen Allah kamar yanda suke cikin kowani yare).

**TAMIMAH: Laya;** wani abu ne da ake rataya shi ma kananan yara don kariya daga kammun baka; amma idan abin da ratayar daga alkur'ani ne, wasu daga cikin magabata sunyi sassauci, wasu kuma ba su yi ba, sun saka shi cikin wanda aka hana, daga cikin su akwai Abdullahi ibn Mas'ud. Allah ya kara yarda a gare shi.

**RUQYAH: (AZA'IM)**; ma'ana: yin tofi ko addu'a, wannan dalili ya tabbatar da shi, sedai idan ya zamo akwai shirka ciki to wannan haramun ne, Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam yayi sassaucin ruqyah domin kammun baka ko cizon abu mai dafi.

**TIWALAH: Wuri;** wani abu ne da mutane suke yinsa, suna riya cewar yana sa miji yaso matarsa, kuma mata taso mijinta.

## ZOBEN DABLA YANA SHIGA CIKIN HUKUNCIN TIWALAH

| Babbar shirka | Karamar shirka | Haram |
| --- | --- | --- |
| Idan mutum yayi imani cewa wannan abun yana tasiri da kansa, yana iya kawo amfani, ko tunkude cuta. | Idan yayi imani cewa wannan abun sababi ne na wanzuwar alakar auratayya tsakanin ma'aurata. | Wannan shine mafi sauki daga kaso ukun, kuma al'ada ce irin ta Nasara, domin suna tabbatar da aqidar ukuntawa sakamakon saka wannan zoben, sa'annan Karin haramcinsa ta fiskan maza idan ya zamo daga zinare. |

**DALILI NA HUDU:**

وَرَوَى الإِمَامُ أَحْمَدُ عَنْ رُوَيْفِعٍ قَالَ: قَالَ لِي رَسُولُ اللهِ ﷺ: «**يَا رُوَيْفِعُ، لَعَلَّ الْحَيَاةَ سَتَطُولُ بِكَ، فَأَخْبِرِ النَّاسَ أَنَّ مَنْ عَقَدَ لِحْيَتَهُ، أَوْ تَقَلَّدَ وَتَرًا، أَوِ اسْتَنْجَى بِرَجِيعِ دَابَّةٍ أَوْ عَظْمٍ، فَإِنَّ مُحَمَّدًا ﷺ بَرِيءٌ مِنْهُ**».

Imam Ahmad ya rawaito daga Ruwaifiu yace: Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya ce da ni: "ya Ruwaifiu, kila rayuwa zatayi tsawo dakai, to ka sanar da mutane cewa; duk wanda ya kitsa gemunsa, ko ya rataya tsirgiya ko ko yayi tsarki da kashin dabba, ko kasha, to lallai Muhammada sallallahu alaihi wasallam ya barranta daga gare shi".

- "Lallai ne duk wanda ya kitsa gemunsa": ko dai saboda girman kai, ko kuma ya sanya ne domin kariya daga kammun baka.
- "Ya rataya tsirgiya" ( zare ne akeyi da jijiyar akuya, suna saka shi domin kariya daga kammun baka).
- "Ko yayi tsarki da kasin dabba" gusarda alamar abinda ke fita daga kafofi biyu.
- "Ko kashi" domin shi abincin aljanu ne, kashin dabbobin bani Adama abincici ne ga dabbobin aljanu.

**DALILI NA BIYAR:**

وَعَنْ سَعِيدِ بْنِ جُبَيْرٍ قَالَ: «مَنْ قَطَعَ تَمِيمَةً مِنْ إِنْسَانٍ كَانَ كَعَدْلِ رَقَبَةٍ». رَوَاهُ وَكِيعٌ.

Daga Said dan Jubair ya ce: "duk wanda ya tsinke laya daga wani mutum Kaman ya yanta baiwa ce." ( Imam Waki'u ne ya rawaito)

**DALILI NA SHIDA:**

وَلَهُ عَنْ إِبْرَاهِيمَ: «كَانُوا يَكْرَهُونَ التَّمَائِمَ كُلَّهَا؛ مِنَ الْقُرْآنِ وَغَيْرِ الْقُرْآنِ».

Daga Ibrahim ya ce: " -Almajiran Abdullahi dan Mas'ud- sun kasance suna kin dukkan layu, na Alqur'ani ko waninsa ".

● "Kamar ya yanta baiwa": saboda ya yanta shi ne daga bautar shaidan wanda ta ginu a kan shirka, kuma wannan shine mafi muhimmanci samada yanta shi daga bautar wani mutum, sedai tsinkewar tazamo ta hanya mafi kyawu (hanyar da ta dace).

**ME YASA AKA KI LAYU NA ALQUR'ANI?**

| | | | |
|---|---|---|---|
| Saboda wasu daga magabata sun karhanta, kuma magabata suna amfani da Kalmar makaruhi a matsayin haramun. | Saboda shigansu karkashin fadin Annabi sallallahu alaihi wasallam: *"lallai Ruqyah, da laya da wuri shirka ne."* | Saboda kar mu bude kofa na sharri, saboda wasu zasu zaci cewa dukkan layu sun halatta har wadanda ba na Alqur'ani ba. | Saboda akwai wulakanta Alqur'ani, wanda ya rataya layar zai iya shiga bandaki da ita, ko najasa ta same shi tana jikinsa. |

***MATSALOLIN BABIN:***

**1.** Bayanin ma'anar ruqah (tofi, ko Addu'a), da ma'anar tama'im (layu).

2. Bayanin ma'anar tiwala (abin da akeyi na sihiri don mallakar mace ko miji)

3. Wadannan abubuwa ukun dukkansu shirka ne ba tare da togacewa ba.

4. Yin addu'a ko tofi da Magana ta gaskiya saboda kammun baka da cizon abu mai dafi ba ya shiga hukuncin shirka. ( halaccin yin tofin ya kunshi waninsu kamar warware sihiri).

5. Laya idan ta zamo daga alkur'ani ne, to malamai sunyi sabani; shin za ta shiga cikin wannan hukuncin ko ba za ta shiga ba? ( mazhabin Ibn Mas'ud: haramcin laya ko da na Alqur'ani ne, wannan yafi zamowa daidai, saboda ba'a shar'anta ba tun asali ).

6. Rataya kittanai a wuyar dabbobi saboda kariya daga kammun baka ya shiga (shirka).

7. Narko mai tsanani kan duk wanda ya rataya tsirgagiya.

8 Sakamako mai gwabi ga duk wanda ya tsinke laya daga wuyar wani.

9. Lallai ne maganar Ibrahim bai saba wa abin da ya gabata ba na sabani; saboda abin da yake nufi: almajiran Abdullah dan Mas'ud. (baya nufin dukkan sahabbai -Allah ya kara yarda a gare su-, kuma baya nufin ta'biai gaba daya ).

## [9] BABIN WANDA YAYI TABARRUKI DA BISHIYA KO DUTSI DA MAKAMANTANSU

**At-Tabarruk:** Neman albarka, ciki akwai:

**Tabarrukin da aka shar'anta**

- Da izinin Shari'a: kamar yin salloli a masallacin Harami (Kaaba), da karatun Alqur'ani maigirma.
- Dalili na zahiri (Hissi): Misalinsa: neman albarka ta hanyar karanta litattafan Shaikhul Islam ibnu Taimiyyah.

**Tabarrukin da aka haramta:** Iyakarsa itace: neman albarka da wani abin da Shari'a baiyi umurni ba kuma dalili na zahiri ba ya goyon baya, Misalinsa: neman albarka ta hanyar shafa garun gidan Annabi sallallahu alaihi wasallam.

### DALILI NA FARKO

Da fadin Allah Ta'ala:

أَفَرَأَيْتُمُ اللَّاتَ وَالْعُزَّى (١٩) وَمَنَاةَ الثَّالِثَةَ الْأُخْرَى (٢٠)

*Ku ba ni labarin Lata da Uzza, da Manata ta ukun dayan (QS. AN-Najm : 19-20).*

### DALILI NA BIYU:

عَنْ أَبِي وَاقِدٍ اللَّيْثِيِّ قَالَ: خَرَجْنَا مَعَ رَسُولِ اللهِ ﷺ إِلَى حُنَيْنٍ، وَنَحْنُ حُدَثَاءُ عَهْدٍ بِكُفْرٍ، وَلِلْمُشْرِكِينَ سِدْرَةٌ يَعْكُفُونَ عِنْدَهَا، وَيَنُوطُونَ بِهَا أَسْلِحَتَهُمْ، يُقَالُ لَهَا: (ذَاتُ أَنْوَاطٍ)، فَمَرَرْنَا بِسِدْرَةٍ، فَقُلْنَا: يَا رَسُولَ اللهِ؛ اجْعَلْ لَنَا ذَاتَ أَنْوَاطٍ كَمَا لَهُمْ ذَاتُ أَنْوَاطٍ، فَقَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «اللهُ أَكْبَرُ، إِنَّهَا السُّنَنُ، **قُلْتُمْ وَالَّذِي نَفْسِي بِيَدِهِ كَمَا قَالَتْ بَنُو إِسْرَائِيلَ لِمُوسَى: (اجْعَلْ لَنَا إِلَهاً كَمَا لَهُمْ آلِهَةٌ قَالَ إِنَّكُمْ قَوْمٌ تَجْهَلُونَ)، لَتَرْكَبُنَّ سُنَنَ مَنْ كَانَ قَبْلَكُمْ**». رَوَاهُ التِّرْمِذِيُّ وَصَحَّحَه.

Daga Abu Waqid Al-Laitsi yace: mun fita zuwa yakin Hunain tareda Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam, a lokacin ba mu dade da shiga musulunci ba, kuma mushrikai sunada wata bishiyan magarya wacce suke tarewa a wajenta, suke lizimtar ta kuma suke rataya makamansu a jikinta, ana kiranta da suna: Zatu anwa'd (wacce ake rataye makamai a jikinta domin neman albarkanta da nasara ), se muka wuce wata bishiyar magarya, sai mukace: ya Manzon Allah; kasanya mana maimarataya kamar yanda mushrikai sukeda maimarataya, se Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya ce:

" Allahu Akbar!, lallai ne, hanyoyi ne da suka gabata –masu muni irin ta kafiran farko wacce na baya ke koyi da su-, na rantse da wanda rayuwata ke hannunsa kun fadi kwatankwacin abin da banu isra'ila suka fada wa Musa" **[ ka sanya mana wani abin bautawa kamar yanda sukeda ababen bautawa, sai yace lallai ne ku mutane ne wadanda ba ku da sani ],** da sannu zaku bibiyi hanyoyin wadanda suka gabace ku " [Tirmizi ne ya rawaito kuma ya inganta shi ].

- أَفَرَأَيْتُمُ اللَّاتَ وَالْعُزَّى: Ku bani labari menene matsayin wadannan gumakan da kuke girmama su? menene halinsu gameda wadannan manyan ayoyin kamar Mi'iraji? domin su suna kudirin cewar wadannan gumakan suna iya amfanar da su ko cutar da su, don haka ma suke zuwa wajensu, suke rokon su, suke yanka don su, kuma suke neman kusanci zuwa gare su.
- اللَّاتَ: (Allaata): [1] Ana karantawa da shadda akan taa: اللَّاتّ, (Allatta) wani mutumin kirki ne da yake kwaba soyayyen gari ya na shayar da Alhazai. [2] kuma ana karantawa da fataha ba tareda shadda ba اللَّاتَ, (Allata), sun ciro shine daga sunan: Allahu, suka rada ma gunkin Laata.
- وَالْعُزَّى: (Al-Uzzah): an cirato ne daga sunan Allah Al-Aziz.
- وَمَنَاةَ: (Al-Manata): an cirato ne daga [1] sunan Allah Al-Mannan. [2] an ciro ne daga Minah, saboda yawan zubar da jini da ake a wajensa (Gunkin Manata), shine sababin kiran Mina da wannan sunan.
- " حدثاء" Hudasa'u : sabbabin shiga musulunci, ya ambaci hakan domin nuna uzurinsu kan abin da suka tambaya.
- "ينوطون" suna ratayar makamansu a jikinta don neman albarka.
- "ذات أنواط ": maimarataya, saboda ana ratayar makamai ajikinta don neman albarka.
- "Ka sanya mana maimarataya kamar yanda suke da maimarataya ": sunsan cewar ibada ba gaban kai ake cikinta ba (ba a yin ta sai sharia ta bada dama) don haka suka nemi izini wajen Annabi sallallahu alaihi wasallam, sai ya nuna musa girman hadarin abin da suka nema, da hakan suka kauce wa aukawa cikin shirka.
- لَتَرْكَبُنَّ : lallai ne da sannu zaku aikata misalin aikinsu, kuma lallai ne zaku fadi kwatankwacin abin da suka fada, akwai labartawa tare da tsoratarswa cikin hakan.

***MATSALOLIN BABIN:***

1. Fassarar ayar surat An-Najm: [ ***Ku ba ni labarin Lata da Uzza, da Manata ta ukun dayan***] *(QS. An-Najm : 19-20).*

2. Sanin surar abin da suka nema. ( don fusata kafirai, ba don su bauta ma bishiyar ba).

3. Kasancewar basu aikata hakan ba.

4. Kasancewa sun nufaci neman kusanci zuwaga Allah ta hanyar wannan aikin, tsammaninsu Allah yanason hakan.

5. Idan har wani bangare na sahabbai ya jahilci wannan, to waninsu shi yafi cancantar ya jahilci wannan hukuncin. (don haka kada ka mu rudu da aikin mutane).

6. Kuma wadannan sahabban sunada kyawawan aiyuka tareda alkawarin gafartawa da waninsu baisamu ba,. ( don haka kada ka ambace su se da kyakkyawan ambato; domin sukansu suka ne ga Allah da Manzonsa da Addini gaba daya).

7. Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam bai karbi hanzarinsu ba, ya yi musu martani ne da fadinsa: " Allahu Akbar! hanyoyi ne da suka gabata, da sannu zaku bibiyi hanyoyin wadanda suka gabace ku " ya kausasa musu da wadannan maganganu uku.

8. Lamari maigirma -shine maqasudi-: "Annabi ya ba da labarin cewa abin da suka nema shine kwatankwacin abin da banu isra'ila suka nema yayin da sukace wa Annabi Musa: [ ka sanya mana abin bauta ]" (cikin wannan akwai hani kan kamanceceniya da mushrikai cikin lafuzza ).

9. Lallai ne hana su wannan aikin yana daga ma'anar (*laa ilaaha illallah*) tareda cewa hakan ya buya garesu, (Kalmar shahada tana kore duk wani abin bautan da ba Allah ba, hakane Albarka bata tabbatuwa wajen wanin Allah).

10. Manzon Allah Sallallahu'alaihi wasallam ya yi rantsuwa wajen fatawa, kuma baya rantsuwa se akan abin da akwai maslaha cikinsa, ( ko ga tunkude barna ).

11. Shirka akwai babba akwai karama; saboda basuyi riddaba da wannan maganar.

12. Fadinsu: (muna sabbabin musulunta), wannan ya nuna wasu daga sahabban sunsan hukuncin hakan. (su sunada uzurin jahilci domin basu dade da musulunta ba ).

13. Yin kabbara yayin mamakin wani abu, sabanin wanda yake gani bai dace ba.

14. *Toshe kafafen barna* ( hanyoyin da suke kaiwa zuwaga wani abu, sun kasu kashi biyu:

[1] Hanyoyi masu kaiwa ga maslahohi, wadannan ba'a rufe su, bude su da neman su akeyi.

[2] Hanyoyi masu kaiwa ga abuuwan zargi; to wadannan rufe su akeyi, shine manufar mawallafin Allah ya jikansa).

15. Hani kan yin kamanceceniya da mutanen jahiliyyah. (Jahiliyyah ba ta kebanci zamani gabanin Annabta ba, A'a, duk wanda ya jahilci gaskiya kuma ya aikata irin aikin jahilai to ya zamo cikin mutanen da ake jingina su da jahiliyyah).

16. Fushi yayin karantarwa (idan akwai bukatar hakan).

17. Ka'ida Gamammiya itace: fadinsa: " **hanyoyi ne** " (wannan domin tsoratarwa ne).

18. Wannan wata alama ce daga alamomin annabta, saboda kasantuwar kamar yanda ya bada labari.

19. Duk abin da Allah ya zargi Yahudu da Nasara saboda shi, a cikin alqur'ani; to muma abin zargine idan muka aikata irin sa.

20 Abu ne tabbatacce a wajensu cewa dukkan ibada an gina su ne karkashin umarni, akwai fadakarwa cikin haka kan tambayoyin kabari uku: amma gameda fadinsa: "wanene Ubangijinka", wannan abu ne a fili, gameda: " wanene Annabinka ": saboda ya bda labarin gaibu, gameda fadinsa "menene addininka": daga fadinsu [ka sanya mana abin bauta ]. zuwa karshe.

21. Tafarkin Ahlul kitabi abin zargi ne kamar tafarkin mushrikai.

22. Duk wanda ya tuba daga wata barna da zuciyarsa ta saba da ita, ba'a amintuwa daga danfaruwar ragowar wannan al'adar cikin zuciyarsa, saboda fadinsa: (ba mu jima da barin kafirci ba). (don haka yana daga cikin hikima a bakontar da mazinaci daga wajen da yayi wannan laifin bayan anyi masa bulala, domin kada ya koma zuwa ga wannnan laifin, yakamata mutum ya nisanci wajajen kafirci da shirka da fasikanci, tafarkin Ahlussunnah shine daukar ilimi a wajen malamai na Allah, kuma ba'a daukan ilimi daga wajen malamin da ya tuba daga bata zuwa Sunnah har sai malamai sun ba da shaida a kan ingancin aqidarsa da gushewar abin da ya kasance a kai na bata.

## [10] Babin abin da yazo na yanka domin wanin Allah

Meyasa yace: “Babin abin da ya zo”, be ce: (Babi; yana daga babban shirka, yanka domin wanin Allah )?

[1] Mawallafin yayi nufin horas da dalibi ne wajen gina hukunci kan dalili, wannan yana cikin tarbiyya a aikace.

[2] Ko kuma saboda yankan da ba na bauta ba ya kasu biyu: halal, da shirka babba.

**DALILI NA FARKO:**

Da fadin Allah Ta'ala:

[ قُلْ إِنَّ صَلاَتِي وَنسُكِي وَمَحْيَايَ وَمَمَاتِي لِلهِ رَبِّ الْعَالَمِينَ (١٦٢) لاَ شَرِيكَ لَهُ... ]

***" Ka ce; lallai ne sallata da baikona, da rayuwata da mutuwana, na Allah ne Ubangijin talikai, ba shi da abokin tarayya***...*(QS. Al-An'am : 162-163).*

**DALILI NA BIYU:**

Da fadinsa:

[فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَانْحَرْ]

***“ Saboda haka kayi sallah domin Ubangijinka kuma ka soke baiko (sukar rakumi ) ”*** *(QS. Al-Kautsar: 2).*

- **{Ka ce }**: ka fada ma wadannan mushrikan, kana maisanar da su jajirtarka wajen tsayar da Tauhidi da tace shi ga Allah shi kadai.
- **{Sallata}** : Ayyukana na jiki, Sallah ce mafi falalar su, ta farilla ko ta nafila.
- **{Da yankata}** **:** Ayyukana na dukiya, yana daga mafi falalarsu yanka domin Allah.
- **{Rayuwata da Mutuwata}:** Dukkan lamurra na da ayiyukana halin rayuwa da na mutuwa duk saboda Allah ne.
- **{Farkon masu mika wiya}:** [1] *Awwaliyah idhafiyah* (Farko ne kayyadadde), ma'ana: nine farkon wanda ya mika wuya daga wannan al'ummah. [2] Farko ne sakakke; abin nufi: shine wanda yafi kowa riko da musulunci, kuma mafi mika wuyan mutane ga dokokin Allah cikin dukkan al'ummomi.
- **{ Kuma ka soke hadayarka}** : Ka sanya yankanka domin Allah shi kadai kamar yanda kasanya sallarka dominsa shi kadai, yanka nau'i ne daga nau' ukan ibada .

**Kashe kashen yanka:**

| Yanka domin Allah: | Yanka na halal: | Yanka domin wanin Allah, saboda soyayya da girmamawa (shirkace babba ): |
|---|---|---|
| Kamar yanka hadaya, da laiya, da suna, aikata su ma wanin Allah shirka ce babba. | Kamar akuyar da aka yanka don aci namanta, da karrama bako, da yanka saboda tijara. | Kamar yin yanka domin ma'abota kaburbura, da aljanu. |

**DALILI NA UKU**

عَنْ عَلِيِّ بْنِ أَبِي طَالِبٍ ﵁ قَالَ: حَدَّثَنِي رَسُولُ اللهِ ﷺ بِأَرْبَعِ كَلِمَاتٍ: «**لَعَنَ اللهُ مَنْ ذَبَحَ لِغَيْرِ اللهِ**، **لَعَنَ اللهُ مَنْ لَعَنَ وَالِدَيْهِ، لَعَنَ اللهُ مَنْ آوَى مُحْدِثًا، لَعَنَ اللهُ مَنْ غَيَّرَ مَنَارَ الأَرْضِ**». رَوَاهُ مُسْلِمٌ

Daga Aliyu dan Abi Dalib Radiyallahu'anhu yace: Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya fada mini wasu maganganu guda hudu; " **Allah ya tsine ma wanda yayi yanka ba dan Allah ba**, **Allah ya tsine ma wanda ya zagi iyayensa, Allah ya tsine wanda ya bada mafaka wa mabarnaci, Allah ya tsine ma wanda ya canza iyakan kasa** ". ( Muslim ne ya rawaito).

● (**Allah Ya tsine**): Tsinuwa daga Allah: kora da nisantarwa daga Rahamar Allah, [1] mai yiyuwa Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam labari ya bayar cewa: Allah ya tsine ma wanda yayi yanka domin wanin Allah.
[2]: ko Manzon Allah yana Addu'a ne cewar: " Ya Allah ka tsine ma wanda yayi yanka domin wanin Allah.

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنْ طَارِقِ بْنِ شِهَابٍ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**دَخَلَ الْجَنَّةَ رَجُلٌ فِي ذُبَابٍ، وَدَخَلَ النَّارَ رَجُلٌ فِي ذُبَابٍ**»، قَالُوا: وَكَيْفَ ذَلِكَ يَا رَسُولَ اللهِ؟ قَالَ: «**مَرَّ رَجُلَانِ عَلَى قَوْمٍ لَهُمْ صَنَمٌ، لَا يَجُوزُهُ أَحَدٌ حَتَّى يُقَرِّبَ لَهُ شَيْئًا، فَقَالُوا لِأَحَدِهِمَا: قَرِّبْ، قَالَ: لَيْسَ عِنْدِي شَيْءٌ أُقَرِّبُ، قَالُوا لَهُ: قَرِّبْ وَلَوْ ذُبَابًا، فَقَرَّبَ ذُبَابًا؛ فَخَلَّوْا سَبِيلَهُ، فَدَخَلَ النَّارَ، وَقَالُوا لِلآخَرِ: قَرِّبْ، فَقَالَ: مَا كُنْتُ لِأُقَرِّبَ لِأَحَدٍ شَيْئًا دُونَ اللهِ ٥، فَضَرَبُوا عُنُقَهُ، فَدَخَلَ الْجَنَّةَ**»، رَوَاهُ أَحْمَدُ.

Daga Dariq dan Shihab; Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya ce: " Wani mutum ya shiga Aljannah a sanadin kuda, kuma wani mutum ya shiga wuta a sanadin kuda ", sai sukace yaya hakan yakasance ya manzon Allah? Sai yace: " wasu mutane biyu sun wuce taron wasu mutane masu gunki, wadanda basa kyale kowa ya wuce

har sai ya yanka wani abu ma wannan gunkin domin neman kusanci, sai sukace ma dayan mutum biyu: ka gabatar da wani abu, sai yace: banida wani abun da zan gabatar, sai sukace da shi: ka gabatar da ko da kuda, **sai ya gabatar da guda, sai suka kyale shi, sai ya shiga wuta sanadin hakan**, sai sukace wa dayan: ka gabatar da wani abu, sai yace: ban kasance mai gabatar da wani abu ma kowa ba face Allah, sai suka sare wuyansa, kuma, ya shiga Aljannah saboda haka ". ( Imam Ahmad ne rawaito).

- " في ذباب ": Ma'ana a sanadiyyar kuda.

***MATSALOLIN BABIN:***

1. Tafsirin fadin allah Ta'ala: [ قل إن صلاتي ونسكي ].

2. Tafsirin fadin allah Ta'ala: [ فصل لربك وانحر ].

3. An fara da tsine ma wanda yayi yanka domin wanin Allah. (saboda dangi ne na shirka, hakkin Allah yafi gaima sama da sauran hakkoki ).

4. Tsine ma wanda ya zagi iyayensa, kamar ka zagi iyayen wani mutum sai shima ya zagi iyayenka. (domin sababin wani abu daidai yake da wannan abun, wajen hukunci, maizagin iyayen wani kamar ya zagi iyayensa ne kaitsaye ).

5. Tsine ma wanda ya bada mafaka wa mabarnaci, shine mutumin da yake kirkirar wani abun da hakkin Allah ke wajaba a kansa (na hukunci), sai ya fake wajen wannan da ke bashi mafaka kan wannan abun. ( kuma wanda wanda yafi tsananin taimako ga mabarnata shine mai shamakance su, barna tana kasancewa ne cikin:

[1] **Addini;** kamar bidi,ar da Jahmiyyah suka kirkira, da Muu'tazilah, da Rafidhah, da wadansunsu.

[2] **Cikin lamarin al'ummah;** kamar aikata lafuka da makamantansu, kamar bada mafaka ma barayi da yan fashi da makami.

6. Tsinuwa kan wanda ya canza iyakokin kasa, sune alamomin da aka sanya don rabe tsakanin hakkinka na kasa da hakkin makwabcinka, sai ka canza su da yin gaba da su ko baya.

7. Banbanci tsakanin tsine wa mutum sananne, da kuma tsine wa masu sabo ta hanya gamammiya. ( na farkon haramunne, na biyun ya halatta, ba yi halatta ka tsine wa mutum sananne, Asali shine rashin halaccin yin tsinuwar) (se wanda dalili na shari'a ya tabbatar).

8. Hakika wannan kissa ce maigirma, wato kissar kuda. (bisa magana kan ingancinta).

9. Kasantuwar wannan mutumin ya shiga wuta sanadin kuda, tareda cewar bai yi kudirin abin da ya gabatar masa ba, kadai ya gabatar ne domin kubuta daga sharrinsu. (Saboda tilastawa ba uzuri ba ne ga al'ummomin da suka gabata).

10. Sanin girman shirka cikin zukatan muminai; ta yanda wannan muminin yayi hakuri akan akashe shi sama da ya amince da abin da sukaso, tareda cewa basu bukaci wani abu daga gare shi ba face aikin zahiri. (idan har cikin amincewarsa da rashin hakurinsa akwar cutar da addini, to sai yayi hakuri, yin hakurin zai iya zamowa wajibi ).

11. Kasancewar wannan da ya shiga wuta musulmi ne; domin da ya kasance kafiri, to da Annabi baice: "ya shiga wuta sanadin kuda ba" (saboda wannan abin da ya gabatar shine sanadin shigansa wutar).

12. Daga ciki akwai shaida wa ingantaccen hadisi: "**Aljannah tafi kusa da dayanku daga igiyar takalminsa, to hakanan wuta ma** " (abin nufi da wannan shine kwadaitarwa da kuma tsoratarwa).

13. Sanin cewa lallai aikin zuci shine babban abin kula har wajen bautar gumaka. (warakan zuci shine Alqur'ani da Sunnah, don haka kada ka shagaltu da duniya ).

**SHIN MENENE YA FI GA MUTUM IDAN AKA TILASTA SHI AKAN AIKATA KAFIRCI, YAYI HAKURI KO DA ZA A KASHE SHI, KO KUMA YA AMINCE A ZAHIRI TAREDA YIN TAWILI?**

1. Ya amince a fili da boye, wannan bai halatta ba domin yin hakan ridda ce.
2. Ya yarda a bayyane ya ki a boye, domin ya kubuta daga tilastawa; ya halatta.
3. Ya ki yarda a zahiri da badini, kuma a kashe shi, wannan ya halatta, kuma wani nau'i ne na hakuri, hakan idan har yazamo yarda da tilastawar zai haifar da cutarwa ga al'ummah a cikin addininsu, in ko ba haka ba, to sai ya amince a fili banda boye.

## [11] BABIN BA YA HALATTA AYI YANKA DON ALLAH A WAJEN DA AKE YANKA DOMIN WANIN ALLAH

Mawallafin -Allah yajikansa- ya kyautata matuka wajen kulla wannan babin, domin bayan da yayi magana hukuncin yin yanka domin wanin Allah, kai tsaye sai ya ciratu zuwaga bayanin rashin halaccin yanka domin Allah a wajen da ake yin yanka domin wanin Allah, kamar wanda ya yi nufin yanka laiya saboda Allah a wajen da a keyin yanka domin gumaka, hikimar hanin sune:

[1] Lallai ne yana kaiwa ga koyi da kafirai.

[2] Yana kaiwa ga ruduwa da wannan aikin, kuma wasu za su yi zaton halaccin abin da mushrikai ke aikatawa.

[3] Mushrikai zasu samu karfin guiwa kan aikinsu, don haka, karfafa su bai halatta, abin da ake bukata shine bakanta musu da raunana su.

### DALILI NA FARKO:

Da fadin Allah ta'ala:

(لاَ تَقُمْ فِيهِ أَبداً...) الآيَةَ.

***[ kada ka tsaya a cikinsa har abada ]...****(QS. At-Taubah: 108).*

**Sababin da yasa mawallafin ya kawo wannan ayar:**

Yayin da munafukai suka riki (Masjidud-dirar) domin sabawa Allah da cutar da musulunci, da kafirci da bagewa ga tamakon masu yakar Allah da Manzonsa, da rarrabe wa tsakanin muminai; sai Allah Ya hana Manzonsa tsayuwa a ciki, tareda cewa sallar da Annabi zaiyi ciki domin Allah ne, sai wannan ya nuna cewa ba'a tsayuwa domin ibada a dukkan wajenda ake sabon Allah cikinsa, ko bayan an kawar da shi, kamar yanda sallah ibada ce to haka yanka ma ibada ce, abin da yayi kusa da wannan hukuncin shine hanin yin sallah yayin fitowar rana da yayin faduwarta, saboda lokuta ne da kafirai suke sujada wa rana; wannan ta fiskar kula da lokaci ne na yin ibada, ayar kuma tana hani ne, ta fiskar kula da wajen yin Ibadan ne….

### DALILI NA BIYU:

عَنْ ثَابِتِ بْنِ الضَّحَّاكِ ۞ قَالَ: نَذَرَ رَجُلٌ أَنْ يَنْحَرَ إِبِلًا بِبُوَانَةَ، فَسَأَلَ النَّبِيَّ ﷺ، فَقَالَ: «هَلْ كَانَ فِيهَا وَثَنٌ مِنْ أَوْثَانِ الْجَاهِلِيَّةِ يُعْبَدُ؟»، قَالُوا: لَا، قَالَ: «فَهَلْ كَانَ فِيهَا عِيدٌ مِنْ أَعْيَادِهِمْ؟»، قَالُوا: لَا، فَقَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «أَوْفِ بِنَذْرِكَ، فَإِنَّهُ لَا وَفَاءَ لِنَذْرٍ فِي مَعْصِيَةِ اللهِ، وَلَا فِيمَا لَا يَمْلِكُ ابْنُ آدَمَ». رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ، وَإِسْنَادُهُ عَلَى شَرْطِهِمَا.

Daga Sabit dan Addahhak yace: (wani mutumi yayi bakancen zai yanka rakuma a Buwana, se ya tambayi Annabi -sallallahu alaihi wasallam- hukuncin hakan, sai annabi ya ce masa: **"shin akwai wani gunki daga gumakan jahiliyyah da ake bauta masa a wannan wajen**? ", suka ce: A'a, yace: **"shin akwai wani idi daga idodinsu? "**, suka ce: A'a, sai Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: **"ka cika bakancenka, domin babu ciko ga bakance cikin saba ma Allah, hakanan, babu ciko ga bakance cikin abin da dan 'Adam baya mallakansa "** (Abu Daud ne ya rawaito, da isnadi kan sharadin Imam Bukhari da Muslim).

**BAKANCE:**

**A Larabce:** daukan alkawari da lizamta ma kai wani abu.

**A Shari'ance:** mutum baligi ya lizimta wa kansa wani abun da ba wajibi ba.

**Bakance domin Allah:**

**Bakance domin wanin Allah (shirka ne babba):** Kaman rantsuwa da wanin Allah cikin lafazi kadai, wannan baya kulluwa, (bazai cika shi ba, kuma babu kaffarah cikinsa, sai a tuba zuwaga Allah)

**Bakance kebantacce:** Kamar yayi bakance akan wani kebantaccen abu.

**Bakance gamamme:** Dukkan musulmi ya shiga cikinsa. Allah yace: {*Suna cika bakance*}. (QS. Al-Insan: 7).
Saboda kowani Musulmi yayi alkawarin bin umarnin Allah da barin abubuwan da Allah Ya hana.

**Bayan furta shi:** Wajibi a cika shi ko ayi kaffaran rantsuwa.

**Kafin furta shi:** Hukuncinsa: haramun ne, saboda Annabi -sallallahu alaihi wasallam- yayi hani akai, da alkhairi ne da Manzon Allah -tsira da amincin Allah ya tabbata a gare shi- ya aikata.

**Bakance kan da'a:** wajibi ne a cika shi, kuma idan yayi nadamar bakancen (ya fasa) to kaffara ta wajaba a kansa (misali: bakance kan sallar nafila).

**Bakance kan sabo:** haramun ne a cika shi, kuma wajibi ne ayi nadamar aikata shi tareda yin kaffara. (misali: bakance kan aikata haramun, kamar giba -yi da wani-)

**Bakance na halal:** yanada zabi tsakanin aikata shi -shine yafi- ko fasa shi, tareda yin kaffara, (misalinsa; yayi bakance kan sanya wani tufafi ).

**Bakancen fusata:** kamar wanda ya halatta a hukunce, ana nufin ma'anar rantsuwa da shi. (Misalinsa: kamar yayi bakancen barin garin).

**Bakance makruhi:** makruhi ne a cika shi, anso a fasa shi sa'annan ayi kaffara, (Misalinsa: kamar wanda yayi bakancen zaiyi juyayi a cikin sallah ).

**Bakance sakakke:** wanda ma'abocinsa bai kaiyade shi da komai ba, to akwai kaffara, (kamar yace: nayi wa Allah bakancen.. sai yayi shiru ).

- Idan bakance ya zamo don Allah madaukaki, to lallai ne yana kudduwa, kodai ya cika shi ko yayi nadama to kaffara ta wajaba a kansa.
- Idan kuma ya zamo domin wanin Allah to wannan baya kulluwa; babu cikawa kuma babu kaffara, wajibi a tuba domin hakan (Shirka ce babba).

## MATSALOLIN BABIN:

**1** Tafsirin fadin Allah Ta'ala [kar ka tsaya cikinsa har abada]*…(QS. At-Taubah: 108)*

2. Sabon Allah yanada tasiri a kan kasa, hakanan da'a wa Allah (idan wani waje ya zamo wajene na shirka; to haramun ne mutum ya aikata abin da zaiyi kama da shirka a wannan wajen, don kar yayi kamanceceniya da mushrikai ).

3. Mayar da mas'alar da ta shiga duhu zuwa fili, domin rikicin ya kauce.

4. Yana da kyau maifatawa ya nemi dalla dalla kafin yayi fatawar idan akwai bukatar hakan. (ko kuma ya yi dalla dalla wajen bada amsa).

5. Kebance wani waje da bakance babu laifi idan wajen ya kubuta daga abubuwan da aka hana. (sedai idan anji tsoron gama garin mutane zasu kudirce cewa wannan wajen yanada falala ta musamman, to ya haramta ).

6. Haramun ne idan akwai gunki daga gumakan jahiliyyah, ko bayan kawar da shi.

7. Haramun ne idan akwai wani idi daga idodinsu, ko bayan an kawar da shi..

8. Bai halatta ya cika bakancen da ya sha alwashi a wannan wajen, domin bakance ne cikin sabon Allah.

9. A kiyayi yin kamanceceniya da mushrikai cikin bukukkuwansu, ko da baiyi nufin koyi da su ba (Shaikhul islam Ibn Taimiya ya nassanta cewa: ba yi daga sharadin kamanceceniya da kafirai mutum yayi niyyar hakan, sedai yafi muni da girman laifi idan yay i niyyar hakan ).

10. Haramun ne yin bakance cikin sabon Allah (ma'ana: bakancen yana kulluwa amma haramun ne a cika shi).

11. Bai halatta ba ga dan Adam yayi bakance cikin abin da bai mallaka (ma'ana: bai halatta ya cika bakancen ba, kuma abin da ya mallaka iri biyu;

[1] **A Shari'ance:** kamar ya ce: na sha alwashi wa Allah zan yanta bawan wane, to wannan bai halatta ba, saboda bawan ba mallakansa ba ne.

[2] **A Kaddare:** kamar yace: na sha alwashi wa Allah in tashi sama da hannayena biyu, to wannan ba shi halatta saboda baya da ikon mallakar hakan.

**Kaffarar bakance domin Allah kamar kaffarar rantsuwa ce:**

● Mutum yanada zabi tsakanin: yanta baiwa musulma ko ciyar da miskinai goma, ko tufatar da su.

● Idan bai samu iko ba, to sai ya je ga yin azumi na kwanaki uku a jere.

## [12] BABI YANA DAGA SHIRKA BAKANCE DON WANIN ALLAH

**DALIL NA FARKO:**

Da fadin Allah ta'ala:

يُوفُونَ بِالنَّذْرِ

*[ **Suna cika bakancen** ]…(QS. Al-Insan : 7).*

**DALILI NA BIYU:**

Da fadinsa madaukaki:

وَمَا أَنفَقْتُم مِّن نَّفَقَةٍ أَوْ نَذَرْتُم مِّن نَّذْرٍ فَإِنَّ اللَّهَ يَعْلَمُهُ

*[ Kuma duk wata ciyarwa da kukayi, ko wani bakance da kuka sha alwashi, to lallai ne Allah yana sane da shi]. (QS. Al-Baqarah : 270).*

Munasabar wadannan ayoyi biyu ga babin shine: cika bakance daya ne daga sabubban da yake kai mutanen kirki ga shiga Aljannah, ( ibada ne ), don haka karkatar da shi ga wanin Allah shirka ne, hakanan rataya wani abu da ilimin Allah da sakamako a kansa.

**DALILI NA UKU:**

وَفِي الصَّحِيحِ عَنْ عَائِشَةَ ، أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**مَنْ نَذَرَ أَنْ يُطِيعَ اللهَ فَلْيُطِعْهُ**، وَمَنْ نَذَرَ أَنْ يَعْصِيَ اللهَ فَلَا يَعْصِهِ».

Yazo cikin Sahihul Bukhari daga Aisha Allah ya kara yarda a gareta, Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam yace: "**duk wanda yayi bakance kan da'a wa Allah to**, **ya cika**, kuma duk wanda yayi bakance kan saba ma Allah to kar ya cika "

Babanci tsakanin bakancen da'a da na sabo, da bakance domin wanin Allah

| Bakancen da'a ga Allah | Bakancen saba ma Allah | Bakance domin wanin Allah |
| --- | --- | --- |
| Kamar rantsuwa ne da Allah, yana kulluwa ( ana cika shi ko ayi kaffara) Wajibi ne a cika shi. | Kamar rantsuwa da Allah ne, yana kulluwa ( ba'a cika shi, a nayin kaffarah ). Haramun ne a cika shi. | Kamar rantsuwa da wanin Allah, bay a kulluwa, sai tuba zuwaga allah. Shirka ce babba. |

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Wajabcin cika bakance (bakance kan da'a wa Allah shi kadai).

2. Idan ya zamo ibada ne ga Allah, to karkata shi ga wanin Allah shirka ce.

3. Ba yi halatta a cika bakance kan sabon Allah. (anayin kaffaran rantsuwa).

**Abun kula:**

Hukunce hukuncen bakance da na rntsuwa sunada matukar kusanci, don haka ne malaman fiqhu suka hada su a babi guda (Babin rantsuwa da bakance).

## [13] BABIN; YANA DAGA SHIRKA NEMAN TSARI DA WANIN ALLAH ( CIKIN ABIN DA BA MAI IKO AKANSA SAI ALLAH )

**DALILI NA FARKO:**

Da fadin Allah ta'ala:

وَأَنَّهُ كَانَ رِجَالٌ مِّنَ الْإِنسِ يَعُوذُونَ بِرِجَالٍ مِّنَ الْجِنِّ فَزَادُوهُمْ رَهَقاً (٦)

***[ Kuma lallai ne wasu mazaje daga cikin mutane sun kasance suna neman tsari da wasu mazaje daga Aljanu, sai suka kara musu girman kai ]*** *(QS. Al-Jinn : 6).*

● يَعُوذُونَ: suna neman tsari, ( mafaka ). فالعياذ (Al iyazu) neman tsari daga abin da ake jin tsoro. اللِّياذ (Alliyazu) cikn abin da ake fata mai kyau.

● *{ Sai suka kara musu girman kai }*: الذُّعر da الخوف ana jin su cikin zukata ne, الرَّهق cikn jiki. Neman tsari da wanin Allah ba ya amfanar me neman tsarin, sedai ya kara masa rauni da kaskanci, domin hakan shirka ce babba, se aka masa ukuba da akasin abin da ya nufa.

**DALILI NA BIYU:**

وَعَنْ خَوْلَةَ بِنْتِ حَكِيمٍ ڤ قَالَتْ: سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُولُ: «مَنْ نَزَلَ مَنْزِلًا فَقَالَ: (أَعُوذُ بِكَلِمَاتِ اللهِ التَّامَّاتِ مِنْ شَرِّ مَا خَلَقَ)، لَمْ يَضُرَّهُ شَيْءٌ حَتَّى يَرْحَلَ مِنْ مَنْزِلِهِ ذَلِكَ»، رَوَاهُ مُسْلِمٌ.

Daga Khaulah bint Hakim Allah Ya Kara yarda a gareta, ta ce: naji Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: " Duk wanda ya sauka a wani masauki sai ya ce: (ina neman tsari da kalmomin Allah cikakku daga sharrin duk wani ma'abocin sharri), to babu wani abun da zai cutar da shi har ya tafi daga wannan wajen nasa " (Muslim ne ya ruwaito).

● مَنْزِلً (wani masauki): ya kunshi wanda ya sauka da niyyar zama na tabbatuwa, ko jirgin sama ko jirgin ruwa.

● أَعُوذُ : ina neman tsari da kariya. بِكَلِمَاتِ اللهِ (da kalmoin Allah): na Kauniyah da na syar'iyyah. ( halittattu da wadanda ba halittattu ba)

● التَّامَّاتِ (cikakku): [1] Gaskiya ta fiskan labari. [2] Adalci cikin hukunce hukunce.

● شَرِّ مَا خَلَقَ (sharrin ma'abocin sharri cikin halittu) : ba'a dangana sharri zuwaga Allah; sabboda ya halicci sharrin domin hikima ce.

**Kashe kashen halittu:**

1. Alkhairi tsantsa, kamar Aljannah, da Manzanni, da Malaiku.

2. Sharri tsantsa; kamar wuta, da Iblis, ta fiskan zatinsu, amma ta fiskar hikima kuma to Halittansu alkhairi ne.
3. Sunada sharri da alkhairi: Kaman mutane, da Aljanu, da Dabbobi.

● لَمْ يَضُرَّهُ شَيْءٌ (babu wani abun da zai cutar da shi): labara wanda babu makawa, domin Magana ce ta maigaskiya kuma abun gasggatawa, sedai idan a ka ga sabanin haka to dalilin samuwar wani cikas ne, ba dmin gazawar sababi ko akasin labarin ba, misalin karatun Fatiha wa marasa lafiya, akwai waraka ciki, wadansu suna karantawa amma mara lafiyan ba ya waraka.

***MATSALOLIN BABIN:***

1. Tafsirin ayar suratul Jin. ***[ Kuma lallai ne wasu mazaje daga cikin mutane sun kasance suna neman tsari da wasu mazaje daga Aljanu, sai suka kara musu girman kai ]*** *(QS. Al-Jinn : 6).*

2. Kasancewar sa shirka ne. (babban shirka, neman tsari da wanin Allah cikin abun da babu mai iko akansa sai Allah).

3. Kafa hujjah akan haka da hadisi; domin malamai suna kafa hujja da shi kan cewar maganar Allah ba halitta ba ne, domin neman tsari da halitta shirka ne (babba cikin irin wannan lamarin, kuma da kalmomin Allah halitta ce, da Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam bai yi nuni zuwaga neman tsari da su ba ).

4. Falalar wannan addu'ar tareda gajertanta. (babu wani abun da zai cutar da kai iya zamarka a wannan masukin).

5. Tabbatuwar amfanin wani abu a duniyance, Kaman tunkudewar wani sharri ko janyo wani amfani, ba ya nini kan cewa wannan abun ba shirka ba ne. ( tabbatu `war wani amfani ba ya lizimta korewar shirka ).

**WADANSU FAIDODI:**

Cikin hadisin akwai dalilin cewar Shari'a ba ta rushe wani abu dag abubuwan Jahiliyyah, har sai ta ambaci abun da yafi shi zamowa alkhairi, Misali: sun kasance a Jahiliyyah suna neman tsari da Aljanu, sai Allah ya canza musu da wadannan kalmomin.

Wannan itace lafiyayyar hanya da yakamata mai da'awa ya kasance a kanta, idan ya toshe kofar shirka wa mutane, to wajibi ne ya bude musu kofa alheri, akwai misalai masu yawa akan wannan a cikin alqur'ani da Sunnah.

## [14] BABIN; YANA DAGA SHIRKA YA NEMI AGAJI WAJEN WANIN ALLAH KO YA ROKE SHI

**DALILI NA FARKO**

Da fadin Allah Ta'ala:

(وَلاَ تَدْعُ مِن دُونِ اللّهِ مَا لاَ يَنفَعُكَ وَلاَ يَضُرُّكَ فَإِن فَعَلْتَ فَإِنَّكَ إِذاً مِّنَ الظَّالِمِينَ (١٠٦) وَإِن يَمْسَسْكَ اللّهُ بِضُرٍّ فَلاَ كَاشِفَ لَهُ إِلاَّ هُوَ) الآية.

***[ kuma kada ka kirayi wanin Allah, wanda baya amfanarka kuma baya iya cutar ka, to idan ka aikata haka, to lallai ne kai, kana daga masu zalunci, kuma idan Allah ya shafe ka da wata cuta, to babu mai yaye ta face shi ]*** *. (QS. Yunus : 106-107).*

**DALILI NA BIYU:**

Da fadinsa:

( فَابْتَغُوا عِندَ اللَّهِ الرِّزْقَ وَاعْبُدُوهُ ) الآية.

***[… Saboda haka, ku nemi arziki a wurin Allah shi kadai, kuma ku bauta masa***…] *(QS. Al-Ankabut : 17).*

**DALILI NA UKU:**

Da fadinsa:

( وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّن يَدْعُو مِن دُونِ اللَّهِ مَن لَّا يَسْتَجِيبُ لَهُ إِلَى يومِ الْقِيَامَةِ ) الآية.

***[ Kuma wanene mafi bata daga wanda yake kiran wanin Allah wanda ba zai amsa masa ba har ranar Alqiyama ]*** *(QS. Al-Ahqaf : 5).*

**DALILI NA HUDU:**

Da fadinsa:

( أَمَّن يُجِيبُ الْمُضْطَرَّ إِذَا دَعَاهُ وَيَكْشِفُ السُّوءَ ) الآية.

***[ Kuma wanene wanda yake amsa ma mai bukata yayin da ya kiraye shi kuma yake yaye mummuna ]*** *…(QS. An-Naml : 62).*

**DALILI NA BIYAR:**

وَرَوَى الطَّبَرَانِيُّ بِإِسْنَادِهِ؛ أَنَّهُ كَانَ فِي زَمَنِ النَّبِيِّ ﷺ مُنَافِقٌ يُؤْذِي الْـمُؤْمِنِينَ، فَقَالَ بَعْضُهُمْ: قُومُوا بِنَا

نَسْتَغِيثُ بِرَسُولِ اللهِ  مِنْ هٰذا الْـمُنَافِقِ، فَقَالَ النَّبِيُّ : «إنّهُ لَا يُسْتَغَاثُ بِي، وَإنّمَا يُسْتَغَاثُ بِاللهِ ٥».

Imam Ad-Dabrani ya rawaito da isnadinsa cewar; an samu wani munafiki a zamanin Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam wanda yake cutar da muminai, sai wasu cikin sahabbai suka ce: ku tashi mu nemi agajin Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam daga sharrin wannan munafikin, sai Annabi sallallahu alaihi wasallam ya ce: " ba'a neman agaji da ni, iyaka dai ana neman agaji ne da Allah maigirma da buwaya ".

- وَلاَ تَدْعُ (kada ka roki): roko irin na ibada, da na bukata, cikin abin da babu mai iko a kai sai Allah.
- عِندَ اللَّهِ ( wajen Allah shi kadai ): gabatar da abin da yakamata a jinkintar da shi (a larabci, yana hukunta: **iyakancewa da takaitawa**); ma'ana: don haka, ku nemi arziki wajen Allah shi kadai ba wajen waninsa ba, mushrikai suna bautan gumakan da ba zasu iya azurta su ba har abada.
- وَاعْبُدُوهُ (kuma ku bauta ma sa): ishara ce kan cewa tace ibada bangare ne na neman arziki kuma, kuma sababi ne na samun arziki.
- وَاشْكُرُوا لَهُ (kuma ku gode ma sa): ni'ima jarabawa ce da take bukatar godiya da zuci, da harshe, da gabbai.
- يُجِيبُ (yana amsawa): ba'a nema daga wani ya gusar da wata cuta ko yaye bakin ciki alhali baya da iko kan hakan.
- Munaafiq: yana baiyana musulunci ya boye kafirci, na daga cutar da al'adarsa wasu.

KASHE KASHEN ARZIKI:

| Arziki gamamme: | Arziki kebantacce ga muminai: |
| --- | --- |
| Ga dukkan halittu; kodai ya zamo halal ko haram. | Shine: imani da tsoron Allah, da aiki na gari. |

***MATSALOLIN BABIN:***

1. Rataya addu'a akan neman agaji na daga rataya gamammen abu ne kan kebantacce.
2. Tafsisin Fadin Allah ta'ala: *[ **kuma kada ka kirayi wanin Allah, wanda baya amfanarka kuma baya iya cutar ka** ] . (QS. Yunus : 106).*

3. Wannan babban shirka ce (rokon wani wanda ba Allah ba).

4. Da mafi shariya daga cikin mutane zai aikata hakan domin neman yardad da waninsa, to da ya zamo cikin azzalumai. (an fiskantar da hanin ne zuwaga wanda ba zai taba aikata abin da akayi hanin akai ba, don haka fiskantar da hanin zuwaga wanda zai iya aikata hakan ita tafi dacewa ).

5. Tafsirin ayar bayanta *[ **kuma idan Allah ya shafe ka da wata cuta, to babu mai yaye ta face shi** ]. (QS. Yunus : 107).*
Idan har babu mai yaye cuta sai Allah, to yazamo wajibi a kadaita shi da bauta shi kadai, hakanan a kadaita shi da neman agaji.

6. Kasancewar hakan ba ya amfanrsa a duniya tareda zamowar hakan kafirci ne, (ya yi asarar duniya da lahira).

7. Tafsirin aya ta uku: *… [**…Saboda haka, ku nemi arziki a wajen Allah kuma ku bauta masa…**] (QS. Al-Ankabut : 17).*

8. Ba ya dacewa a nemi arziki wajen kowa sai wajen Allah, kamar yanda ba,a neman aljannah a wajen kowa sai wajen Allah.

9. Tafsirin aya ta hudu *[ **To wanene mafi bata daga wanda yake kiran baicin Allah** ] (QS. Al-Ahqaf : 5).*

10. Babu mafi bata sama sa wanda yak e kiran wanin Allah ( Ana nufin korewa ne da wannan tambayar, ma'ana babu batacce sama da shi ).

11. Gafalar wanda ake kiran daga mai kiransa (baisan wani na kiran sa ba) .

12. Kiran wanin Allallah sababi ne na adawarsa da adawarsa ga mai kiransa.

13. Allah ya kirayi wannan kiran da bauta ga wanda ake kiran na sa.

14. Kafircewar wanda ake kiran ma wannan ibadar (raddinsa da inkarinsa).

15. Ya zamo mafi batan mutane ne saboda wannan kirar. ([1] domin yana kiran wanin Allah ne wanda ba zai amsa masa ba har abada. [2] wadanda ake kira din gafalallu ne daga kirar da ake musu. [3] mai kiran ya kafirta ne saboda bautan wasun Allah (Kiransu).

16. Tafsirin aya ta biyar: *[**Kuma wanene yake amsa wa mai bukata yayin da ya kiraye shi kuma yake yaye mummuna** ]…(QS. An-Naml : 62).*

17. Lamari mai ban mamaki, ikirarin masu bautar gumaka cewar Allah ne kadai yake amsa kirar wanda ya shiga cikin tsanani, domin haka ne ma suke kiransa yayin tsanani kuma suke tsarkake addini gare shi.

18. Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya tsare shingen Tauhidi, da cikakken ladabi tareda Allah. (ya yi tasyuwar daka wajen karantar da al'umma Allah shi kadai zata fake da shi lokacin tsanani, kuma bai halatta ta nemi agaji wajen kowa sai wajensa shi kadai.

## Jarabawar kashi na biyu (Babuka:9)

| [1] Tambaya ta farko: ambaci banbanci tsakanin nau'ukan bakance masu zuwa: | | |
|---|---|---|
| Bakancen da'a | Bakancen sabo | Bakance domin wanin Allah |
| | | |
| | | |
| | | |

[2] Bayyana hukunce hukuncen aiyuka masu zuwa, zabi lambar da ta dace da kowani aiki: Halal (1) Makruhi (2) Karamin laifi (3) Babban laifi (4) Karamar shirka (5) Babban shirka (6), Hukuncin na banbanta (7) Wajibi (8) Mustahabbi (9).

| | | | |
|---|---|---|---|
| Son macen aure | | Son Annabi Muhammadu sallallahu alaihi wasallam | |
| So tareda Allah | | Kokwanton kafircin ahlul kitab | |
| Mus hafin Alqur'ani domin tunkude kammun baka | | Mummunar addu'a kan wanda ya rataya tsirgiya | |
| La'anta sanannen mutum | | Zoben ma'aurata | |
| Rataya Layu | | Shafa dakunan gidan Annabi | |
| Yin tsarki da kasha ko kashin dabba | | Kebance wani waje da bakance | |
| Neman albarka da tilawar Alqur'an | | Halartar bukukkuwar kafirai | |
| Neman agaji da wani abun halitta | | Tsoron Aljanu | |
| Bakancen domin wanin Allah | | Rataya ayaoyin Alqur'ani | |
| Bakancen sabon Allah | | Laya daga Alqur'ani | |
| Rataya tsumma ko takalmi | | Ruqyah da yaren da ba larabci ba | |
| Rataya zare domin ado | | Ambaton allah da yaren da ba larabci ba | |
| Shafar hajarul aswad | | Shan ruwan Zamzam don neman waraka | |
| Lalata dukiya saboda maslaha | | Sanin wajen Masjid addirar | |
| Fadadin mu nemi agaji da Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam | | | |

[3] Tambaya ta uku: sanya alamar (☒) a wajen da yadace ko ka cikita maganar:

1. Tafsirin tauhidi shine: ☐ Kashi na biyu ☐ Babi na shida ☐ duka biyun.
2. Sharhin wannan tarjamar (Tafsir Tauhid da Shahadat an *Laa Ilaaha Illallah*), abun da suka biyo baya na babuka har zuwa:
☐ karshen littafin ☐ karshen wannan kashin.
3. Mawallafin Allah ya jikansa ya fassara tauhidi da:
☐ Da kishiyansa ☐ da bayyanannun abubuwa ☐ duka biyun.
4. Kashi na biyu na wannan littafin: ☐ 5 Bab ☐ 9 Bab ☐ 7 Bab
5. {*suna son su kamar yanda suke son Allah*}, Ma'ana:
…………………………………………………………………………………………
6. kashe kashen soyayya: [1] ………………………hukuncinsa………………………………
[2]…………………………………hukuncinsa……………………………………………..
[3]…………………………….…hukuncinsa……………………………………………..
7. So domin Allah yana kasancewa ne: ………………………………………da………………
………………….da…………………………..da…………………………………………….
8. Sabubban haramta laya na Alqu'ani:
[1]……………………………………………[2]…………………………………………………
[3]……………………………………………[4]…………………………………………………
9. Sharuddan halaccin ruqyah : [1]………………………………………………………….
[2]……………………………………………[3]…………………………………………………
10. Sababin kawo ayar: {*kada ka tsaya a cikinsa har abada …} (QS. At-Taubah: 108)* a Babin " ba'a yin yanka domin Allah a wajen da akeyin yanka domin wanin Allah " shine:
…………………………………………………………………………………………
11. Sababin kawo ayar: {*suna cika bakance …(QS. Al-Insan : 7)*}, a Babin " yana daga shirka yin bakance domin wanin Allah" shine:……………………………………..........
……………………………………………………………………………………………
12. Bakance a shari'ance shine: ……………………………………………………..........
13. Ma'anar kulluwar bakance shine:……………………………………..
14. Ma'ana "bakance bayi halatta cikin abinda dan Adam baya mallaka"?...........................
……………………..…………………………………………………
15. Ma'anar: بُوَانَةً Buwana:…………………………………………………………
لاَ يَجُوزُهُ Babu mai wuce shi:……………………………………………………………..
16. An gina Masjid addirar ne domin kafirci da …………………………da………………
da…………………………………………………………………………………….
17 Me yasa ba'a yanka domin Allah a wajen da ake yanka domin wanin Allah?
[1]......................................................................... [2]……………………………………..
[3]…………………………………………………………………………………………

18. Me yasa Annabi yace: “ba a neman agaji da ni”………….……………………………..
19. Ma'ana آوَى: …………………………………….da مُحْدِثًا:………………………………
ko……………………………………………………………………………………….
20. Hadisin “wanda ya zagi iyayensa” na nufin:……………………………………………
ko……………………...…………………………
21. Fadin Allah {*nine farkon musulmai* }, yana nufin: ……………………………………..
…………………………..ko……………………………………………………………....
22. Ma'anar fadin Allah: أَفَرَأَيْتُم…………………………..,اللَّاتَ ……………………………......
23. Ma'anar fadin Allah: وَالْعُزَّى……………………………..,وَمَنَاةَ :……………………………...
ko daga:…………………………………………………………………………………
24. Ma'anar: أَعُوذُ……………………………………,بِكَلِمَاتِ الله ……………………………..
25. Tabarruk ya kasu zuwa: [1]………………………[2]…………………………………
Za mu iya banbance tsakaninsu da cewa:…………………………………………………
26. Kashe kashen mutane a babin yin uzuri da jahilci:
[1]………………………………………..[2]…………………………………………………
27. Ana samun wanda yake salalh, yake bada zakkah, yake azumi, kuma yake yin sujada wa kaburbura: ☐ babban kafirci ☐ karamin kafirci ☐ babban laifi ☐ Munafiki.
28. Babban shirka ta kasu ☐ kashi 3 ☐ kashi 4 ☐ kashi 2.
29. Yanka ya kasu ☐ kashi 3 ☐ kashi 4.
30 Fadin Allah ta’ala a harshen Annabi Ibrahim: ***" Lallai ni na barranta daga abinda kuke bautawa, face wannan da ya kage ni"*** *(QS. Az-Zukhruf : 26-27)*, wannan ayar ta kunshi: ☐ Ma'anar la ilaha illallah. ☐ wanda yayi halitta shi ya cancanta a bauta masa. ☐ gajiyawar gumaka. ☐ duka gaba daya.
31. Ma'anar fadin Allah Ta'ala {أَحْبَارَهُمْ}: ☐ Malamansu. ☐ masu yawan ibada cikinsu.
32. Ma'anar fadin Allah Ta'ala {وَرُهْبَانَهُ }: ☐ masu yawan ibada cikinsu. ☐ Malamansu.
33. {أَرْبَابا } shirka ne cikin: ☐ soyayya. ☐ da'a.
34. Kashe kashen mutane gameda sabubba: ☐ bangarori biyu da wanda yake tsakiya. ☐ Sahihi, da babban shirka, da karama.
35. Yanka layya yana daga manyan aiyukan jiki. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
36. Ba ya halatta a tsine wa masu sabon Allah a daidaikunsu, sai a gamammiyar fiska. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
37. Wajibi ne musulmi ya kiyaye harshensa daga tsinuwa, ba zai tsine wa kowa ba sai wanda ya cancanci tsinuwar da nassi: ☐ gamamme Kaman tsine wa kafirai. ☐ kebantacce Kaman riba. ☐ duka biyun.
38. Sallah ba ta halatta a wajajen da aka tanada domin yakar Allah da Manzonsa, sedai Masallaci kadai : ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
39. Amma idan za a iya mayar da su wajen bautar Allah, to babu laifi a mayar da su. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.

40. Ya halatta a niki gari domin sallah a Masallacin Quba. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
41. Tafiya zuwa wajajen shirka wadanda suka shafe, babu laifi idan ya zamo saboda wa'azantuwa ne: ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
42. Ya halatta a tafi zuwaga kogon hira domin sanin yaya bautar Annabi sallallahu alaihi wasallam ta kasannce a wajen. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
43. Mi'iraji shine tafiyar Annabi sallallahu alaihi wasallam daga Makkah zuwa Baitul Maqdis. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.
44. Wanda ya canza alamomin da ake gane hanya da su: ☐ tsinanne ne. ☐ mai laifi ne.
45. Suna tauye hakkin salihai, kuma suna musun falalarsu:
☐ Ghulatu (masu wuce iyaka). ☐ Jufah (masu sakaci) ☐ tsaka tsakiya.

[4] Ambaci hukuncin bakance a rarrabe:

Bakance domin Allah:

……………………

Bakance domin wanin Allah (babban shirka):

……………………………………………………………………..

Bakance a kebe:

Bakance gamammiya:

Bayan anyi furuci:

Kafin ayi furuci:

Bakance kan da'a ma Allah:

Bakance kan sabon Allah:

Bakance na halal:

Alwashin fushi:

Bakancen na makruhi:

Alwashi sakakke:

[5] Sanya daga jerin (A) abinda ya dace da shi a jerin (B)

| No | (A) | (B) |
|---|---|---|
| 1 | Bakance | Ana kiranta *al-adzaaim* (tofi), dalili ya kebance shi, matukar ba a hada shi da shirka ba. |
| 2 | Munafiki | Wani abune da suke yinsa, suna riya cewa yana sanya soyayyar juna tsakanin miji da matarsa (ma'aurata). |
| 3 | Ruqyah | Wani abu ne da ake rataya ma yara domin kariya daga kammun baka. |
| 4 | Tiwalah | Kora da nisantarwa daga rahamar allah. |
| 5 | Layu | Baligi ya lizimta wa kansa abinda ba wajibi ba. |
| 6 | La'anta | Shine wanda yake bayyana musulunci ya boye kafirci, cutar da wasu na daga dabi'arsa. |

## Na Uku: Bacin bautar Wanin Allah (Babuka Hudu)

Bayan tafsirin tauhidi mawallafin ya ambaci hujjoji da suke nuni akan bacin bautar wanin Allah cikin babuka hudu:

● Bacin bautar gumaka, da bautar wanin Allah ta'ala, da bautar Annabi sallallahu alaihi wasallam.

● Bacin bautar Mala'iku, sune suka fi kusaci da Allah, face kebantattun Banu Adama.

● Bacin ceton da aka kore shi daga wanin Allah, kuma ceto hakkin Allah ne tsantsa.

● Bacin shiryarwa ta gamdakatar daga wanin Allah, babu mai mallakar ta sai Allah shi kadai.

### [15] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

أَيُشْرِكُونَ مَا لاَ يَخْلُقُ شَيْئاً وَهُمْ يُخْلَقُونَ (١٩١) وَلاَ يَسْتَطِيعُونَ لَهُمْ نَصْراً وَلاَ أَنفُسَهُمْ يَنصُرُونَ (١٩٢)

*[ yanzu suna yin shirka da Allah da wanda baya iya halittan komai alhalin su din halittansu akayi, kuma basa iya taimakon wadansunsu, sannan basa iya taimakon kawunansu ]. (QS. Al-A'araf : 191-192).*

● Allah ya bayyana gajiyawar wadannan gumakan, kuma baya halatta a bautata musu sabida dalilai guda hudu:

1. Kasancewar ba su halittan, wanda ko baya halitta to bai cancanci a bautata masa ba.
2. Kasancewar halittansu akayi daga babu, suna bukatuwa zuwaga waninsu, a farkonsu da dawwamarsu.
3. Kasancewar ba su iya taimakon wanda ya roke su.
4. Kasancewar ba su iya taimakar kawunansu.

### DALILI NA UKU:

وَالَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِهِ مَا يَمْلِكُونَ مِن قِطْمِيرٍ (١٣) إِن تَدْعُوهُمْ لَا يَسْمَعُوا دُعَاءَكُمْ وَلَوْ سَمِعُوا مَا اسْتَجَابُوا لَكُمْ وَيَوْمَ الْقِيَامَةِ يَكْفُرُونَ بِشِرْكِكُمْ وَلَا يُنَبِّئُكَ مِثْلُ خَبِيرٍ (١٤)

**[ Kuma wadanda kuke kira ba Allah ba, ba su mallakar ko da kidmir, idan kun kiraye su, ba za su ji kiranku ba, kuma ko da sunji bazasu amsa muku ba, Ranar kiyama za su kafirce,**

**ma shirkanku, kuma babu mai baka labari kamar masani ]**.*" (QS. Fadir 13-14).*

- {قِطْمِير}: (Kidmir), shine bawo mara kauri wanda ya kewaye kwallon dabino.
- Allah Ya bata bautar wadanda ba shi ba ta fiskoki mabanbanta:

1. Cewa ba sa mallakar komai.
2. kasancewar ba su jin kiran wanda ya kira su.
3. Ko da sunji kiran bazasu iya amsawaba, domin ba su da iko akan hakan.
4. Ranar kiyama Allah ta'ala zaizo da wadanda ake bauta musu baicin sa, kuma zasu kafirce ma shirkan da akayi musu.

**DALILI NA HUDU:**

وَفِي الصَّحِيحِ عَنْ أَنَسٍ قَالَ: شُجَّ النَّبِيُّ ﷺ يَوْمَ أُحُدٍ، وَكُسِرَتْ رَبَاعِيَتُهُ، فَقَالَ: «**كَيْفَ يُفْلِحُ قَوْمٌ شَجُّوا نَبِيَّهُمْ؟**» فَنَزَلَتْ: فَأَنْزَلَ اللهُ لَيْسَ لَكَ مِنَ الأَمْرِ شَيْءٌ

Ya zo cikin sahihul Bukhari daga Anas ya ce: ( ***Anyi rotsi wa Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ranar yakin Uhud kuma an karya raba'iyyarsa -hakora- sai ya ce:" ta yaya mutane zasu rabauta alhali sunyi rotsi wa Annabinsu?*** *" sai Allah Ya saukar da fadinsa [**ba ka da mallakar komai cikin lamarin** ] . (QS. Ali Imran 128)."*

**DALILI NA BIYAR:**

وَفِيهِ عَنِ ابْنِ عُمَرَ ﭬ: أَنَّهُ سَمِعَ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُولُ -إِذَا رَفَعَ رَأْسَهُ مِنَ الرُّكُوعِ فِي الرَّكْعَةِ الأَخِيرَةِ مِنَ الْفَجْرِ-: «**اللَّهُمَّ الْعَنْ فُلَانًا وَفُلَانًا**»، بَعْدَ مَا يَقُولُ: «**سَمِعَ اللهُ لِمَنْ حَمِدَهُ، رَبَّنَا وَلَكَ الْحَمْدُ**»؛ فَأَنْزَلَ اللهُ فَأَنْزَلَ اللهُ لَيْسَ لَكَ مِنَ الأَمْرِ شَيْءٌ

Cikin sahihul Bukhari, daga Imrana daga Abdullahi dan Umar -radiyallahu anhu- yaji Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yayin da ya dago kansa daga ruku'u a rakaar karshe na sallar alfajr yana cewa: " **ya Allah ka tsine ma wane da wane** ", bayan yace: " samiallahu liman hamidahu, Rabbana wa lakal hamdu ", sai Allah Ya saukar da: *[**ba ka da mallakar komai cikin lamarin** ] . (QS. Ali Imran 128)."*

وَفِي رِوَايَةٍ: يَدْعُو عَلَى صَفْوَانَ بْنِ أُمَيَّةَ، وَسُهَيْلِ بْنِ عَمْرٍو، وَالْحَارِثِ بْنِ هِشَامٍ، فَنَزَلَتْ: ( لَيْسَ لَكَ مِنَ الأَمْرِ شَيْءٌ ).

A cikin wata riwayar; yana mummunar addu'a akan Safwan dan Umaiya da Suhail dan Amru, da Al-Harith dan Hishsam, sai wannan ayar ta sauka: *[**ba ka da mallakar komai cikin lamarin** ].*

**DALILI NA SHIDA:**

وَفِيهِ عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ۞ قَالَ: قَامَ رَسُولُ اللهِ ﷺ حِينَ أُنْزِلَ عَلَيهِ: ( وَأَنْذِرْ عَشِيرَتَكَ الْأَقْرَبِينَ )، فَقَالَ: «يَا مَعْشَرَ قُرَيْشٍ - أَوْ كَلِمَةً نَحْوَهَا - اشْتَرُوا أَنْفُسَكُمْ؛ لَا أُغْنِي عَنكُمْ مِنَ اللهِ شَيْئًا، يَا عَبَّاسُ بْنَ عَبْدِ الْمُطَّلِبِ لَا أُغْنِي عَنْكَ مِنَ اللهِ شَيْئًا، يَا صَفِيَّةُ - عَمَّةَ رَسُولِ اللهِ ﷺ - لَا أُغْنِي عَنْكِ مِنَ اللهِ شَيْئًا، وَيَا فَاطِمَةُ بِنْتَ مُحَمَّدٍ، سَلِينِي مِنْ مَالِي مَا شِئْتِ، لَا أُغْنِي عَنْكِ مِنَ اللهِ شَيْئًا».

Kuma yazo cikin Sahihul Bukhari daga Abu Hurairah -radiyallahu anhu- **ya ce:** Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya mike tsaye, yayin da aka saukar masa fadin Allah Ta'ala: **[ kuma kayi gargadi ga danginka mafiya kusanci ]** *(QS. Ash Shu'ara, 214),* **sai ya tashi a tsaye sannan ya ce: " Ya ku taron quraishawa -kodai wata kalmar makamanciyarta- ku fanshi kawunanku; ba zan iya wadatar da ku da komai a wajen Allah ba, ya Abbas dan Abdul Muddalib, ba zan iya wadatar da kai komai a wajen Allah ba, ya Safiyyah -gwaggwon Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam- ba zan iya wadatar da ke komai a wajen Allah ba, ya Fadimah yar Muhammad, -sallallahu alaihi wasallam- ki roke ni cikin dukiyata duk abin da kike so, ba zan iya wadatar da ke komai ba a wajen Allah ".**

● شُجَّ: (الشَّجَّةُ**Ashshajjatu**), ya kebanci rauni a kayi ko a fiska .

● رَبَاعِيَّتُهُ: (**Raba'iyya**); hakwaa biyu da suke tsaki ana kiran su ثنايا (sanaya) wadanda suke biye da su guda biyu -dama da hagu- ana kiran su: رباعيَّتين (raba'iyya biyu).

● Cikn hadisin akwai dalili kan cewa Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- mutum ne, abinda yake samun sauran mutane -na musibu- shima yana samun sa, wannan yana nuni kan bacin bauta ma sa (صلى الله عليه وسلم).

● Akwai wa'azi ga dukkan mai wa'azantuwa; kada mu nisanta rahamar Allah daga duk kan wani mutumin da yake aikata sabon Allah.

● (( Safwan bin Umayyah, da Suhail dan Amru, da Al-Haris dan Hisham )), dukkan ukun su musulunta kuma musuluncinsu ya kyautatu, dan haka ka kula dakyau yanda adawa take juyawa ta dawo soyayya.

● Abubuwan da aka hana:

[1] La'antar kafirai sanannu, amma la'antar kafirai gaba daya a game, to wannan babu laifi, kuma babu laifi ayi mummunar addu'a ma kafiri, kamar muce; (ya Allah ka hutasar da musulmai daga sharrin wannan kafirin).

[2] Addu'a kan Allah Ya halaka dukkan kafirai, Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam baiyi adduar Allah ya halaka dukkanin kafirai ba, domin Allah -ta'ala- ya kaddara wanzuwarsu.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tafsirin ayoyi biyu. (sun kunshi bayanin bacin bautar gumaka da wanin Allah).

2. Qisasar yakin Uhud (Akwai dalili kan bacin karkatar da bauta ga Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam-, kuma bacin bautar waninsa shi yafi dacewa ).

3. Alqanutun shugaban Manzanni, kuma shuwagabannin waliyyai a bayansa suna cewa Amin cikin sallar, (babu wani cikin wannan al'ummar da yafi shi –sallallahu alaihi wasallam- ko yafi sahabbansa kusanci da Allah, tareda haka suna neman kariya da fakewa ga Allah; tabbas waninsu shine yafi dacewa da hakan ).

4. Kuma wadanda akayi mummunar addu'a akansu kafirai ne, (Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam baya mallaka wani abu daga lamarinsu).

5. Kuma lallai ne sun aikata abubuwan da yawancin kafirai ba su aikata ba; da ciki: sunyi rotsi wa Annabin su, kuma sunyi kwadayin su kashe shi, sannan sun yanke wasu bangarori na wadanda suka kashe daga musulmai, tare kasancewarsu diyan baffansu ne.

6. Allah ya saukar wa Annabinsa cikin lamarinsu:

لَيْسَ لَكَ مِنَ الأَمْرِ شَيْءٌ

*“**Ba ka da mallakar komai cikin lamarin**”. (QS. Ali Imran 128).*

(Dukkan al'amura na Allah ne).

7. Da fadin Allah ta'ala:

يَتُوبَ عَلَيْهِمْ أَوْ يُعَذِّبَهُمْ فَإِنَّهُمْ ظَالِمُونَ

*“Ko Allah Ya karbi tubansu, ko yayi musu azaba, hakika sunyi zalunci” (QS. Ali Imran, 128).*

Allah ta'ala Ya karbi tubansu kuma sunyi imani.

8. Halaccin yin alkanuti yayin saukar wasu masifu, (ba a shar'anta ba sai cikin al' amuran da Allah ya sauka dasu na masifu, kamar girgizan kasa).

9. Ambaton wadanda ake musu mummunar Addu'a cikin sallah, sunayensu da na ubanninsu. (ya halatta).

10. La'antar sanannen mutum a cikin Al'qanuti. (ya auku a farkon lamari sai aka hana).

11. Kissar Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yayin da aka saukar masa da ***“Ka yi gargadi ga danginka mafi kusanci ”.*** (sai ya zartar da umarnin Allah ).

12. Jajircewar Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- wajen aiwatar da abin da aka umarce shi, kan haka suka jingina ma sa hauka, to haka halin musulmi a yau yake, (don haka wajibi ne a yi tsayuwan daka da namijin kokari wajen da'awa da hikima ).

13. Fadin Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- wa na nesa da na kusa: "ba na iya mallaka maka wani abu wajen Allah har yace "ya ke Fadimatu; diyar Muhamma! Ba zan mallaka miki wani abu wajen Allah ba " to idan ha ya faiyace haka –A matsayinsa na shugaban Manzanni- cewa bazai iya mallakar wani abu wa shugaban matan duniya ba, kuma mutum yasan cewa duk abin da ya fada gaskiya ce, sannan ya dubi halin da wadansu kebantattun mutane suke ciki ayau, to lallai ne zai fahimci yanda akayi watsi da Tauhidi, da bakuntar wannan addinin. (abinda zai amfani mutum dangane da Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- shine: yin imani da shi, da yi masa da'a, dudda karkatuwar zuciyar mumini da tsananin kaunarsa da Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- abu ne da ba'a muzanta shi, to Amma ba ya halatta mutum ya hukuntar da tsaninin kaunarsa da son zuciyarsa kan komai, abin da ya zamo wajibi a kansa shine ya bi abin da Alqu'ani da Sunnah suka yi nuni a kai kuma lafiyayyen hankali, ingatacce, kubutacce daga shubuhohi da sha'awa ya karfafe shi ).

## [16] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

حَتَّى إِذَا فُزِّعَ عَن قُلُوبِهِمْ قَالُوا مَاذَا قَالَ رَبُّكُمْ قَالُوا الْحَقَّ وَهُوَ الْعَلِيُّ الْكَبِيرُ

***[ har sai lokacin da aka yaye tsoro daga zukatansu sai su ce: menene Ubangijinku ya ce? Suka ce: Gaskiya, kuma shi ne madaukaki, maigirma ]***.*(QS. Sabai: 23).*

● Wannan yana daga hujjoji da suke nuni cewa babu wanda ya cancanci ya zamo abokin tarayya tare da Allah, domin Mala'iku sunfi kowa kusanci da Allah in banda kebantattu daga Banu Adam, tare da haka, suna firgita yayin da suka ji maganar Allah madaukaki.

### MENENE ABUBUWAN DA IMANI DA MALAIKU YA KUNSA?

● Imani da Mala'iku ya kunshi yin imani da cewa; su wasu halitta ne da suke boye, Allah ta'ala ya halicce su daga haske, suna da a wa Allah kuma ba su saba masa, sunada rayuka da hankula da jukkuna da zukata, munyi imani da su, kuma munyi imani da abin da Allah ya ba mu labari na ayyukansu, da sifofinsu da dukkan labaran da suka zo game da su.

● {فُزِّعَ }: An tafiyar da tsoro mai firgitarwa daga zukatansu.

● {*ALLAH shi ne madaukaki kuma maigirma* }: Ahlus Sunnah Waljama'ah suna tabbatar wa Allah da: [1*] Daukakar Zati*. [2] *Daukakar Sifa*. [3] *Daukakar rinjaye kan komai da kowa*.

### Faidodi daga Ayar:

● Hakika Mala'iku suna tsoron Allah, Allah ta'ala yana cewa:

يَخَافُونَ رَبَّهُم مِّن فَوْقِهِمْ وَيَفْعَلُونَ مَا يُؤْمَرُونَ

*[**Suna tsoron Ubangijinsu daga samansu, kuma suna aikata abin da ake Umurtarsu**]. (QS. An-Nahl : 50).*

● Tabbatar da zukata wa Mala'ku; Allah Ta'ala ya ce: { *har lokacin da aka yaye tsoro daga zukatansu }*.

● Tabbatar da cewar Mala'iku jukkuna ne, ba kakai rauhaniyya ce da ba su da ciki ba, Allah ta'ala ya ce:

جَاعِلِ الْمَلَائِكَةِ رُسُلاً أُولِي أَجْنِحَةٍ مَّثْنَى وَثُلَاثَ وَرُبَاعَ

***[Mai sanya Mala'iku Manzanni, ma'abuta fuka fukai, bibbiyu, da uku uku da hur hudu** ]. (QS. Fadir :1).*

● Mala'iku sunada hankula, saboda zukata sune madaukar hankula.

● Tabbatar wa Allah Ta'ala da sifar Magana, kuma maganrsa tana alaka ne da mashi'arsa (idan yaso yayi maganar sai yayi).

● Tabbatar da cewa maganar Allah gaskiya ce, kuma gaskiyar Magana tana kasancewa ne kamar haka; [1] Gaskiya cikin labari . [2] Adalci cikin Hukunci, Allah ya ce:

وَتَمَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ صِدْقاً وَعَدْلاً

***[ Kuma Kalmar Ubangijinka ta cika, ta -fiskar- gaskiya da adalci ].***

**Dalilan Daukakuwar Zatin Allah Biyar ne a dunkule**

| Alqur'ani | Sunnah | Ijma'i | Hankali | Fidrah |
|---|---|---|---|---|

**DAALILI NA BIYU:**

فِي الصَّحِيحِ عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ڤ، عَنِ النَّبِيِّ ﷺ قَالَ: «إِذَا قَضَى اللهُ الأَمْرَ فِي السَّمَاءِ ضَرَبَتِ الْمَلَائِكَةُ بِأَجْنِحَتِهَا خُضْعَانًا لِقَوْلِهِ، كَأَنَّهُ سِلْسِلَةٌ عَلَى صَفْوَانٍ، يَنْفُذُهُمْ ذَلِكَ حَتَّى إِذَا فُزِّعَ عَنْ قُلُوبِهِمْ؛ قَالُوا: مَاذَا قَالَ رَبُّكُمْ؟، قَالُوا: الْحَقَّ؛ وَهُوَ الْعَلِيُّ الْكَبِيرُ، فَيَسْمَعُهَا مُسْتَرِقُ السَّمْعِ، وَمُسْتَرِقُ السَّمْعِ هَكَذَا بَعْضُهُ فَوْقَ بَعْضٍ - وَصَفَهُ سُفْيَانُ بِكَفِّهِ، فَحَرَفَهَا وَبَدَّدَ بَيْنَ أَصَابِعِهِ- فَيَسْمَعُ الْكَلِمَةَ فَيُلْقِيهَا إِلَى مَنْ تَحْتَهُ، ثُمَّ يُلْقِيهَا الآخَرُ إِلَى مَنْ تَحْتَهُ، حَتَّى يُلْقِيَهَا عَلَى لِسَانِ السَّاحِرِ أَوِ الْكَاهِنِ، فَرُبَّمَا أَدْرَكَهُ الشِّهَابُ قَبْلَ أَنْ يُلْقِيَهَا، وَرُبَّمَا أَلْقَاهَا قَبْلَ أَنْ يُدْرِكَهُ، فَيَكْذِبُ مَعَهَا مِائَةَ كَذْبَةٍ، فَيُقَالُ: أَلَيْسَ قَدْ قَالَ لَنَا يَوْمَ كَذَا وَكَذَا: كَذَا وَكَذَا؟ فَيُصَدَّقُ بِتِلْكَ الْكَلِمَةِ الَّتِي سُمِعَتْ مِنَ السَّمَاءِ».

Hadisi ya zo a cikin Sahihul Bukhari daga Abu Hurairah -Allah ya kara yarda a gare shi-, daga Annabi -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " **idan Allah ya hukunta wani al'amari a sama, sai Mala'iku su sauke fuka fukansu, suna masu kan kan da kai saboda maganar Allah, kamar wata sarka ce da a ke janta a kan kamfan dutse, tsoron wannan sautin yana ratsa su,** ***[ <u>har sai lokacin da aka yaye tsoro daga zukatansu</u>, sai sashi su ce ma junansu: menene Ubangijinku ya ce? Sai Su ka ce: Gaskiya, kuma shi ne madaukaki, maigirma ], sai masu satar Magana (daga alajanu) su ji, kuma masu satan magana sashinsu na saman sashe, Sufyanu –ma ruwaicin Hadisin- ya siffanta su da tafin hanunsa, ya mikar da shi, sannan ya rabe tsakanin yatsun hanunsa, idan na saman ya jiyo wata mgana sai ya isar da ita wa na kasa da shi, sannan shima ya isar ga wanda yake kasa da shi har, su isar da ita bisa harshen me sihiri ko boka, wani sa'in tauraro yana cim masa kafin ya isar da ita, wani sa'in kuma yakan isar da ita kafin tauraron ya riske shi, sai ya kara karya dari akan wannan maganar, har wadansu su ce: ai kuwa ya fada mana kaza da kaza, ranar kaza da kaza, sai su gasgata shi da wannan maganar da aka jiyo ta daga sama ].***

● صَفْوَانٍ: (**Safwan**), dutse mai karfi , sannan ga sarka a kansa yanada sauti mai karan gaske, abin nufi anan; kamanta halin da mala'iku suke shiga na tsoro yayinda sukaji maganar Allah.

● يَنْفُذُهُمْ ذَلِكَ : karan wannan sautin yana ratsa su matukar ratsawa.

### Fa'idodi daga Hadisin:

● Tabbatuwar sifar Magana ga Allah Ta'ala, da tabbatar da girman Allah, kuma duk abinda yazo daga Allah Ta'ala gaskiya ne.

● Tabbatar da fuka fukai da Magana da hankali da wa Mala'iku, kuma tsoro yana kama su, kuma kan kan da kansu wa Allah.

● Allah ya na ba da iko ma Aljanu isa zuwa ga sama, domin jarabtar mutane.

● Yawan Aljanu, kuma jikinsu ba shi da nauyi, suna tashi sama matukar tashi.

● Bokaye suna daga mafi karyan mutane, suna kara karerayi masu yawa kan abinda suka ji.

● Mai sihiri yana suranta ma wanda akayi wa sihiri sabanin gaskiya, ya zama wajibi a kiyaye su.

● **Matakan sato maganan sama daga aljanu:**

1. kafin aiko Annabi Muhammad sallallahu alaihi wasallam: satan magana ta yawaita.
2. Yayin aiko shi: an hana musu ikon sato maganar.
3. Bayan mutuwarsa: sun koma suna sato maganar, amma ba da yawa ba.

### DALILI NA UKU:

وَعَنِ النَّوَّاسِ بْنِ سَمْعَانَ ؓ قَالَ: قَالَ رَسُولُ الله ﷺ: «إِذَا أَرَادَ اللهُ تَعَالَى أَنْ يُوحِيَ بِالأَمْرِ، تَكَلَّمَ بِالْوَحْيِ أَخَذَتِ السَّمٰوَاتِ مِنْهُ رَجْفَةٌ - أَوْ قَالَ: رِعْدَةٌ - شَدِيدَةٌ، خَوْفًا مِنَ اللهِ ۵، فَإِذَا سَمِعَ ذَلِكَ أَهْلُ السَّمٰوَاتِ صَعِقُوا وَخَرُّوا لله سُجَّدًا، فَيَكُونُ أَوَّلَ مَنْ يَرْفَعُ رَأْسَهُ جِبْرَائِيلُ، فَيُكَلِّمُهُ اللهُ مِنْ وَحْيِهِ بِمَا أَرَادَ، ثُمَّ يَمُرُّ جِبْرَائِيلُ عَلَى الْمَلَائِكَةِ، كُلَّمَا مَرَّ بِسَمَاءٍ سَأَلَهُ مَلَائِكَتُهَا: مَاذَا قَالَ رَبُّنَا يَا جِبْرَائِيلُ؟ فَيَقُولُ جِبْرَائِيلُ: قَالَ الْحَقَّ، وَهُوَ الْعَلِيُّ الْكَبِيرُ، فَيَقُولُونَ كُلُّهُمْ مِثْلَ مَا قَالَ جِبْرَائِيلُ، فَيَنْتَهِي جِبْرَائِيلُ بِالْوَحْيِ إِلَى حَيْثُ أَمَرَهُ اللهُ ۵». ٢٥ ش جعفر

Daga An–Nawwas bin Sam’an –radiallahu anhu- ya ce: Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya ce: idan Allah Ta'ala ya yi nufin yin wahayi kan wani al'amari, sai yayi magana ta wahayin, sai sammai su girgiza saboda maganarsa, -ko ya ce: sai tsawa mai tsanani ya kama su- saboda tsoron Allah maigirmaa da buwaya, yayin da wadanda suke cikin sammai suka ji hakan sai su sume, kuma su fadi kasa suna sujada wa Allah, Mala'ika Jibrilu shi ne farkon wanda zai dago kansa, sai Allah ya yi masa wahayi da abin da ya so, sa'annan sai Jibrilu ya wuce ga Mala'iku, duk lokacin da ya isa ga dayan sammai sai Mala'ikunta su tambaye shi: me Ubangijinmu ya ce ya Jibrilu?

Sai Jibrilu ya ce: Ya fadi Gaskiya, Shi ne madaukai kuma maigirma, sai dukkansu su fadi kwatankwacin abin da Jibrilu ya fada, sai Jibrilu ya isar da wahayin zuwa yanda Allah maigirma da buwaya Ya umarce shi.

**Fa'idodi daga hadisin:**

- Tabbatar da irada wa Allah, iradar Allah ta kasu biyu:

1. Irada ta fiskar Shari'a da Addini (Al'iradah ash Shar'iyyah Ad-Diniyyah).
2. Irada ta fiskar Halitta da qaddarah (Al'iradah Al'kauniyyah Al'kadariyyah)

- Halittun Allah ko da sandararrun abubuwa ne suna riskar girman Allah.
- Sammai sunada adadi sananne, kuma kowace sama tana da Mala'ikunta kebantatu.
- Falalar Mala'ika Jibril, Allah ya dora masa amanar wahayi, kuma shi Amintacce ne.
- Tabbatar da Sifar Buwaya da Girma wa Allah.

**" Zuwa ga yanda Allah Madaukaki Ya umarce shi ":**

((**Jalla**)): ma'anar Aljalalu: girman da babu wani girman da ke sama da shi.

((**Azza**)): ma'anar: Al-izzatu: rinjaye da karfi, da Al'aziz yana da ma'anoni guda uku:

**Azizun:** wanda ya hanu daga cutarwar kowa.

**Azizun:** Mai ikon da babu wani mai tarayya da shi cikin ikonsa.

**Azizun**: wanda ya rinjayi kowa da komai kuma ya buwaya.

*MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Tafsirin ayar: *[ **har lokacin da aka yaye tsoro daga zukatansu -mala'iku- su ka ce: menene Ubangijinku ya ce? Su ka ce: Gaskiya**]. (QS. Saba : 23).*

2. Abin da ayar ta kunsa na hujjoji kan bacin shirka, musamman abin da ke da alaka da salihai, itace ayar da akace: ta yanke jijiyoyin bishiyar shirka daga zuci.

3. Tafsirin fadin Allah Ta'ala: *[ **Su ka ce: Gaskiya, kuma shi ne madaukaki, maigirma** ].*

4. Sababin tambayar Mala'iku game da me Allah ya ce: (tsananin tsoronsu).
5. Mala'ika Jibril ya amsa tambayarsu da fadinsa. (Yace: kaza da kaza).
6. Ya ambaci cewa farkon wanda zai dago kansa shi ne Maa'ika Jibrilu. (wannan yana nuni akan falalarsa).
7. Jibril -alaihis salam- yana fada wa dukkanin Mala'ikun da suke cikin sammai sabo da sun tambaye shi. (wannan yana nini kan matsayinsa a tsakaninsu).
8. Sumar ta game dukkan Mala'ikun da suke sama.
9. Girgizan sammai yayin maganar Allah. (domin girmama Allah).
10. Jibril -alaihis salam- shi ne wanda ya ke isar da wahayi zuwa ga yanda Allah ya umarce shi. (saboda shi Amintaccen Allah ne).
11. Hadisin ya yi nuni kan yanda Shaidanu suke satan maganar sama.
12. Siffar yanda sashensu (Shaidanu) suke hawar sashe.
13. Aika tauraro. (wadanda suke kona masu satar maganan sama).
14. Wani lokaci tauraro yakan riski Shaidanin kafin ya isar da abin da ya ji, wani lokacin kuma yakan isar zuwa kunnen majibincinsa cikin mutane kafin ya rike shi.
15. Wani lokaci boka yakan fadi gaskiya.
16. Boka yana kara karya dari akan gaskiyar da yake fada. (wannan babi ne na zurfafawa ba iyakancewa ba).
17. Kuma ba a gasgata karyarsa ba, se saboda wannan gaskiyar da aka jiyo daga sama.
18. Yanda gurbatattun zukata suke karbar karya, suna ratayuwa da karkata zuwa ga gaskiya guda, kuma suke kawar da kansu daga karya dari?
19. Sashin Shaidanu suna karbar wannan maganar daga sashensu, suna hardace ta kuma suna kafa hujja da ita. (domin itace take saka kasuwarsu tayi armashi, da dukkan abubuwan da suke fada sun kasance karya, to lallai da kasuwarsu ba tayi farashi ba).
20. Tabbatar da sifofin Allah sabanin kungir asha'ira masu kore siffofin Allah.
21. An baiyana karara cewa wannan firgitar da sumar saboda tsoron Allah ne maigirma da buwaya.
22. Suna sujada wa Allah. (domin girmama Ubangiji da tsoronsa).

## [17] BABIN CETO

**Meyasa Mawallafin -Allah Ya jikansa- ya kulla wannan Babin?**

● Saboda bayanin bacin bautar gumaka, domin kafirai suna kudurta cewa gumaka suna ceto a wajen Allah.

● Saboda Allah Ta'ala mai cikakken ilimi ne da iko, kuma mai cikakken mulki, ba Kaman sarakunan duniya ba, domin su suna bukatuwa zuwaga wadanda za su zamo musu tsani, kan wasu bukatunsu, saboda tawayar iliminsu da mulkinsu, da kuma gazawar ikonsu, se wadannan tsanin nasu su taimake su cikin bukatunsu, kuma suna yi musu karfin hali a wasu lokuta wajen ba da ceto ma wadansu ba tareda izininsu ba.

### DALILI NA FARKO:

Da fadin Allah Maigirma da buwaya:

وَأَنذِرْ بِهِ الَّذِينَ يَخَافُونَ أَن يُحْشَرُواْ إِلَى رَبِّهِمْ لَيْسَ لَهُم مِّن دُونِهِ وَلِيٌّ وَلاَ شَفِيعٌ

*“ **Kuma kayi gargadi da shi –Alqur'ani- wadanda suke jin tsoron a tara su zuwaga Ubangijinsu, ba su da wani masoyi baicin Allah kuma babu wani maiceto** ”… (QS. Al-An’am: 51).*

### DALILI NA BIYU:

Da fadin Allah ta'ala:

قُل لِّلَّهِ الشَّفَاعَةُ جَمِيعاً

***Ka ce: ceto gaba daya ga Allah yake.** (QS. Az-Zumar : 44).*

### DALILI NA UKU:

Da fadin Allah ta'ala:

مَن ذَا الَّذِي يَشْفَعُ عِنْدَهُ إِلاَّ بِإِذْنِهِ

***Wanene wanda zaiyi ceta a wajenSa face da izininSa.** (QS. Al-Baqarah : 255).*

### DALILI NA HUDU:

4. Da fadin Allah ta'ala:

وَكَم مِّن مَّلَكٍ فِي السَّمَاوَاتِ لَا تُغْنِي شَفَاعَتُهُمْ شَيْئاً إِلَّا مِن بَعْدِ أَن يَأْذَنَ اللَّهُ لِمَن يَشَاءُ وَيَرْضَى

***Akwai Malaiku da yawa a cikin sammai, cetonsu ba ya wadatar da komai, face bayan Allah yayi izini ga wanda ya so, kuma ya yarda da shi.**. (QS. An-Najm : 26).*

**DALILI NA BIYAR:**

Da fadin Allah ta'ala:

قُلِ ادْعُوا الَّذِينَ زَعَمْتُم مِّن دُونِ اللَّهِ لَا يَمْلِكُونَ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ فِي السَّمَاوَاتِ وَلَا فِي الْأَرْضِ وَمَا لَهُمْ فِيهِمَا مِن شِرْكٍ وَمَا لَهُ مِنْهُم مِّن ظَهِيرٍ (٢٢) وَلَا تَنفَعُ الشَّفَاعَةُ عِندَهُ إِلَّا لِمَنْ أَذِنَ لَهُ

***" Ka ce: " ku kirayi wadanda kuke riyawa (cewa ababen bautawa ne ) baicin Allah, ba su mallakar misalin kwayar zarra a cikin sammai, ko a cikin kasa, kuma ba su da wani tarayya a cikinsu, sannan - Allah- ba ya da wani mataimaki daga garesu, (22) sannan wani ceto ba ya amfani a wajensa face ga wanda yayi izini a gare shi "*** *(QS. Saba 22-23).*

● وَأُنذِرْ بِهِ (kuma kayi gargadi da shi) : *Gardadi shi ne: yin shela wanda yake kunshe da tsoratarwa,* abin nufi shi ne: kayi gargadi da Alqur'an.

● وَكَم مِّن مَّلَكٍ (*Da yawan mala'iku*): ma'ana mafi yawan mala'ikun da suke sama, tare da haka cetonsu ba zatayi amfanin komai ba, se bayan izinin Allah da yardarsa ga maiceton da wanda za a ceta.

● ادْعُوا (*ku kirayi*): kalu balanta ne da gajiyarwa, ma'ana: ku halarto da su ko ku roke su, bukatunku.

● مِن شِرْكٍ: Ma'ana : ba su mallakar sammai da kasa ta fiskar kadaita, kuma ba suyi tarayya da Allah cikin mallakarsu ba.

● مِّن ظَهِيرٍ (wani mataimaki) : Allah ya kore kasantuwar gumaka su zamo mataimaka.

● Duk abubuwan da masu bautan gumaka suka rataya da su , sun koru daga gumakan; domin ba su kadaita da mallakar wani abu ba, kuma ba suyi tarayya da Allah cikin mallakar ba, sannan ba su taimake shi kan wani abu ba, domin duk wanda ya taimake ka kan abu ko da baiyi tarayya da kai cikin mallakar wannan abun ba, zai zamo yanada wata kyauta a kanka, mai yiwuwa ne ka karkata zuwaga duk abin da yake so saboda wannan kyautar nasa gare ka, to idan wadannan abubuwa uku suka koru; to babu wani abin da ya saura sa ceton, kuma Allah ya riga ya bata ta, don haka ceton wadannan gumakan ba zaiyi amfani ba.

● Imam Ibnul Qayyim Allah ya jikansa ya ce: wannan ayar (QS. Saba : 22) : da wacce take biye da ita suna yanke jijiyoyin bishiyar shirka da zukata.

Ma'anar ceto: (yin tsani ma wani wajen janyo masa wani amfani ko tunkude cuta)

**KASHE KASHEN CETO:**

**Musbatah (Tabbatacce)**

Allah Ya tabbatar da ita wa kansa, kuma ana neman ta a wajensa da sharudda:

- Izinin Allah kan ceton.
- Yardar Allah ga mai ceton.
- Yardar Allah kan wanda za a ceta.

**Manfiyyah (Korarre)**

Itace wacce Al'qur'ani ya kore ta, itace wacce ake nema a wajen wanin Allah, cikin abin da babu mai iko akai sai Allah, kuma itace wacce ta kunshi babbar shirka.

**Cikin abin da bawa yake da iko akai:**

Wannan tana inganta da sharadin mai ceton ya kasance:

- Rayayye.
- Yana da iko akai.
- ya na Halarce.
- Kasancewarsa sa babi ne, kadai.

***Akwai Malaiku da yawa a cikin sammai, cetonsu ba ya wadatar da komai, face bayan Allah yayi izini ga wanda ya so, kuma ya yarda da shi.***

**Ceto kebantacce:** ya kebanta da Manzon Allah sallalahu alaihi wasallam shi kadai.

- Ceto mafi girma, Shi ne *al-maqam al-mahmud* (Matsayi abin godiya), wanda Allah ya yi masa alkawari.
- Cetonsa -Sallallahu alaihi wa sallam- ga Baffansa Abu Thalib, domin saukaka azaba gare shi.
- Cetonsa domin a bude kofofin Aljannah ga muminai.

**Ceto gamamme:** ya game Annabi sallallahu alaihi wasallam da dukkan Annabawa da Mala'ku da masu tauhidi da kananun yara:

- Ceto domin daga darajojin Mumina a cikin Aljannah.
- Ceton wadanda suka cancanci shiga wuta daga muminai domin kada su shigeta.
- Ceton wadanda suka shiga wuta daga musulmai, domin su fita daga cikin ta.

قَالَ أَبُو الْعَبَّاسِ: «نَفَى اللهُ عَمَّا سِوَاهُ كُلَّ مَا يَتَعَلَّقُ بِهِ الْـمُشْرِكُونَ، فَنَفَى أَنْ يَكُونَ لِغَيْرِهِ مِـلْكٌ، أَوْ قِسْطٌ مِنْهُ، أَوْ يَكُونَ عَوْنًا للهِ، وَلَمْ يَبْقَ إِلَّا الشَّفَاعَةُ، فَبَيَّنَ أَنَّـهَا لَا تَنْفَعُ إِلَّا لِمَنْ أَذِنَ لَهُ الرَّبُّ، كَمَا قَالَ: ( وَلَا يَشْفَعُونَ إِلَّا لِمَنِ ارْتَضَى ).

فَهٰذه الشَّفَاعَةُ الَّتِي يَظُنُّـهَا الْـمُشْرِكُونَ هِيَ مُنْتَفِيَةٌ يَوْمَ الْقِيَامَةِ، كَمَا نَفَاهَا الْقُرْآنُ، وَأَخْبَرَ النَّبِيُّ ﷺ أَنَّـهُ يَأْتِي فَيَسْجُدُ لِرَبِّهِ وَيَحْمَدُهُ - لَا يَبْدَأُ بِالشَّفَاعَةِ أَوَّلًا - ثُمَّ يُقَالُ لَهُ: «ارْفَعْ رَأْسَكَ، وَقُلْ يُسْمَعْ، وَسَلْ تُعْطَ، وَاشْفَعْ

تُشَفَّعْ».

وَقَالَ لَهُ أَبُو هُرَيْرَةَ: مَنْ أَسْعَدُ النَّاسِ بِشَفَاعَتِكَ؟ قَالَ: «**مَنْ قَالَ: (لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ) خَالِصًا مِنْ قَلْبِهِ**»، فَتِلْكَ الشَّفَاعَةُ لِأَهْلِ الإِخْلَاصِ بِإِذْنِ اللهِ، وَلَا تَكُونُ لِمَنْ أَشْرَكَ بِاللهِ.

وَحَقِيقَتُهُ: أَنَّ اللهَ سُبْحَانَهُ هُوَ الَّذِي يَتَفَضَّلُ عَلَى أَهْلِ الإِخْلَاصِ، فَيَغْفِرُ لَهُمْ بِوَاسِطَةِ دُعَاءِ مَنْ أَذِنَ لَهُ أَنْ يَشْفَعَ لِيُكْرِمَهُ، وَيَنَالَ الْـمَقَامَ الْـمَحْمُودَ.

فَالشَّفَاعَةُ الَّتِي نَفَاهَا الْقُرْآنُ مَا كَانَ فِيهَا شِرْكٌ، وَلِهَذَا أَثْبَتَ الشَّفَاعَةَ بِإِذْنِهِ فِي مَوَاضِعَ، وَقَدْ بَيَّنَ النَّبِيُّ ﷺ أَنَّهَا لَا تَكُونُ إِلَّا لِأَهْلِ التَّوْحِيدِ وَالإِخْلَاصِ»، انْتَهَى كَلَامُهُ.

Abul Abbas ya ce: *(( Ubangiiji Allah Ya kore dukkan abubuwan da mushrikai suka rataya da su daga waninsa, ya kore mallakar sammai da kasa daga waninsa, kamar yanda ya kore mallakar wani bangare cikinsu, ko taimakonsa wajen halittansu, Babu wani abinda ya saura face ceto, Allah Ya bayyana cewa ceton wani ba zaiyi amfani ba face wanda Allah yayi izini gare shi, kamar yanda Allah yace:* ***[ kuma ba su yin ceto face ga wanda Allah ya yarda ]*** (QS. Al-Anbiya : 28).

Wannan ceton da mushrikai suke zato a ranar tashin alkiyama hakika Allah ya kore shi cikin Alqur'ani, kuma Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya bada labarin cewa zaizo yayi sujada wa Allah sannan ya yabe shi -ba ceto yake fara gabatarwa ba- sannan sai Allah yace da shi: " **daga kanka, ka fada, za a ji maganarka, kuma ka tambaya za a baka, kuma ka yi ceto a baka** "

( Bukhari da Muslim suka ruwaito).

Abu Hurairah -Allah Ya kara yarda a gare shi- ya tambayi Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam: ( wanene mafi rabautan mutane da cetonka? Sai ya ce: " **Wanda ya ce: ( la'ilaha illallahu), ya na me ikhlasi a cikin zuciyarsa** ", wannan ceton na masu ikhlasi ne da izinin Allah, banda masu hada Allah da wani (Masu shirka).

Hakikanin ceto: Kyautar Allah ce ga masu Tauhidi, Allah zai gafarta mu su sanadin addu'ar wanda Allah Ya yi ma sa izinin ceto domin Ya Karrama shi, kuma ya ba shi matsayi abin godiya.

Ceton da Alqur'ani ya kore shi ne wanda ya kunshi ma'anar shirka, don hakane Allah Ya shardanta izininsa dangane da ceto a wajaje da dama cikin Alqur'ani, kuma Annabi -sallallahu alaihi wasallam- ya bayyana cewa: Babu wanda zai samu cetonsa sai ma'abota tauhidi da ikhlasi kadai )). Karshen maganar Abul Abbas.

## *MATSALOLIN BABIN:*

1. Tafsirin ayoyin babin. (ayoyi biyar).

2. Sifar ceto korarre. (shi ne ceton da ya kunshi shirka).

3. Sifar ceto tabbatacce (shi ne ceton masu tauhidibayan izinin Allah maigirma da daukaka da yardarsa kan mai ceton da wanda za a ceta).

4. Ambaton babban ceto, shi ne: Al Maqam Al Mahmud (Matsayi abin yabo). (wannan ceton ga dukkan wadanda suke filin kiyama ne domin ayi musu hisabi ).

5. Sifar abin da Manzon Allah salallahu alaihi wasallam ya keyi, ba ya fara yin ceto har sai ya yi sujada wa Allah, idan Allah ya yi masa izini sai ya yi ceton. (wannan yana nuni akan girman Allah ta'ala, da cikar ladabin Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ).

6. Wanene mafi rabautan mutane da ceton? (sune ma'abota tauhidi da ikhlasi).

7. Kuma wanda ya mutu a kan shirka ba ya samun ceton.

8. Bayani akan hakikanin ceto. (Allah maitsarki shi ne mai yin falala ga masu ikhlasi, sai ya gafarta musu ta hanyar adduar wanda Allah ya yi izini a gare shi da yin ceton, domin Allah Ya karrama shi, kuma ya dace da matsayi abin godewa.

## [18] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:
## *(Lallai ne kai ba ka shiryar da wanda ka so).*

### DALILI NA FARKO:

Fadin Allah ta'ala:

إِنَّكَ لَا تَهْدِي مَنْ أَحْبَبْتَ وَلَكِنَّ اللَّهَ يَهْدِي مَن يَشَاءُ وَهُوَ أَعْلَمُ بِالْمُهْتَدِينَ (٥٦)

***(Lallai ne kai baka shiryar da wanda kake so, sedai Allah ne kadai yake shiyar da wanda yake so, kuma shi ne mafi sanin masu shiriya.*** *(QS. Al-Qasas : 56).*

### DALILI NA BIYU:

فِي الصَّحِيحِ عَنِ ابْنِ الْمُسَيَّبِ، عَنْ أَبِيهِ قَالَ : لَمَّا حَضَرَتْ أَبَا طَالِبٍ الْوَفَاةُ، جَاءهُ رَسُولُ اللهِ ﷺ، وَعِنْدَهُ عَبْدُ اللهِ بْنُ أَبِي أُمَيَّةَ وَأَبُو جَهْلٍ، فَقَالَ لَهُ: «**يَا عَمِّ، قُلْ: لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ، كَلِمَةً أُحَاجُّ لَكَ بِهَا عِنْدَ اللهِ**»، فَقَالَا لَهُ: أَتَرْغَبُ عَنْ مِلَّةِ عَبْدِ الْمُطَّلِبِ؟ فَأَعَادَ عَلَيْهِ النَّبِيُّ ﷺ، فَأَعَادَا، فَكَانَ آخِرَ مَا قَالَ: هُوَ عَلَى مِلَّةِ عَبْدِ الْمُطَّلِبِ، وَأَبَى أَنْ يَقُولَ: لَا إِلَهَ إِلَّا اللهُ، فَقَالَ النَّبِيُّ ﷺ: «**لَأَسْتَغْفِرَنَّ لَكَ، مَا لَمْ أُنْهَ عَنْكَ**»، فَأَنْزَلَ اللهُ: ( مَا كَانَ لِلنَّبِيِّ وَالَّذِينَ آمَنُواْ أَن يَسْتَغْفِرُواْ لِلْمُشْرِكِينَ )، وَأَنْزَلَ اللهُ فِي أَبِي طَالِبٍ: ( إِنَّكَ لَا تَهْدِي مَنْ أَحْبَبْتَ وَلَكِنَّ اللَّهَ يَهْدِي مَن يَشَاءُ وَهُوَ أَعْلَمُ بِالْمُهْتَدِينَ

Ya zo cikin Sahihul Bukhari daga Ibnul Musayyib daga babansa ya ce: yayin da ajalin Abu-Dalib yazo, Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya tafi zuwa gare shi, sai ya tad da Abdullahi dan Abu Umayyah, da Abu Jahal a wajensa, sai Manzon Allah ya ce da shi: " Ya Baffana, kace la'ilaha illallahu, kalma ce wacce zan b aka kariya da ita a wajen Allah ", sai Abu-Dalib ya ce ma sa: kana kyamar addinin Abdul mudallib ko? Sai Annabi sallallahu Alaihi wasallam ya nanata masa, sai Abu-Dalib ya nanata abin da ya fada a farko, karshen Abin da ya tabbatar shi ne: yana kan Addinin Abdul Muddalib, sai yaki fadin La'ilaha illallah, sai Annabi sallallahu alaihi wasallam ya ce: " lallai ne zan nema maka gafara matuka ba' a hana nib a ", sai Allah maigirma da buwaya Ya saukar da ayar: [ **Ba ya kakasancewa ga Annabi da muminai su nemi gafara wa mushrikai** ], kuma Allah Ya saukar cikin lamarin Abi dalib: **[*Lallai ne kai baka shiryar da wanda ka so, amma kuma Allah yana shiyar da wanda yake so,*].**

Kashe kashen Shiriya:

Hidayatut taufik (Shiriya ta gamda katar):
Babu mai mallakarta sai Allah:
إِنَّكَ لَا تَهْدِي مَنْ أَحْبَبْتَ
***Lallai ne kai ba ka shiryar da wanda ka so.***

Hidayatud dilalah wal'irshad (Shiriya ta nuni da fadakarwa ):
Manzon allah sallallahu alaihi wasallam yana mallakarta. Allah Allah Ya ce:
وَإِنَّكَ لَتَهْدِي إِلَى صِرَاطٍ مُّسْتَقِيمٍ
*Lallai ne kai kana shiryarwa zuwa ga hanya madaidaiciya.*

● Mawallafin ya kawo shi ne domin bayanin cewa babu mutumin da ya isa ya shiryar da wani shiriya ta gamdakatar kuma ya aikata abubuwan da Allah yake so.

● **Mas'ala:** me ya sa Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam yake son Abu Dalib alhali shi ba musulmi ba ne? **Amsa;** ma'anar maganan zai iya kasancewa dayan abubuwa uku: [1] Annabi ya so shiriyarsa ne kan imani ba wai ya so shi a karan kansa ba, (wannan shi ne mafi karfin zantuka ). [2] Ko kuma soyayya ce irin ta dabi'a, halal ne, [3] Ko kuma ya so shi ne kafin a hana soyayya ga kafirai.

● **"Manzon Allah ya zo masa"** wannan hadisin ya nuna cewa mustahabbi ne a ziyarci kafiri idan ana fatar shiriyarsa.

● **"Ya Baffah"**: ya kira shi da wannan alkunyar da take nuna tausayinsa gare shi, wannan yana daga hikima cikin da'awa .

● Yaya zamu daidata sakanin; wannan hadisin, da maganar malamai cewa; Sunnah ce a lakkana wa mutumin da yake shimfidin mutuwa -kalmar shahada- ba tare da ance masa " kace ba"? amsa: Abu Dalib Kafiri ya kasance ne, to idan akace masa kace –la'ilaha illallahu- sai yaki fada, to shi ya tabbata cikin kafircinsa, yin talkini da wannan sigar ba zai cutar da shi ba, sabanin musulmi da yake cikin hadari, akwai yiwuwar yi masa talkini da hakan ya cutar da shi.

● **" Mutuwa ta zo masa"**: Ma'ana: [1] alamun mutuwa sun bayyana gare shi, amma dai mutuwar ba ta sauka ba tukkunna, akan haka, idan ya tuba za a karbi tubansa, Magana ta biyu kuma ba za a karbi tubansa ba, Saboda fadin Allah:

وَلَيْسَتِ التَّوْبَةُ لِلَّذِينَ يَعْمَلُونَ السَّيِّئَاتِ حَتَّى إِذَا حَضَرَ أَحَدَهُمُ الْمَوْتُ قَالَ إِنِّي تُبْتُ الآنَ

***[Kuma ba tuba ba ce ga wadanda suke aikata munanan aiki har idan mutuwa ta halarci dayansu sai ya ce: lallai ne ni na tuba a yanzu ].*** *(QS An-Nisa'i : 18).*

Wannan ayar da dace da hadisin babin.

[2] Saboda fadin Annabi: “ **Kalmace wanda zan ba ka kariya da ita** ”, bai yanke shakku ba kan amfanin Kalmar gare shi.

[3] Wannan lamari ne wanda ya kebanci Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam, gameda ceton baffansa tare da kafircinsa.

● Al-Musayyib da Abdullah bin Abi Umayyah sun musulunta -Allah Ya kara yarda a gare su- sabanin Abu Dalib da Abu Jahl.

● “ Shi ya na kan addinin ”: an sanya lamirin " shi " Maimakon fadin “ Ni ”, wannan yake nuni kan tsananin tsayuwar maruwata hadisin wajen tace tauhidi.

***MATSALOLIN BABIN:***

1. Tafsirin fadin Allah: *[ Lallai ne kai baka shiryar da wanda ka so, amma kuma Allah yana shiyar da wanda yake so]. (QS. Al-Qasas : 56).*

2. Tafsirin fadinsa: [ Ba ya kasancewa ga Annabi ] *Al-ayaa. (QS. At Tauba, 113).* (Haramun ne bayyana bakin ciki saboda mutuwar kafirai, da yi musu ta'aziyya ).

3. Mas'ala Maigirma; Tafsirin fadinsa: " kace: la'ilaha illallahu ", wannan sabanin abin da masu da'awar ilimi suke rayawa ne (don haka yaki fadan kalmar).

4. Hakika Abu Jahal da wadanda suke tare da shi sunsan manufar Annabi -sallallahu alaihi wasallam- yayin da ya nemi wani da ya ce: (la'ilaha illallahu); Allah wadaren duk wanda Abu Jahal ya fi shi sanin ginshikin musulunci.

5. Dogewar Annabi sallallahu alaihi wasallam da kaiwarsa matuka wajen ganin Baffansa ya shiga musulunci. [1] Saboda kusancinsa. [2] Da kuma kyautatwarsa ga Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam da Musulunci, lallai wannan abin yabawa ne, tareda kasancewarsa mailaifi bias kafircinsa.

6. Raddi kan wanda yay i da'awar musuluntar Abdul Mudallib, da magabatansa. (Addininsu shi ne: kafirci).

7. Kasancewar Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya nema masa gafara amma Allah bai gafarta masa ba, hasali ma an hana shi ya roka masa gafaran daga baya. (Dukkan al'amura suna hanun Allah).

8. Cutarwar abokan banza ga mutum.

9. Cutarwar girmama magabata da Manya. (idan suka kasance akan bata)

10. Shubuhar mabarnata, saboda kafa hujjar abu Jahal cikin wannan lamarin da ita.

11. Hadisin yana nuni kan cewa aiyukan da mutum ya mutu a kansu da su Allah yake masa sakayya, da Abu Dalib ya fadi (la'ilaha illallahu da), da ta amfane shi.

12. Girmar wannan shubuhar cikin zuciyarsu, kissar ta nuna cewa ba su yi jayayya da shi ba seda ita, tareda jajircewar Annabi sallallahu alaihi wasallam da nanatawarsa wajen kiran Baffansa, sun tsaya ne a kan wannan shubuhar saboda girmanta da bayyanarta cikin zuciyarsu. (wato: shubuhar girmama magabata da manya).

## Jarabawa kashi na uku ( Babuka 4)

[1] Ambaci babukan wannan bangaren da sababin da kulla kowani babi:

| No | Sunan babin | Sababin kulla babin |
|---|---|---|
| 1 | | |
| 2 | | |
| 3 | | |
| 4 | | |

| [2] Bayyana hukuncin aiyuka masu zuwa ta hanyar zabar daya daga hudun: (1) Halal (2) Bai halatta ba (3) Babban Shirka (4) Mustahabbi/sunnah. | | | |
|---|---|---|---|
| Neman ceto daga mutattu. | | Tawassuli da alfarman Annabi Alaihis Salam. | |
| Gaishe da Mushriki idan ba shida lafiya. | | Talqini ga wanda yake shirin mutuwa. | |
| La'antar mutum sananne (mu'ayyan). | | Tsine wa dukkan kafirai | |

[3] Sanya alamar (☒) a wajen da ya dace, ko ka/ ki cike gurbin .

1. Kashi na uku na Kitabut Tauhid shi ne:
☐ Tafsirin tauhidi. ☐ Bacin bautar wanin Allah.
2. Kashi na uku ya kunshi:
☐ Babuka biyar ☐ Babuka hudu ☐ Babuka shida.
3. Tambayar da tazo cikin fadin Allah Ta'ala: أَيُشْرِكُونَ [shin suna shirki da….]? Tambaya ce ta inkari da zargi ga mushrikai? ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
4. Allah ya bayyana gajiyawa da bacin bautar gumaka cikin fadinsa: أَيُشْرِكُونَ [shin suna shirki da… ]? *berhala-berhala yang tak dapat menciptakan sesuatupun?...*} dengan: ☐ fiskoki 4 ☐ Fiskoki uku.
5. Fadin Allah Ta'ala: {*Wadanda kuke kiransu koma bayan Allah* ), wannan addu'a ce ta: ☐ ibadah ☐ Ta mas'alah ☐ yakunshi duka biyun.
6. Ba mu debe tsammani ma kowa daga rahamar Allah koda kuwa mai sabo ne, sedai kadai jagororin kafirci. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

7. Fadin mawallafin cewar wadanda ake mummunan addu'a akansu kafirai ne, abin da yake nufi shi ne: sanarwa dangane da kafircinsu. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
8. Fadin mawallafin "قنوت سيِّد المُرسَلين (Alqanutin shugaban Manzanni)", manufarsa: ☐ Halaccin Alqanut. ☐ Babu wani daga cikin wannan al'ummah wanda yafi Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam da Sahabbansa kusanci da Allah, tareda haka suna komawa ga Allah su fake da shi.
9. Ya ya za muyi mummunar addu'a kan kafurai ?............................................................. ………………………………………….
10. فُزِّعَ (kwaranyewa), An tafiyar da tsoro daga zuci:
☐ mai firgitarwa ☐ mai wanzuwa daga zukatansu.
11. Kasancewar "Boka yakan kara karya dari akan gaskiya daya ", wannan babi ne: ☐ *Mubalaga* ( Zurfafawa ) ☐ iyakancewa ne.
12. Fadin Allah ta'ala: [ Akwai da yawan Mala'iku a cikin sammai ]. *(QS. An-Najm : 26).* Sharuddan ceto guda uku ne:

☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
13. Dukkan ceton da ya kunshi shirka, to wannan ceton ya zamo:
☐ korarre ☐ shirka ne ☐ duk biyun.
14. Ceto ba ta nufin taimakon Allah cikin wani abu daga abun da za a yi ceto cikinsa, wannan abu ne mara yiwuwa ☐ Haka ne ☐ kuskure ne. iyakan manufofin ceto sune : ☐ Karramcin Allah ga wanda ya masa izinin ceton ☐ fa'idar wanda za a ceta ☐ duka biyun.
15. Ayar da akace tana yanke jijiyoyin bishiyar shirka daga zuci itaace: …………… ………………………………………………………………………………………..
16. Hidayah tabbatacciya itace: ………………………………………………………… Hidayah korarriya itace:..…………………………………………………………………..
17. Ma'anar Ayar: [ Lallai ne kai baka shiryar da wanda kaso ], ma'ana wanda kakeson: ☐ Shiriyarsa ☐ soyayya ce ta dabi'a ☐ kafin ayi hani kan soyayya ga kafirai ☐ duka.
18. "Yayin da Abu Dalib ya yi kusan mutuwa ", Ma'ana: ………………………………………ko:……………………………………………………….
19. Addinin Abdul Mudallib shi ne:
☐ Shirka da bautar gumaka ☐ Kiristanci ☐ Majusanci.
20. أُحَاجُّ (Zan baka kariya ), ma'ana ☐ Zan bada shaida a gaban Allah cewa ka fadeta ☐ Zanyi maka jayayya da husuma a gaban Allah don baka kariya.
21. Sunnah ce a laqqana Kalmar Shahada ga wanda yake dab da mutuwa, da lafazin: (kace: laa ilaaha illallahu) dalili kan haka shi ne: fadin Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam wa Baffansa. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
to yaya zamu daidaita tsakanin aikin Annabi da fadin malamai cewa: (Sunnah ce: a laqqana Kalmar Shahada ga wanda yake dab da mutuwa ba tare da ance masa: kace: ba? ) …………………………………………………………………………………………

………………………………………………………………………………………………

22. Meyasa maruwaicin hadsin ya ce: " shi, yana kan Addinin .." baice: ( Ni ina kan addinin ba?)………………………………………………………………………………………

………………………………………………………………………………………………

23. Kwadayin Annabi -sallallahu alaihi wasallam- bisa Musuluntar baffansa Abu Dalib da sababin : ☐ kusancinsa ☐ kyautatawar sa gare shi da musulunci ☐ duka biyun.

24. Girmama magabata da manya abin zargi ne.

☐ A sake. ☐ idan suka kasance a kan bata.

[4] Cike kashe kashen ceto:

………………………………
Allah ya tabbatar da shi wa kansa, ana neman sa ne wajen Allah da sharudda:
- ……………………………
- ……………………………
- ……………………………

…………………………
Shi ne ceton da Alqur'ani ya kore, itace wanda
…………………… ..
…………………………
Hukuncinsa Shi ne:
……………………..
……………………..

……………………………..:
Yana inganta da sharadi:
- …………………………..
- …………………………..
- …………………………..
- …………………………..

Ceton da suka kebanta da Annabi Sallallahu alaihi wasallam, daga ciki:
- ……………………………………..........
……………………………………………..
- ……………………………………..........
……………………………………………..
- ……………………………………..........
……………………………………………..

Ceto gamamme ya kunshi…………………... Daga ciki:
- ……………………………………..........
……………………………………………..
- ……………………………………..........
……………………………………………..
- ……………………………………..........
……………………………………………..

## Na Hudu: Sababin kafircin Banu Adam ( Babuka 4)

● Mawallafin ya kulla wannan babin ne domin bayanin sabubban kafirci saboda mu nuisance su, da kuma bayar da amsa kan meyasa wadansu mutane suke aukawa cikin kafirci? Ya bada amsa ne cikin babuka uku masu zuwa, sannan a babi na hudu ya bayyana cewa: Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya toshe duk wata kofar da zata iya kaiwa zuwa ga shirka.

## [19] BABIN (ABIN DA YA ZO KAN SABABIN KAFIRCEWAR BANU ADAM DA BARINSU ADDINI; SHINE: WUCE IYAKA CIKIN SALIHAN BAYI ).

● Wannan shi ne mafi girman hadari cikin sabubban kafircewar Bani Adam, kuma shi ne farkon shirka da ta faru a bayan kasa: (Shubuhar wuce iyaka cikin salihan bayi).

**DALILI NA FARKO:**

Da Fadin Allah Ta'ala:

يَا أَهْلَ الْكِتَابِ لاَ تَغْلُواْ فِي دِينِكُمْ

*[ **Ya ku mutanen littafi kada ku zurfafa a cikin addininku** ] (QS. An-Niisa : 171).*

**DALILI NA BIYU:**

فِي الصَّحِيحِ عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ﭬ -فِي قَوْلِهِ تَعَالَى: ( وَقَالُوا لَا تَذَرُنَّ آلِهَتَكُمْ وَلَا تَذَرُنَّ وَدّاً وَلَا سُوَاعاً وَلَا يَغُوثَ وَيَعُوقَ وَنَسْراً )-؛ قَالَ: (هٰذه أَسْمَاءُ رِجَالٍ صَالِحِينَ مِنْ قَوْمِ نُوحٍ، فَلَمَّا هَلَكُوا أَوْحَى الشَّيْطَانُ إِلَى قَوْمِهِمْ؛ أَنِ انْصِبُوا إِلَى مَجَالِسِهِمُ الَّتِي كَانُوا يَجْلِسُونَ فِيهَا أَنْصَابًا، وَسَمُّوهَا بِأَسْمَائِهِمْ، فَفَعَلُوا، وَلَمْ تُعْبَدْ، حَتَّى إِذَا هَلَكَ أُولَئِكَ وَنُسِيَ الْعِلْمُ عُبِدَتْ)،

وَقَالَ ابْنُ الْقَيِّمِ: (قَالَ غَيْرُ وَاحِدٍ مِنَ السَّلَفِ: لَمَّا مَاتُوا عَكَفُوا عَلَى قُبورِهِمْ، ثُمَّ صَوَّرُوا تَمَاثِيلَهُمْ، ثُمَّ طَالَ عَلَيْهِمُ الأَمَدُ فَعَبَدُوهُمْ).

Hadisi ya tabbata cikin Sahihul Bukhari, daga Ibnu Abbas -Allah ya kara yarda a gare shi- game da fadin Allah Ta'ala: [ **kuma sukace: kada ku bar gumakanku, kuma kada ku bar " Wadda", kuma kada ku bar "Suwa'a" kuma kada ku bar " Yagusa " da "Ya'uqa " da "Nasra"]** *(QS. Nuh : 23);* ya ce: "Wadannan sunayen wadansu mutane ne salihai cikin mutanen Annabi Nuhu –Alaihis Salam- bayan mutuwarsu Shedan ya yi wahayi zuwa ga jama'arsu cewa; ku kakkafa mutum mutumi a wajajen zamamsu, kuma sanya musu sunayensu, sai suka aikata hakan,

ba a bautata musu ba sai bayan mutuwan wadannan mutanen, kuma bayan an mance ilimi sai aka bauta musu ".

Ibnul Qayyim -Allah ya jikansa- ya ce: (mutane masu yawa daga maabata sun fadi cewa: yayin da wadannan salihan suka mutu, sai -jahilai- suka lizimci kaburburansu, sannan sukayi mutum mutuminsu, bayan tsawon zamani kuma sai aka samu wadanda suka bauta musu ).

● { *Ahlul Kitab*}: Sune Yahudawa; littafinsu: **Attaura,** da Nasara; littafinsu; **Injila**.
● {*Kada ku zurfafa cikin addininku* }: Ma'ana kada ku ketare iyaka wajen yabo ko suka, Nasara sun wuce iyaka cikin lamarin Isah -Alaihis Salam- ta fiskar yabo har sukace: dan Allah ne, kuma dayan ukun, Yahudu sun wuce iyaka wajen sukarsa.
● هَلَكُوا: yayin da suka mutu.
● أَوْحَى الشَّيْطَانُ : Shedan ya sanya musu was wasi.
● انْصِبُوا (ku kakkafa): duk abin da ake iya kafawa na sanda ko dutsi, domin ya fada musu cewa: duk lokacin da kuka gan su zaku samu nashadi cikin ibadarku, da haka suka saba wa Shari'a, domin niyya ita kadai bata wadatarwa, wajibi ne aiki ya zamo ya dace da Shari'a, manufarsu mai kyau ne, amma aikinsu batacce.
● حَتَّى إِذَا هَلَكَ أُولَئِكَ ( bayan mutuwarsu) : Wadanda suka kakkafa gumaka da hotunan wadannan bayin.
● Mutanen da suka rigayi Annabi Nuhu sun aikata abubuwa uku::
1. صَوَّرُوا تَمَاثِيلَهُمْ (Sun yi hotunan Salihansu ), Wannan yana nuni akan hadarin hotuna da mutum mutumi.
2. عَكَفُوا Sun lizimci kaburburan salihansu.
3. "Bayan tsawon lokaci" : Ma'ana bayan zamanin Annabta ya shude, aka rasa masu ilimi, sai babbar shirka ta auku cikikin wadannan mutanen, suka bauta ma wadannan hotunan baicin Allah, wajibi ne a kula da ilimi da aiki domin kada irin wadannan abubuwa su ringa aukuwa cikin al'ummah.

**Barnar wuce iyaka a Addini:**

1. Ana daga wanda aka wuce iyaka cikinsa sama da matsayinsa idan ta wajen yabo, kuma sauke shi kasa da matsayinsa idan suka ce.

2. Sanadi ne na bautar wanda akayi guluwwi -wuce gona da iri- cikinsa.
3. Yana katange babin girmama Allah taala, domin zuciya idan bata shagaltu da gaskiya ba to zata shagaltu da karya.
4. Wanda aka wuce iyaka cikinsa idan rayayye ne, to zai rudu da kansa, wannan kuma mafsada ce da take bata wanda aka wuce iyaka akansa, idan yabo ne, kuma tana wajabta adawa da bala'i idan suk ce.

**Kashe kashen mutane gameda Salihan bayi**

| Wadanda suka wuce iyaka a babin yabo: | Wadanda suka wuce iyaka ta fiskar suka: | Tsaka tsakiya: |
|---|---|---|
| Kamar Kirista tareda Annabi Isah -Alaihis Salam-. | Kamar Yahudawa tare da Annabi Isah -Alaihis Salam-. | Ba su wuce iyaka ba, kuma ba su yi sakaci ba, sune Ahlus Sunnah. |

**DALILI NA UKU:**

وَعَنْ عُمَرَ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ  قَالَ: «**لَا تُطْرُونِي كَمَا أَطْرَتِ النَّصَارَى ابْنَ مَرْيَمَ**، إِنَّمَا أَنَا عَبْدٌ، فَقُولُوا: عَبْدُ اللهِ وَرَسُولُهُ»، أَخْرَجَاهُ.

Daga Umar -Allah Ya kara yarda a gare shi- ya ce: Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: "Kada ku wuce iyaka wajen yabona, **kamar yanda kirista suka wuce iyaka wajen yabon Dan Maryam** -Alaihis Salam-, iyaka dai, Ni Bawa ne, don haka sai kuce bawan Allah kuma Manzonsa " ( Bukhari da Muslim suka rawaito).

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ๏ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ : «إِيَّاكُمْ وَالْغُلُوَّ، **فَإِنَّمَا أَهْلَكَ مَنْ كَانَ قَبْلَكُمُ الْغُلُوُّ**».

Daga Abdullahi dan Abbas Allah Ya kara yarda a gare su, ya ce Manzon Allah sallallahu Alaihi wasallam ya ce: kashedinku da wuce gona da iri, **iyaka dai, abin da ya halaka wadanda sukazo gabanninku shi ne wuce gona da iri** ”

**DALILI NA BIYAR:**

وَلِـمُسْلِمٍ عَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ  قَالَ: «**هَلَكَ الْـمُتَنَطِّعُونَ**»، قَالَـهَا ثَلَاثًا.

A cikin Sahihu Muslim a riwayar Abdullahi dan Mas'ud; Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya ce: **" Masu zurfafawa sun halaka "**, ya nanata hakan so uku.

● **"لَا تُطْرُونِي ", (الإطراء): (Al idra'i):** Zurfafawa wajen yabo, abin da yayi kama da guluwwin Nasara ko kusa da shi.

● **" Bawan Allah kuma Manzonsa":** Wadannan siffofi guda biyu sune siffofi mafi girma kuma mafi dacewa da matsayin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-.

● **الْغُلُوّ:** Shine: ketare iyaka wajen yabo da ibada da kuma aiki.

● Cikin me guluwwi ya ke halakarwa ? [1] Cikin addini. [2] Da jikkuna.

● Ghuluwwi yanada kashe kashe masu yawa; Guluwwi cikin Aqida da ibada da da Mu'amala, da al'adu, Addinin Allah tsaka tsakiya ne, tsakanin mai wuce iyaka cikinsa da mai sakaci.

● **الْمُتَنَطِّعُونَ:** (**Al Mutanaddi'u**): Shine mai zurfafawa da wuce gona da iri wajen kallafa fasaha cikin Magana da aiyuka, saboda abin da ke ciki na ruduwa da kai, zurfafawa cikin addini yana daidai da guluwwi, sababi ne daga sabubban halaka.

***MATSALOLIN BABIN:***

1. Duk wanda ya fahimci wannan babin da babuka biyu bayansa, to bakuntar addinin musulunci zata bayyana gare shi, kuma zaiga abin mamaki cikin ikon Allah, yanda yake jujjuya zukata.

2. Sanin farkon shirka da ta auku a kan kasa, ta auku ne saboda shubuhar girmama salihai.

3. Sanin abu na farko da aka canza addinin Annabawa (shine: shirka), menene sababin hakan? (Wuce iyaka gameda salihan bayi). Tare da sanin cewa Allah ta'ala shine wanda ya aiko wadannan manzanni.

4. Imanin wadansu da bidio'i, tareda cewa dukkan Shari'oi da Fitdrah suna raddinsu.

5. Sababin haka shine cakuda gaskiya da karya, abu na farko shine: son salihai, abu na biyu kuma shine: abin da wadansu ma'abota ilimi da addini suka aikata da kyakkyawar manufa, wadanda suka zo daga bayansu sai suka zaci sabanin abinda magabatansu suke nufi. (Duk wanda yakeson karfafa addininsa ta hanyar bidi'a, to lallai ne yasan cewa babu alheri cikin bidi'oi ko kadan ).
6. Tafsirin ayar Suratu Nuh. (akwai dalili cikinta cewa mutane suna wasici da bata).
7. Gane dabi'ar dan Adam, yanda gaskiya take raguwa daga zuciyarsa karya take karuwa, (sai wanda Allah yayi masa baiwa ).
8. Ciki akwai dalili kan abinda aka cirato daga magabata cewa: bidi'a tana kaiwa ga kafirci. (domin sabubban kafici suna yawa)

9. Shaidan yasan abin da bidi'a ke iya kaiwa gare shi, koda kuwa niyyar me aikata bidi'ar niyya ce mai kyawu.

10. Sanin gamammiyar qa'ida, itace: hani kan wuce iyaka, da barnar da wuce iyakan yake iya jawowa.

11. Cutarwar lizimtar kabari, da niyyar aikata kyakkyawan aiki. (tana auka mutane ga bautar ma'abota kabarin).

12. Gane hikimar hani kan rikan mutum mutumi, da hikimar kawar da su. (domin toshe kofofin shirka).

13. Girmar sha'anin wannan qissar, da tsananin bukatuwa zuwa ga saninta, da gafalar mutane daga gareta.

14. Mafi girman abin mamaki, mutane suna karantata cikin litattafan tafsiri da hadisi, kuma sun fahimci ma'anar zancen, amma Allah ya sanya shamaki a zuciyarsu har sukayi imani da cewa aikin mutanen Annabi Nuhu shine mafificin ibada, kuma sukayi imani da cewa abin da Allah da Manzonsa suka hana, -na ridda da makamancinsa- shine kafircin da yake halarta jinin mutum da dukiyarsa, (amma wannan abin da sukeyin Allah da Manzonsa basu hana ba ballantana su zamo kafirci).

15. Ya bayyana karara cewa ba komai suke nema wajen wadannan salihan ba face cetonsu, (tare da hakan, sun auka cikin shirka).

16. Zatonsu cewa wadannan masanan da suka ajiye mutum mutimin wadannan salihan sunyi hakan domin (neman cetonsu ne, hakika wannan zato ne mai muni).

17. Bayani muhimmi, Fadin Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallam: " kada ku zurfafa wajen yabona kamar yanda Nasara suka suka zurfafa wajen yabon Isa dan Maryam " - Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya isar da sako isarwa mabayyani. (yayi hani wajen zurfafawa da wuce iyaka cikin yabo, kuma hakika wasu daga cikin wannan al'ummar sun auka cikin abin da aka hana, mafi munin aukawa ).

18. Nasiha a garemu dangane da halakar masu zurfafawa. (domin mu kiyaya).

19. Bayani karara cewa ba su bauta musu ba, har sai da aka mance ilimi, wannan dalili ne kan muhimmancin ilimi da illar rasa shi.

20. Sababin rasa ilimi shine mutuwar Malamai, (wannan yana cikin manyan sabubba, hakanan rafkana da kawar da kai daga ilimin, da shagaltuwa da lamurran duniya, da rashin damuwa da ilimin ).

## [20] BABIN ABIN DA YAZO NA KAUSASAWA A KAN WANDA YA BAUTA WA ALLAH A WURIN KABARIN MUTUMIN KWARAI, TO YAYA KUMA IDAN YA BAUTA MASA?

Mawallafn ya kulla wannan babin nedon ya bayyana maka bakuntar wannan addinin da yanda mutane sukayi watsi da tauhidi, da bayanin abin da yazo na hanin bautar Allah ta'ala a wajen kaburburan salihan bayi, domin kada su zamo wasila zuwa ga shirka da Allah ta'ala.

### DALILI NA FARKO:

فِي الصَّحِيحِ عَنْ عَائِشَةَ ف؛ أَنَّ أُمَّ سَلَمَةَ ذَكَرَتْ لِرَسُولِ اللهِ ﷺ كَنِيسَةً رَأَتْهَا بِأَرْضِ الْـحَبَشَةِ، وَمَا فِيهَا مِنَ الصُّوَرِ، فَقَالَ: «أُولَئِكِ إِذَا مَاتَ فِيهِمُ الرَّجُلُ الصَّالِحُ، أَوِ الْعَبْدُ الصَّالِحُ، **بَنَوْا عَلَى قَبْرِهِ مَسْجِدًا، وَصَوَّرُوا فِيهِ تِلْكَ الصُّوَرَ، أُولَئِكَ شِرَارُ الْـخَلْقِ عِنْدَ اللهِ**»، فَهَؤُلَاءِ جَمَعُوا بَيْنَ الفِتْنَتَيْنِ: فِتْنَةِ الْقُبورِ، وَفِتْنَةِ التَّمَاثِيلِ.

Hadisi ya tabbata cikin Shihul Bukhari –da Muslim- daga Aisha -radiyallahu anha- ta ce: Ummu Salma ta ba da labara wa Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- kan wani coci da ta gani a kasar habasha da hotunan da suke ciki, sai yace: " wadannan sune wadanda idan mutuin kirki ko bawa na kwarai daga cikinsu ya mutu **sai su gina masallaci a kan kabarinsa, sannan su sassaka wadannan a ciki hotunan a ciki, wadannan sune mafiya sharrin halitta a wajen Allah** ", wadannan sun hada fitintinu guda biyu: fitinar kabari, da fitinar hoto.

● Wadannan sun hada fitina guda biyu: Wannan maganar Ibnu Taimiyya ne Allah ya jikansa, abin da yasa ya kira hakan fitina; saboda sabubba ne da suke kawar da mutane daga addininsu.
● Abin da yafi dacewa gameda kaburbura su zamo a wajen gari, saboda kada su zamo hanyoyi masu kaiwa zuwa ga shirka.
● Fitinar kaburbura tafi tsanani sama da fitinar hotuna, saboda dalilai kamar haka:
1. Saboda ko ina akwai kaburbura sabanin hotuna.
2. Abubuwa masu yawa suna faruwa a wajen kabari irin wadanda basu faruwa a wadansu wajajen, kamar: Tsoro.

### DALILI NA BIYU:

وَلَهُمَا عَنْهَا، قَالَتْ: (لَـمَّا نُزِلَ بِرَسُولِ اللهِ ﷺ طَفِقَ يَطْرَحُ خَمِيصَةً لَهُ عَلَى وَجْهِهِ، فَإِذَا اغْتَمَّ بِهَا كَشَفَهَا، فَقَالَ - وَهُوَ كَذَلِكَ -: «**لَعْنَةُ اللهِ عَلَى الْيَهُودِ وَالنَّصَارَى، اتَّخَذُوا قُبورَ أَنْبِيَائِهِمْ مَسَاجِدَ**»؛ يُحَذِّرُ مَا صَنَعُوا، وَلَوْلَا ذَلِكَ لأُبْرِزَ قَبْرُهُ، غَيْرَ أَنَّهُ خُشِيَ أَنْ يُتَّخَذَ مَسْجِدًا، أَخْرَجَاهُ.

Hadisi cikin Bukhai da Muslim, daga Aisha Allah ya kara yarda a gareta, tace: ( yayin da mala'ikan mutuwa ya sauka wa Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- sai -Manzon Allah- ya fara sanya tufafinsa a fiskarsa, idan yaji zafi da gajeren numfashi, sai ya cire shi daga fiskarsa, kuma ya ce: " Allah ya tsine wa Yahuduwa da Nasara, saboda sun riki makabartun Annabawansu wuraren bauta "; yana tsawatarwa dangane da abin da sukayi, idan ba domin haka ba, da anga kabarin Manzon Allah a fili, saidai anji tsoron kar mutane su rike shi a matsayin wurin bauta). (Bukhari da Muslim ne suka ruwaito).

**DALILI NA BIYU:**

وَلِـمُسْلِمٍ عَنْ جُنْدَبِ بْنِ عَبْدِ اللهِ، قَالَ: سَمِعْتُ النَّبِيَّ ﷺ قَبْلَ أَنْ يَمُوتَ بِخَمْسٍ، وَهُوَ يَقُولُ: «**إِنِّي أَبْرَأُ إِلَى اللهِ أَنْ يَكُونَ لِي مِنْكُمْ خَلِيلٌ؛ فَإِنَّ اللهَ قَدِ اتَّخَذَنِي خَلِيلًا، كَمَا اتَّخَذَ إِبْرَاهِيمَ خَلِيلًا، وَلَوْ كُنْتُ مُتَّخِذًا مِنْ أُمَّتِي خَلِيلًا؛ لَاتَّخَذْتُ أَبَا بَكْرٍ خَلِيلًا، أَلَا وَإِنَّ مَنْ كَانَ قَبْلَكُمْ كَانُوا يَتَّخِذُونَ قُبورَ أَنْبِيَائِهِمْ مَسَاجِدَ، أَلَا فَلَا تَتَّخِذُوا الْقُبورَ مَسَاجِدَ، فَإِنِّي أَنْهَاكُمْ عَنْ ذَلِكَ**».

فَقَدْ نَهَى عَنْهُ فِي آخِرِ حَيَاتِهِ، ثُمَّ إِنَّهُ لَعَنَ - وَهُوَ فِي السِّيَاقِ - مَنْ فَعَلَهُ، وَالصَّلَاةُ عِنْدَهَا مِنْ ذَلِكَ، وَإِنْ لَمْ يُبْنَ مَسْجِدٌ؛ وَهُوَ مَعْنَى قَوْلِهَا: «**خَشِيَ أَنْ يُتَّخَذَ مَسْجِدًا**»، فَإِنَّ الصَّحَابَةَ لَمْ يَكُونُوا لِيَبْنُوا حَوْلَ قَبْرِهِ مَسْجِدًا.

وَكُلُّ مَوْضِعٍ قُصِدَتِ الصَّلَاةُ فِيهِ فَقَدِ اتُّخِذَ مَسْجِدًا، بَلْ كُلُّ مَوْضِعٍ يُصَلَّى فِيهِ يُسَمَّى مَسْجِدًا، كَمَا قَالَ ﷺ: «**جُعِلَتْ لِيَ الْأَرْضُ مَسْجِدًا وَطَهُورًا**».

Imam Muslim ya ruwaito daga Jundab dan Abdullahi, yace: ( naji Annabi -sallallahu alaihi wasallam- kafin mutuwarsa da kwana biyar yana cewa: "lallai ne ni na barranta zuwa ga Allah wani daga ckinku ya zame mini badadi, hakika Allah ya rike ni badadi, kamar yanda ya riki Ibrahim badadi, da zan riki wani badadi daga al'ummata to da na riki Abubakar badadi, **ku saurara! Lallai ne wadanda suka zo gabaninku sun kasance suna rikan kaburburan Annabawansu wuraren ibada, don haka, kada ku riki kaburbura wuraren ibada, lallai ne ni na hane ku daga aikata hakan "**.

Manzon Allah yayi wannan haninne a karshen rayuwarsa, sannan kuma ya la'anci wanda ya aikata hakan, yin sallah a wurin kabarin shima ya shiga ciki, ko da ba a gina masallaci ba, shine ma'anar fadinta: ((Ya ji tsoron kada a rike shi masallaci)), kuma hakika sahabbai basu zamo wadanda zasu gina masallaci a wurin kabari ba.

Dukkan wajen da aka nufi yin Sallah a cikinsa to hakika an rike shi masallaci, sannan duk wani wajen da ake Sallah cikinsa ana kiran sa masallaci, kamar yanda Annabi - sallallahu alaihi wasallam- ya ce: "kuma an sanya mini kasa wurin sallah da tsarki "

● Yayin da ya sauka ga Manzon Allah : Ma'ana: Mala'kan mutuwa domin karbar ran Annabi (Sallallahu alaihi wasallam).

● خَمِيصَةً : (**Khamisa**), tufafi mai wasu alamu a ikinsa.

● “La'ana Allah” : kora da nisantawarsa, wannan labara ne daga Allah, kuma zai iya daukar ma'anar mummunar addu'a yayi musu.

● “Sun riki kaburbran Annabawansu wuraren ibada”: ko dai ya zamo sunayin sujada ne a kan kabuburan, ko kuma sun gina masallatai a kan kaburbran.

● “Da an fito da kabarin fili” : da an bayyana shi, ma'ana da ba a bisine shi a gidansa ba, da an kai shi "MAKABARTAR BAQI'A".

**ME YASA AKA BISINE MANZON ALLAH SALLALLAHU ALAIHI WASALLAM A CIKIN GIDANSA, KUMA WANI BA YA IYA GANIN DAKUNAN GIDAN BALLANTANA YA GA KASAN KABARIN?**

● Sabo da fadin Annabi -sallallahu alaihi wasallam- Allah bai taba karban ran wani Annabi ba face sai an bisine shi a wurin da ya rasu.

● (( خَشيَ )): da (fatha, wa kha'un ) Annabi -sallallahu alaihi wasallam shine yaji tsoron kada a mayar da kabarinsa gunki abin bautawa.

● ((خُشِيَ )): da ( domma wa kha'un ), Sahabbai ne suka ji tsoron kada a mayar da kabarin gunki, saboda tsananin kwadayinsu wajen tace tauhidi.

**WANI MARTANI ZA MU BAYAR GA WANDA YAYI DAAWAR CEWA KABARIN ANNABI SALLALLAHU ALAIHI WASALLAM A CIKIN MASALLACI YAKE?**

1. **Martani a dunkule:** Muce masa: wannan yana daga abubuwa na shubuha, abin da ya zamo wajibi a kanka shine yin aiki da bayyananun dalilai daga al qur'ani da Sunnah, kana daga cikin wadanda suke bibiyar shubuha kuma su dalilai bayyanannu, don haka har abada ba za mu saurareka ba.

2. **Martani Dalla Daalla:**

**a**. Masallacin Annabi ba a kan kabarin aka gina ba , an gina shi Annabi yana raye.

**b.** Kuma ba a bisine Annabi sallallahu alaihi wasallam a masallaci ba, an bisine shi a cikin gidansa ne –dakin Aisha- kuma gidan nasa yana wajen Masallaci ne.

**c.** Sahabbai ba su yi ittifaki ba kan shigar da gidan Annabi cikin Masallacin, sai bayan rasuwar mafi yawansu, ragowarsu sunyi inkari, kamar yanda Said ibn al Musayyab -cikin Tabi'ai- shima yayi inkarin hakan.

**d.** Kabarin ba a cikin masallaci yakeba, yana kebe ne a wuri na musamman a gidan Annabi, kuma ba a gina masallacin a kan sa ba, hasali ma, kabarin yana gewaye ne

Katangaye uku, sannan an sanya wadannan katangaye a kusurwar karkatacciya daga alqiblah domin kada wani mai sallah ya samu daman fiskantar kabarin.

**e.** Massallacin Annabi yanada Karin daraja ta fikar ninka ladan sallah ciknsa, da halaccin ziyararsa daga ko ina a duniya.

## FADAKARWA:

**Alkhullah:** Shine: mafi daukakan nau'ukan soyayya, kuma Allah bai tabbatar da ita wa kowa ba gwargwadon saninmu sai wa mutum biyu daga bayinsa sune; Ibrahim -Sallallahu alihi wasallam- da Muhammad -Sallallahu alaihi wasallam-, da wannan zaka gane jahilci maigirma cikin fadin gama garin mutane: (Ibrahim Khalilullah, -Badadin Allah-, Muhammada Habibullah -masoyin Allah-), wannan tauye hakkin Annabi ne, domin sun sanya martabarsa kasa da ta Ibrahim -Amincin Allah ya tabbata a gare su-, ba su rabe tsakanin sa da waninsa cikin mutane ba, Misali; Allah yana son dukkan masu kyautatawa daga mutane, don haka akwai tawaya cikin siffanta shi da habibullah (Masoyin Allah).

## DALILI NA HUDU:

وَلِأَحْمَدَ - بِسَنَدٍ جَيِّدٍ - عَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ ؓ مَرْفُوعًا: «**إِنَّ مِنْ شِرَارِ النَّاسِ مَنْ تُدْرِكُهُمُ السَّاعَةُ وَهُمْ أَحْيَاءٌ، وَالَّذِينَ يَتَّخِذُونَ الْقُبور مَسَاجِدَ**». رَوَاهُ أَبُو حَاتِمٍ فِي «صَحِيحِهِ».

Daga Imam Ahmad -da isnadi mai kyau- daga Ibn Mas'ud -Allah ya kara yarda da shi- daga Annabi -sallallahu alaihi wasallam-: " Yana daga mafi sharrin mutane wadanda Alqiyama zata riske su a raye, da wadanda suke rikan kaburbura wuraren ibada".

(Abu Hatim ne ya ruwaito cikin Sahihnsa).

● "Mafiya sharin mutane" : Wannan dalili ne kan mutane suna da fifiko wajen sharri, wasu sunfi tsananin sharri sama da wasu.

## SAKON BABIN A TAKAICE:

Wajibi ne nisantar Shirka da sabubbanta, kuma a kausasa kan wanda ya bauta wa Allah a wurin kabarin wani mutumin kirki, sallah ce yayyi ko waninta na bautar Allah, duk wanda ya riya cewar gabatar da sadaka a wurin wani kabari yafi falala sama da wurin da ba shi ba, to lallai yayi kamanceceniya da wanda ya riki kabarin masallaci.

## MAS'ALOLIN BABIN:

1. Abin da Manzon Allah -Sallallahu wasallam- ya ambata na tsinuwa gameda wanda ya gina masallaci a wurin kabarin mutumin kirki, ake bauta wa Allah a wajen, ko da da kyakkyawar niyya yayi (wannan aikin ba ya bukatan niyya; saboda yanada alaka na kai tsaye ne da aiki, kuma ciki akwai kamanceceniya da mushrikai ).

2. Hani kan rikan mutum mutumi, da kausasawa cikin haka. (Musammam, idan wadan da akayi mutum mutuminsu masu matsayi ne da a ke girmama su a al'adance Kamar; shuwagabanni da iyaye, ko wadanda a ke girmama su a shari'ance kamar; waliyyai da salihan bayi ).

**3.** Akwai wa'azi cikin dogewar manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- wajen bayanin illar hotuna sannan kafin mutuwarsa da kwanaki biyar ya nanata, kuma ya kara fito da abun fili.

4. Kuma Manzon Allah ya hana aikata hakan wajen kabarinsa tun kafin a samu kabarin.

5. Sunna ce ta Yahudu da Nasara game da kaburburan annabawansu.

6. Manzon Allah Ya tsine musu akan wannan aikin.

7. Daga manufar Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- na yin hakan shine: Tsawatar mana kada muyi hakan game da kabarinsa.

8. Dalilin da yasa aka ki bayyana kabarinsa a fili. (Tsoron kada a bauta ma sa, kowani Annabi ana bisine shi ne a wajen da ya mutu).

9. Ma'anar rikan kaburbura masallaci; (Gina masallatai a kansu, mayar da su wuraren ibada ).

10. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya hada tsakanin masu rikan kaburbura wuraren ibada, da wadanda qiyama zata riske su suna raye, kuma ya ambaci hanyar da ke kaiwa ga shirka yayin mutuwarsa tun kafin aukuwan abun.

11. Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- cikin hudabarsa kafin mutuwarsa da kwanaki biyar yayi raddi wa kunkiyoyi biyu, mafi sharin yan bidi'a, (Sune: Jahmiyyah da Rafidha), wasu daga cikin maluma sun fitar da su daga kungiyoyin musulmai guda saba'in da biyu, saboda Rafidah -Yan shi'a- Shirka da bautan kaburbura suka auku a bayan kasa, domin su suka fara gina masallata a kan kaburbura.

12. Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya dandani zafin mutuwa.

13. Allah Ya karrama Annabinsa, ya rike shi Badadi.

14. Bayani kan cewa matsayin " Badadi " yana sama da matsayin " soyayya ".

15. Bayani karara cewa Abubakar Siddiq shine mafificin Sahabbai gaba daya. (Fifiko cikin imani da aiki na kwarai yana sama da fifiko ta fiskar nasaba, kan haka aka fifita Abubakar Assiddiq akan Aliyu (Allah Ya kara yarda a gare su).

16. Ishara kan khalifancin Sayyidina Abubakar, Allah ya kara yarda a gare shi.

## [21] BABIN (ABINDA YAZO NA CEWAR: WUCE IYAKA CIKIN KABURBURAN SALIHAI YA NA MAYAR DA SU GUMAKA DA AKE BAUTA MUSU BA ALLAH BA

● Wannan shine sababi na uku cikin sabubban faruwar shirka a bayan kasa, al'amarin masu wuce iyaka yana karewa da bautar kaburbura ko masu su, **Guluwwi** shine: wuce iyaka wajen yabon wani abu ko kushe shi.

● Kashe kashen mutane dangane da kaburbura, bangare biyu ne da tsaka tsakiya:

1. Wadanda suka zurfafa wajen bautarsu da gina kubbobi a kansu.
2. Wadanda suka tauye abinda ya wajaba na mutunta kaburbura, suke zama akan su, ko tone su.
3. Maganar gaskiya: Mutunta kaburbura kamar yanda Shari'a tayi umarni, kar a zurfafa ballantana a bauta musu. (Ahlussunnah).

### DALILI NA FARKO:

رَوَى مَالِكٌ فِي «الْـمُوطَّأِ»؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**اللَّـهُمَّ لَا تَجْعَلْ قَبْرِي وَثَنًا يُعْبَدُ**، **اشْتَدَّ غَضَبُ اللهِ عَلَى قَوْمٍ اتَّخَذُوا قُبور أَنْبِيَائِهِمْ مَسَاجِدَ**».

Imam Malik ya rawaito cikin " Muwaddaa ", cewa Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasaallam- ya ce: "Ya Allah kar ka sanya kabarina gunki abin bautawa, fushin Allah ya tsananta kan mutanen da suka riki kaburburan Annabawansu wuraren ibada ".

### DALILI NA BIYU:

وَلِابْنِ جَرِيرٍ بِسَنَدِهِ عَنْ سُفْيَانَ، عَنْ مَنْصُورٍ، عَنْ مُجَاهِدٍ: { أفرأيتم اللات والعزى}، قَالَ: (كَانَ يَلُتُّ لَهُمُ السَّوِيقَ فَمَاتَ، فَعَكَفُوا عَلَى قَبْرِهِ).

Daga Ibn Jarir yayi riwaya da isnadi zuwa ga Sufyan, daga Mansur, daga Mujahid, game da fadin Allah Ta'ala: [Kubani laabarin Lata da Uzzah ], yace: (ya kasance yana kwaba ma Alhazaai soyayyen gari ya shayar da su, sai ya mutu, sai mutane suka lizimci kabarinsa ).

### DALILI NA UKU:

[٣] وَكَذَا قَالَ أَبُو الْـجَوْزَاءِ، عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ: (كَانَ يَلُتُّ السَّوِيقَ لِلْـحَاجِّ).

Hakanan ga ruwayar Abul Jauzaa daga Ibnu Abbas Allah Ya kara yara a gare shi,

( Ya kasance yana kwaba soyayyen gari ya shayar da Alhazai).

وَعَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ﴾ قَالَ: «لَعَنَ رَسُولُ اللهِ ﷺ زَائِرَاتِ الْقُبُورِ، وَالْـمُتَّخِذِينَ عَلَيْهَا الْـمَسَاجِدَ وَالسُّرُجَ». رَوَاهُ أَهْلُ السُّنَنِ.

Dga Abdullahi dan Abbas -(Allah Ya kara yarda a gare shi-, ya ce: ( Manzon Allah - Sallallahu alaihi wasallam- " ya tsine wa mata masu ziyarar makabartu, da wadanda suka rike su wuraren ibada, kuma suka sanya fitilu a kansu ") ( Ma'abota kutub Sunan suka ruwaito).

● "Fushin Allah Ya tsananta" Fushi: Sifa ce tabbatacciya ga Allah, wacce ba ta kama da fushin halittu.

● ((Sun riki kaburburan Annabawansu wuraren ibada ))" ko dai suna yin sujada a wajen kaburburan, ko gina masallatai a kansu.

● Shin Allah Ya amsa addu'ar manzonsa -Sallallahu alaihi wasallam- kar ya mayar da kabarinsa gunki da za a ringa bauta masa? Ko hikimar Allah ta hukunta sabanin haka? Ibnul qayyim Allah Ya jikansa yana cewa: Hakika Allah ya amsa addu,ar Manzonsa, ba a samu labarin cewa kabarinsa ya zamo abin bauta ba, Kabarin nasa ya sami kariya da bango uku: Ibnul qayyim ya fada cikin "Nuniyyah"

فَأَجَابَ رَبُّ الْعَالَمِينَ دُعَاءَهُ    وَأَحَـــــاطَهُ بِثَلَاثَةِ الْجُدْرَانِ

*Ubangijin talikai Ya amshi addu'arsa*
*Sai ya gewaye shi da katangu uku*

Na'am, za a iya samun masu ketare iyaka game da kabarin nasa, sedai ketare iyakan nasu bai kai matsayin mayar da shi wani abin bauta ba.

● "{*Ku ban i labara ya ku mushrikai* } Menene matsayin waɗannan gumakan a kusa da manyan ayoyin da Annabi ya gani a daren Miraj?:

● السَّوِيقَ : Sha'ir ne gyararre, sannan a nika, a gauraya da dabino sannan a gabatar da shi wa mahajjata domin hidimta musu.

● السُّرُجَ: (**Assuruj**) Jam'i ne na (**Assiraj**), fitila, suna kunna fitilu a kaburburan dare da rana, domin girmamawa da wuce gona da iri.

● Ziyaran kaburbura ga mata babban zunubi ne, haka nan rikan kaburbura masallatai (wurin ibada), da kunna fitilu a kansu shima babban zunubi ne, saboda a cikin hadisin akwai la'ana a kan wanda ya aikata hakan.

● **Nau'ukan Ziyarar Makabartu:**

[1] Wanda aka Shar'anta (Halala):

- Kar a niki gari domin ziyarar.
- Mai ziyaran yayi niyyar wa'azantuwa da tuna Lahira.
- Addu'a wa kansa da mamatan.

[2] Idan yayi niyyar rokon matattu to wannan ziyarar Shirka ce.

[3] Idan kuma yayi niyyar rokon Allah a wajen kabarin to bidi'a ce.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Bayanin ma'anar gumaka (abin da ake bauta wa koma bayan Allah, gunki ne ko kabari ko wani abu daban).

2. Ma'anaar bauta (Kankan da kai da sallamawa ga allah cikin tsoro, da fata, da kauna da girmamawa).

3. Manzon Allah -sallallahu alihi wasallam- bai nemi tsari daga komai ba, sai abinda yake tsoron faruwarsa.

4. Ya didaita wannan, da rikan kaburburan annabawa a matsayin masallatai.

5. Ya ambaci tsananin fushi daga Allah.

6. Mafi muhimmancin waɗannan mas'alolin itace: bayanin yanda aka bauta ma Lata, wanda itace mafi girman gumaka..

7. Sanin cewa kabari ne na mutumin kirki.

8. Cewa shine sunan mai kabarin (Laata), kuma an ambaci dalilin saka wannan sunan.

9. An la'anci mata masu -yawan- ziyarar makabartu.

10 Ku ya la'anci wanda ya sanya fitilu domin manufar bauta.

● **Mas'alah Muhimmiya:** Guluwwi (wuce iyaka) cikin kaburburan salihai yana mayar da su gumaka, kamar yanda ya faru da kabarin Al-Laata.

● **Mas'alah:** Idan mace tajeta Rauda a masallacin Annabi domin Sallah, Kabarin yana kusa da ita, don haka babu laifi ta tsaya ta gaishe shi, abinda yafi kyau: a nisanci cinkoso da cakuduwa da maza, Kuma saboda kar wadanda ke kallon ta suyi tunanin cewa halal ne mace ta ziyarci kabari.

## [22] BABIN (ABIN DA YA ZO NA KARIYAR MANZON ALLAH -SALLALLAHU ALAIHI WA SALLAM- GA JANABIN TAUHIDI, DA TOSHE DUK WATA HANYAR DA ZA TA KAI ZUWA GA SHIRKA).

Mawallafin ya kulla wannan babin ne don ya bayyana cewa Annabi Muhammad -Sallal Lahu alaihi wasallam- ya sanya katangar shinge mai aminci don hana mutane kusantar iyakokin tawhid, kuma bai bar kofa daya a bude ba ga duk wanda yake son shigarta. Kuma hakika, ya rufe dukkan hanyoyin da zasu iya haifar da shirka.

**DALILI NA FARKO:**

وَقَوْلُ اللهِ تَعَالَى: {لَقَدْ جَاءكُمْ رَسُولٌ مِّنْ أَنفُسِكُمْ عَزِيزٌ عَلَيْهِ مَا عَنِتُّمْ حَرِيصٌ عَلَيْكُم بِالْمُؤْمِنِينَ رَؤُوفٌ رَّحِيمٌ} (١٢٨).

*Da fadin Allah Madaukaki: [ **Lallai ne Hakika Manzo daga cikinku ya je muku, don ku** ]. (QS. At Taubah, 128).*

**DALILI NA BIYU:**

عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ؓ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «لَا تَجْعَلُوا بُيُوتَكُمْ قُبورا، وَلَا تَجْعَلُوا قَبْرِي عِيدًا، وَصَلُّوا عَلَيَّ؛ فَإِنَّ صَلَاتَكُمْ تَبْلُغُنِي حَيْثُ كُنْتُمْ»، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ بِإِسْنَادٍ حَسَنٍ، وَرُوَاتُهُ ثِقَاتٌ.

Daga Abu Hurairah -Allah Ya kara yarda a gare shi- ya ce: Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Kada ku mayar da gidajenku makabartu, kuma kada ku riki kabrina a matsayin idi, kuma ku yi mini salati, domin salatinku zai iso gare ni a duk yanda kuke. "Abu Dawud ya ruwaito shi da isnadi mai kyau, kuma maruwaitan hadinsin amintattu ne.

- [ لقد جاء كم رسول ] (*Lallai ne Haqiqa manzo ya je muku*) : Ankarfa wannan zancen da abubuwa uku; Rantsuwa, harafin: Laamun " اللَّام ", da harafin: Qad " قد ".
- [ مِنْ أَنْفُسكم ] (*Daga jinsinku*), ma'ana; [1] Mutum ne daga jinsinku, sedai ya banbance ku ta fiskar wahayi, . [2] Cikin wata qira'ar: مِنْ أَنْفَسِكُمْ da yin fatha ma harafin الفاء, Ma'anarsa: Mafi darajarku kuma Mafi tsoron Allah daga cikinku.
- [ عزيزٌ عليه ] (*>>*).
- [ حَرِيصٌ عَلَيْكُم ](*mai kwadayin alkhairi ne a gareku*): yayi matukar kokari wajen tabbatar da maslahohinku.
- [ بِالْمُؤْمِنِينَ رَؤُوفٌ رَّحِيمٌ ] (*Kuma mai tausayi da jinkai ne ga muminai*).

Gabatar da abin da yakamata a jinkirta shi yana hukunta iyakancewa da takaitawa, ma'ana: shi mai tsanantawa ne kan wadanda suka kafirce . Allah Ta'ala yace:

مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ اللَّهِ وَالَّذِينَ مَعَهُ أَشِدَّاء عَلَى الْكُفَّارِ رُحَمَاء بَيْنَهُمْ

*Muhammadu manzon Allah ne, wadanda suke tare da shi sunada tsanani a kan kafirai masu tausayin junansu ne… (QS. Al-Fath : 29).*

● فَإِن تَوَلَّوْاْ (*To idan sun juya baya*): Allah baice: فإن توليتم (idan kuka juya baya ) [1] Saboda juya baya tareda wannan bayanin makruhi ne. [2] Kuma domin fadakar da mai karatu, ya canza lamirinne domin maikaratu ya fadaka.

● فَقُلْ حَسْبِيَ اللّهُ (*To sai kace: Allah Ya isar mini* ): Ma'ana: kada kawar da kansu ya dameka, ka fada da harshenka kuma da zuciyrka, cewa: " Allah aYa isar mini " .

● بُيُوتَكُمْ قُبورا (Gidajenku makabartu), Ma'ana: [1] Kada kabar yin Sallah a cikinsu. [2] Kada ku bisine matattu a cikinsu.

● عِيدًا ( idi ): Ma'ana kada ku yawaita kaiwa da komowa wajen kabarina, (kar ku shi kamar al'ada ) wanda zaku nanata shekara shekara ko wata wata, ko duk sati, iyaka, ana ziyararsa ne saboda sababi, kamar dan ya dawo daga tafiya ko saboda tuna Lahira.

● وَصَلُّوا عَلَيَّ ( Kuma kuyi mini Salati ): Salatin Allah shine: Yabo daga Allah cikin tawaga madaukakiya.

● تَبْلُغُنِي (Zata riskeni) : Saboda fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-:

«إِنَّ لِلَّهِ مَلائِكَةً سَيَّاحِينَ فِي الأَرْضِ يُبَلِّغُونِي عَنْ أُمَّتِي السَّلامَ»

" Allah Yanada wadansu Mala'iku masu zagayawa a bayan kasa, suna isar mini da sallamar al'ummata". Don haka babu bukatar yin cincirindo –Musamman ta fiskar al'ada- wajen kabarinsa (Sallallahu alaihi wasallam).

**DALILI NA UKU:**

وَعَنْ عَلِيِّ بْنِ الْـحُسَيْنِ؛ أَنَّهُ رَأَى رَجُلًا يَجِيءُ إِلَى فُرْجَةٍ كَانَتْ عِنْدَ قَبْرِ النَّبِيِّ ﷺ، فَيَدْخُلُ فِيهَا فَيَدْعُو، فَنَهَاهُ، وَقَالَ: أَلَا أُحَدِّثُكُمْ حَدِيثًا سَمِعْتُهُ مِنْ أَبِي، عَنْ جَدِّي، عَنْ رَسُولِ اللهِ ﷺ قَالَ: «**لَا تَتَّخِذُوا قَبْرِي عِيدًا، وَلَا بُيُوتَكُمْ قُبورا؛ فَإِنَّ تَسْلِيمَكُمْ يَبْلُغُنِي أَيْنَ كُنْتُمْ**»، رَوَاهُ فِي «الْـمُخْتَارَةِ».

Daga Aliyu bin Husain, yaga wani mutum yana zuwa wajen wata kafa a jikin kabarin Manzon Allah -Sallahu alaihi wasallam- sai ya shigeta yayi addu'a, sai ya hana shi, yace masa: (ba na baka labarin wani hadisi ba? Wanda da na ji daga wajen babana, daga kakana, daga Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam)? Yace:

" kada ku riki kabarina idi, kuma kada ku mayar da gidajenku makabartu, -kuyi mini salati- domin sallamarku tana riska na a duk yanda kuke " ( An ruwaito shi cikin kitab Al Mukhtarah ).

● فَيَدْعُو (Sai yayi addu'a ): Kasancewar shi yayi zaton cewa yin addu'a a wajen kabarin Annabi yanada wani falala ta musamman, hakika wannan bude wata hanya ce da za ta iya kaiwa zuwa ga shirka da Allah.

● أَيْنَ كُنْتُمْ (a duk yanda kuke ): Abin nufi; kuyi mini salati a duk yanda kuke, ba lallai sai kunzo wajen kabarin domin kuyi mini sallama ko salati ba.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tafsirin ayar suratu Bara'ah. {*Hakika Manzo daga cikinku ya je muku} (QS. At Taubah, 128).*

2. Manzon Allah ya nisantar da al'ummarsa matukar nisantarwa daga kusantar wannan shingen. Cikin fadinsa: ( Kada ku mayar da gidajenku makabartu……).

3. Ambaton kwadayinsa da tausayi da jinkayinsa -sallallahu alaihi wasallam- gare mu. (Ayar Bara'ah).

4. Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yayi hani kan ziyarar kabarinsa a kai a kai, tareda cewa ziyararsa na daga mafifitan aiyuka. (domin cikin ziyararsa akwai yin sallama a gare shi, kuma hakkinsa yana sama da na kowa).

5. Manzon Allah ya yi hani kan yawaita ziyarar kabarinsa.

6. Manzon Allah ya kwadaitar kan yin sallolin nafila a cikin gidaje.

7. Abune sananne wajen sahabbai cewa ba'a yin sallah cikin makabartu.

8. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya baiyana dalilin hanin; shine: salatin mutum da sallamarsa suna riskarsa komi nisa, ba dole ba ne sai an tafo kusa da kabarin kamar yanda wadansu suke zato. (Ali bin Al-Husain yace:

ما أنت ومن بالأندلس إلَّا سواءٌ

" Da kai da wanda yake andalos duk daya kuke ".

9. Kasancewar Manzon Allah yana barzakh, tareda haka ana bijiro masa da wani sashe na aiyukan al'ummarsa.

## NA BIYAR: LALATA HUJJAR WADANDA SUKE CEWA: SHIRKA BA ZA TA AUKU A CIKIN WANNAN AL'UMMAR BA, KO A JAZIRAH (BABI 1)

### [23] BABIN ( WANI SASHE NA WANNAN AL'UMMUR ZAI BAUTA WA GUMAKA).

● Mawallafin ya kawo wannan babin ne domin ya lalata hujjojin wadanda suke cewa: shirka ba za ta auku cikin wannan al'umma ba; domin wannan al'ummar tsararriya ce, da dalilin fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-

" إِنَّ الشَّيْطَانَ أَيِسَ أَنْ يَعْبُدَهُ الْمُصَلُّونَ فِي جَزِيرَةِ الْعَرَبِ ".

“ Lallai ne Shaidan ya debe tsammanin masallata su bauta masa a yankin larabawa ”.

● **Jawabin wannan shubuhar a dunkule**:

Wannan nau'i ne na bibiyar shubuha da watsi da dalilai bayyanannu.

● **Jawabin shubuhar a rarrabe:**

1. Ba da labari kan debe tsammanin shaidan ba ya nuni kan rashin aukuwar shirkar.
2. Ya debe tammani daga masallata, amma bai debe tsammani daga wadanda ba masallata ba, (Masallaci - Mai Tauhidi), .
3. Wannan Fahimtar ta saba wa nassoshi masu yawa na Alqur'ani da Sunnah.
4. Sahabbai -Allah ya kara yarda a gare su- sun yaki wadanda sukayi ridda a yankin larabawa saboda shirkarsu.
5. Zahiri yana tabbatar da sabanin wannan fahimtar, domin zaka iya ganin wurare a yankin larabawa da ake yin yanka domin wanin Allah (Ta'ala).
6. Wannan abu ne da ya auku cikin zuciyar shaidan, alhali shi bai bar aiki wajen batar da banu Adama ba.
7. Debe tsammanin nasa ya auku ne yayin da musulmai suka bude garuruwa masu yawa da yake kuma mutane sukayi ta shiga addinin Allah jama'a jama'a.
8. Maluman musulunci sun ambaci abubuwa da suke warware musulunci koda kuwa a yankin larabawa.

● Duk wanda ya yi da'awar cewa musailamata -Alkazzab- Annabi ne to wannan ya kafirta, fadin Lailaha illallahu ba zata amfane shi ba -har sai ya tuba-, to ina kuma ga wanda ya daga Tijjani da waninsa ya ba su matsayin Allah, wannan bai zamo kafiri ba? Hakika wannan abin mamaki ne mai girma!!

**Me yasa Mawallafin ya kawo ayoyin da zahirunsu ba dalili ne kan tarjamar ba?**

● Manufar ba za ta bayyana ba sai an hada Ayoyin da hadisin Abu Said, nan ne za a fahimci cikakken dacewarsu da tarjamar .

**DALILI NA FARKO:**

**Da fadin Allah Ta'ala:**

أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ أُوتُواْ نَصِيباً مِّنَ الْكِتَابِ يُؤْمِنُونَ بِالْجِبْتِ وَالطَّاغُوتِ

*[ Shin ba kayin dubi ba zuwaga wadanda da aka ba su wani rabo na littafi, tareda hada sunayin imani da gunki, kuma sunayin da dagutu] …(QS. An-Niisa : 51).*

**DALILI NA BIYU:**

**Da fadin Allah ta'ala:**

قُلْ هَلْ أُنَبِّئُكُم بِشَرٍّ مِّن ذَلِكَ مَثُوبَةً عِندَ اللّهِ مَن لَّعَنَهُ اللّهُ وَغَضِبَ عَلَيْهِ وَجَعَلَ مِنْهُمُ الْقِرَدَةَ وَالْخَنَازِيرَ وَعَبَدَ الطَّاغُوتَ

*[ **Ka ce : bana ba ku labarin mafi sharrin sakamako daga wannan ba, a wajen Allah, shine wanda Allah ya tsine masa kuma ya yi fushi da shi, kuma ya sanya birrai da aladu daga cikinsu, kuma ya bauta ma Dagutu** ](QS. Al-Maidah :60).*

● أَلَمْ تَرَ إِلَى (*Baka yi duba zuwa ga)*: Tambaya ce domin tabbatar da zancen tare da mamaki, ga duk wanda ya dace a fiskantar da zancen zuwa gare shi.

● أُوتُواْ (*Wadanda aka ba su)*: An basu wani rabo na littafi ba dukkan littafin ba, saboda an haranta musu wani sashe saboda zunubbansu.

● *(Suna imani da gunki kuma da dagutu)* Ma'ana suna gasgata gumaka da dagutu, kuma suna tabbatar da su, ba sa muzanta su.

**Daga Fa'idodin Ayar farko:**

1. Abin mamaki ne kwarai aba wa mutum wani rabo na littafi, sannan tareda haka yana imani da gunki da dagutu.
2. Ilimi kadai baya tsare ma'abucinsa daga sabon Allah.
3. Ya zama wajibi ayi inkarin gunki da dagutu, haramun ne tabbatar da su.
4. Tabbas daga cikin wannan al'mmar akwai masu yin imani da gumaka da dagutu, kamar yanda aka samu cikin banu Isra'il.

● (*Kace da su: ba na baku labari ba?*): wannan Magana ce zuwa ga Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- domin mayar da martani kan Yahudawa wadanda suka riki addinin musulunci a matsayin izgili da wasa, tambayar domin tabbatar da zance ne da kuma janyo hankula.

**Daga Faidodi daga Aya ta biyu:**

1. Tabbatar da abokin husuma da kafa masa hujjah kan abin da yake iya muzanta shi, saboda yahudawa sunsan cewa daga cikinsu akwai wadanda Allah ya yi fushi da su, kuma ya tsine musu, sannan ya sanya birrai da aladu daga cikinsu, to idan har sun kasance suna tabbatar da hakan, kuma sunayin izgili wa musulmai, to sai mu fada musu cewa: ( Ai wadanda ukubar Allah ta sauka a kansu sune sukafi cancantar izgili ).
2. Matsayin mutane tare a wajen Allah ya banbanta, lura da karuwa da raguwar imaninsu, da kuma sakamakon hakan.
3. Mummunan yanayin yahudawa, yadda aka hukunta su da la'anar Allah, da shafewa, da bautar dagutu.
4. Tabbatar da Aiyukan Allah wadanda yaga damar aikatasu (أفعال الاختيارية), kamar; tsinuwa da fushi da sauransu, kuma hakika Allah yana aikata duk abin da ya so.
5. Fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-:

إِنَّ اللهَ لَمْ يَجْعَلْ لِمَسْخٍ نَسْلًا وَلَا عَقِبًا

" Allah bai sanya zuriya ko baya ba ga duk al'ummar da ya shafe ta".
Birrai halittu ne da suka kasance abayan kasa, tun kafin ukubar yahudawa.
6. Ukubar Allah kan mutane gwargwadon aikinsu ne, yahudawa sun aikata aikin da zahiransa halal ne amma kuma Allah Ya haramta musu shi.
7. Yahudawa sun koma bautar dagutu, babu shakka har zuwa wannan lokacin suna bautata ma dagutai.

**DALILI NA UKU:**

قَالَ الَّذِينَ غَلَبُوا عَلَى أَمْرِهِمْ لَنَتَّخِذَنَّ عَلَيْهِم مَّسْجِداً

*[ **Wadanda sukayi rinjaye a kan al'amarinsu suka ce: lallai zamu riki masallaci a kansu** ]. (QS. Al-Kahfi : 21).*

● (*Wadanda sukayi galaba sai suka ce*): Ma'ana: mahukumtansu ne sukayi wannan maganar tareda rantsuwa mai karfi.
1. Abin da ke cikin kiswsar Ashabul Kahfi na Ayoyi da suke nuni kan kamalar ikon Allah.

2. Wuce iyaka cikin ma'abota kaburbura na daga sabubban da ke sa a gina masallatai kan kaburbura.
3. Wuce iyaka cikin kaburbura koda da kankanin abu ne, yana iya kaiwa ga laifin da ya dara wannan muni.

**DALILI NA HUDU:**

عَنْ أَبِي سَعِيدٍ ڤ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «لَتَتَّبِعُنَّ سَنَنَ مَنْ كَانَ قَبْلَكُمْ، حَذْوَ الْقُذَّةِ بِالْقُذَّةِ، حَتَّى لَوْ دَخَلُوا جُحْرَ ضَبٍّ لَدَخَلْتُمُوهُ»، قَالُوا: يَا رَسُولَ اللهِ، الْيَهُودَ وَالنَّصَارَى؟ قَالَ: «فَمَنْ؟!» أَخْرَجَاهُ.

Daga Abu Sa'id Alkhudri -Allah Ya kara yarda a gare shi- yace: Manzon Allah -Sallallahu alihi wasallam- yace: "Lallai ne zaku ringa bibiyar hanyoyin wadanda suke gabanninku daidai wa daida , ko da sun shiga ramin damo, kuma tabbas sai kun shige shi " sai sukace ya ma'aikin Allah, kana nufin Yahudawa ne da nasara? Sai yace: " Wanene idan ba su ba ?! " ( Bukhari da Muslim ne suka ruwaito ).

**DALILI NA BIYAR:**

وَلِمُسْلِمٍ عَنْ ثَوْبَانَ ڤ، أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «إِنَّ اللهَ زَوَى لِيَ الأَرْضَ فَرَأَيْتُ مَشَارِقَهَا وَمَغَارِبَهَا، وَإِنَّ أُمَّتِي سَيَبْلُغُ مُلْكُهَا مَا زُوِيَ لِي مِنْهَا، وَأُعْطِيتُ الْكَنْزَيْنِ: الأَحْمَرَ وَالأَبْيَضَ، وَإِنِّي سَأَلْتُ رَبِّي لِأُمَّتِي أَنْ لَا يُهْلِكَهَا بِسَنَةٍ بِعَامَّةٍ، وَأَنْ لَا يُسَلِّطَ عَلَيْهِمْ عَدُوًّا مِنْ سِوَى أَنْفُسِهِمْ، فَيَسْتَبِيحَ بَيْضَتَهُمْ، وَإِنَّ رَبِّي قَالَ: يَا مُحَمَّدُ، إِذَا قَضَيْتُ قَضَاءً فَإِنَّهُ لَا يُرَدُّ، وَإِنِّي أَعْطَيْتُكَ لِأُمَّتِكَ أَنْ لَا أُهْلِكَهَا بِسَنَةٍ بِعَامَّةٍ، وَأَنْ لَا أُسَلِّطَ عَلَيْهِمْ عَدُوًّا مِنْ سِوَى أَنْفُسِهِمْ فَيَسْتَبِيحَ بَيْضَتَهُمْ، وَلَوِ اجْتَمَعَ عَلَيْهِمْ مَنْ بِأَقْطَارِهَا، حَتَّى يَكُونَ بَعْضُهُمْ يُهْلِكُ بَعْضًا، وَيَسْبِيَ بَعْضُهُمْ بَعْضًا».

وَرَوَاهُ الْبُرْقَانِيُّ فِي صَحِيحِهِ، وَزَادَ: «وَإِنَّمَا أَخَافُ عَلَى أُمَّتِي الأَئِمَّةَ الْمُضِلِّينَ، وَإِذَا وَقَعَ عَلَيْهِمُ السَّيْفُ لَمْ يُرْفَعْ إِلَى يَوْمِ الْقِيَامَةِ، وَلَا تَقُومُ السَّاعَةُ حَتَّى يَلْحَقَ حَيٌّ مِنْ أُمَّتِي بِالْمُشْرِكِينَ، وَحَتَّى تَعْبُدَ فِئَامٌ مِنْ أُمَّتِي الأَوْثَانَ، وَإِنَّهُ سَيَكُونُ فِي أُمَّتِي كَذَّابُونَ ثَلَاثُونَ كُلُّهُمْ يَزْعُمُ أَنَّهُ نَبِيٌّ، وَأَنَا خَاتَمُ النَّبِيِّينَ، لَا نَبِيَّ بَعْدِي، وَلَا تَزَالُ طَائِفَةٌ مِنْ أُمَّتِي عَلَى الْحَقِّ مَنْصُورَةً، لَا يَضُرُّهُمْ مَنْ خَذَلَهُمْ حَتَّى يَأْتِيَ أَمْرُ اللهِ تَبَارَكَ وَتَعَالَى».

Imam Muslim ya ruwaito daga sauban -Allah ya kara yarda a gare shi- Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yace: "Lallai ne Allah Ya taro min kasa, -ya kusan to mini da ita- sai naga mafudan rananta da mafadan rananta, kuma lallai mulkin al'ummata zai kai ga wuraren da aka taro min na kasar, kuma an bani taska biyu; jaa, da fari, kuma lallai ni na roki ubangijina kada ya halaka gaba dayan al'ummata da fari a lokaci, kuma kada ya dora abokin gabansu akansu daga wajensu -kamar kafirai-, wanda zai halatta kasashensu, kuma lallai Ubangijina Yace:

" Ya Muhammad, lallai ni idan har na zartar da wani lamari to ba a mayar da shi, kuma lallai ni na ba wa al'ummarka, ba zan halakar da su da fari ba gaba dayansu, kuma ba zan daura abokin adawa akansu ba daga wajensu a kansu ba, wanda zai yi galaba a kansu, halatta garurawansu, ko da duk wadanda suke bayan kasa za su taru kan yakarsu, har sai idan har sashinsu -su musulmai- zai ringa halaka sashe, sannan sashensu zai kama sashe ya mayar da su bayi ".

Al burqani ya ruwaito wannan hadisin cikin sahihinsa kuma ya kara da fadin Annabi: " iyaka dai ina ji wa al,ummata tsoron shuwagabanni masu batarwa, kuma idan har takwabbi ya auka cikinsu, to ba za a iya dage shi ba har tashin alkiyama, kuma kiyama ba za ta tsaya ba har sai wata jama'a daga al'ummata sun hadu da mushrikai, kuma har sai wasu mutane daga al'ummata sun bauta a gumaka, kuma da sannu makaryata guda talatin za su kasance daga al'ummata kowansu yana da'awar cewa shi annabi ne, kuma nine cika makin annabawa babu wani annabi bayana, kuma wata jama'a daga al'ummat ba za ta gushe ba kan gaskiya, ana taimakonta, wanda ya kyamace su bazai cutar da su da komai ba har lamarin Allah madaukaki ya zo ".

● **سَنَنَ:** Anyi fataha wa " Sinun- Sanan " Ma'anarta: Hanya, idan akayi domma kuma; " Sunan " tana nufin: tafarki.

● **حَذْوَ الْقُذَّةِ بِالْقُذَّةِ: (Alquzzah):** shine: hakwaran mashi, kinaya ce kan matukar kamanceceniya.

1. Sashen wannan al'ummar zai bauta wa gumaka, domin bautar gumaka hanya ce ta wadanda suka gabace mu, kuma babu makawa wasunmu zasuyi koyi da su.
2. Sanin tafarkin wadanda suka zo gabaninmu yana da kyau, domin gujewa abin da ya wajaba a kanmu mu kiyaye shi, kuma yawancin wadannan abubuwan an yi mana bayaninsu a cikin Al qur'ani da Sunnah, don haka, haramun ne muyi koyi da su cikin sabon Allah.
3. Sahabbai sun girmama lamarin kaucewa bibiyar tafarkin wadanda suka zo gabaninmu, bayan shiriya ta zo mana.
4. Gwargwadon nisan mutum da sakon Allah, gwargwadon nisan shi da gaskiya.

● **زَوَى :** Taro wani abu da Hada shi waje guda.

● **الأَحْمَرَ وَالأَبْيَضَ:** (Ja, da Fari ): Zinare da Azurfa, Taskokin Kisra da Qaisar.

● “kuma tabbas na roki Ubangijina” : Annabi -sallallahu alaihi wasallam- ya roki abubuwa uku, an ba shi guda biyu an hana shi na ukun:

1. Kada Allah Ya halaka al'ummarsa da fari: Ma'ana : Allah ba zai jarabci dukkanin al'ummar Annabi da fari lokaci guda ba.

2. Kafurai ba zasu taba samun iko a kan al'ummar musulmai gaba daya ba.
3. Kada al'ummarsa su rinka yakar junansu a tsakaninsu, wannan na karshen an hana Manzon Allah sallallahu alaihi wasallama shi.

● **" Shuwagabanni masu batarwa ":** Ya iyakance tsoronsa kan limamai masu batarwa, limami zai iya zamowa cikin aikin:

1. **Alkhairi**, kamar yanda Allah ya ce:

وَجَعَلْنَا مِنْهُمْ أَئِمَّةً يَهْدُونَ بِأَمْرِنَا لَمَّا صَبَرُوا وَكَانُوا بِآيَاتِنَا يُوقِنُونَ (٢٤)

***Kuma Mun sanya shuwagabanni daga cikinsu suna shiryarwa da umarninMu yayinda sukayi hakuri, kuma suna yin yakni da ayoyinMu.*** *(QS. As-Sajadah : 24).*

2. **Sharri**, kamar yanda Allah ya ce:

وَجَعَلْنَاهُمْ أَئِمَّةً يَدْعُونَ إِلَى النَّارِ وَيَوْمَ الْقِيَامَةِ لَا يُنصَرُونَ (٤١)

***Kuma muka sanya su shuwagabanni suna kira zuwa ga wuta, kuma Ranar qiyama ba za a taimake su ba.*** *(QS. Al-Qasas : 41).*

● "Idan takwabi ya fada a kansu ba za a dauke shi ba": wannan shine abin da ya faru tun bayan kashe Sayyidina Usman -Allah ya kara yarda a gare shi- har zuwa wannan lokacin.

● "Kuma har sai wasu jama'a daga al'ummata sun bauta wa gumaka ": wadansu jama'a daga al'ummata zasu bauta wa gumaka.

● "كذابون ثلاثون" " Makaryata talatin", Misali ne na yawan adadinsu, ko iyakance wa.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tafsirin ayar Suratu An-Nisa'i, [ Suna imani da gunki da dagutu ]*(QS. An-Niisa: 51).*

2. Tafsirin ayar surat Al-Maidah. [Kuma ya bauta wa dagutu] *(QS. Al-Maidah : 60).*

3. Tafsirin ayar surat Al Kahfi. ( [ Lalai ne zamu riki masallaci a kansu ]. *(QS. Al-Kahfi : 23).* Yayin da aka samu wadanda suka bauta wa gumaka cikin al'ummomin baya, to babu makawa cikin wannan al'ummar sai an samu wadanda za su bi tafarkinsu na bautar gumaka ).

4. Mafi muhimmancin wadannan mas'alolin, sanin menene ma'anar (Al jibtu da Ad-Dagut, wato: gunki da dagutu )? A wannan warin, shin abin nufi shine kudirin zuci kadai? ko kuma yarda da ma'abutansu, tareda wani sashe nasu, da sanin bacinsu?. ( [1] Zai kafirta, idan har ya yarda da su, kuma yarda da cewa su din gaskiya ne. [2] Ba zai kafirta ba, idan ya amince a fili, amma a cikin zuciyarsa bai yarda da gaskiyarsu ba ).

5. Fadin Yahudawa cewar kafiran Makkah -wadanda yahudawa sukasan kafircinsu karara-, cewa su ne suka fi zamowa shiryaryu sama da muminai –Annabi da sahabbansa- ( Lallai wannan maganar kafirci ne kuma ridda ce, domin sun fifita kafirci a kan imani).

6. Wannan mas'alar itace manufar tarjamar, cewa babu makawa sai an samu cikin wannan al'ummar wadanda za su bauta wa gumaka kamar yana yazo cikin hadisin Abu Sa'id. ( hadisin ya kunshi tsoratarwa ).

7. Annabi yayi bayani karara cewa hakan zai auku ba makawa -ma'ana bautar gumaka- cikin mutane masu yawa na wannan al'ummar.

8. Babban abin mamaki; baiyanar masu da'awar annabta, kamar; Mukhtar tare da yana fadin Kalmar Shahada, kuma yana riya cewa shi daya ne daga wannan al'ummar, kuma Manzon Allah gaskiya ne, Al qur'ani gaskiya ne, kuma cikin Al qur'anin akwai bayanin cewa Annanbi Muhammad shine cikamakon Annabawa, tare da gaskata duk wadannan abubuwan amma kuma ya kafirce musu karara, Mukhtar ya bayyana ne a karshen zamanin sahabbai, jama'a masu yawa sun bi shi kan wannan kafircin (Mukhtar shine: dan Abu ubaid Assaqafi ).

9. Bushara kan cewa gaskiya ba za ta gushe gaba daya ba kamar yanda ta gushe cikin zamunan da suka gabata, wadansu jama'a ba za su gushe ba suna tsaye akan gaskiya (Daga wannan al'ummar, Allah Yana taimakonsu har tashin qiyama ).

10. Hakika wanna babbar aya ce; tare da karancin masu tsayuwa akan gaskiyar cikin wannan al'ummar, sedai wadanda suka kyamace su ko suka saba musu bazasu iya cutar da su da komai ba.

11. Kuma wannan sharadi ne har zuwa (kusan) tashin al qiyama.

12. Cikin hadisin babin akwai manya manyan ayoyi daga cikinsu:

- Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya bada labarin cewa Allah Ya taro masa mafudan rana da mafadanta.
- Labartawarsa da ma'anar hakan, kuma abin ya auku kamar yanda ya labarta, sabanin kudancin kasa da arewacinta.
- Ya bada labarin cewar an ba shi taska biyu.
- Ya bada labarin cewa an amshi adduarsa dangane da al'ummarsa cikin abubuwa biyu, amma ba a amshi addu'arsa ta uku ba.
- Ya bada labarin aukuwar takwabi kuma idan ya auku ba za a dage shi ba.
- Ya bada labarin cewa sashen al'ummarsa za su halaka sashe, sannan sashinsu za su bautar da sashe.
- Ya bada labarin tsoronsa ga al'ummarsa daga shuwagabanni masu fatarwa. Kuma da bayyanar masu da'awar annabta cikin wannan al'ummar, kuma wani bangare na al'ummarsa ba za su gushe ba suna kan gaskiya, Allah Yana taimakonsu, duk wadannan abubuwan sun auku kamar yanda ya bada labara, tare da cewa dukkansu abubuwa ne da hankali zai nisanta aukuwarsu.

13. Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya iyankance jin tsoro wa al'ummarsa da shuwagabanni masu batarwa.

14. Fadakarwa game da ma'anar bautar gumaka. (bautar gumaka bata kebanci yi musu ruku'u ko sujada ba, ta kunshi yin biyayya ga masu batarwa).

## Jarabawar kashi na hudu da na biyar (babuka biyar)

**[1] Ambaci babukan kasha na hudu da na biyar da munasabar kowani babi da kitabut tauhid:**

| No | Sunan Babin | Sababin da yasa mawallafin ya kulla Babin |
| --- | --- | --- |
| 1 | | |
| 2 | | |
| 3 | | |
| 4 | | |
| 5 | | |

**[2]: Sanya alamar (☒) awajen da ya dace da shi ko kuma ka ciki gurbin:**

1. Wuce iyaka dangane salihai shine tushen shirka a da can da yanzu? ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
2. Guluwwi shine:……………………………………………………………………………..
3. Fitinuwa da kaburbura kamar fitinuwa da gumaka ne, tafi tsanani ma. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
4. Kawata kaburbura, da sanya musu fitillu, da flastesu, da yin rubutu a kansu, da gina kubbobi a kansu, da sanya musu labulayya, da hidimta wa mai ziyararsu, da bayar da kudi wa masu kula da kaburburan:
☐ Wajibi ne ☐ Haramun ne.
5. Mawallafin (Shaikh Muhammad bn Abdul Wahhab) ya ce: " Ziyarar kabarin Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yana daga mafifitan Aiyuka ". ☐ Haka ne ☐ Kuskurene.
6. Bibiyar wurare da guraben Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam-:
☐ Mustahab ☐ Hukuncin ya banbanta gwargwadon nauin bibiyar ☐ Haramunne.
7. Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam ya- ya iyakance tsoro ga al'ummarsa kan:
………………………………………………………………………………………
8.Munasabar da tasa Mawallafin ya kawo ayoyi uku karkashin babin: " Abin da yazo na cewa wani bangare daga wannan al'ummar zai bauta wa gumaka ":
☐ Babu wata munasaba. ☐ Ma'anar babin ba za ta fito fili ba sai da hadisan. ☐ Kuskure ne daga wasu makwafan littafin.
9. Mutane sun kasu dangane da salihai zuwa: ☐ Bangare biyu da tsaka tsakiya ☐ Mai Zurfafawa da mai sakaci.

10. Soyayyar salihan bayi tana kasancewa ne da yi musu addu'a, da ba su kariya, da daukar ilimi daga gare su. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

11. Ghuluwwi (wuce iyaka ) dangane da salihai ba shine kadai sababin da ke kaiwa ga kafirci ba, sedai shine mafi haddarinsu . ☐ haka ne ☐ kuskure ne.

12. Shin wuce iyaka yana iya shiga cikin ibadah? ☐ Na'am ☐ A'a.

13. Idan bawa ba ya tuna bautar Allah har sai yayin da yaga hotunan salihai, to wannan ibada ta shi tawayaya ce ko ma rasassa ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

14. " Bawan Allah ne kuma Manzonsa " wadannan mafi gaskiya kuma mafi daukakar sifofin Annabi -sallallahu alaihi wasallam- ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

15. Ma'anar Al-idra'u shne: ……………………………………………………misalinsa: ..........................................................................................................

16. Fadin Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam-: " Kada ku zurfafa wajen yabo na " yayi kama da zurfawawar Nasara gameda Annabi Isah ko kusa da shi. ☐ Haka ne. ☐ kuskure ne.

17 Wuce iyaka yaana kasancewa cikin: ☐ Yabo ☐ Bauta ☐ Aiki ☐ duka baki daya.

18. Su wanene الْمُتَنَطِّعُونَ?:……………………………………………………………………

19." أَهْلَكَ " (ya hallaka), Ma'anarsa halakar ☐ Addini ☐ Gangan jiki ☐ Duka biyun.

20 Addinin Allah yana gudana ne tsakanin masu wuce iyaka cikinsa da masu tauyewa? ☐ Haka ne . ☐ Kuskure ne.

21.*At-Tanaddu'u* yana aukuwa ne cikin ☐ *Al-Kalam* (zance) ☐ *Aqwal* (maganganu) ☐ Duka biyun.

22. Dukkan al'ummah sunyi ittifaqin cewa Sayyidinal Hussain kayi daya ne gare shi, amah a zahiri kuma yanada sama da kayuka biyar ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

23. Farkon aukuwar shirka a bayan kasa ta auku ne cikin mutanen annabi: ☐ Adam ☐ Nuhu ☐ Ibrahim.

24. Shirka itace farkon abin da aka canza addinin annabawa da ita, kuma sababin hakan shine wuce iyaka dangane da salihan bayi ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

25. Duk wanda yake son ya karfafi addininsa da bidi'a to lallai cutarwarta tafi amfaninta ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

26. Duk abin da aka rike shi a matsayin idi wanda yake maimaituwa duk sati, ko shekara kuma Shari'a bata tabbatar da shi ba, ya zamo ☐ Bid'ah ☐ Halal ☐ Sunnah.

27. Bid'ah sababi ne na kafirci, ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne, saboda sabubban kafirci sunada yawa.

28. Sababin dauke ilimi ☐ Mutuwar malamai ☐ Rafkana ☐ Kawar da kai daga ilimin ☐ Shagaltuwa da duniya ☐ Duk gaba daya.

29. Ziyarar Makabartu ☐ Ya halarta ☐ Bid'ah ce ☐ Shirka ce ☐ Duka gaba daya.

30. Ziyarar da aka nufi amfanar da matattu da ita tare da tuna lahira bidi'a ce (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ), Ziyarar da aka yi ta da nufin amfanuwa da matattu halal ce. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

31. Duk wani sababin da yake katange mutane addininsu ana kiransa
☐ Fitinah ☐ Bid’ah ☐ Shirme.
32. " La'anar Allah kan Yahudawa ":
☐ Mummunar addu'a ce a kansu ☐ Labari ne cewa Allah Ya tsine musu ☐ Zai iya daukar ma'anonin biyu.
33. Ma'anar “ Rikan kaburbura masallatai ” ☐ Yin sujada a wajensu ☐ Gina wuraren ibada a kansu ☐ Duka biyun.
34. Riwayar خُشِيَ ( An ji tsoro ), jin tsoron ya auku ne daga?
☐ Annabi Muhammad ☐ Sahabbai.
35. An ki fitar da kabarin annabi fili saboda ☐ An ji tsoro ☐ Ya ji tsoro ☐ Dukkan Annabi ana bisine shi a wajen da ya mutu ☐ Duka ukun.
36. Ma'anar “ Fitar da kabarinsa fili ”?…………………………………………………
37. Hukuncin cewa annabi Muhammad habiibullah ☐ Halal ne ☐ An rage matsayinsa ☐ Mustahabbi ne.
38. Fadin: “Ibrahim khalilullah, Muhammad habibullah”
☐ Halal ne ☐ Mustahabbi ne ☐ Bai halatta ba.
39. *Al-Khullah* ( Matsayin Badadi ) Bata tabbata ba sai wa mutum biyu:
☐ Annabi Ibrahim ☐ Annabi Ibrahim da Annabi Muhammad ☐ Su biyun da wasunsu.
40. Wanda ya gina Masallaci a kan kabari ☐ Sai a tone kabarin ☐ Sai a rushe Masallacin a bar kabarin.
41. Sallah ba ta halatta ☐ Zuwa ga kaburbura ☐ a kan kaburbura ☐ Cikin kaburbura ☐ Duka ukun.
42. Mutane sun sha ban ban ta fiskar: ☐ Alkhari ☐ Sharri ☐ Duka biyun.
43. Mafi sharrin mutane sune wadanda ☐ Kiyama zata riske su suna raye ☐ Suna rikan kaburbura wuraren ibada ☐ Duka biyun.
44. Wajibi ne mu nisanci: ☐ Shirka ☐ Hanyoyin da suke kaiwa ga shirka ☐ Duka.
45. Babu laifi gabatar da sadaka a wajen kabari, sallah ce kadai aka hana.
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
46. Kamanceceniya da mushrikai babban laifi ne. ☐ Idan aka nufaci kamanceceniyae ☐ Duka daya ne, anyi nufin kamanceceniya da su ko ba ayi ba.
47. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya tsoratar kan rikan kaburbura masallatai. ☐ A rayursa ☐ Kafin mutuwarsa da kwanaki biyar. ☐ Yayin mutuwarsa ☐ Duka ukun.
48. Falalar imani da aiyuka na kwarai yana sama da falala ta nasaba. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
49. Fadin Annabi "Ya Allah karka sanya kabarin gunki ". ☐ Allah Ya amsa addu'arsa ☐ Hikimar Allah ta hukumta sabanin haka.
50 Ziyarar mata zuwa ga makabartu yana cikin manyan laifuka. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
51. Annabi Muhammad -sallallahu ‘alaihi wasallam- ☐ Ya kare janabin tauhidi ☐ Ya toshe dukkan hanyar da zata kai ga shirka. ☐ Duka biyun.

52. Ma'ana fadin Annabi " Kada ku mayar da gidajenku makabartu ". ☐ Kada kuyi biso a cikinsu. ☐ Karku bar yin sallah a cikinsu ☐ Duka biyun.

53. Ba a nikan gari don ziyarar kabarin Annabi -sallallahu alaihi wasallam-, kuma kuskure ne mu yawaita kaikomo awurin kabarin. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

54. Karanta salati da sallama wa Annabi -sallallahu alaihi wasallam- tana kasancewa ne: ☐ A wajen kabarinsa, kuma ana iya bada wasici ga matafiyi zuwa ga Madina da ya isar da gaisuwar muta ne zuwa ga Annabi ☐ Ana iya masa salati da sallam daga ko ina ( Da kai da wanda yake andalos duk daya ne, -ma'ana gaisuwarku da salatinku suna isa zuwa gare shi - ).

55. Ma'anar " Karku mayar da kabirina idi ":……………………………………………….

56. Shirka ba za ta auku cikin wannan al'umma ba, saboda Allah Ya tsare ta.
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

57. *Fadin Allah Ta'alah [..Aka ba su wani kaso na littafi ](QS. An-Niisa : 51).*
Ba a ba su dukan littafin ba, an haramta mu su wani sashensa saboda zunubbansu.
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

58. Ilimi baya hana ma'abocinsa aukawa cikin sabon Allah. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

59. Shin birrai da aladu ragowar wadancan mutanen da aka shafe su ne.
☐ Na'am ☐ A'a

60. Wuce iyaka cikin kaburbura ko da kadan ne zai iya kaiwa zuwa ga abin da yafi shi muni. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

61. Babu wani sabon Allah da ake yin ta a yau face sai ka samu tanada asali daga al'ummar baya. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

62. Bayan rarrabuwar wannan al'ummar, da kasaantuwar sashenta na halaka sashe, Allah Ya dora abokin gaba a kansu daga wajensu.
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

63. Shugaba zai iya zamowa cikin: ☐ Alheri kadai ☐ Alheri da sharri.

64. Mafi girman abin da ake tsoro wa al'umma shine: ☐ Jagorori masharranta ☐ Bibiyar tafarkin Yahudu da Nasara.

65. An amsa addu'oin Annabi -sallallahu alaihi wasallam- guda biyu , [1]…………………
…………………………………………[2]………………………………………………………..
Ba a amsa ma sa ta ukun ba………………………………………………………………

## [24] BABIN ABIN DA YAZO KAN SIHIRI

● Sihiri ba ya yiyuwa sai ta hanyar shirka da Allah, kuma shaidanu ba sa hidimta wa mutum se domin maslaharsu, itace batar da banu Adama da aukar da su cikin shirka da sabon Allah.

**DALILI NA DAYA:**

Da fadin Allah Ta'ala:

وَلَقَدْ عَلِمُواْ لَمَنِ اشْتَرَاهُ مَا لَهُ فِي الآخِرَةِ مِنْ خَلاَقٍ

*[ **Kuma lallai ne hakika sun sani cewa tabbas duk wanda ya saye shi -sihiri- ba ya da wani rabo a cikin lahira** ] (QS. Al-Baqarah : 102).*

**DALILI NA BIYU:**

Da fadin Allah Ta'ala:

يُؤْمِنُونَ بِالْجِبْتِ وَالطَّاغُوتِ

*[ Suna yin imani da gunki da dagutu ] (QS. An-Niisa : 51)*

قَالَ عُمَرُ: (الجبتُ: السِّحْرُ، وَالطَّاغُوتُ: الشَّيْطَانُ)

Umar yace: (( Aljibt: sihiri, Addagut: Shaidan )).

وَقَالَ جَابِرُ: (الطَّوَاغِيتُ: كُهَّانٌ كَانَ يَنْزِلُ عَلَيْهِمُ الشَّيْطَانُ، فِي كُلِّ حَيٍّ وَاحِدٌ).

Jabir kuma ya ce. (Addawagit: sune: bokaye, shaidan yana sauka a gare su, cikin kowace kabila shaidani guda ).

● اشْتَرَاهُ : Ma'ana: تعلّمه ( Ya koye shi ).

● (( Dagutu: Shaidan )): Wannan tafsiri ne ta hanyar buga misali, domin ma'anar dagutu yafi fadi sama da ma'anar shaidan .

( Shin ana iya rasa rabon lahira kwata-kwata ko kawai wani bangare ake iya rasawa? )

**Magana ta farko:** Ana karanta ayoyin gargadi ne gwargwadan yanda suka zo, kuma ba a hada su da ayoyin da suka kunshi alkawarin gafara, domin kada a raina sha'aninsu; saboda fadin Allah: *[ kuma ba ma aikawa da ayoyi sai don tsoratarwa ]. (QS. Al-Israa: 59)*; Allah ta'ala Ya kawo su a siyakin tsoratarwa ne da razanarwa daga wannan aikin (munanan aiyuka).

**Magana ta biyu:** Ana hada nassoshin gargadi tare da ayoyin alkawari, sannan ana rasaba rabon kamar haka:

**Dukkan rabon ake rasawa:** idan sihirin ya kasance ta hanyar anfani da shaidanu.

**Wani bangare ake rasawa:** idan anyi amfani ne da magunguna da kwayoyi.

**DALILI NA UKU:**

عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ڤ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «اجْتَنِبُوا السَّبْعَ الْـمُوبِقَاتِ»، قَالُوا: يَا رَسُولَ اللهِ، وَمَا هُنَّ؟ قَالَ: «الشِّرْكُ بِاللهِ، وَالسِّحْرُ، وَقَتْلُ النَّفْسِ الَّتِي حَرَّمَ اللهُ إِلَّا بِالْـحَقِّ، وَأَكْلُ الرِّبَا، وَأَكْلُ مَالِ الْيَتِيمِ، وَالتَّوَلِّي يَوْمَ الزَّحْفِ، وَقَذْفُ الْـمُحْصَنَاتِ الْغَافِلَاتِ الْـمُؤْمِنَاتِ».

Daga Abu hurairah -Allah Ya kara yarda agare shi- cewa Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Ku nisanci abubuwa bakwai masu halakarwa " sai sukace: wadansu abubuwa ne ya ma'aikin Allah? Sai ya ce: " Shirka da Allah, da sihiri, da kashe ran da Allah Ya haramta kashe shi sai in da hakki, da cin riba, da cin dukiyar maraya, da juyawa da baya ranar yaki, da yin kazafi wa ya' ya mata, kamammu, muminai da zina ".( Bukhari da Muslim suka rawaito ).

● اجْتَنِبُوا ( ku nisanci ) : Ku barsu tare da nisantarsu, a'ana: mu kasance a wani janibi, su kansance awani janibin wanda ba yanda muke ba.

● السَّبْعَ (Abubuwa bakwai ) : Wannan ba ya nufin iyakance abubuwan da suke halakarwa, soboda akwai wasu abubuwan wadanda ba su ba.

● وَأَكْلُ الرِّبَا (Da cin riba): Ma'anar sa: karbar riba, duka daya ne; yayi amfani da shi wajen abinci ne, ko shimfida, wani abun daban, riba shine: fifiko wajen cinikayya cikin abubuwan da wajibi ne a daidaisu, da jinkiri wajen cinikayya cikin abubuwan da wajibi ne karbarsu yayin cinikin: [1] riba fadl (Kari). [2] Riba nasiah (Jinkiri).

● " Da cin dukiyar maraya " : Maraya shine wanda babansa ya mutu kafin balagarsa, namiji ne ko mace.

● Juya baya ranar yaki tsakanin kafurai da musulmai.

● " Da kazafi wa kamammun mata mumina da zina ": Jifar mumina ya', da zina.

**Rayukan da Allah Ya haramta kashe su guda Hudu**

**MUMINI:** Haramun ne kashe shi, saboda imaninsa.

**KADON AMANA:** Kafiri zimmiy shine wanda yake zaune a kasar musulmai bisa sharadin ya bada jizya (haraji).

**ANYI ALKAWARIN ZAMAN LAFIYA DA SHI:** Ba zai yakemu ba, muma ba zamu yake shi ba.

**WANDA AKA BASHI AMINCI:** Tsakaninmu da shi akwai aminci, domin kasuwanci ko fahimtar da shi Addini.

(Sai idan da hakki ) Dayan uku:

- Ran da ta kashe rai
- Bazawari mazinaci
- Wanda yayi ridda

Juya baya yana halatta a wurare uku:

***Face wanda ya karkata domin sake komawa*** *(QS. Al-Anfal : 16)*:

kamar wanda ya juya domin gyara kimtsi ko shirya makamai, ko kuma domin ya bullo ta wata jiha ta daham

***Ko wanda ya je domin haduwa da gungu na wata jama'ar*** *(QS. Al-Anfal :16)*:

domin komawa cikin wata rundunar mayaka saboda wata larura da sharadin kada mayakan su cutu..

**Yayin da yawan kafirai yafi ninki biyu na musulmai:**

To ya halatta a gudu a wannan yanayin.

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنْ جُنْدُبٍ مَرْفُوعًا: «حَدُّ السَّاحِرِ: ضَرْبُهُ بِالسَّيْفِ»، رَوَاهُ التِّرْمِذِيُّ، وَقَالَ: (الصَّحِيحُ أَنَّهُ مَوْقُوفٌ).

Daga Jundub daga annabi: " **Haddin mai sihiri: a sare wuyarsa da takwabbi** " [Tirmizi ne ya rawaito kuma ya ce: abin da yafi inganci shine hadisi ne mauqufi - Hadisi Mauqufi shine maganar sahabi ba na Annabi ba- ].

**DALILI NA BIYAR:**

وَفِي «صَحِيحِ الْبُخَارِيِّ» عَنْ بَجَالَةَ بْنِ عَبَدَةَ قَالَ: كَتَبَ عُمَرُ بْنُ الْخَطَّابِ: أَنِ اقْتُلُوا كُلَّ سَاحِرٍ وَسَاحِرَةٍ، قَالَ: فَقَتَلْنَا ثَلَاثَ سَوَاحِرَ.

Yazo cikin (( Sahihul Bukhari )) daga Bajalatu dan Abadata ya ce: Umar dan khaddab ya rubuta cewa: "**Ku kashe dukkan mai sihiri namiji ko mace**", ya ce: sai muka kashe mata masu sihiri guda uku.

**DALILI NA SHIDA:**

وَصَحَّ عَنْ حَفْصَةَ أَنَّهَا أَمَرَتْ بِقَتْلِ جَارِيَةٍ لَهَا سَحَرَتْهَا، فَقُتِلَتْ.

Kuma ya tabbata daga Hafsah, ta bada umurni da akashe wata baiwarta da tayi mata sihiri, sai aka kashe ta.

**DALILI NA BAKWAI:**

وَكَذَا صَحَّ عَنْ جُنْدَبٍ، قَالَ أَحْمَدُ: (عَنْ ثَلَاثَةٍ مِنْ أَصْحَابِ رَسُولِ اللهِ ﷺ).

Hakanan ya tabbata daga Jundub, Imam Ahmad ya ce: (Hakan ya tabbata daga mutum uku cikin sahabban Annabi saliallahu ‘alaihi wassallam ).

**Menene hukuncin sihiri?**

**Magana ta farko TA: (Shaikh Muhammad bin Abdul Wahhab rahimahullah):** Sihiri dukkaninsa kafirci ne, kuma mai sihiri kashe shi a keyi kai tsaye, hunkuncin tubarsa yana ga Allah ta’ala.

**Magana ta biyu TA: ( Al-Imam Shafi’i Rahimahullah),** Shaikh Muhammad bin Shaleh Al-Utsaimin rahimahullah ya rinjayar da wannan maganar.

**Sihirin Shaidanu:** Mai aikata shi yayi ridda ana umurtarsa da ya tuba, idan ya tuba, sai akashe shi a matsayin haddi saboda shi musulmi ne, idan yaki tuba sa a kashe shi a matsayin kafiri wanda yayi ridda.

**Sihir magunguna da kwayoyi:** Hukuncin mai aikata shi hukuncin dan ta'adda, ana tsayar ma sa da haddin kisa a matasayin musulmi.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tafsir Ayar surat Al-Baqarah. ( ***Kuma hakika sun sani duk wanda ya koye shi)*** *(QS. Al-Baqarah : 102)*

2. Tafsir Ayar surat An-Nisa'i. ***[Sunayin imani da gunki da dagutu ]*** *(QS. An-Niisa : 51)*

3. Tafsirin Al Jibt da Atdagut da banbancin da ke tsakaninsu. (**Al-Jibt**: dukkan abin da babu alkhairi cikinsa na sihiri ko waninsa, **Dagutu**: Duk abin da bawa ya ketare iyakansa; na wani abin biyayya, ko wani abin bauta, ko wani wanda ake ma sa da'a).

4. Dagutu zai iya zamowa daga cikin aljanu ko mutane. ( idan aka ambaci dagutu saki-wawai to Shaidanin aljanu ake nufi, boka shaidani ne daga cikin mutane. ).

5. Sanin abubuwa masu halakarwa guda biyar wadanda akayi hani kansu a kebe.

6. Mai sihiri kashe shi akeyi.

7. Kashe shi a keyi ba a neman ya tuba. ( idan hukuncin haddi ya isa zuwa ga shugaba to ba a neman mai laifin da ya tuba kashe shi akeyi ta ko wani hali, amma wanda ya kafirta ana nemansa da ya tuba ).

8. Idan har an samu masu sihiri a zamanin Umar, to yaya bayansa kuma?

Fatawar cewa kashe mai sihiri daga Jagora abu ne da ya dace da kaidodin Shari'a, domin masu sihiri barna suke yadawa a bayan kasa, barnarsu itace mafi girman barna, kashe su wajibi ne a kan shugaba, baya halatta ga shugaba yaki kashe su, saboda barin irinsu bada dama ce ta yaduwar barnarsu a kasashensu da ma wadansu kasashen amma idan aka kashe su to mutane za su kubuta daga sharrinsu, kuma sauran al'umma za su dauki darasi suji tsoron aikata sihirin.

## [25] BABIN BAYANIN WASU NAU'UKA NA SIHIRI

Bayan mawallafin ya ambaci sihiri da hukuncinsa, yanzu kuma zai bayyana maka wani abu daga nau'ukan sihirin don kasan cewa sihiri yana da nau'uka sannan kuma ka nuisance su.

### DALILI NA FARKO:

قَالَ أَحْمَدُ: حَدَّثَنَا مُحَمَّدُ بْنُ جَعْفَرٍ، حَدَّثَنَا عَوْفٌ، عَنْ حَيَّانَ بْنُ الْعَلَاءِ، حَدَّثَنَا قَطَنُ بْنُ قَبِيصَةَ، عَنْ أَبِيهِ، أَنَّهُ سَمِعَ النَّبِيَّ ﷺ قَالَ: «**إِنَّ الْعِيَافَةَ، وَالطَّرْقَ، وَالطِّيَرَةَ؛ مِنَ الْجِبْتِ**»، قَالَ عَوْفٌ: (الْعِيَافَةُ: زَجْرُ الطَّيْرِ، وَالطَّرْقُ: الْخَطُّ يُخَطُّ بِالأَرْضِ)، وَالْجِبْتُ -قَالَ الْحَسَنُ-: (رَنَّةُ الشَّيْطَانِ). إِسْنَادُهُ جَيِّدٌ، وَلِأَبِي دَاوُدَ وَالنَّسَائِيِّ وَابْنِ حِبَّانَ فِي «صَحِيحِهِ» الْمُسْنَدُ مِنْهُ.

Imam Ahmad ya ce: Muhammad dan Ja'afar ya bamu labarin cewa Aufu ya bamu labara, daga Hayyan dan Alaa, Qadanu dan qabisa ya bamu labari, daga babansa, cewa yaji Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " **lallai ne, tsorata tsuntsaye, da bugun kasa, da camfi; nau'uka ne na sihiri** " Aufu ya ce: (**Al-iyafah:** tsorata tsuntsaye, **Addarku:** Zane ne da ake zanawa a kasa ), **Aljibt**: -Al-Hassan ya ya ce-: (**Rannatushaidani** – wahayin shaidan ). Labarin yazo ta hanya mai kyau.

### DALILI NA BIYU:

وَعَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ڤ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «**مَنِ اقْتَبَسَ شُعْبَةً مِنَ النُّجُومِ فَقَدِ اقْتَبَسَ شُعْبَةً مِنَ السِّحْرِ؛ زَادَ مَا زَادَ**»، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ بِإِسْنَادٍ صَحِيحٍ.

Daga Abdullahi dan Abbas –Radiyallahu anhu- yace: Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " **Duk wanda ya koyi wani bangare na ilimin taurari hakika ya koyi wani bangare na sihiri; ya kara abin da ya kara** " ( Abu Dawud ne ruwaito da sanadi mai inganci ).

### DALILI NA UKU:

وَلِلنَّسَائِيِّ مِنْ حَدِيثِ أَبِي هُرَيْرَةَ ڤ: «**مَنْ عَقَدَ عُقْدَةً ثُمَّ نَفَثَ فِيهَا فَقَدْ سَحَرَ**، وَمَنْ سَحَرَ فَقَدْ أَشْرَكَ، وَمَنْ تَعَلَّقَ شَيْئًا وُكِلَ إِلَيْهِ».

Yazo cikin sunan na Imam An-Nasa'i Abu Hurairah -Radhiallahu'anhu- Ya ce: " **Duk wanda ya kulla wata kulli sa'annan yayi tofi a cikintsa, to hakika yayi sihiri**, kuma duk wanda yayi sihiri to lallai yayi shirka, kuma duk wanda ya rataya wani abu to za a sa shi ya dogara da wannan abun ".

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «أَلَا هَلْ أُنَبِّئُكُمْ مَا الْعَضْهُ؟ هِيَ النَّمِيمَةُ؛ الْقَالَةُ بَيْنَ النَّاسِ».
رَوَاهُ مُسْلِمٌ.

Daga Ibnu Mas'ud; Manzon -Sallallahu'alaihi wasallam- ya ce: " Shin ba na fada muku menene Al'adhu ba? Itace annamimanci; tsegumi tsakanin mutane " ( Muslim ne ya rawaito shi ).

**DALILI NA BIYAR:**

وَلَهُمَا عَنِ ابْنِ عُمَرَ ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «إِنَّ مِنَ الْبَيَانِ لَسِحْرًا».

Yazo cikin sahihul Bukhari da muslim daga ibnu Umar -Radiyallahu'anhu- Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Lallai ne daga cikin bayani akwai sihiri ".

- *Iyafah*: Tsawatar da tsuntsu domin campi ko fatan wani abu mai kyau da aikinsa.
- A'd'darq : Bugun kasa domin sihiri ko bokanci.
- *Ath-'diyarah*: Campi da wani sanannen tsuntsu, wanda ake ganinsa, ko a ji kukansa, a wani zamani ko wani waje.
- رَنَّةُ الشَّيْطَانِ: Wahayin Shaidan, da shiftarsa.
- **الْعَضْهُ:** Yankewa da rabawa, menene dalilin kawo shi karkashin babin sihiri: domin bayanin cewa raba tsanin wadansu itace babbar manufar kowani annamimi da mai sihiri, kuma barnar Annamimi a cikin mutaane tafi barnar mai sihiri.

**Ilimin taurari ya kasu kashi biyu:**

**Ilmut ta'asir**

Yayi nuni da taurari game da abubuwan da za su faru -na gaibu- a bayan kasa

**Karamar shirka:** Idan ya kudurce cewa taurari sabubba ne, Alhali Allah ta'aala bai sanya su zamo sabubba ba wajen sanin gaibu.

**Babbar shirka:** Idan ya kudurce cewa taurari suna da tasirin yin wani abu da kansu, kuma suna iya jawo amfani da tunkude cuta.

**Ilmut tasyiir**

Ilimin falaki (taurari) da yake taimakawa wajen sanin jihohi, lokuta, Alqiblah.

**halal:** yana nuni da su akan lokuta da wurare, kamar yanda Allah ya fadi: ***{kuma da alamomi, kuma da taurari suke neman shiriya }*** *(QS. An-Nahl 16).*

**Wajibi:** Duk abin da wajibi ba zai cika ba seda shi to wajibi ne, Kaman wanda yake sahara ko yake dokan daji wajibi ne a kansa sanin qibla.

● الْبَيَانِ: Bayani, cikakkiyar fasaha da take kama hankula, kuma ta canza tunani, bayani ya kasu gida biyu:

1. **Mai kyau**: bayanin da ya kunshi tabbatar da gaskiya da bata karya.

2. **Mara kyau**: Wanda ya kunshi mayar da gaskiya da tabbatar da karya.

● **Menene alakar bayani da sihiri?** Saboda bayanin da aka gina shi akan karya yayi tarayya da sihiri wajen gaskiya hakikaninsa ( zuwa karya ).

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tsawatar da tsuntsu da bugun kasa da campi nau'uka ne na sihiri (Al-jibt).

2. Tafsirin AL-iyafah da AD- 'darq.

3. Ilmin taurari naui ne na sihiri. (Ilmut ta'asir - ilimin sanin gaibu da iayawarsu).

4. Yin kulli tare da tofi shima naui ne na sihiri.

5. Annamimanci tsakanin mutane nau'i ne na sihiri. (Domin yana raba tsakanin mutane Kaman yanda sihiri yakayi ).

6. Wani sashe na fasaha yana daukan ma'anar sihiri. ( Mutum mai fasaha yana iya kawar da tunanin wani ko ya zaburar da shi ).

## [26] BABIN ABINDA YAZO KAN BOKAYE DA MAKAMANTANSU

Wannan tartibi na mawallafin ya dace kwarai, bayan yayi maka bayanin sihiri da wasu nau'uka na sihirin, yanzu kuma a wannan babin zai bayyana maka su wanene bokaye, da masu bugun kasa, sannan masu kirdado da taurari, tare da bayanin hukuncin zuwa gare su, da kuma hakikanin yanda ake zuwa wajen nasu.

**DLILI NA BIYU:**

رَوَى مُسْلِمٌ فِي «صَحِيحِهِ» عَنْ بَعْضِ أَزْوَاجِ النَّبِيِّ صلى الله عليه وسلم، عَنِ النَّبِيِّ صلى الله عليه وسلم قَالَ: «مَنْ أَتَى عَرَّافًا فَسَأَلَهُ عَنْ شَيْءٍ فَصَدَّقَهُ؛ لَمْ تُقْبَلْ لَهُ صَلَاةٌ أَرْبَعِينَ يَوْمًا»

Imam Muslim ya rawaito cikin sahihinsa, daga wani sashe na matan Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- daga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " **Duk wanda yaje wajen boka/danduba, sai ya tambaye shi wani abu sannan ya gasgata shi, to ba za a karbi sallarsa ba tsawon kwanaki arba'in** ".

**DALILI NA BIYU:**

وَعَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ڤ، عَنِ النَّبِيِّ ﷺ قَالَ: «مَنْ أَتَى كَاهِنًا فَصَدَّقَهُ بِمَا يَقُولُ؛ فَقَدْ كَفَرَ بِمَا أُنْزِلَ عَلَى مُحَمَّدٍ ﷺ» رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ.

Daga Abu Hurairah -Radiyallahu'anhu- daga Annabi -sallallahu alaihi wasallam- yace: "Duk wanda ya je wajen boka, ya gasgata shi kan abin da yake fada; to hakika ya kafirce wa abin da aka saukar wa Annabi Muhammadu -sallallahu alaihi wasallam-" (Abu Dawud ne ya rawaito ).

**DALILI NA UKU:**

وَلِلأَرْبَعَةِ وَالْحَاكِمِ - وَقَالَ: صَحِيحٌ عَلَى شَرْطِهِمَا - عَنْ ... : «مَنْ أَتَى عَرَّافًا أَوْ كَاهِنًا فَصَدَّقَهُ بِمَا يَقُولُ؛ فَقَدْ كَفَرَ بِمَا أُنْزِلَ عَلَى مُحَمَّدٍ ﷺ».

Ma'abota litattafan sunnah hudu, da Hakim -Kuma Hakim yace: hadisin sahihi ne bisa sharadin Bukhari da Muslim- daga.... "Duk wanda ya je wajen danduba ko boka, sannan ya gasgata shi kan abin da yake fada, to hakika ya kafirce wa abin da aka saukar wa Annabi Muhammad sallallahu alaihi wasallam ".

**DALILI NA HUDU:**

وَلِأَبِي يَعْلَى بِسَنَدٍ جَيِّدٍ عَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ مِثْلُهُ مَوْقُوفًا.

Abu ya'ala ya rawaito misalin hadisin da ya gabata ta hanya maikyau daga Abdullahi dan Mas'ud

● **Litattafan Sunnah hudu: Abu dawud, Tirmizi, Nasa'i, Ibn Majah**.

● “Duk wanda ya je ” : zuwa wajen boka ko da duba na tabbata ne ta hanyar; zama da shi, buga masa waya, ko aika wani zuwa gare shi, ko tura masa da wasika, ko bibiyar tashoshinsu na sadarwa, ko ko shiga yanar gizonsu, ko sayan majallolinsu musamman wadanda suka kunshi Magana kan ilimin taurari, ko sauraran abubuwan da suke fadi, lallai wannan akwai barna maigirma a cikinsa.

● “Ba za a karbi sallarsa ba” : ma'ana ladan da yake samu na sallar, an canza masa da mummunan da ta saryar da ladar. ( zuwa wajensa ba tare da gasgata shi ba ).

● “ Hakika ya kafirce wa abin da aka saukar wa Annabi Muhammad ”: shine: Alqur’ani.

Allah yana fada a cikin Alqur'ani:

قُل لَّا يَعْلَمُ مَن فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ الْغَيْبَ إِلَّا اللَّهُ

*Ka ce: "**Babu wanda yasan gaibi a cikin sammai da kasa face Allah**", (QS. An-Naml : 65).*

Wanda yake gasgata boka cikin da'awar sanin gaibu tareda saninsa cewa babu wani wanda yasan gaibu sai Allah; to wannan ya kafurta babban kafirci, -wanda yafitar da shi daga musulunci- idan kuma jahili ne, wanda ba ya kudurta cewa akwai karya cikin alqu'ani to kafircinsa karamin kafirci ne, kuma zai yiwu yaki gasganta shi a lokacin da ya ba shi labarin, sai bayan aukuwar abinda ya ba shi labarin.

● عَرَّافًا: ***ARRAFAN:*** Suna ce gamammiya da ta kunshi: boka, da masu kirdadon sanin gaibu ta hanyar taurari, da masu bugun kasa da makamantansu, wadanda suke da'awar sanin gaibu da hanyar amfani da gabatar da wadansu abubuwa.

**DALILI NA BIYAR:**

وَعَنْ عِمْرَانَ بْنِ حُصَيْنٍ ؓ مَرْفُوعًا: «لَيْسَ مِنَّا مَنْ تَطَيَّرَ أَوْ تُطُيِّرَ لَـهُ، أَوْ تَكَهَّنَ أَوْ تُكُهِّنَ لَـهُ، أَوْ سَـحَرَ أَوْ سُـحِرَ لَـهُ، وَمَـنْ أَتَـى كَاهِنًـا فَصَـدَّقَهُ بِمَـا يَقُـولُ؛ فَقَـدْ كَفَـرَ بِمَـا أُنْـزِلَ عَلَى مُحَمَّدٍ ﷺ»، رَوَاهُ الْبَزَّارُ بِإِسْنَادٍ جَيِّدٍ.

Daga Imran dan Husain -Allah ya kara yarda a gare shi-, ya daga hadisin zuwaga Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Baya cikinmu wanda yayi campi ko akayi masa campi, ko ya yi bokanci ko aka yi masa bokanci, ko ya yi sihiri ko akayi masa sihiri, duk wanda yaje wajen boka sai ya gasgata shi kan abin da yake fada; to hakika ya kafirce wa abin da aka saukar wa Annabi Muhammadu -sallallahu alaihi wasallam- ". Bazzar ne ya rawaito shi da sanadi mai kyau.

**DALILI NA SHIDA:**

وَرَوَاهُ الطَّبَرَانِيُّ فِي الأَوْسَطِ بِإِسْنَادٍ حَسَنٍ مِنْ حَدِيثِ ابْنِ عَبَّاسٍ؛ دُونَ قَوْلِهِ: «**وَمَنْ أَتَى ...**» إِلَى آخره.

قال الْبَغَوِيُّ: (الْعَرَّافُ: الَّذِي يَدَّعِي مَعْرِفَةَ الأُمُورِ بِمُقَدِّمَاتٍ يَسْتَدِلُّ بِهَا عَلَى الْمَسْرُوقِ وَمَكَانِ الضَّالَّةِ وَنَحْوِ ذَلِكَ)، وَقِيلَ: هُوَ الْكَاهِنُ، وَالْكَاهِنُ هُوَ الَّذِي يُخْبِرُ عَنِ الْمُغَيَّبَاتِ فِي الْمُسْتَقْبَلِ، وَقِيلَ: الَّذِي يُخْبِرُ عَمَّا فِي الضَّمِيرِ.

وَقَالَ أَبُو الْعَبَّاسِ ابْنُ تَيْمِيَّةَ: (الْعَرَّافُ: اسْمٌ لِلْكَاهِنِ وَالْمُنَجِّمِ وَالرَّمَّالِ وَنَحْوِهِمْ مِمَّنْ يَتَكَلَّمُ فِي مَعْرِفَةِ الأُمُورِ بِهٰذه الطُّرُقِ).

Dabarani ya rawaito cikin " Al'ausad " da isnadi mai kyau, daga hadisin ibn Abbass, ba tare da lafazin: " kuma duk wanda ya je…. " zuwa karshensa.

Bagawi ya ce: (**Al'arraf**: shine wanda yake da'awar sanin gaibu bayan gabatar da wasu abubuwa wadanda yake nuni da su a kan wani abun da aka sace ko wurin da wani abu ya bace da makamantansu ), wadansu malaman suka ce: **Al'arraf**: shine boka wanda yake bada labarin abubuwan da zasu kasance a gaba na gaibu, wadansu kuma sukace: **Al'arraf**: shine wanda yake bada labarin abin da ke cikin zuciyar wani.

Abul Abbas ibn Taimiyyah ya ce: (**Al'arraf**: sunane na; boka, mai duba ta hanyar taurari, mai bugun kasa da makamantansu, wanda yake da'awar sanin gaibu ta wadannan hanyoyin ).

- **مَنْ تَطَيَّرَ** (wanda ya yi campi da kansa) : ya kunshi wanda yayi wa kansa ko yayi wa waninsa.
- **أَوْ تُطُيِّرَ لَهُ :** wanda ya umarci wani da yayi masa campin, ko ya yada ayi masa.
- **أَوْ سُحِرَ لَهُ** ( ko akayi masa sihiri ): Saboda wani yana fada ma wanda yake korafin matarsa cewa: zaiyin masa sihiri ba tare da ka aikata wani abu ba, sai ya zaci cewa babu komai a kansa.

**DALILI NA BAKWAI:**

وَقَالَ ابْنُ عَبَّاسٍ - فِي قَوْمٍ يَكْتُبُونَ أَبَا جَادٍ، وَيَنْظُرُونَ فِي النُّجُومِ -: (مَا أَرَى مَنْ فَعَلَ ذَلِكَ لَهُ عِنْدَ اللهِ مِنْ خَلَاقٍ).

Ibnu Abbas ya ce game da wadanda suke rubuta haruf fan: أبا جا د (A, b, j, d) sannan suyi dubi cikin taurari-: ( ba na ganin wadanda suuka aikata hakan

Sunada wani rabo a wajen Allah ).

● Koyon aiki haruffan: أبا جا د (abjad) ya kasu kasha biyu:

1. **Wanda ya halatta:** koyansu domin lissafin jumloli, da makamantansa, malamai basu gushe ba suna amfani da su wajen rubuta tarihi.

2. **Haramun:** wanda ya koye su domin kulla alaka da tafiyar taurari, motsawarsu, fudowarsu da faduwarsu.

Hukumcin tambayar 'dan duba da makamantansa

| Tambaya kadai: | Tambaya tare da gasgata shi: | Tambayarsa domin gwada shi: | Tambayarsa domin bayyana gajiyawarsa da karyarsa: |
|---|---|---|---|
| Babban laifi ne: saboda fadin Annabi sallallahu alaihi wasallam: "Ba za a karbi sallarsa na kwanaki arba'in ba". | Wannan babban kafirci ne, domin karyata Alqur'ani ne. | Ya halatta, domin sanin gaskiyarsa daga karyarsa, bai tambaye shi domin daukar maganarsa ba, da sharadin cancantar mai tambayar. | Abin nema ne, wajibi ne, da sharadin cancantar wanda zai yi tambayar. |

**Alamun Mai sihiri (Matsafi):**

1. Ya saba wa sharuddan ruqya ta shari'a.
2. Kulla wani abu tareda yin tofi a cikinsa.
3. Rubuta daidaikun haruffa, ko maganar da ba a fahimtar ma'anarta ta.
4. AsSarfu da Al'adfu (Raba wasu abin da suke hade ko hada suke rabe ta hanyar sihiri ).
5. Yana dubi zuwa ga taurari ( domin da'awar sanin gaibu).
6. Karatun ALkaf ( Tafin hannu ), da Finjan (Karamin kofi).
7. Yakan tambayi sunan mahaifiyar mutum ko sunan wani.
8. Yana da'awar sanin gaibu.
9. Yakan umarci maras lafiya da ya saba ma Shari'a da barin sallah ko barin ambaton Allah wajen yanka.
10. Yanasa maras lafiyan ya ratay da shi ba da Allah ba.
11. Yana jibintar shaidanu.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Gasgata boka da imani da Alqur’an ba sa taba haduwa waje guda. ( wannan yana daga mafi girman kafurci ).

2. Bayani karara cewa bokanci kafirci ne.

3. An fadi hukuncin wanda akayi masa bokanci ( ma'ana: shi da bokan hukuncinsu daya ne, ta fiskan barrantar Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- da su ).

4. An ambaci hukuncin wanda akayi masa camfi.

5. An anbaci hukuncin wanda a kayi masa sihiri ( duk wanda ya nemi ayi masa sihirin to hukuncinsu daya ne da shi da wanda ya yi sihirin wajen uquba ).

6. An ambaci hukuncin wanda ya koyi haruffan: أبا جاد (Abjad). ( hukuncin ya banbanta ta fiskan: halacci ko haramci ).

7. An ambaci banbanci tsakanin boka da dan duba.

## [27] BABIN ABIN DA YAZO NA AN-NUSHRAH (WARWARE

Wannan tartibin yayi kyau matuka, bayan malam ya yi Magana game da sihiri, yanzu kuma zai yi maka bayanin yanda ake warware sihirin bayan aukuwarsa, babu shakka warware sihiri daga wanda akayi wa sihirin, ta hanyar shari'a, akwai falala maigirma ga wanda ya yi domin neman yarda Allah ta'alah.

**DALILI NA FARKO:**

عَنْ جَابِرٍ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ سُئِلَ عَنِ النُّشْرَةِ، فَقَالَ: «**هِيَ مِنْ عَمَلِ الشَّيْطَانِ**»، رَوَاهُ أَحْمَدُ - بِسَنَدٍ جَيِّدٍ - وَأَبُو دَاوُدَ.

Daga Jabir; an tambayi Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- dangane da warware sihiri, sai yace: **" yana daga aiyukan shaidan "**, ( Ahmad ne ya rawaito - da sanadi mai kyau- da Abu Daud ).

**DALILI NA BIYU:**

وَقَالَ: سُئِلَ أَحْمَدُ عَنْهَا؛ فَقَالَ: ابْنُ مَسْعُودٍ يَكْرَهُ هٰذَا كُلَّهُ.

An tambayi Imam Ahmad gameda An-Nushrah sai yace: ibn Mas'ud yana kinsa – yana haramta- shi gaba daya.

- " An-Nushrah ": Ma'ana irin wanda suka sani a lokacin jahiliyyah da mutane ke yi.
- " Yana daga aiyukan shaidan ": jingina shi zuwa ga shaidan yafi kaiwa matuka wajen bayanin muninsa da nisanta mutane daga gare shi.
- " Yana kinsa ": " Makruhi " a wajen magabata suna amfani da shi a matsayin haram.
- Yana kin An-Nushra gaba daya : Ma'ana: yana haramta Nushrah wanda yake dangin aikin shaidan, shine: warware sihiri da sihiri.

**DALILI NA UKU:**

وَفِي الْبُخَارِيِّ عَنْ قَتَادَةَ: قُلْتُ لِابْنِ الْمُسَيِّبِ: رَجُلٌ بِهِ طِبٌّ أَوْ يُؤَخَّذُ عَنِ امْرَأَتِهِ؛ أَيُحَلُّ عَنْهُ أَوْ يُنَشَّرُ؟ قَالَ: (لَا بَأْسَ بِهِ، إِنَّمَا يُرِيدُونَ بِهِ الإِصْلَاحَ، فَأَمَّا مَا يَنْفَعُ فَلَمْ يُنْهَ عَنْهُ) انْتَهَى.

Yazo cikin sahihul Bukhari daga katada: nace wa ibnul Musayyab; mutumin da akayi masa asiri ko aka katange shi daga matarsa; shin za a iya warware masa wannan asirin? Sai yace: ( babu laifi a warware masa, domin gyara suka nufata da shi, duk wanda akwai amfani cikinsa to ba a yi hani a kansa ba ).

● "طِبٌّ ": Ma'ana: sihiri, abun da aka sani shine **Addibbu**: maganin rashin lafiya, an kira sihiri dibbu ne a babin fata maikyau, kamar yanda aka kirayi wanda maciji ko kunama ta sare shi da: warkakke, sannan aka kirayi wanda ya karye da: dorarre.

● " يُؤَخِّذُ عَنِ امْرَأَتِهِ ": mutumin da aka sanya shamaki tsakaninsa da matarsa -ta hanyar sihiri-, baya iya saduwa da ita, kuma lafiyarsa kalau, to wannan nau'i ne na sihiri.

**DALILI NA HUDU:**

وَرُوِيَ عَنِ الْـحَسَنِ أَنَّهُ قَالَ: (لَا يَحُلُّ السِّحْرَ إِلَّا سَاحِرٌ).

قَالَ ابْنُ الْقَيِّمِ: (النُّشْرَةُ: حَلُّ السِّحْرِ عَنِ الْـمَسْحُورِ، وَهِيَ نَوْعَانِ:

أَحَدُهُمَا: حَلٌّ بِسِحْرٍ مِثْلِهِ، وَهُوَ الَّذِي مِنْ عَمَلِ الشَّيْطَانِ، وَعَلَيْهِ يُحْمَلُ قَوْلُ الْـحَسَنِ، فَيَتَقَرَّبُ النَّاشِرُ وَالْـمُنْتَشِرُ إِلَى الشَّيْطَانِ بِمَا يُحِبُّ، فَيُبْطِلُ عَمَلَهُ عَنِ الْـمَسْحُورِ. الثَّانِي: النُّشْرَةُ بِالرُّقْيَةِ، وَالتَّعَوُّذَاتِ، وَالدَّعَوَاتِ، وَالأَدْوِيَةِ الْـمُبَاحَةِ؛ فَهٰذا جَائِزٌ).

An rawaito daga Al Hasan ya ce: (ba a warware sihiri ta hanyar sihiri ).

Ibnul qayyim ya ce: ( Warware sihiri daga wanda akayi wa sihirin iri biyu ne:

**Na farko:** Warware sihiri da sihiri irinsa, to wannan shine dangin aikin shaidan, a kansa ake daukan maganar Al Hassan, saboda mai warwarewan da wanda ya nemi a warware duk suna neman kusanci zuwa ga shaidan da aikata abin da yake so, daga nan sai ya lalata wannan sihirin daga wanda akayi wa sihirin.

**Na biyu:** Lalata sihiri ta hanyar ruqyah, da karanta ayoyi da addu'oin neman tsari, da magungunan da ya halatta ayi amfani da su, to wannan halal ne ).

**Yaya zamu yi raddi ga wanda ya halatta warware sihiri da sihiri?**

1. Wannan ya saba wa Alqur'ani da, Sunnah, da abin da Sahabbai da salaf suke kai.
2. Kuma hakan zai raunana abin da ya tabbata na yin magani da Al qur'ani da Addu'oin da suka tabbata a cikin Sunnar Annabi`.
3. Kuma akwai karfafa sihiri da matsafa wajen kara samun matsayi a wajen gama garin mutane.
4. Akwai sauya abinda ake da yakini kansa, na yin magani da Alqur'ani da adduo' i tabbatattu zuwa ga abin da yake zato.

5. Babu makawa cikin warware sihiri da sihiri neman kusancin mai warwarewan da wanda yasa a warware sihirin zuwaga shaidan da irin abin da yake so har ya warware musu wannan sihirin .
6. Idan wanda akayi masa sihiri ya yi hakuri to yanada aljannah kamar yanda ya tabbata daga Annabi sallallahu alaihi wasallam..
7. Warware sihiri da sihiri yana kara ma wanda akayi wa sihirin a kan sihirin farkon.
8. Anyi asiri wa Annabi -sallallahu alaihi wasallam- baiyi magani ta hanyar sihiri ba, ya ya yi magani ne ta hanyar ruqyah a shari'ance .

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Hani kan An-Nushrah ( warware sihiri da sihiri ).

2. Banbanci tsakanin An-Nushrah wanda aka hani a kai -warware sihiri da sihiri- da wanda akayi rangwami cikinsa, wanda yake kawar da matsalar.

(Ana daukan maganganu duk wadanda suka halatta warware sihiri akan; Ruqyah, da karanta ayoyin neman tsari, da magunguna, da adduoi wadanda suka tabbata.

Sannan wadanda suka haramta An-Nushrah, suna nufin idan yazamo ta hanyar sihiri ne, -domin warware sihiri da wani sihirin dukkaninsu haramun ne- Allah ne mafi sani.

## [28] BABIN ABIN DA YAZO NA HUKUNCIN CAMPI (ATTADAYYUR)

● **Campi yana kore tauhidi:**
1. Saboda mai campi ya yanke tawakkalinsa da Allah, ya dogara da waninsa.
2. Mai campi ya rataya da abin da ba shi da hakika, dimuwa da kirdado, riko da tauhidi ibada ce kuma neman taimako ne da Allah.

● **At-Tadayyur:** Ma'anar campi a Shari'ance: Yin campi da wani abin da ake ganinsa, ko ake jin sautinsa ko wani sanannen abu na zamani ko lokaci.
1. **Wanda ake ganinsa:** Misali, mutum ne yaga tsuntsu sai yayi campi da shi saboda kasancewarsa baki ko mai ban tsoro.
2. **Wanda ake jinsa:** Misali; wanda yake cikin wata damuwa sai yaji wani yana fada ma wani cewa ( ya asararre ), sai yayi campi da wannan maganar da yajin.
3. **Wani abu sananne:** Kamar yin campi da wadansu kwanaki ko watanni ko shekaru, ko wadansu wuraren.

**DALILI NA FARKO:**

Allah berfirman:

أَلا إِنَّمَا طَائِرُهُمْ عِندَ اللَّهُ وَلَـكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لاَ يَعْلَمُونَ

*[ To, shu'umcinsu a wurin Allah yake, kuma amma mafi yawansu ba su sani ]. ( QS. Al-A'raf : 131).*

**DALILI NA BIYU:**

قَالُوا طَائِرُكُمْ مَعَكُمْ

[ **Sukace: shu'ucinku yana tareda ku** ]. (QS. Yasin : 19)

● طَائِرُهُمْ عِندَ اللَّهُ : ( shu'umcinsu yana wurin Allah ) ma'ana abin a yake samunsu na fari da yankewan ruwan sama duka daga Allah ne, domin shi ya kaddara hakan, Annabi Musa -Alaihis Salam- da mutanensa ba su da wata alaka da faruwar hakan, lamrin yana hukunta cewa su sababi ne na samuwar albarkatu da alkharai.

● طَائِرُكُمْ مَعَكُمْ (shu'umcinku yana tare da ku) : Duk abin da ya faru da ku to kune sababin faruwarsa sakamakon aiyukankum, ku ne sababin janyo shi.

● **Babu cin karo tsakanin ayoyin biyu**: Ayar farko tana nuni kan cewa Allah shine wanda ya kaddara faruwan wannan abun, aya ta biyu kuma tana bayanin cewa sune sababin faruwarsa kuma daga gare su ne, don haka, a hakika campinsu yana tare dasu, ma'ana laziminsu ne.

**DALILI NA UKU:**

وَعَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ؓ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «لَا عَدْوَى، **وَلَا طِيَرَةَ**، وَلَا هَامَةَ، وَلَا صَفَرَ»، أَخْرَجَاهُ، زَادَ مُسْلِمٌ: «وَلَا نَوْءَ، وَلَا غُولَ».

Daga Abu Hurairah -Allah ya kara yarda a gare shi- Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yace: " **Babu harbuwar cuta daga wani zuwa kan wani, kuma babu camfi, babu Mujiya, sannan babu Safar** ". ( Bukhari da Muslim ne suka fitar da shi). Imam Muslim ya kara lafazin: " **Babu Tauraro, kuma babu Fatalwa** ".

**DALILI NA HUDU:**

وَلَهُمَا عَنْ أَنَسٍ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «لَا عَدْوَى، **وَلَا طِيَرَةَ**، وَيُعْجِبُنِي الْفَأْلُ» قَالُوا: وَمَا الْفَأْلُ؟ قَالَ: «الْكَلِمَةُ الطَّيِّبَةُ».

Daga Bukhari da Muslim, daga Anas, Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yace: " **Babu harbuwar cuta daga jikin wani zuwa wani, kuma babu campi, kyakkyawar fata tana burge ni** ", sai sahabbai suka ce menene kyakkyawar fata? ya ce: " **Magana mai kyau** ".

● " لا عدوى ": Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- Ya bata aqidar jahiliyyah ce ta cewar wannan cutar tana tasiri da kanta, ko kuma abin nufi: babu wata cuta da take harbuwa da kanta, iyaka dai sababi ne na harbuwarta da izinin Allah.

● " ولا هامة " : [1] Tsuntsu ne yana kama da mujiya, [2] Mujiya, suna campi da ita.

● "ولا صفر," : Abin nufi da safar kodai ya zamo:

1. Watar Rajab, larabawa sun kasance suna campi da ita, musamman cikin auratayya.
2. Ko kuma: wata cuta ce a cikin ciki, wanda yake kama da rakuma, yana harbuwa daga rakumi zuwa jikin wani rakumin.
3. Ko kuma: **AN-nasi'u,** abin da larabawa sukeyi na haramta watar Safar a madadin Al Muharram, sai su keta alfarmar watar Al Muharram su halarta yaki a cikinsa.

● " ولا نوء " : Masaukan taurari, ko wani masauki yana da tauraronsa, larabawa sun kasance suna campi da su, suna cewa: wannan taurarone shu'umi babu alheri tare da shi, wadansu kuma da akasin haka, suna cewa, wannan tauraro ne mai albarka da alheri.

● " ولا غولا ": Larabawa sun kasance idan zasuyi tafiya sai shaidanu su bayyana musu cikin wani irin yanayi ( Fatalwa ), sai tsoro da bakin ciki su shiga zukatansu, daganan sai su campa wannan tafiyar da rashin sa'a, sai su fasa tafiya yanda suka nufa.

● Abinda Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya kore shine: tasirin wadannan abubuwan, ba samuwarsu ba, don haka, duk abin da bawa yasa a gaba na alheri to ya yi shi cikin dadin rai da sauki da dogaro ga Allah, kar ka munana zato ga Allah.

**DALILI NA BIYAR:**

وَلِأَبِي دَاوُدَ بِسَنَدٍ صَحِيحٍ عَنْ عُقْبَةَ بْنِ عَامِرٍ قَالَ: ذُكِرَتِ الطِّيَرَةُ عِنْدَ رَسُولِ اللهِ  ، فَقَالَ: «أَحْسَنُهَا: الْفَأْلُ، وَلَا تَرُدُّ مُسْلِمًا، فَإِذَا رَأَى أَحَدُكُمْ مَا يَكْرَهُ؛ فَلْيَقُلْ: اللَّهُمَّ لَا يَأْتِي بِالْحَسَنَاتِ إِلَّا أَنْتَ، وَلَا يَدْفَعُ السَّيِّئَاتِ إِلَّا أَنْتَ، وَلَا حَوْلَ وَلَا قُوَّةَ إِلَّا بِكَ».

Abu Daud ya rawaito da sanadi sahihi, daga Uqbatu dan Amir ya ce: an ambaci campi a gaban Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- sai ya ce: mafi kyawunta: Magana mai dadi, saboda bata mayar da musulmi, idan dayanku yaga abinda ba ya so, to ya ce: ya Allah babu mai kawo kyawawa face kai, kuma babu mai tunkude mu'nana face kai, kuma babu dabara babu karfi saida taimakonka ".

| **Banbanci tsakanin Al-Fa'alu da At-Tadayyur** | |
|---|---|
| **Al-Fa'alu (Magana mai kyau)** | **At-Tadayyur (Campi)** |
| Duk abin da zai kara wa mutum nashadi kan wani abu mai kyawu, na Magana ko aiki ko wani abun gani ko abun ji. | Yin campi da wani abun gani ko abun ji ko wani sanannen abu na zamani ko waje. |
| Yana kara tawakkali da Allah. | Yana raunana tawakkali |
| Hukuncinsa: mustahabbi ne. | [1] Karamar shirka: in ya sanya shi sababi.<br>[2] Babbar shirka: idan yayi imani da cewa tana tasiri da kanta. |
| Akwai kyautata zato ga Allah Ta'ala cikinsa | Akwai munana zato ga Allah Ta'ala cikinsa. |
| Wannan hali ne na musulmin da ya tace tauhidi. | Wannan hali ne na munafiki da kafiri. |
| Yana zuwa ne ba tareda nufi ba, ko wata wahala. | Yana zuwa ne tareda nufi kamar (Al-iyafa): tsorata tsuntsu. |
| Baya sanya ka ka zartar da abin da kakeso ko ya hana ka, baya dogara kan abinda ya ji, ko ya gani, sedai yana sa shi cikin farin ciki da nashadi. | Duk abin da ya sa ka yin wani abu ko ya hana ka, tare da dogaro a kan wani abinda ake ganinsa, ko jinsa, wanda ya zamo sababin aikata abinda yakeso. |
| Yana wajabta rataya zuciya da Allah. | Yana wajabta masa ratayuwa abinda yayi campi da shi. |

● **Misali na farko:** mutum ne yake son aure, ko da ya tambayi sunan budurwar sai akace masa sunanta: Hannah, sai ya ci gaba da neman auren, dayan kuma da ya tambayi sunan budurwar sai akace masa sunanta: Sakhrah, sai ya fasa neman auren, duk biyun suna babin campi ne, campi shine abinda ya sa ka, ko ya hana ka.

● **Misali na biyu:** wani mutum ya tambayi sunan budurwa bayan ya riga ya dukufa cikin neman auren, bayan an ba shi labarin sunanta: **Su'ad**, ce, sai yaji dadi ya yi farin ciki, wannan yana shiga babin (**Alfa'al**) ne; kyakkyawar fata, domin hakan bai zamo sanadiyar ci gaba cikin neman auren ko fasawarsa ba, iyaka dai yayi farin ciki ne bayan yariga yayi nisa cikin lamarin.

● Wadansu mutanen kuma suna bude Mushafin Alqur'ani domin suyi kyakkyawar fata, idan idonsa ya sauka kan ayar da ambaton wuta ya zo cikinta sai yayi campi, idan kuma ambaton Aljannah ne sai yace: wannan fata ce mai kyau, wannan yayi kama da aikin Jahiliyyah wadanda suke rabo da kibau na caca.

● **عُقْبَةَ بْنِ عَامِرٍ:** kuskure ne, abinda yake daidai shine: (عروة بن عامرٍ): Urwatu bn Amir.

● “ **Bata mayar da musulmi** ”: Abinda za a fahimta ta hanyar akasi shine: duk wanda campi ya mayar da shi daga bukatarsa to wannan ba musulmi ba ne. (Abun nufi: wanda campi ya hana shi yin wani abina yasa a gaba ).

● **وَلَا قُوَّةَ إِلَّا بِكَ** (Kuma babu karfi se da Taimakon Allah ): Ma'anar haraf in (ب) cikin fadinsa: **بِكَ** kodai ya zamo : [1] **في** (cikin). [2] ko kuma: Isti’anah (se da taimakon Allah ). [3] Ko kuma: Sababiyyah ( sababi ).

**Kashe kashen mutane dangane da**

**Wanda campi bai hana shi yin bukatarsa ba, yana cigaba tare da dogaro da Allah:**
Wannan shine halin musulmi mai kadaita Allah ta'ala cikin bauta. Kuma wannan shine asali.

**Wanda campi ya hana shi yin abinda ya sa a gaba:**
Karamar shirka ce idan ya sanya shi sababi. Babbar shirka ce idan yayi imani da cewa yana da tasiri da kansa.

**Wanda ya cigaba da bukatarsa tare da damuwa da bakin ciki da tsoron abinda aka campa:**
Wannan ya saba wa Allah.

**DALILI NA SHIDA:**

وَعَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ مَرْفُوعًا: «الطِّيَرَةُ شِرْكٌ، الطِّيَرَةُ شِرْكٌ، وَمَا مِنَّا إِلَّا؛ وَلَكِنَّ اللهَ يُذْهِبُهُ بِالتَّوَكُّلِ»، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ وَالتِّرْمِذِيُّ وَصَحَّحَهُ، وَجَعَلَ آخِرَهُ مِنْ قَوْلِ ابْنِ مَسْعُودٍ

Daga Ibnu Mas’ud, -Hadisine da yazo daga Annabi-: " **Campi shirka ce, Campi shirka ce, babu daya daga cikinmu face** -wani abu na campi yakan bijiro masa-, **sedai Allah Ya na tafiyar da shi da tawakkali** ".

Abu Dawud da Tirmizi ne suka rawaito, Tirmizi ya inganta shi, kuma ya ce: jumlar karshen maganar ibn Mas'ud ce ba ta Annabi ba. -fadinsa babu daya daga cikinmu face-.

**DALILI NA BAKWAI:**

**وَلِأَحْمَدَ مِنْ حَدِيثِ ابْنِ عَمْرٍو: «مَنْ رَدَّتْهُ الطِّيَرَةُ عَنْ حَاجَتِهِ؛ فَقَدْ أَشْرَكَ»، قَالُوا: فَمَا كَفَّارَةُ ذَلِكَ؟ قَالَ: «أَنْ يَقُولَ: اللَّهُمَّ لَا خَيْرَ إِلَّا خَيْرُكَ، وَلَا طَيْرَ إِلَّا طَيْرُكَ، وَلَا إِلَهَ غَيْرُكَ».**

Imam Ahmad ya rawaito daga hadisan ibn Amr: " Duk wanda campi ya mayar da shi daga bukatarsa; to hakika ya yi shirka ", sai suka ce: to menene kaffaran wannan? Ya ce: " yace: Ya Allah babu alhairi sai Alhairinka, kuma babu wani campi sai abinda ka hukunta, sannan babu abin bautawa bisa cancanta face kai ".

**DALILI NA TAKWAS:**

وَلَهُ مِنْ حَدِيثِ الْفَضْلِ بْنِ الْعَبَّاسِ: «**إِنَّمَا الطِّيَرَةُ مَا أَمْضَاكَ أَوْ رَدَّكَ**».

Daga Imam Ahmad, ya rawaito daga hadisan Fadl dan Abbas: " **Iyaka dai campi shine abinda ya sa ka yin wani abu ko ya hana ka** ".

● **وَمَا مِنَّا إِلَّا :** Ma'ana babu daya daga cikinmu face wani abu na campi yakan bijiro masa, wannan salo ne na barin ambaton abinda ake kyamar ambatansa, da nisantar lafuzzan shika, da kuma tace tauhidi cikin lafuzza, tare da cewa hikayar Kalmar kafirci ba kafirci ba ne.

● **Tawakkali:** Shine gaskiyar dogaro da Allah cikin janyo amfani ko tunkude cuta, tare da amintuwa da shi, da yin riko da sabubban da Allah ya sanya kasantuwarsu sabubban.

**Menene Maganin Campi:**

1. Da tace tauhidi, domin Allah Yana tafiyar da campi da tawakkali ne, sai mutum ya samu yalwar zuciya da dadinta.

2. Karanta addu'ar da ta tabbata daga Annabi -sallallahu alaihi wasallam-:

**اللَّهُمَّ لَا خَيْرَ إِلَّا خَيْرُكَ، وَلَا طَيْرَ إِلَّا طَيْرُكَ، وَلَا إِلَهَ غَيْرُكَ».**

" Ya Allah babu alhairi sai Alhairinka, kuma babu wani campi sai abinda ka hukunta, sannan babu abin bautawa bisa cancanta face kai ".

3. Ya yi fatan alkhiri, kuma kar yayi campi ko tunaninsa.

4. Duk abinda akwai maslaha cikinsa kar ka yi kasa a guiwa tun farkon yunkuri, yi matukar kokarinka babu kasa a guiwa har Allah Ya yi maka budi.

| Banbanci tsakani quri'a da kibau na caca: | |
|---|---|
| **Quri'a** | **Kibau** |
| **Hukunci**: Halal. | **Hukunci:** Babban laifi ne, Nau'i ne na caca. |
| Manufar shari'a na tabbatuwa da ita | Manufar shari'a baya tabbatuwa da ita. |
| Anayin quri'a ce domin sanin mai hakki a tsakanin masu jayayya kan wani abu da kowansu yake da'awar yanada hakki a ciki. | Ana amfani da shi ne, domin banbance alkhairi daga sharri, yana kamanceciniya da da'awar sanin gaibu ta hanyar bugun kasa. |
| Aikin musulmai ne. | Aikin mushrikai ne. |
| Contohnya, mengundi siapa yang berhak menjadi muadzin atau berada pada barisan yang pertama. | Membuat pilihan dengan melempar uang koin dan menghitungnya. |
| Mennyeleksi siapa yang paling berhak sementara perkaranya tidak bisa dibagi. | Menyeleksi yang tidak memiliki hak sementera perkaranya bisa dibagi. |

## *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Fadakarwa game da fadin Allah ta'ala: [ **shu'umcinsu yana wajen Allah** ] *(QS. Al-A'roof : 131).* Tare da Fadinsa: [ **shu'umcinku yana tare da ku** ] *(QS. Yasin : 19).* ( Babu cin karo tsakanin ayoyin biyu).

2. Kore harbuwar cuta daga wani zuwa wani. (Abinda aka kore shine tasirin harbuwar cutar da kanta ba wai kasantuwarta sababi ba ).

3. An kore campi. (An kore tasirinsa ba samuwarsa ba).

4. An kore Mujiya. ( Mujiya ko wani tsuntu mai kama da ita).

5. An kore Safar. ( Zamunna ba sada wani tasiri cikin qaddarar Allah, watar Safar kamar saurar watanni ne da ake kaddara alhairi da sharri a cikinsu, wadansu mutanen idan suka kamala wani abu cikin watan safar sai su rubuta tarihin hakan da fadin: An kare wannan abun cikin watan Alhairi; **Safar**, wanna nau'i ne….. na bidi'a da wata bidi'ar, … jahilci da wani jahilcin, watan safar ba wata ce ta alheri kadai ba, ba kuma wata ta sharri kadai ba ).

6. **Al Fa'al**, (kyakkyawar fata, Magana mai kyau ), ba ta daga campi.

7. Bayanin ma'anar: Al-fa'al. ( Duk abinda yake sanya nashadi wa mutum kan wani abu mai kyau).

8. Campin da ya auku cikin zuciyar mutum ba za ta cutar da shi ba, matukar yaki abun cikin zuciyarsa, Allah yana tafiyar da shi da tawakkali.

9. Addu'ar da wanda campi ya bijiro masa zaiyi:

اللَّهُمَّ لَا خَيرَ إِلَّا خَيْرُكَ، وَلَا طَيْرَ إِلَّا طَيْرُكَ، وَلَا إِلَهَ غَيْرُكَ».

"Ya Allah, babu alhairi se Alhairinka, kuma babu campi sai abinda ka hukunta, kuma babu abin bautawa bisa cancanta sai kai ".

10. Bayani karara cewa campi shirka ce. ( idan ya yi imani da cewa wannan abinda ya campa din yana da tasiri da kansa, to wannan babban shirka ce, amma idan yayi imani da cewa sababi ne kadai to wannan karamar shirka ce.

11. Tafsrin campi mummuna. ( Abinda ya saka ko ya hanaka yin wani abu ).

## [29] BABIN ABINDA YAZO KAN ILIMIN TAURARI

● Mawallafin baice: (yana daga shirka ba), domin yin dubi cikin taurari ya kasu kashi biyu; ilmutta'asir (wanda ake da'awar sanin gaibu da shi,), ilmuttasyir (wanda ake sanin jihohi da lokuta da shi ), bayani a kansu ya gabata.

**DALILI NA FARKO:**

قَـالَ الْبُخَـارِيُّ فِـي «صَـحِيحِهِ»: قَـالَ قَتَـادَةُ: (خَلَـقَ اللهُ هٰـذِه النُّجُـومَ لِـثَلَاثٍ: زِينَـةً لِلسَّـمَاءِ، وَرُجُومًـا لِلشَّيَاطِينِ، وَعَلَامَاتٍ يُهْتَدَى بِهَا، فَمَنْ تَأَوَّلَ فِيهَا غَيْرَ ذَلِكَ أَخْطَأَ، وَأَضَاعَ نَصِيبَهُ، وَتَكَلَّفَ مَا لَا عِلْـمَ لَـهُ بِهِ) انْتَهَى.

Imamul Bukhari ya fada cikin " Sahihin littafinsa " cewa: Qatadah ya ce: " Allah ya halicci wadannan taurarin saboda abubuwa uku; kawa ga sama, jifan shaidanu, kuma alamomi ne da ake shiriya da su, duk wanda ya raya wani abu sabanin wadannan abubuwa uku, -da da'awar sanin gaibi- to ya yi kuskure, kuma ya tozarta rayuwarsa, kuma yayi da'awar abinda bai san shi ba ".

**DALILI NA BIYU:**

وَكَرِهَ قَتَادَةُ تَعَلُّمَ مَنَازِلِ الْقَمَرِ، وَلَمْ يُرَخِّصِ ابْنُ عُيَيْنَةَ فِيهِ. ذَكَرَهُ حَرْبٌ عَنْهُمَا.

Qatadah ya karhanta koyan ilimin masaukan taurari, Ibnu Uyainah shima baiyi sausauci cikinsa ba, Harbu ne ya rawaito hakan daga garesu.

**DALILI NA UKU:**

وَرَخَّصَ فِي تَعلمِ ا لنمَنَازِلِ أَ حمَدُ وَإِسحَاقُ.

Imam Ahmad da Ishaq sunyi rangwami cikin koyan ilimin masaukan taurari.

● Dukkan wanda ya haramta koyon ilimin masukan taurari daga cikin magabata ana daukar maganarsa kan ilmutta'asir.

● Dukkan wanda ya halatta koyon ilimin masaukan tarari daga magabata, ana daukar maganarsa kan ilmuttasyir ne.

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنْ أَبِي مُوسَى قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «**ثَلَاثَةٌ لَا يَدْخُلُونَ الْـجَنَّةَ: مُدْمِنُ الْـخَمْرِ، وَقَاطِعُ الرَّحِمِ، وَمُصَدِّقٌ بِالسِّحْرِ**»، رَوَاهُ أَحْمَدُ وَابْنُ حِبَّانَ فِي «صَحِيحِهِ».

Daga Abu Musa -radiallahu'anhu- ya ce: Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Mutane uku ba za su shiga aljannah ba: mai yawan shan giya, da mai ya yanke zumunci, da mai gasgata sihiri ". ( Ahmad ne ya rawaito da Ibnu Hibban cikin sahihinsa).

● "Ba za su shiga aljannah ba ": wannan yana cikin hadisai ne masu tsoratarwa wadanda ake karanta su kamar yanda suka zo, ba a gwara su da nassoshin da suka zo na alkawari da aljannah, wannan kaiwa matuka ne wajen tsoratarwa.

● "Mai yawan shan giya ": Giya itace: duk abin da ke rufe hankali a gefen jin daɗi da farin ciki.

● "Mai yanke zumunci ": Zumuntar mutum sune danginsa da makusantansa, kuma sada zumuncin da ba a iyakance a shari'a ba, ana mayar da shine zuwa ga al'adan mutane matukar dai bai saba wa Shari'a ba.

● "Wanda ya gasgata mai sihiri " : Wannan shine shaidan babin, kuma a ciki akwai bayanin cewa ilimin taurari wani nau'i ne na sihiri.

**Tattaunawa kan manyan zunubai:**

● Ma'anar babban laifi : Shaikhul Islam Ibnu Taimiyya yace: ( babban zunubi shine: duk laifin da aka tanadar masa ukuba ta musamman) kamar la'ana, ko fushi, ko kora -daga rahama- ko a barranta daga mai laifin, ko ace yana cikin kafirai, ko mushrikai, ko ba ya cikin muminai, ko kuma a kamanta shi da mafi munin dabba.…

● Hukuncin wanda yake aikata babban laifi: Mumini ne da imaninsa, fasiki ne da sabonsa, yana karkashin ganin damar Allah, -Ma'ana idan ya mutu bai tuba ba-idan Allah Yaga dama sai Ya masa azaba, idan Yaga dama kuma Ya gafarta masa.

● Shin manyan laifuka sunada adadi na musamman? Za a iyakance abinda ake nufi da manyan laifuka da ta'arifin da ya gabata, amma ba su da adadi ayyananne.

● Shin manyan laifuka sunfi girma sama da karamar shirka? Zunubbai suna farawa ne da ƙananan laifuka, sannan manyan zunubai, sannan ƙaramar shirka, sannan babbar shirka. Saboda fadin Allah ta'ala:

إِنَّ اللّهَ لاَ يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَلِكَ لِمَن يَشَاءُ

***Lallai ne, Allah ba Ya gafartawa idan akayi tarayya da shi, kuma Yana gafarta abin da bai kai wannan ba ga wanda Yake so.*** *(QS. An-Niisa 48).*

Ibnu Mas'ud Radhi Allahu Anhu berkata:

لَأن أحلف بالله كاذبًا خيرٌ من أن أحلف بغيره صادقًا

" Wallahi, nayi rantsuwa da Allah a kan karya, ya fi mini alheri sama da nayi rantsuwa da wanin Allah a kan gaskiya ".

Domin rantsuwa da Allah akan karya babban laifi ne, amma rantsuwa da wanin Allah koda kan gaskiya ne, karamar shirka ce.

● Shin ana iya kankare manyan laifuka da aiyukan kwarai ko kuma babu makawa sai an tuba? Babu makawa sai an tuba saboda fadin Annabi -Sallallahu alaihi wasallam-:

النَّائِحَةُ إِذَا لَمْ تَتُبْ قَبْلَ مَوْتِهَا تُقَامُ يَوْمَ الْقِيَامَةِ وَعَلَيْهَا سِرْبَالٌ مِنْ قَطِرَانٍ وَدِرْعٌ مِنْ جَرَبٍ

**" Mai kukan mutuwa idan ba ta tuba ba kafin mutuwarta, za a tayar da ita ranar qiyama, a kanta akwai tufafi daga farar wuta, da sulke na kazuwa ".**

الصَّلَوَاتُ الْخَمْسُ وَالْجُمُعَةُ إِلَى الْجُمُعَةِ وَرَمَضَانُ إِلَى رَمَضَانَ مُكَفِّرَاتٌ مَا بَيْنَهُنَّ إِذَا اجْتَنَبَ الْكَبَائِرَ

"Salloli biyar, Juma'a zuwa wata juma'ar, Ramadan zuwa wata ramadana, suna kankare abinda ke tsakaninsu ( na laifi ) idan aka nisanci manyan laifuka."

● Shin tuba daga wani sashe na laifi tana inganta? "Na'am, tuba tana inganta daga wani sashe na laifi, kuma wajibi ne a kaurace wa dukkan sabon Allah.

● Shin ana iya son mai aikata babban laifi ko kinsa akeyi? Ana sonsa gwargwadon abinda yake da shi na imani, kuma ana kinsa saboda abinda yake kai na sabon Alla, ba a zama da shi lokacin da yake aikata laifin.

● Shin manyan laifuka suna fifiko? Na'am, wani laifin yafi wani girma, saboda fadin Annabi -Sallallahu alaihi wasallam-:

أَلَا أَدُلُّكُمْ عَلَى أَكْبَرِ الْكَبَائِرِ

Bana yi muku nuni ba kan manyan laifuka?.

● Wani suna zamu ba wa mai aikata babban laifi? Mumini ne da imaninsa, fasiki da sabonsa, Mumini ne mai tawayar imani, ba za mu fadi kamar yanda yan kungiyar murji'a suke fada ba cewa: Mumini mai cikakken imani, ko kamar yanda kawarijawa suke fadi cewa shi: kafiri ne.

**Mas'alolin babin:**

1. Hikimar halittar taurari. ( 'kawata sama, Jifar shaidanu, Alamomi ).

2. Mayar da martini ga duk wanda ya raya wani abu sabanin haka. (Ilmuta'sir).

3. An ambaci sabani game da hukuncin koyon masaukan tarari.

4. Tsoratarwa dangane da gasgata wani abu na sihiri, koda kuwa yasan sihiri cewa bata ce.

## [30] BABIN ( ABIN DA YA ZO NA ROKON TAURARI RUWAN SAMA)

1. **Babban shirka:** Idan ya roki taurari saukar da ruwan sama, ko ya kudirce cewa taurari su aikata abinda suka so kuma suna iya biyan bukatu da kansu.
2. **Karamar shirka:** Idan ya kudirce cewa su taurari sabubba ne kadai, Allah shine mahalicci kuma mai aikata abinda yaso.

**DALILI NA FARKO:**

Fadin Allah ta'alah:

وَتَجْعَلُونَ رِزْقَكُمْ أَنَّكُمْ تُكَذِّبُونَ (٨٢)

*"**Kuma kuna sanya arzikinku, lallai ku, kuna karyata shi?**" (QS. Al-Waqi'ah, 82).*

**DALILI NA BIYU:**

[٢] وَعَنْ أَبِي مَالِكٍ الأَشْعَرِيِّ ، أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**أَرْبَعٌ فِي أُمَّتِي مِنْ أَمْرِ الْجَاهِلِيَّةِ لَا يَتْرُكُونَهُنَّ: الْفَخْرُ بِالْأَحْسَابِ، وَالطَّعْنُ فِي الْأَنْسَابِ، وَالاِسْتِسْقَاءُ بِالنُّجُومِ، وَالنِّيَاحَةُ**»، وَقَالَ: «**النَّائِحَةُ إِذَا لَمْ تَتُبْ قَبْلَ مَوْتِهَا؛ تُقَامُ يَوْمَ الْقِيَامَةِ وَعَلَيْهَا سِرْبَالٌ مِنْ قَطِرَانٍ، وَدِرْعٌ مِنْ جَرَبٍ**» رَوَاهُ مُسْلِمٌ.

Daga Abu Malik Al-Ash'ari -Allah Ya kara yarda agare shi- Manzon Allah -Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: Dabi'u hudu a cikin al'ummata suna daga lamurran jahiliyyah, ba za su barsu ba, fariya da matsayi, suka ga nasaba, **neman shayar da ruwan sama wurin taurari**, da kukan mutuwa ", kuma ya ce: " **Mai kukan mutuwa idan ba ta tuba ba kafin mutuwarta, za a tayar da ita ranar qiyama, a kanta akwai tufafi daga farar wuta, da sulke na kazuwa** ".

". ( Muslim ne ya ruwaito ).

- وَتَجْعَلُونَ: Kuna karyata kasantuwarsa daga wajen Allah, kuna jingina samuwarsa zuwaga wanin Allah.
- "**Abubuwa Hudu**": Ba iyakancewa akayi da wadannan abubuwa hudun ba, saboda akwai wadansu abubuwan da suke tarayya da su, manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya fadi haka ne a babin iyakance ilimin da tara su ta hanyar rarrabe su da gidaya domin kusanto da fahimta da kuma tabbatar da hadda.
- "**Jahiliyyah**": Kafin aiko Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- abin nufi shine: munin wannan lokacin da nisantar da mutane daga yin koyi da ayyukan jahiliyyah, domin dukkanta jahilci ne, abu ne mai muni.

- "Ba zasu daina su ba": A ciki akwai labartawa da tsoratarwa, ba tabbatawa ba ce.
- " Fariya da matsayi " : Dagawa da girman kai saboda abinda yake da shi na matsayi da shugabanci, ana alfahari ne da tsoron Allah wanda yake hana girman kai da dagawa, sannan duk lokacin da niimar Allah ta karu ga bawa, ana fatan ya kara tawali'u wa Allah, sannan wa bayin Allah.
- " Suka cikin nasaba ": Ta hanyar aibanta tushen wani, kamar yace masa: kai dan masu jiman fata ".
- **وَالاسْتِسْقَاءُ بِالنُّجُومِ:** Wannan itace shardar babin, ma'anarsa: jingina ruwan sama zuwa ga taurari.
- An-Niyahah: Daga murya da kuka kan mutuwar wani, da gangan ta hanyar ihu.
- تُقَامُ ( za a tayar da ita daga kabarinta ). **سِرْبَالٌ:** tufafi mai cikan saka. قَطِرَانٍ : Narkakken azurfa.
- جَرَبٍ ( Kirci, Kazuwa): Cuta ce da take kasancewa a jikin fatan mutum, yana jin zafin duk abinda ya shafe shi, ma'ana: dukkan fatan jikinta zai zamo kazuwa kamar sulke, idan narkakken azurfa ya hadu da kazuwa sai bala'i ya karu, hikimar haka itace: yayin da mai kukan mutuwa ta kasa boye musibar da ta sameta da hakuri sai aka sanya mata wadannan tufafin, sakamako yana dacewa ne da jinsin aiki ne.

**An kira qiyama da wannan sunan saboda tsayuwar:**

| Mutane: | Shaidu: | Ma'auni/Mizani: |
| --- | --- | --- |
| يَوْمَ يَقُومُ النَّاسُ لِرَبِّ الْعَالَمِينَ<br>***A yinin da mutane ke tashi zuwa ga Ubangijin halitta*** *(QS. Al-Mudaffifin : 6)* | وَيَوْمَ يَقُومُ الْأَشْهَادُ<br>***Da ranar da shaidu ke tsayawa*** *(QS. Ghafir : 51).* | وَنَضَعُ الْمَوَازِينَ الْقِسْطَ لِيَوْمِ الْقِيَامَةِ<br>***Kuma muna aza ma'aunan adalci ga ranar kiyama*** *(QS. Al-Anbiya : 47)* |

**DALILI NA UKU:**

وَلَهُمَا عَنْ زَيْدِ بْنِ خَالِدٍ ؓ قَالَ: صَلَّى لَنَا رَسُولُ اللهِ صَلَاةَ الصُّبْحِ بِالْحُدَيْبِيَةِ، عَلَى إِثْرِ سَمَاءٍ كَانَتْ مِنَ اللَّيْلِ، فَلَمَّا انْصَرَفَ أَقْبَلَ عَلَى النَّاسِ، فَقَالَ: «**هَلْ تَدْرُونَ مَاذَا قَالَ رَبُّكُمْ؟**» قَالُوا:

اللهُ وَرَسُولُهُ أَعْلَمُ، قَالَ: «أَصْبَحَ مِنْ عِبَادِي مُؤْمِنٌ بِي وَكَافِرٌ، فَأَمَّا مَنْ قَالَ: مُطِرْنَا بِفَضْلِ اللهِ وَرَحْمَتِهِ؛ فَذَلِكَ مُؤْمِنٌ بِي كَافِرٌ بِالْكَوْكَبِ، وَأَمَّا مَنْ قَالَ: مُطِرْنَا بِنَوْءِ كَذَا وَكَذَا؛ فَذَلِكَ كَافِرٌ بِي مُؤْمِنٌ بِالْكَوْكَبِ».

Bukhari da Muslim sun rawaito hadisi, daga Zaidu dan Khalid -Allah Ya kara yarda a gare shi- ya ce: Manzon Allah ya yi mana Sallar Asubahi a hudaybiyyah, bayan ruwan sama da akayi cikin daren wannan ranar, yayin da ya idar da sallar sai ya juyo ya fiskanci mutane sai yace: " Shin kunsan abinda Ubangijinku ya ce: suka ce: Allah da Manzonsa su sukafi sani, ya ce: (( Wani sashe na bayina ya wayi gari yana mai imani da ni wani sashen kuma ya kafirce mini, duk wanda yace: anyi mana ruwan sama da Falalar Allah da Rahamarsa, to wannan ya yi imani da ni kuma ya kafirce wa tauraro, amma wanda kuma ya ce: **anyi mana ruwan sama da tauraro kaza kaza to wannan ya kafirce mini** kuma ya yi imani da tauraro )).

**DALILI NA HUDU:**

وَلَهُمَا مِنْ حَدِيثِ ابْنِ عَبَّاسٍ مَعْنَاهُ، وَفِيهِ: قَالَ بَعْضُهُمْ: لَقَدْ صَدَقَ نَوْءُ كَذَا وَكَذَا؛ فَأَنْزَلَ اللهُ هٰذِه الآيَاتِ: {فَلَا أُقْسِمُ بِمَوَاقِعِ النُّجُومِ} (٧٥) إِلَى قَوْلِهِ {أَنَّكُمْ تُكَذِّبُونَ} (٨٢)

Daga Bukhari da Muslim, cikin hadisin Ibnu Abbas ma'anarsa, yazo a cikinsa: wadansu daga cikinsu suka ce: Hakika tauraro kaza da kaza sunyi gaskiya; sai Allah Ya saukar da wannan ayoyin: [ **ina rantsuwa da mafadan taurari** ] zuwa fadinsa: [ **Lallai ne kuna karyata Shi** ]

● { فَلَا }: Kalmar ( لا - LA), kalmace ta janyo hankali, ma'ana: kasaurara, ina rantsuwa da mafadan taurari.

● Faidoji dangane da rantsuwar Ubangiji tareda cewa shi maigaskiya ne, babu bukatar yayi rantsuwar:

1. Wannan salo ne na Magana a harshen larabci, domin karfafa zance.
2. Mumini yana kara samun yakini, karfafa zance da rantsuwa abu ne mai kyau, domin tana kara wa bawa yakini.
3. Allah Yana rantsuwa kan manya manyan lamurran da suke nuni kan KamalarSa, da IkonSa, da GirmarSa, da iliminSa.
4. Nuni a kan halin abin da Allah Ya rantse dashi, Saboda Allah ba ya rantsuwa da komai seda abu muhimmi.
5. Muhimmancin abunda akayi rantsuwa a kansa, ya cancanta a bashi kula ta musamman.

● { إِنَّهُ لَقُرْآنٌ كَرِيمٌ }: كَرِيمٌ : Ma'anarsa: [1] Mai matukar kyawu, babu wani abunda yakai Alqur'ani kyau, [2] Mai yawan baiwa, Alqur'an yana ba wa ma'abotansa

Alhairai, na duniya da lahira, na zuci da gangan jiki.

● { فِي كِتَابٍ مَّكْنُونٍ }: Shine: Lauhul Mahfuz, ko takardun da ke hannun Mala'iku.

● { لَّا يَمَسُّهُ إِلَّا الْمُطَهَّرُونَ }: Mala'iku, a ciki akwai ishara kan cewa duk wanda ya tsarkake zuciyarsa, daga sabon Allah to zai fahimci Alqur'ani samada waninsa (wanda bai tsarkake nasa zuciyar ba ).

● { تَنزِيلٌ مِّن رَّبِّ الْعَالَمِينَ }: cikin wannan akwai nunin cewa:

1. Alqur'ani ya sauka ne ga dukkan halitta, gamammen sako ne.
2. Ya sauka ne daga wurin Ubangijin halittu, to idan ko har haka ne, to shine mai hukunci a tsakaninsu, kuma mai hukunci a kansu.
3. Saukar Alqur'ani yana daga kamalar Rububiyyar Allah, kuma mun fahimci cewa lallai Alqu'ani Rahama ce ga bayi .
4. Alqur'ani maganar Allah ce, abin saukarwa ne ba halitta ba.

● { أَفَبِهَٰذَا الْحَدِيثِ أَنتُم مُّدْهِنُونَ }: kuke jin tsoro, ai hakan bai kamaceku ba, ya kamata ga duk wanda Allah Ya bashi Alqur'ani ya tsage gaskiya dashi.

● وَتَجْعَلُونَ رِزْقَكُمْ أَنَّكُمْ تُكَذِّبُونَ: kuna sanya godiyarku karyatawa, wannan wauta ne babu shakka.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

**1.** Tafsirin ayar suratul waqi'ah: [ ***Kuma kuna sanya arzikinku, lallai ne ku kuna karyata Shi*** ]. *(QS. Al-Waqi'ah : 82).*

2. An ambaci abubuwa guda hudu daga lamurran jahiliyah: (fariya da matsayi, suka ga nasaba, neman shayar da ruwan sama wurin taurari, da kukan mutuwa).

3. An ambaci wasu daga cikinsu kafirci. ( neman shayarwa da taurari, suka ga nasaba, kukan mutuwa ).

4. Daga cikin kafirci akwai wanda ba ya fitar da mutum daga musulunci. ( shine: neman shayarwa da taurari, wani bangare nasa yana fitarwa daga musulunci, wani bangaren kuma karamin kafirci ne wanda baya fitarwa daga musulunci ).

5. Fadin Allah: أَصْبَحَ مِنْ عِبَادِي مُؤْمِنٌ بِي وَكَافِرٌ (wasu daga bayina sun wayi gari suna masu imani da ni, wadansu kuma sun kafirce ) sanadiyyar saukan niima. (wajibi ne akan mutum yayin da wata niima ta zo masa kar ya jingina ta zuwa ga wani sabubba kadai kuma ya mance da Allah ).

6. Fadakuwa dangane da imani a wannan wurin . (Jingina saukar ruwa da Rahamar Allah da Falalarsa.

7. Fadakuwa dangane da kafirci a wannan wajen. (jingina zuwan ruwa da ga taurari).

8. Fadakuwa dangane da fadinsa: " hakika tauraro kaza da kaza sunyi gaskiya ": ( Ma'ana da zartarwar wannan tauraron, kuma da alkawarinsa).

9. Malami yakan fitar wa dalibi da wata mas'ala ta hanyar jefa masa tambaya a kanta cikin fadinsa: ((shin ko kunsan me Ubangijinku yace ?)) (wannan yana wajabta karkato da zukatar daliban zuwa gare shi, kuma yana daga kakkyawar karantarwar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ).

10. Mummunan narko da aka tanada wa mai kukan mutuwa. ( Tufafi daga narkakken azura, da silke na kirci ).

## Jarabawa kashi na shida (Babuka 7)

| **Tambayar Farko:** menene banbanci tsakanin abubuwa masu zuwa? | | |
|---|---|---|
| No | Al-fa'al | At-Tadayyur |
| 1 | | |
| 2 | | |
| 3 | | |
| No | Quri'a | Kibau - caca |
| 1 | | |
| 2 | | |
| 3 | | |

**Tambaya ta biyu:** sanya alamar (☒) a wajen da ya dace da shi, ko ka cika gurbin da babu komaai:

1. Daga alamomi na sihiri akwai:
1………………………………………………………………………….2…………………
…………………………………………………………..
3………………………………………………………………………….4…………………
…………………………………………………………..
5……………………………………………………………………………………………
…………………………………………………………..
2. Umar ya Fassarar dagut da: shaidan, wannan tafsiri ne ta hanyar misali. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
3. Ma'anar: اشْتَرَاهُ………………………… مِنْ خَلاَقٍ……………………………….
4. Kalmar: اجْتَنِبُوا ( ku nisanci ), ya fi karfi a wajen hani sama da kalmar اتْرُكُوا (ku bar), domin nisantar wani abu ya kunshi: nisantar abun, da barinsa. ☐ haka ne ☐ Kuskure ne.
5. Hadisin " ku nisanci abubuwa bakwai masu halakarwa ", ambaton wannan adadin: ☐ yana nufin abubuwa masu halakarwa guda bakwai ne kadai ☐ baya nuni kan hakan.
6. Shin ambaton adadi acikin nassoshi yana kore akasinsa?
………………………………………………………………………………………………
7. Idan ba ya korewa meyasa ake ambata?......................................................................
8. Rayukan da ya haramta a kashe su ☐ guda uku ne ☐ hudu ne, **Abinda aka haramta:** ☐ cin riba ☐ ba shi kadai aka haramta ba.
9. Maraya shine wanda waninsa ya mutu ( ☐ Babansa ☐ Uwarsa ), namiji ko mace ( ☐ kafin balagarsa ☐ bayan balagarsa ).
10. Al Muhsanat tsarrun mata sune: ☐ mata wadanda ba bayi ba ☐ wadanda suka tsare kawunansu daga zina.

11. Wajibi ne a kan shugaba ya kashe mai sihiri. ☐ ba a karbar tubarsa ba ☐ za a nemi ya tuba idan bai tuba ba sai ya kashe shi.
12. Al-Jibtu shine ☐ Sihiri ☐ Duk abinda babu alheri cikinsa, sihiri ne ko waninsa.
13. Daghutu Shine ☐ Shaidan ☐ Duk abinda bawa ya ketare iyakansa, na wani abin bauta ko abin biyaya, ko wanda ake masa 'da a.
14. Al-Iyafah nau'i ne na camfi ☐ haka ne ☐ kuskure ne.
15. Duk wanda ya koyi wani abu na taurari to lallai ya koyi wani bangare na sihiri. ☐ haka ne ☐ Kuskure ne.
16. Halittun abubuwa na falaki (☐ Ba su da wata alaqa da abubuwan da suke faruwa a kan kasa ☐ suna da alaqa.
17. Ilimin taurari ya kasu:
1……………………………………………..hukuncinsa……………………………………….
2……………………………………………..hukuncinsa……………………………………….
18. Kawo annamimanci cikin ma'anar sihiri ☐ Kuskure ne daga masu kwafan littafin ☐ yayi tarayya da sihri wajen raba tsakanin mutane.
19. Hadisin: " Lallai daga cikin bayani akwai sihiri " ☐ Yabo ne ☐ Zargi ne ☐ bayani ne kan hakikaninsa sannan ana dubi zuwaga tasirinsa.
20. Al-Arraf shine ☐ Boka ☐ Suna ne gamamme.
21. Mawallafin ya kawo babin da yake Magana kan bokaye don yayi bayanin ☐ Su waye bokaye ☐ ma'anar zuwa wajensu ☐ hukuncin zuwa wajensu ☐ Duka ukun.
22. Koyon haruffan أبا جادٍ Ya kasu kashi:
☐ Biyu ☐ Kashi daya ne, saboda hadisin Ibnu Abbas -Radiyallahu Anhuma-.
23. Wanda ya gasgata boka, amma ya tabbatar da cewa babu wanda yasan gaibu se Allah, wannan kafiri ne ☐ Babban kafirci ☐ Karamin kafirci.
24. Wata mace ta fada ma wata macen cewa: zanyi sihiri wa mijinki ke babu komai akanki:
☐ Su biyun duka sunyi tarayya cikin laifin sihirin ☐ Mace ta biyun babu komai a kanta.
25. Mutum ne aka masa dibbu ma'anar wannan ☐ Sihiri ake nufi, kiran shi dibbu, fatan sauki ne gare shi ☐ Magani ne na rashin lafiya.
26. Nassoshin Alqur'ani da Sunnah da maganganun salaf sunyi nuni cewa ( ☐ Bai halatta ba warware sihiri da sihiri ☐ Ya halatta a warware sihiri ta hanyar sihiri.
27. Ana warware sihiri ne da ☐ Kaho ☐ Karanta ayatul kursiyyi ☐ Addu'a, kamar fadin : **رَبَّ النَّاسِ أَذْهِبِ الْبَأْسَ...** (Ya Ubangijin mutane ka tafir da rashin lafiya ) ☐ Duka gaba daya.
28. An-Nushrah ta kasu zuwa:
1…………………………………………………2………………………………………………….
29. Allah Ya lalata campin mutanen fir'auna da fadinsa: ☐ "Campinsu yana wajen Allah" ☐ " Campinku yana tare daku".
*30.* Campi yana kore tauhidi saboda mai yin campi:

☐ Ya yanke dogaronsa da Allah zuwa ga dogaro da wanin Allah ☐ Ya rataya da abinda ba shi da hakika ☐ Duka biyun.

31. Fadin Allah: قَالُوا طَائِرُكُمْ مَعَكُمْ "Suka ce: campinku yana tare da ku " wadanda sukayi wannan maganar sune: ☐ Mutanen Al'karya ☐ Manzanni.

32. Ma'anar: "Campinku yana wajen Allah ": ..…………………………………..………

Ma'anar: "Campinku yana tare da ku " ……………………………………………

33. Harbuwar cuta daga wani zuwa wani da izinin Allah yana takaita ne cikin:
☐ Cututtuka na fili. ☐ Cutar dabi'a wanda ba a ganinsu ☐ Duka

34. Hadisin " **Babu harbuwar cuta, babu campi, babu mujiya, babu safar** ", abinda aka kore ciki shine: ☐ Samuwarsa ☐ Tasirinsa.

35. Fadin Annabi : "Babu harbuwar cuta", shin yana cin karo da Fadinsa: " Ka gudu daga mai ciwon kuturta "?……………………

36. Yaya za a daidaita tsakanin hadisin: " Babu campi da fadinsa: " Babu campi sai cikin abubuwa uku " …………………………………………………………………….

37. Ma'anar " Babu mujiya: ……………………………………………………………….

[2] Ma'anar " babu Safar ……………………………………………………………….

38. Ma'anar " babu daya cikinmu face " : …………………………………………….

39. Ma'anar [1] " babu tauraro " : ……………………………………….....[2] Ma'anar babu Fatalwa: ………………………………………

40.Fadin " Safar mai alherai " ☐ halal ne ☐ kyakkyawar fata ce ☐ Babi ne na magance bidi'a da wata bidi'ar.

41. Abina ake nufi da: ( tsawatar da tsuntsu ) shine: cutar da shi ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

42. Larabawa sun tanadar wa kawunansu wadansu ilmi na karya kamar campi, da tsawatar da tsuntsu, da tofi, kuma sun kirkiri karerayi da suka yada tsakanin mutane, na kayar cewar fatalwa tana bayyana a garesu cikin tafiye tafiyensu, da fitar wani tsuntsu daga jinin macacce wanda ake kiransa: (**Al-hammah**) mujiya, sannan da da'awar cewa suna zantawa da aljanu da wadansunsu. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

43. Fadin: "خيرًا إن شاء الله (Alheri da yardar Allah) yayin jin haushin kare ko kukan jaki jaki: ☐ Ya haalatta ☐ Bai halatta ba.

44. Fadin: " Wannan tauraron daukaka ne " ☐ Ya halatta ☐ Bai halatta ba.

45. Al-Fa'alu shine: ☐ Kyakkyawar fata kadai, saboda hadisin da ya gabata.
☐ Dukkan abinda zai sanya nashadi wa mutum akan wani abu mai kyau, na wata magana ko aiki ko wani abin gani ko abin ji.

46. Idan mutum ya campa wani abu sannan ya zartar da abinda ya sa a gaba cikin fushi da bacin rai, to ana ji masa tsoron tasirin wannan abin da ya campa din. (☐ Ya halatta ☐ karamar shirka ☐ yayi laifi ). Amma idan ya yi campin sai ya fasa abin da yasa a gaba na aiki ☐ karamar shirka ne. ☐ Babban laifi ne.

47. ( Mummunar campi ): ishara ce, cewa akwai campi mai kyau. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
48. Kin wadansu lambobi ko wurare ko hanyoyi ☐ Halal ne. ☐ Campi ne.
49. Wani yayi niyyar aure se ya dauki wani fure…… wannan yana shiga babin ☐ Fa'al ☐ Campi.
50. Yana kokwanto cikin yin tafiya ko kar yayi, sai ya bude mushafi sai ya ga ayar rahama daga nan sai yayi tafiyar, wannan: ☐ kyakkyawar fata ce. ☐ Campi ne.
51. Ya kma hanyar tafiya sai ya kara samun nashadi yayin da yaji wani ya fada ma wani cewa: Allah ya datar da kai, wannan yana shiga babin: ☐ Fa'al ne ☐ Campi ne.
52. Ya ji wani abu na campi cikin zuciyarsa amma campin bai mayar da shi daga bukatarsa ba sannan baiyi fushi ba: ☐ Yayi laifi ☐ Babu wani abu a kansa.
53. Ya ji wani abu na campi cikin zuciyarsa amma dai ya ci gaba da da bukatarsa bai waiwaici campin ba ☐ Yayi shirka ☐ baiyi shirka ba.
54. Allah Ya sanya wasu rashin lafiyan sabubba ne na harbuwar cutar daga wani zuwa wani: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
55. Duk wanda ya ji tsoron wani abu wanda ba Allah ba, sai wannan abun ya rinjaye shi, ukuba ce a kansa, waannan itace ukubar mai aikata ampi: ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
56. Fadin: ( Allah ya isar mana daga sharrin dariya ), bayan yawaita dariyar ☐ Ya halatta ☐ bai halatta ba.
57. Ya yi istikhara sai yayi barci, sannan yaga wani abun da ya firgita shi sai ya bar wannan abinda yayi istikhara akayi ☐ Campi ne ☐ sakamakon istikharan ne.
58. Yayi kokwanto tsakanin abubuwa biyu: ☐ sai yayi addu'a ☐ yayi shawari ☐ ya yi istikhara ☐ yayi quri'a tsakanin abu byun ☐ Na farko da na biyun, idan har yayi niyyar daya daga cikin biyun sai yayi sallah sannan yayi istikhara ☐ Duka.
59. Ya yi istikhara sannan sai ya yi tafiya, sai rigarsa ta yage yana kan hanyarsa na tafiyar sai ya fasa tafiyar ☐ Camfi ne ☐ sakamako ne na istikharan.
60. Anayin istikharah ne bayan mutum yayi niyyar wani abu guda saboda fadin Annabi: "Cikin wannan lamarin " ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
61. Abin da mutum yayi istikharah akansa yana takaita ne kan abinda ake iya ganinsa kadai ko wanda shari'a ta tabbatar da shi: ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
62. wani yayi imani da cewa tauraro sababi ne na saukan ruwa, Allah shine wanda ya saukar da ruwan: ☐ Gaskiya ce. ☐ karamar shirka.
63. Anwaa (bintang-bintang) jahiliyah telah pergi dan telah datang udara yang rendah ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
64. Wani ya fada wa rana cewa: ( Ki dau shekaruna ki bani shekarun amarya ). ☐ Haka ne ☐ shirka ne.
65. Za mu iya daidaita sabanin malamai kan koyan masaukan taurari, kamar yanda muka daidaita mas'alar warware sihiri .
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

66. Alamomin da ake gane wurare da lokata da: ☐ A kasa suke ☐ A sassan sama ☐ Duka biyun.
67. Zumunta sune : ☐ Makusanta ☐ Makusantan mata da miji.
68. Sihiri yana iya tasiri cikin wadansu abubuwa ta yadda zai iya mayar da katako zinare:
☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
69. Hadisan tsorataswa ana karanta su ne kamar yanda suka zo, ba a gwara su da nassoshin alkawari da aljannah, wannan yafi kaiwa matuka wajen tsawatawa .
☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
70. Ana iya ambaton adadi cikin nassoshi a babin iyakance wasu ilmomi da hada su ta hanyar rabawa da sanya musu adadi' saboda hakan yana kusanto da fahimta da tabbatar da hadda ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
71 Dalilin jingina abubuwa marasa kyau zuwa ga jahiliyyah shine: ☐ Kyamatarwa ☐ domin jahiliyyah ta kunshi jahilci ne da wauta ☐ Duka.
72. Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yana bada labari kan wasu abubuwa da za su faru, ba ya nufin a yi riko da su, kamar fadinsa: " ba sa barin su.. " ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
73. Manyan zunubbai, ba a kankare su da aiyuka na kwarai kawai, har sai ya tuba daga laifin. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
74. Ma'anar Alqur'ani Karimun ne: ☐ Mai yawan baiwa ☐ Mai matukar kyawu ☐ Duka biyun.
75. Ma'anar: المُطَهَّرون (Wadanda ake tsarkake su )?
☐ Mala'iku ☐ Babu mai shafan Alqur'ani sai mai tsarki.

**Tambaya ta Uku:**
Sanya daga sahun (A) abinda ya dace da shi daga sahun (B):

| No | (A) | (B) |
|---|---|---|
| 1 | Al-Mu'aahad | Tsakninmu da shi akwai amana ta kasuwanci, ko saboda ya fahimci addinin Musulunci. |
| 2 | Az-Zimmi | Suna bugun kasa domin aikata sihiri da bokanci. |
| 3 | Al-Jibt | Tsakaninmu da shi akwai alkawari kar mu yaki juna. |
| 4 | Al-Musta'man | Wanda yake zaune a garin musulmai zama madawwami da sharadin zai ringa bayar da haraji. |
| 5 | A'd-'diyarah | Yanke wani abu da rarrabe shi. |
| 6 | Al-'Adhu | Cikakkar fasaha wacce take janyo hankula, ta canza tunani. |
| 7 | Al-Kabirah | Suna ce da ta game; boka, mai aiki da taurari, mai bugun kasa da sauransu. |
| 8 | Al-Bayan | Duk abinda aka tanada masa ukuba kebantacciya. |

| | | |
|---|---|---|
| 9 | A'd-'darqu | Tsawatar da tsuntsu domin campi ko Fa'al, yana cikin campi ta hanyar aiki. |
| 10 | Al-Arraf | Yin campi da sanannen abu wanda ake gani ko ake jin sa, ta fiskan lokaci ko wuri. |
| 11 | Al-“iyaafah | Duk abin da babu alheri cikinsa, sihiri ne, ko waninsa. |

**AIYUKAN ZUKATA (Babuka 9)**

## [31] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

وَمِنَ النَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ اللّهِ أَندَاداً يُحِبُّونَهُمْ كَحُبِّ اللّهِ

“ ***Kuma akwai daga mutane wanda yake rikan kishiyoyi baicin Allah, suna sonsu kamar son Allah*** ” *(QS. Al-Baqarah: 165).*

Kashe kashen Soyayya

| | | |
|---|---|---|
| **Soyayya tare da Allah** (Shirka ce babba). | **Soyayya domin Allah** (wajibi ne), yana daga mafi amincin igiyar imani domin Allah: | **Soyayya ta dabi'a** (Halal ne), kamar soyayyar mahaifi ga dansa. |

| | | | |
|---|---|---|---|
| Aikin da Allah Ta'ala Ya yarda da shi, shine duk abinda shari'a ta zo da shi, kamar tauhidi. | Masu aiki, kamar: Annabawa, da Manzanni, Mala'iku, da Sahabbai, da dukkan Musulmai. | Zamunnan da Allah Ta'ala Yake son su, kamar Lailatul qadr, da sulusin karshe na kowani dare. | Wuraren da Allah Yake sonsu kamar Makkah da Madinatul Munawwara. |

### DALILI NA BIYU:

**Da fadin Allah Ta'ala:**

قُلْ إِن كَانَ آبَاؤُكُمْ وَأَبْنَآؤُكُمْ إلى قوله: أَحَبَّ إِلَيْكُم مِّنَ اللّهِ وَرَسُولِهِ

***[ Ka ce, idan har ubanninku, da diyanku sun kasance ] har zuwa fadinsa: [ sunfi soyuwa a gare ku daga Allah da Manzonsa ].*** *(QS. At-Taubah : 24).*

### DALILI NA UKU:

عَنْ أَنَسٍ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**لَا يُؤْمِنُ أَحَدُكُمْ حَتَّى أَكُونَ أَحَبَّ إِلَيْهِ مِنْ وَلَدِهِ وَوَالِدِهِ وَالنَّاسِ أَجْمَعِينَ**» أَخْرَجَاهُ.

Daga Anas -Allah Ya kara yarda a gare shi- Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam Ya ce: " imanin daayanku ba zai cika ba har sai na fi soyuwa a gare shi, daga 'ya'yansa, da babansa, da dukkan mutane ". ( Bukhari da Muslim suka rawaito ).

● {*Ubanninku da 'ya'yanku }*: Soyayyar da akeyi ma wadannan ba soyayyar bauta ba ce, -soyayyar dabi'a ce- amma idan aka fifita ta akan soyayyar Allah to ta zamo sababin ukuba .

● " Dayanku ba zai yi imani ba " : Abinda aka kore shine: kamalar imanin wajibi, idan ya wofanta daga wannan soyayyar .

**Halayen kore wani abu:**

| **Kore samuwar abun:** | **Kore ingancinsa:** | **Kore kamalarsa:** |
|---|---|---|
| Wannan shine asali, misalinsa: " babu imani ga mai bautar gumaka ", Idan daukarsa kan wannan bai yiwu ba to sai mu dauke shi kan: | Misalinsa: " babu sallah sai da alola ". Idan daukarsa kan wannan bai yiwu ba to sai mu dauke shi kan: | Misali: " babu sallah a wajen abinci ". |

● Munasabar hadisin a fili ta ke, domin son Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- yana cikin son Allah, kuma son Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallah- tana kasancewa ne da abubuwa kamar haka:

1. Saboda shi dan aiken Allah ne, to idan har kafi son Allah sama da komai, to wajibi ne ka so dan aikensa sama da dukkan halittu.
2. Saboda jajircewarsa wajen bautar Allah da isar da sakonsa.
3. Saboda baiwar da Allah Ya masa na kyawawan 'dabi'u da kyawawan aiki.
4. Shine sababin shiriyarka da ilmantuwarka da fadakuwarka.
5. Domin hakurin sa kan cutarwar da aka masa, wajen isar da sakon Allah.
6. Saboda namijin kokarinsa wajen bayar da dukiya da ransa wajen daukaka Kalmar Allah maigirma da buwaya.

**Yaya soyayarsa zata zamo bayan rasuwarsa?**

Da koyan Sunnarsa, kuma da aiki da ita, sannan kira zuwa gareta, sannan da ba ta kariya, da gabatar da maganarsa a kan maganar kowa, da yin riko da shiriyarsa sallallahu alaihi wasallam.

Mutane kashi hudu ne dangane da soyayya tare da

- Yana son Allah, baya hada son Allah tare da son wani (wannan shine ikhlas ).
- Yana son kishiyoyi daidai da yana yake son Allah (wannan babban shirka ce ).
- Yana son kishiyoyi sama da yanda yake son Allah, (wannan babban shirka ce ).
- Yana son kishiyoyi kadai baya son Allah kwata kwata (shine: mafi girman shirka).

**DALILI NA HUDU:**

وَلَهُمَا عَنْهُ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «ثَلَاثٌ مَنْ كُنَّ فِيهِ وَجَدَ بِهِنَّ حَلَاوَةَ الإِيمَانِ: أَنْ يَكُونَ اللهُ وَرَسُولُهُ أَحَبَّ إِلَيْهِ مِمَّا سِوَاهُمَا، وَأَنْ يُحِبَّ الْـمَرْءَ لَا يُحِبُّهُ إِلَّا للهِ، وَأَنْ يَكْرَهَ أَنْ يَعُودَ فِي الْكُفْرِ بَعْدَ إِذْ أَنْقَذَهُ اللهُ مِنْهُ؛ كَمَا يَكْرَهُ أَنْ يُقْذَفَ فِي النَّارِ»، وَفِي رِوَايَةٍ: «لَا يَجِدُ أَحَدٌ حَلَاوَةَ الإِيمَانِ حَتَّى...» إِلَى آخِرِهِ

Daga Bukhari da Muslim, daga Anas yace: Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su taabbata a gare shi- ya ce: "Abubuwa uku, wanda duk ya siffantu da su to lallai ya samu 'dan'danon imani da su; Allah da Manzonsa sufi soyuwa a gare shi sama da wadansunsu, kuma ya so mutum ba don komai ba sai don Allah, kuma ya kyamaci komawa cikin kafirci bayan Allah Ya tsamar da shi daga cikinsa, kamar yanda yake kin a jefa shi cikin wuta ", a cikin wata riwayar kuma: "dayanku ba zai samu 'dan'danon imani ba har sai ya…" zuwa karshen hadisin.

**DALILI NA BIYAR:**

وَعَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ؓ قَالَ: «مَنْ أَحَبَّ فِي اللهِ، وَأَبْغَضَ فِي اللهِ، وَوَالَى فِي اللهِ، وَعَادَى فِي اللهِ؛ فَإِنَّمَا تُنَالُ وَلَايَةُ اللهِ بِذَلِكَ، وَلَنْ يَجِدَ عَبْدٌ طَعْمَ الإِيمَانِ - وَإِنْ كَثُرَتْ صَلَاتُهُ وَصَوْمُهُ - حَتَّى يَكُونَ كَذَلِكَ، وَقَدْ صَارَتْ عَامَّةُ مُؤَاخَاةِ النَّاسِ عَلَى أَمْرِ الدُّنْيَا، وَذَلِكَ لَا يُجْدِي عَلَى أَهْلِهِ شَيْئًا»، رَوَاهُ ابْنُ جَرِيرٍ.

Daga Ibnu Abbas ya ce: " duk wanda ya so domin Allah, kuma ya ki domin Allah, ya jibinta domin Allah, kuma ya yi adawa domin Allah, to iyaka , ana samun soyayyar Allah ne da hakan, bawa ba zai samu dandanon imani ba -komai yawan sallarsa da azuminsa- har sai ya zamo kamar hakan "

Saboda yawancin yan'uwantakar mutane suna gina su ne akan al'amuran duniya, wannan kuma ba zai taimake su da komai ”. ( Ibnu Jarir ne ya rawaito ).

**DALILI NA SHIDA:**

وَقَالَ ابْنُ عَبَّاسٍ فِي قَوْلِهِ تَعَالَى: ( وَتَقَطَّعَتْ بِهِمُ الأَسْبَابُ )، قَالَ:«الْمَوَدَّةُ».

Ibnu Abbas ya ce game da fadin Allah Ta'alah: " **kuma sabubba suka yanke da su** ” *(QS. Al baqarah, 166)*, ya ce: " **Soyayya** ".

**Soyayya ta fiskar Ibada:**

**Bauta ce a karan kanta:**

Soyayya ta bauta tana kasancewa ne domin Allah Maigirma da Buwaya, kuma tana wajabta Kankan da kai tare da girmamawa wanda suke hukunta bin umarnin Allah, da nisantar ababen da Ya yi hani a kansu.

**Ba bauta ce a karan kanta ba:**

1. Soyayya domin Allah: kamar son Annabawa da Manzanni ( Alaihimus salam ) …
2. Soyayya ta tausayi da jinkai: kamar son 'da, ko 'kananun yara…
3. Soyayya ta girmamawa: kamar son mahaifi da malami…
4. Soyayya ta dabi'a: kamar son abinci da abin sha…

● Mafi girmar wadannan nau'ukan shine kason farko ( Ibada a karan kanta ), amma sauran kason suna shiga bangaren halacci ne, sedai idan an alakanta su da bautar Allah, to daga nan kuma tana iya zamowa ibada.

● “**Dan 'danon imani** ” : Abinda bawa yake samu cikin ransa da zuciyarsa na nutsuwa da hutu da farin ciki.

● “Duk wanda ya so domin Allah ”: Ya na kin wanda Allah yake kinsa, kuma yana son wanda Allah yake sonsa.

● وَتَقَطَّعَتْ : Dukkan sabubban da mushrikai suka rataya da su, sun yanke da su, da soyayyarsu.

**( الولاية – Soyayya- Taimako - jibinta)**

**jibintar Allah ga bawa:**

**Gamammiya:**
Jibintar lamurran bawa ta fiskar juya dukkan lamurransa, wannan ya hada mumini da kafiri.

**Kebantacciya:**
Jibintar bawa ta fiskar kula ta musamman da datar da shi, da shiryar da shi, wannan ta kebanci muminai ne kadai.

**Soyayyar bawa ga Allah:**
Wannan wajibi ne a Shari'ance, Allah ya ce:
وَمَن يَتَوَلَّ اللّٰهَ وَرَسُولَهُ
*[ Kuma duk wanda ya jibinci Allah da Manzonsa ]*
*(QS. Al-Maidah : 56)*

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tafirin ayar suratul Baqarah: [ *Akwai daga mutane wanda yake rikon kishiyoyi baicin Allah ]. (QS. Al-Baqarah: 165).*

2. Bayanin ma'anar ayar suratut taubah: ( [ *Ka ce: idan har ubanninku da 'ya'yanku…] ) (QS. At-Taubah : 24).*

3. Wajibi ne ( a gabatar da) son Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- akn rai, da iyalai, da dukiya.

4. Kore imani daga wani ba ya nuni a kan ya fita daga musulunci. (se har idan zuciyar ta tubu gaba daya daga son manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam-, ta lallai babu kokwanton koruwar asalin imani daga wannan mutumi ).

5. Lallai imani wani 'dan'dano ne da mutum yake jinsa, akwai wanda ba ya jin sa.

6. Ayyukan zuci guda hudu, da sune ake samun wilayar Allah, babu wani wanda zai samu 'dan'danon imani se da su. (Ya yi so domin Allah, ya yi kiyayya domin Allah, ya jibinci wani domin Allah, sannan yayi adawa domin Allah ).

7. Fahimtar sahabi dangane da halin da mutane suke ciki na cewa galibin alakar mutane da junansu a kan duniya ce. (wannan a lokacinsa kenan, to ina kuma ga lokacinmu? ).

8. Tafsirin fadinsa: " kuma dukkan sabubba sun yanke musu " ( Misali: Soyayya da waninta na daga sabubba ).

9. Mun gane cewa daga cikin mushrikai akwai wadanda suke tsananin son Allah. (Muminai suna tsananin son Ubangijinsu sama da soyayyar mushrikai ga gumakansu).

10. Al'kawarin narko ga wanda yaso abubuwa takwas sama da addininsa. –Abubuwa takwas sune wadanda Allah Ya ambace su cikin fadinsa: [ kafada musu: idan har ubanninku da 'ya'yanku…] zuwa karshen ayar-.

11. Duk wanda ya riki wani kini, sai ya daidaita sonsa da son Allah, to hakika ya auka cikin babban shirka.

## [32] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

إِنَّمَا ذَٰلِكُمُ الشَّيْطَانُ يُخَوِّفُ أَوْلِيَاءهُ فَلاَ تَخَافُوهُمْ وَخَافُونِ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ

**[ IYAKA DAI, WANCAN SHAIDAN NE YAKE TSORATAR DA KU MASOYANSA, DON HAKA KAR KU JI TSORON SU, KU JI TSORO NA IDAN HAR KUN KASANCE MUMINAI ]** *(QS. Ali Imran, 175).*

Mawallafin Allah Ya jikansa ya kulla wannan babin ne a bayan babin soyayya domin bautar Allah ta kunshi abubuwa guda biyu: [1] **Soyayya**: da ita ake bin umarnin Allah. [2] **Tsoro:** da shi ake nisantar ababen da Allah yayi hani a kan su.

### Kashe Kashen Tsoro:

**Tsoro na (sirri) ibada da kaskantar da kai, da girmamawa, da tawali'u:** karkatar da wannan nau'in ga wanin Allah shirka ce babba, mutane dangane da wannan nau'in bangarori biyu ne da na tsakiya.

**Tsoro na 'dabi'a (Halal ne):** Allah Ya ce: [ **Sai ya fita daga gareta, yana mai jin tsoro yana sanda** ] *(QS. Al-Qasas : 21).* Amma idan ze kai ga barin wani wajibi ko aikata wani abinda aka haramta to ya zama haramun.

- " *Yana tsoratar da ku masoyansa* " : Shaidan yana tsorata da duk wanda yake so ya aikata wani wajibi.
- "*Kar ku ji tsoronsu* " : Ku aikata abinda aka umarce ku da shi, da abin da aka wajabta a kanku, na jihadi, kar ku ji tsoron wadannan, idan Allah yana tare da mutum, to babu wanda zai rinjaye shi.

### DALILI NA BIYU:

إِنَّمَا يَعْمُرُ مَسَاجِدَ اللّهِ مَنْ آمَنَ بِاللّهِ وَالْيَوْمِ الآخِرِ وَأَقَامَ الصَّلاَةَ وَآتَى الزَّكَاةَ وَلَمْ يَخْشَ إِلاَّ اللّهَ فَعَسَى أُوْلَـئِكَ أَن يَكُونُواْ مِنَ الْمُهْتَدِينَ

***[ Iyaka dai, mai raya masallatan Allah shi ne wadanda ya yi imani da Allah, da Ranar lahira, kuma ya tsayar da sallah, kuma ya bayar da zakkah***

***kuma bai ji tsoron kowa ba sai Allah, to tabbas wadannan za su kasance daga cikin shiryayyu ".*** *(QS. At Taubah : 18).*

● *"Wanda ya yi imani da Allah"* : Allah Yana hada yin imani da shi, da imani da ranan lahira cikin ayoyi masu yawa, domin imani da Allah yana hukunta fatan samun rahamar Allah, imani da ranar karshe kuma yana hukunta jin tsoro.

● " Kuma ya tsayar da sallah " : Ma'ana: ya tsayar da sallar tare da bata hakkinta yanda ya kamata bai rage komai ba, tsayar da sallah ta kasu kashi biyu:

[1] Tsayarwa ta wajibi: yana taitawa a kan abubuwan da suka zamo wajibai, tun daga sharuddan sallar da rukunnanta da dukkan wajibai.

[2] Tsayarwa ta mustahabbi: yana karawa a kan wajibai, yana aikata wajibai sannan ya kara da mustahabbai.

● وَلَمْ يَخْشَ إلا الله [***kuma bai ji tsoron kowa ba face Allah*** ]: ***Al-Khasyah***: tsoron da aka gina shi akan sanin girman wanda ake jin tsoro, da sanin cikan ikonsa.

● Banbanci tsakanin: ***Al-khauf*** da ***Al-khasyah***.

1. **Al-Khasyah**: tana kasantuwa ne tare da sanin girman wanda ake tsoro, da sanin halinsa, sabanin ***Al-khauf*** domin ana iya jin tsoron wanda ba a sanshi ba.

2. **Al-Khasyah** tana kasantuwa ne saboda girmar wanda ake tsoro, sabanin ***Al-khauf,*** yana aukuwa ne saboda r aunin mai tsoron.

● فَعَسَى (Tabbas) : Ibnu Abbas ya ce kalmar: عَسَى idan tazo daga Allah ma'anarta: wajabi, kuma tana zuwa ne da sigar fata, domin kar mutum ya rudu a cewa ya riga ya samu wannan alherin .

**Kashe kashen rayanta Masallatai/ kishiyanta: lalata su:**

( ***Wanene mafi zalunci sama da wanda ya hana masallatan Allah, domin kada a ambaci sunanSa a cikinsu, kuma ya yi sa'ayi wajen rushe su?*** *(QS. Al-Baqarah :*

**Rayantawa na fili da ake gani:** da gina masallatan, da yin shimfidi cikin su, da tsaftace su, da sabunta su.

Kishiyar wannan itace: lalata su, kamar rusa su da bata su.

**Rayantawa ta ma'ana:** da yin salloli da zikiri da karatun alqur'ani cikinsu.

Kishiyar wannan itace: lalata su ta ma'ana: kamar mayar da masallatai wajen shirka da bidi'oi.

**DALILI NA UKU:**

وَمِنَ النَّاسِ مَن يَقُولُ آمَنَّا بِاللَّهِ فَإِذَا أُوذِيَ فِي اللَّهِ جَعَلَ فِتْنَةَ النَّاسِ كَعَذَابِ اللَّهِ

***Kuma daga cikin mutane akwai mai cewa: munyi imani da Allah, sa'annan idan aka cutar da shi wajen aikin Allah sai ya sanya fitinar mutane kamar azabar Allah** … (QS. Al-Angkabuut : 10).*

- Sanannen abu ne mutum yana gujewa ma azabar Allah, sai ya dace da umarninsa, amma wannan ya sanya fitinar mutane tamkar azabar Allah, yana gujewa ma cutarwarsu, ta hanyar mika wuya wa son zuciyarsu, yana me sanya wannan fitinar kamar azabar Allah; sai ya zamo yana jin tsoron su kamar yanda yake tsoron Allah, domin ya sanya cutarwarsu kamar azabar Allah, wanda ya guje mata ta hanyar mika wuya ma umurnin wadannan mutanen.
- Cikin ayar akwai tsoratarwa dangane da mutum ya fadi abu sabanin abinda ke cikin zuciyarsa.

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنْ أَبِي سَعِيدٍ ۞ مَرْفُوعًا: «إِنَّ مِنْ ضَعْفِ الْيَقِينِ أَنْ تُرْضِيَ النَّاسَ بِسَخَطِ اللهِ، وَأَنْ تَحْمَدَهُمْ عَلَى رِزْقِ اللهِ، وَأَنْ تَذُمَّهُمْ عَلَى مَا لَمْ يُؤْتِكَ اللهُ، إِنَّ رِزْقَ اللهِ لَا يَجُرُّهُ حِرْصُ حَرِيصٍ، وَلَا يَرُدُّهُ كَرَاهِيَةُ كَارِهٍ».

Daga Abu Sa'id Allah Ya kara yarda a gare shi, daga Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-: " Raunin yakini ne ka nemi yardan mutane da fusata Allah, ko ka gode musu bisa arzikin Allah, ko ka zarge su akan abinda Allah bai baka shi ba, kwadayin wani mai kwadayi baya janyo arzikin Allah, kuma kin wani mai ki baya mayar da shi ".

- "Ka nemi yardan mutane" : Ka ji tsoron su sama da yanda kake tsoron Allah, maigirma da buwaya, da kin yi musu nasiha.
- " Ko ka gode musu " Ka sanya dukkan godiya gare su, ka manta da wanda wanda ya yi sanadin samun wannan ni'imar, shine Allah maigirma da buwaya.
- " Ko kazarze su " : Saboda idan Allah Ya kaddara zaka samu wani abu to babu makawa se an samu sabubba, abinda ya zamo wajibi kan bawa shine yarda da Allah.

**DALILI NA BIYAR:**

وَعَنْ عَائِشَةَ ڤ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «مَنِ الْتَمَسَ رِضَا اللهِ بِسَخَطِ النَّاسِ؛ رضي الله عنه وَأَرْضَى

عَنْهُ النَّاسَ وَمَنِ الْتَمَسَ رِضَا النَّاسِ بِسَخَطِ اللهِ؛ سَخِطَ اللهُ عَلَيْهِ وَأَسْخَطَ عَلَيْهِ النَّاسَ»، رَوَاهُ ابْنُ حِبَّانَ فِي «صَحِيحِهِ».

Daga Aisha Allah Ya kara yarda a gare ta ; Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Duk wanda ya nemi yardar Allah da fishin mutane to Allah Zai Yarda da shi, kuma Zai sa mutane su yarda da shi, kuma duk wanda ya nemi yardar mutane da fishin Allah, Allah Zaiyi fushi da shi, kuma Zai sa mutane su yi fushi da shi ", ( Ibnu Hibban ne ya rawaice shi cikin Sahihinsa).

● "Wanda ya nemi yardan wasu ": yana mai tsoron su, saboda su yarda da shi, kuma ya gabatar tsoronsu akan tsoron Allah ( maigirma da buwaya ) .

**Fa'idodin Hadisin:**

1. Wajibi ne a nemi yardar Allah ( Maigirma da buwaya ) koda mutane za su yi fushi, domin Allah shi kadai shine mai amfanarwa da cutarwa.
2. Ba ya halarta mutum ya jawo wa kansa fushin Allah domin yardar neman yardar mutane ko wanene su.
3. Tabbatar da siffar fushi da yarda wa Allah a hakika ba tare da kamanta shi da halittu ba.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tafsirin fadin Allah ta'ala : ( *Iyaka dai wancan shaidan ne, yake tsoratar da ku masoyansa ) (QS. Ali-Imran: 175).*

2. Tafsirin ayar suratut Taubah. *( Iyaka wanda yske raya masallatai ... (QS. At-Taubah : 18)..*

3. Fassarar ayar surat Al-Ankabut: ( *Daga cikin mutane akwai wanda yake cewa: " munyi imani da Allah "...) (QS. Al-Angkaabut : 10).*

4. Yakini yana iya raunana kuma yana yin karfi.

5. Alamar raunin yakini, daga ciki akwai wadannan abubuwa ukun: (ka nemi yardan mutane da fusata Allah, ko ka gode musu bisa arzikin Allah, ko kazarge su akan abinda Allah bai baka shi ba).

6. Tsoro na hakika, ga Allah yana cikin farillai.

7. An ambaci sakamakon wanda ya ji tsoron Allah shi kadai. (Allah Zai yarda da shi kuma Zai yardar da shi ga mutane ).

8. An ambaci ukubar wanda ya saba ma hakan (Allah Zai yi fushi da shi kuma Zai sa mutane suyi fushi da shi ).

## [33] BABIN FADIN ALLAH TA'ALAH:

وَعَلَى اللّهِ فَتَوَكَّلُواْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ

***( Kuma ga Allah kadai sai ku dogara idan kun kasance muminai ).*** *(QS. Al-Maidah: 23).*

● Bayan Malam ya yi Magana a kan mas'alar soyayya, da tsoro sai ya bayyana cewa samun biyan bukata da gushewar abin ki ba za su samu ba sai an samu dogaro da Allah, kuma tace bauta ba zai yiwu ba sai da tawakkali ga Allah, domin shine mafi kwololuwar matsayi, wajibi ne ga kowani musulmi ya lizimci tawakkali cikin dukkn lamurransa.

● *" Ga Allah kadai sai ku dogara "* : Gabatar da abinda aiki ya fadi a kansa yana hukunta iyakancewa, wannan kuma dalili ne kan cewa: ana iya rasa cikan imani yayin da aka rasa tawakkali, amma idan aka samu cikakken dogaro ga wanin Allah to wannan kuma ya zamo babban shirka.

**Tawakali**: Shine gaskiyar dogaro da Allah tareda amintuwa da shi, dayin riko da sabubba wadanda suka halatta, babu makawa sai an samu dogaro ga Allah na gaskiya kuma na hakika, da aikata dukkan sabubban da aka bada daman ayi riko da su, a shar'ance, Tawakkali ya kasu zuwa:

- Mayar da dukkan lamurra wajen Allah, da yin kudirin cewa: janyo amfani da tunkude cuta duka suna hanun Allah ne, to wannan nau'in karkatar da shi ga wanin Allah shirka ce babba.
- Dogaro da wani rayayye kan wani lamari tareda nuna bukatuwa zuwa gare shi, to wannan shirka ce karama, kamar wanda ya dogara da wani tareda bukatuwarsa gare shi wajen arzikinsa.
- ***Al-Wakaalah*** (Wakiltarwa), ba ya halatta a ce: na dogaa ga wane, ko kuma: na dogara ga Allah sannan wane, a'a, abinda ya halatta ya ce shine: na wakilta wane, na dora wane, Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam ya wakilta wasu cikin kebantattun lamurransa da gamammu.

### DALILI NA BIYU:

إِنَّمَا الْمُؤْمِنُونَ الَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ اللّهُ وَجِلَتْ قُلُوبُهُمْ وَإِذَا تُلِيَتْ عَلَيْهِمْ آيَاتُهُ زَادَتْهُمْ إِيمَاناً وَعَلَى رَبِّهِمْ يَتَوَكَّلُونَ
(٢) الَّذِينَ يُقِيمُونَ الصَّلاَةَ وَمِمَّا رَزَقْنَاهُمْ يُنفِقُونَ (٣)

*[ Abin sani kawai, muminai sune wadanda idan aka ambanci Allah sai zukatanu su firgita, kuma idan an karanta ayoyinSa a kansu sai su kara musu imani kuma ga Ubangijinsu kadai suke dogara (2 ), wadanda suke tsayar da sallah kuma suna ciyarwa daga abinda muka azurta su da shi ]. (QS. Al-Anfaal 2-3).*

**DALILI NA UKU:**

يَا أَيُّهَا النَّبِيُّ حَسْبُكَ اللّهُ وَمَنِ اتَّبَعَكَ مِنَ الْمُؤْمِنِينَ (٦٤)

*[ Ya kai wannan Annabi, Allah ne Ma'ishinka kai da wanda ya biye maka daga muminai ]. (QS. Al-Anfaal: 64).*

- Mutum yana iya zamowa mumini koda ba shi da wadannan siffofin, sedai tare da shi akwai asalin imani ( Musulunci ).

- *[ Ya kai wannan Annabi, Allah ne Ma'ishinka kai da wanda ya biye maka daga muminai ]:* Allah kadai shine wanda ya isar maka kuma ya isar ma wadanda suka yi maka bi ka daga muminai, don haka sai ku dogara ga Allah gaba daya da kai da wadanda suka bi ka.

Allah Ya ambaci siffofin imani cikakke, guda biyar cikin wadannan ayoyi:

| | |
|---|---|
| *[ Idan aka ambanci Allah sai zukatansu su firgita].* | Sun ji tsoro ne saboda abinda ke cikinsu na girmama Allah, alamar imani itace: yayin da aka tunasar da mutum Allah sai ya ji tsoro. |
| *[ Kuma idan aka karanta ayoyinSa a kansu sai su kar mu su imani ]* | Suna masu gasgata su da yin da a, wanda dalili ne cewa mutum yakan amfana da karatun waninsa sama da yanda amfanuwa da karatunsa. |
| *[Kuma ga Ubangijinsu kadai suke dogara ].* | Suna dogaro da Allah shi kadai ba da waninsa ba, kuma tare da haka suna riko da sabubba, wannan itace shaidar. |
| *[ Wadanda suke tsayar da sallah ].* | Sunayin Sallar cikakkiya, sallah suna ce wacce ta kunshi farillai da nafilfili. |

*[ Kuma suna ciyarwa daga abinda muka azurta su da shi ].*

Wannan yabo ya kunshi wanda ya ciyar da sashen dukiyarsa ko duka, wanda ya ciyar da dukkan dukiyar zai shiga cancanci yabon ne idan an samu tawakkali da dogaro da Allah.

**DALILI NA HUDU:**

وَمَن يَتَوَكَّلْ عَلَى اللَّهِ فَهُوَ حَسْبُهُ

*[ **Kuma wanda ya dogara ga Allah, to Allah ne ma'ishinsa** ]. (QS. A'ddalaq: 3).*

● Allah ne Mai isar ma sa kan bukatunsa kuma zai sauwake masa lamurransa, kuma idan ya hadu da wata cutarwa to lallai Allah zai isar masa, Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam shine shugaban masu tawakkali tare da haka wasu lokutan ana cutar da shi amma cutarwar bata yi masa wani tasiri.

● Ayar tana fa'idantar da cewar duk wanda ya dogara ga wanin Allah zai tabe kuma Allah zai fita daga sha'aninsa.

**DALILI NA SHIDA:**

**عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ﭬ قَالَ: «حَسْبُنَا اللهُ وَنِعْمَ الْوَكِيلُ؛ قَالَهَا إِبْرَاهِيمُ □ حِينَ أُلْقِيَ فِي النَّارِ، وَقَالَهَا مُحَمَّدٌ □ حِينَ قَالُوا{ إِنَّ النَّاسَ قَدْ جَمَعُواْ لَكُمْ فَاخْشَوْهُمْ فَزَادَهُمْ إِيمَاناً وَقَالُواْ حَسْبُنَا اللّهُ وَنِعْمَ الْوَكِيلُ} رَوَاهُ الْبُخَارِيُّ.**

Daga Ibnu Abbas -Allah Ya kara yarda a gae shi- ya ce: (**HASBUNALLAHU WA NI'IMAL WAKIL**; Annabi Ibrahim -Alaihis Salam - ya fade ta yayin da aka jefa shi a cikin wuta, kuma Annabi Muhammadu -Sallallahu alaihi wasallam- shi ma ya fade ta yayinda suka ce: { **Lallai mutane sun tara -gangami- saboda ku, don haka ku ji tsoronsu, Sai -wannan magana- ta kara mu su imani, kuma suka ce: Allah ne Mai isar mana kuma madalla da -Allah- abin dogaro**}) *(QS. Ali Imran, 173).* ( Bukhari ne ya rawaito ).

● Wannan kissar nassi ne na Alkur'ani, yayinda Abu Sufyan ya ke komawa daga Uhudu, sai ya yi niyyar sake komawa domin yakar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- da Sahabbansa domin gamawa da su kamar yanda ya raya, sai ya hadu da wasu tawaga na mutane: sai ya ce musu: ina zaku je? suka ce: Madina, sai ya ce musu: ku isar wa Muhammadu da Sahabbansa cewa gamunan muna dawowa zuwa gare su domin mu gama dasu, da tawagar suka iso Madinah sai suka isar da sakon Abu Sufyan, sai Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- da wadanda suke tare da shi suka ce: (**HASBUNALLAHU WA NI'IMAL WAKIL**; *(QS. Ali Imran, 173).*

Sai suka fita cikin mahaya saba'in, har sai da suka isa: **HAMRA'UL ASAD**, sai Abu Sufyan ya tsorata ya juya zuwa Makkah, wannan yana daga isarwar Allah ga Manzonsa -Sallallahu Alaihi wasallam- da Muminai; saboda sun dogara ga Allah Ta'alah.

**Fadakarwa:**

● Kasancewar Ibn Abbas -Allah Ya kara yarda a gare su-, yana daga cikin masu ruwaya daga banu isra'ila, wannan Magana ce shahararriya a wajen Malaman Musdalah, sedai wannan Magana ce wacce akwai shakku cikinta; saboda ibn Abbas -Allah Ya kara yarda a gare su- yana daga ciin masu hana riwaya daga banu isra'ail.

● Shin zamu gasgata labaran da suka zo daga banu isra'ila, ko kuwa?

1. Zamu gasgata su idan ya tabbata cikin Shari'armu cewa gaskiya ce.
2. Zamu karyata su idan ya tabbata cikin Shari'armu cewa karya ce.
3. Zamu tsaya tsaka tsaki idan Shari'armu ba ta gaskata ba kuma ba ta karyata ba.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tawakkali ga Allah yana cikin Farillai. ( Saboda Allah Ya rataya imani a kansa ).

2. Tawakkali ga Allah yana cikin sharuddan imani.

3. Tafsirin ayar suratul Anfal. [ *Abin sani kawai muminai sune wadanda idan aka ambanci Allah sai zukatansu su firgita* ]. *(QS. Al-Anfal 2-3).*

4. Tafsirin ayar karshenta: *[ Ya kai Annabi, Allah ne mai isar maka ] ". (QS. Al-Anfal: 64).*

5. Tafsirin ayar suratut 'dalaq. [ *wanda ya dogara da Allah to, Allah ne mai isar ma sa ]. (QS. A'd'dalaq : 3 ).*

6. Girmar sha'anin Kalmar: حسبنا الله ونعم الوكيل kuma itace Kalmar da Annabi Ibrahim -Alaihis sallam- da Annabi Muhammadu -Sallallahu alaihi wasallam- suka fada cikin tsanani.

( Cikin wannan babin akwai Karin imani, kuma wajibi ne mutum ya dogara ga Allah -Maigirma da buwaya- yayin da ya shiga tsanani, tare da riko da sabubba, kuma yin biyayya ga Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- sababi ne na samun isuwar Allah ga bawa ).

## [34] BABIN FADIN ALLAH TA'ALAH:

أَفَأَمِنُواْ مَكْرَ اللّهِ فَلاَ يَأْمَنُ مَكْرَ اللّهِ إِلاَّ الْقَوْمُ الْخَاسِرُونَ

*[ Shin fa Sun amince wa makarun Allah? To babu mai amincewa wa makarun Allah face mutane masu hasara ]. (QS. Al-A'araf: 99).*

● Wannan babin ya kunshi:

● Amintuwa daga Makrun Allah, debe tsammani daga Rahamar Allah, dukkan biyun kuskure ne, malam yayi nufin fadaakar da musulmi cewa bautar Allah ta hada abubuwa biyu; tsoron azabar Allah, da fatan Rahamarsa, Abinda zamu fa'idantu da su cikin wannan ayar sune:

1. Muyi taka tsan tsan da ni'imar da Allah ya ba mu, don kar ta zamo talala ce.
2. Haramun ne amintuwa daga makrun Allah.

**DALILI NA BIYU:**

قَالَ وَمَن يَقْنَطُ مِن رَّحْمَةِ رَبِّهِ إِلاَّ الضَّآلُّونَ (٥٦)

**[ Ya ce, kuma wanene yake yanke tsammani daga Rahamar Ubangijinsa face batattu** ] (QS. Al-Hijr : 56)

● Ma'ana: babu mai yanke tsammani daga rahamar Allah sai marashin shiriya, mai dimuwa, wanda bai san abubuwan da suka wajaba ga Allah ba, ?????, yanke tsammani daga rahamar Allah ba ya halatta, domin munana zato ne ga Allah, kuma lallai yin hakan:

1. Su'ka ce cikin ikon Allah; domin duk wanda yasan cewa Allah Mai iko ne kan komai, to hakika yasan cewa babu wani abinda zai gagare shi.
2. Su'ka ce cikin rahamar Allah; saboda duk wanda yasan cewa Allah mai jinkai ne, to ba zai nisanta Allah yayi masa Rahamar ba.

**DALILI NA UKU:**

وَعَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ؓ: أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ سُئِلَ عَنِ الْكَبَائِرِ؛ فَقَالَ: «الشِّرْكُ بِاللهِ، وَالْيَأْسُ مِنْ رَوْحِ اللهِ، وَالأَمْنُ مِنْ مَكْرِ اللهِ».

Daga Ibn Abbas -Allah Ya kara yarda a gare shi- antambayi Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- dangane da manya manyan zunubbai sai ya ce: " Shirka da Allah, da yanke tsammani daga Rahamar Allah, da amintuwa daga makrun Allah ".

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ قَالَ: «أَكْبَرُ الْكَبَائِرِ: الإِشْرَاكُ بِاللهِ، وَالأَمْنُ مِنْ مَكْرِ اللهِ، وَالْقُنُوطُ مِنْ رَحْمَةِ اللهِ، وَالْيَأْسُ مِنْ رَوْحِ اللهِ»، رَوَاهُ عَبْدُ الرَّزَّاقِ.

"Daga Ibn Mas'ud Yace: Mafi girman zunubbai: Yin shirka da Allah, da amintuwa daga makarun Allah, da yanke tsammani daga Rahama Allah, " (Abdur Razzaq ne ya rawaice shi ).

● " Shirka da Allah ": Abinda ake nufi shine babbar shirka, da karama, karamar shirka tafi girma sama da babban laifi.

● " Amintuwa daga makarun Allah ": Ya na sabon Allah -Maigrma da buwaya- tareda kasancewar yana cikin ni'imomin Allah, to wannan talala ake masa.

● " Yanke kauna daga Rahamar Allah ": Ya nisanta samun Rahamar Allah, ko nisanta samun wata bukatarsa.

● " Debe tsammani daga taimakon Allah ": Ya nisanta gushewar wani abu mai muni da ya faru da shi.

**Atakaice:**

Lallai ne duk wanda ya kama hanyar Allah to zai gamu da cikas guda biyu sune; amintuwa daga makarun Allah, da kuma yanke kauna daga RahamarSa. Yayinda wata musiba ta same shi, ko ya rasa wani abin da yake so, to idan har bai samu taimako daga Allah ba, sai ya fitar da rai daga samun nasara daga Allah, ba zai yi ƙoƙarin aikata sabubban samun nasara ba, sannan dangane da amintuwa daga makarun Allah, muna iya samun bawa wanda ko yaushe yake cikin sabon Allah bayan Allah Ya asa ni'imomi masu yawa, kuma sai ya ya ringa gwada cewa shi maigaskiya ne sai ya ci gaba da kasancewa akan batarsa, to babu shakka wannan talala akeyi masa.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Fassarar ayar surat Al-Aaraf. [ ***Shin fa sun amince wa makarun Allah ne?].*** *(QS. Al-Aaraf: 99).*

2. Tafsirin ayar surat Al-Hijr. ***[ Ya ce, kuma wanene yake yanke tsammani daga Rahamar Ubangijinsa face batattu ] .*** *(QS. Al-Hijr : 56).*

3. Bayanin tsananin narko kan wanda ya aminta daga makrun Allah. ( Cewa yana daga manyan zunubbai ).

4. Tsananin tsoratarwa dangane da debe tsammanin Rahamar Allah.

# [35] BABIN ( YANA DAGA IMANI DA ALLAH: HAKURI KAN KADDARAR ALLAH )

## Hakuri ya kasu kashi uku

- Hakuri kan da'a wa Allah har a aikata: wannan yana cikin hakuri kan abubuwan da Allah Yayi Umarni a kansu, kamar: Sallah da Azumi.
- Hakuri daga sabon Allah har a nisanceta: kamar nisantar shirka da sauran abubuwan da Allah Ya haramta su.
- Hakuri a kan kaddarar Allah masu radadi: Kamar mutuwar wani makusanci.

Ya gabatar da hakuri akan da'a domin ya kunshi lizimtawa da aikatawa, sannan yin hakuri daga sabon Allah saboda akwai kamewa ciki, amma hakuri a kan kaddarar Allah, saboda bawa baya da zabi dangane da sababinsa, sanna dangane da wanda hakurin yake alaka da shi, yin hakuri daga barin sabon Allah yafi wahala a kan mutum samada hakurinsa a kan da'a wa Allah.

## Kashe kashen mutane yayin musibah:

- **Mai yin fushi (babban laifi ne, yana iya kaiwa ga kafirci ).** Da zuciyarsa (ya ke fushi), kuma da harshensa ( yake addu'a, da kururuwa da halaka ), da gabbabnsa kuma (yake marin kumatunsa kuma yake yaga tufafinsa, ko tsige gashin jikinsa ).
- **Mai hakuri ( Wajibi ne bisa ijma'ai ).** Hakuri da zuci, da harshe sannan da gabbai, yana da nauyi kam a kansa to amma kuma baya so, to amma yana juriya kuma yayi hakuri.
- **Mai yarda (Mustahabbi ):** Saboda cikan yardarsa da Ubangijinsa, a wajensa da ni'ima da kishiyanta duka daya ne, yana kallonsu duka a matsayin kaddara ce daa Ubangijinsa.
- **Mai godiya (Wannan itace mafi daukakan martabobin ).** Ya yarda da cewa hakurin zai kankare masa zunubbansa sannan zai kara masa kyawawan sakamako da karuwar imani, domin akwai wadansu masifun da suka fi wannan din girma.

**DALILI NA FARKO:**

Da fadin Allah Ta'alah:

وَمَن يُؤْمِن بِاللَّهِ يَهْدِ قَلْبَهُ

***Kuma wanda yayi imani da Allah, Allah zai shiyar da zuciyarsa.*** *(QS. Attaghabun 11).*

قَالَ عَلْقَمَةُ: ( هُوَ الرَّجُلُ تُصِيبُهُ الْمُصِيبَةُ فَيَعْلَمُ أَنَّهَا مِنْ عِنْدِ اللهِ؛ فَيَرْضَى وَيُسَلِّمُ ).

Al-Qamatu ya ce: ( shine wanda musiba take samunsa sai yasan cewar daga waje Allah ne, sai ya yarda sannan ya mika wuya.

● ***" Zai shiryar da zuciyarsa "***: Zai azurta shi da natsuwa, idan zuciyarsa ta shiriyu, sai gabbansa su shiriya.

**DALILI NA BIYU:**

وَفِي «صَحِيحِ مُسْلِمٍ» عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ڤ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**اثْنَتَانِ فِي النَّاسِ هُمَا بِهِمْ كُفْرٌ: الطَّعْنُ فِي النَّسَبِ، وَالنِّيَاحَةُ عَلَى الْمَيِّتِ**».

Ya zo cikin (( Sahihu Muslim )) daga Abu Hurairah -Allah Ya kara yarda a gare shi- Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: " Dabi'u guda biyu cikin mutane butulci ne: **su'ka ga nasabar wani, kukan mutuwa** "

● " Su'ka cikin nasabar wani " : Ma'ana: aibantawa ko kore shi, wannan aiki ne daga aiyukan kafirci.

● *"Kukan mutuwa*: Wannan shine dalilin tarjamar, kukan mutuwa daga fushi yake.

**DALILI NA UKU:**

وَلَهُمَا عَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ مَرْفُوعًا: «**لَيْسَ مِنَّا مَنْ ضَرَبَ الْخُدُودَ، وَشَقَّ الْجُيُوبَ، وَدَعَا بِدَعْوَى الْجَاهِلِيَّةِ**».

Daga Bukhari da Muslim, daga Ibnu Mas'ud daga Manzon Allah -Sallallahu Alaihi wasallam-: " Baya daga cikinmu, wanda ya bigi kumatunsa, ko ya ya'ga aljihunsa, ko yayi ya fadi wani abu daga abubuwan jahiliyyah "

**DALILI NA HUDU:**

وَعَنْ أَنَسٍ ڤ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**إِذَا أَرَادَ اللهُ بِعَبْدِهِ الْخَيْرَ؛ عَجَّلَ لَهُ الْعُقُوبَةَ فِي الدُّنْيَا**، وَإِذَا

أَرَادَ بِعَبْدِهِ الشَّرَّ؛ أَمْسَكَ عَنْهُ بِذَنْبِهِ حَتَّى يُوَافِيَ بِهِ يَوْمَ الْقِيَامَةِ».

Daga Anas -Allah Ya kara yarda a gare shi- Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yace: "idan Allah Ya nufi bawansa da alkhairi sai ya gaggauta jarabtarsa a duniya, idan kuma Ya nufi bawansa da sharri sai Ya kyale shi kan zunubbansa har Ya hadu da shi ranar lahira ".

● "Da'awar Jahiliyyah " : Duk wata da'awar da ta samo asali daga jahiliyyah, kamar: rusa gidaje, ko farfasa kwanuka, da lalata abinci, da makamantansu na abubuwan da mutane suke aikatawa yayin masifa.

● "Idan Allah Ya nufi bawansa " : Allah Ba ya son sharri a karan kansa, saboda fadin Annabi Sallallahu alaihi wasallam:

" وَالشَّرُّ لَيْسَ إِلَيْكَ ".

"sharri ba ya gare Ka"

Allah Ya kan nufi sharri saboda wata hikima, a lokacin kuma sai ya zamo alheri lura da ya kunsa na hikima.

● Fa'idar hadisin shine: lallashin wanda aka jarrabe shi kar yayi fushi, qila wannan jarabawar alheri ne a gare shi, azabar duniya tafi sauki daga azabar lahira, sai ya gode ma Allah da bai jinkirta ukubarsa zuwa ranar lahira ba.

**DALILI NA BIYAR:**

وَقَالَ النَّبِيُّ ﷺ: «إِنَّ عِظَمَ الْـجَزَاءِ مَعَ عِظَمِ الْبَلَاءِ، وَإِنَّ اللهَ تَعَالَى إِذَا أَحَبَّ قَوْمًا ابْتَلَاهُمْ؛ فَمَنْ رَضِيَ فَلَهُ الرِّضَا، وَمَنْ سَخِطَ فَلَهُ السُّخْطُ»، حَسَّنَهُ التِّرْمِذِيُّ.

Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: "Lallai ne babban sakamako gwargwadon girmar jarabawa ce, kuma idan Allah Ta'ala Yana son bawa sai ya jarabce shi, wanda ya yarda, sai ya samu yadar Allah, wanda kuma yayi fushi sai ya hadu da fushin Allah ". ( Imam Tirmizi yace hadisi ne mai kyau).

**Fa'idodi daga hadisin:**

1. Duk lokacin da bala'i ya tsananta ga bawa, idan yayi hakuri to zai samu babban sakamako.
2. Idan Allah Yana son wadansu mutane sai Ya jarabce su ta fiskan kaddara da shari'a.
3. Tabbatar da siffofin; Soyaya, da Fushi, da Yarda ga Allah maigirma da buwaya, tare da guje wa ma kamanta wadannan sifffin ko bayanin yanayinsu.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1 Tafsirin ayar surat At-Taghabun. ( ***Kuma wanda yayi imani da Allah, Allah zai shiyar da zuciyarsa*** ). *(QS. Attaghabun 11).*

2. Wannan bangare ne na imani da Allah. ( hakuri kan kaddarar Allah).

3. Suka cikin nasabar wani ( da aibanta ta, ko kore ta, wannan karamin kafirci ).

4. Narko mai tsanani dangane da wanda ya mari kumatunsa, kuma ya keta aljihunsa, sannan ya yi da'awa da irin da'awar jahiliyyah (domin Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya barranta daga gareshi ).

5. Alamar Allah Yana nufin bawansa da alheri (Yakan gaggauta masa ukuba a duniya ).

6. Alamar Allah Yana nufin bawansa da da sharri (Yana jinkirta masa ukuba zuwa ranar lahira ).

7. Alamar soyayyar Allah ga bawansa ( Allah Yakan jarabce shi ).

8. Haramun ne bawa yayi fushi (yayin da aka jarabce shi ).

9. Sakamakon yarda da jarabawa ( shine Yardar Allah -Maigirma da buwaya- ga bawa ).

## [36] BABIN ABINDA YAZO NA HUKUNCIN RIYA

**DALILI NA FARKO:**

**Da fadin Allah Ta'ala:**

قُلْ إِنَّمَا أَنَا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُوحَى إِلَيَّ أَنَّمَا إِلَهُكُمْ إِلَهٌ وَاحِدٌ فَمَن كَانَ يَرْجُو لِقَاء رَبِّهِ فَلْيَعْمَلْ عَمَلاً صَالِحاً وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِ أَحَداً (١١٠)

***[ Ka ce, iyaka ni mutum ne kamar ku, anayin wahayi zuwa gare ni cewa lallai ne, abin bautawanku, abin bauta ne Guda, saboda haka, wanda ya kasance yana fatan haduwa da Ubangijinsa to ya aikata aiki na kwarai, kuma kar ya hada kowa ga bautar Ubangijinsa ]*** *(QS. Al-Kahfi- 110 ).*

**DALILI NA BIYU:**

وَعَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ مَرْفُوعًا: «**قَالَ اللهُ تَعَالَى: أَنَا أَغْنَى الشُّرَكَاءِ عَنِ الشِّرْكِ، مَنْ عَمِلَ عَمَلًا أَشْرَكَ مَعِي فِيهِ غَيْرِي تَرَكْتُهُ وَشِرْكَهُ**»، رَوَاهُ مُسْلِمٌ.

Daga Abu Hurairah -Allah Ya kara yarda agare shi- daga Annabi -Sallallahu alaihi wa sallam- Allah Ta'ala Yace: " Nine mafi wadatan masu tarayya daga barin tarayyar, wanda ya aikata wani aiki ya tara ni da wanina a cikinsa, na kyale shi da shirkarsa ".

**DALILI NA UKU:**

وَعَنْ أَبِي سَعِيدٍ مَرْفُوعًا: «**أَلَا أُخْبِرُكُمْ بِمَا هُوَ أَخْوَفُ عَلَيْكُمْ عِنْدِي مِنَ الْـمَسِيحِ الدَّجَّالِ؟**» قَالُوا: بَلَى يَا رَسُولَ اللهِ، قَالَ: «**الشِّرْكُ الْـخَفِيُّ؛ يَقُومُ الرَّجُلُ فَيُصَلِّي فَيُزَيِّنُ صَلَاتَهُ؛ لِـمَا يَرَى مِنْ نَظَرِ رَجُلٍ**»، رَوَاهُ أَحْمَدُ.

Daga Abu Sa'id, daga Annabi -Sallallahu alaihi wa sallam- ya ce: " Ba na labarta muku abinda nafi jin tsoronsa akanku sama da Masihu Addajjal ba? " sai suka ce: hakane ya Ma'aikin Allah, sai yace: " Boyayyar shirka, mutum ya na tashi yayi sallah, sai ya kawata sallarsa; saboda wani daga mutane yana ganinsa ". ( Ahmad ne ya rawaito ).

● "*Kace ni mutum ne*" : Allah Ya umarci Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya labarta wa mutane cewar shi mutum ne, sannan ya karfafi kasantuwarsa na mutum da fadinsa: "*Kamar ku*", *sedai ana yin wahayi a gare shi, don haka wajibi ne ayi masa biyayya, kuma haramun ne a bautata ma sa.*

● *“ Saduwa da Ubangijinsa ”* : Saduwa irin ta yardar Allah da ni'imtawarsa ta, kebanci muminai ne kadai, sannan ta kunshi ganin Allah a lahira.

● “ Aiki na kwarai ” : wanda aka yi ikhlasi cikinsa, kuma bisa Sunnar Annabi.

● **“ Nine mafi wadatuwa ”** yanada ma'anoni biyu:

1. Bacin aikin da riya ta shige shi, da bayanin haramcin riya.
2. Bayanin wadatuwar Allah ta'ala, da girmar hakkinsa, kuma ba ya halatta ga wani ya tara wani da Allah cikin komai .

● **“ Almasihu Addajjal ” :** An shafe idanunsa na bangaren dama, mutum ne daga banu Adam, makaryaci.

**Me ya sa Annabi -Sallallahu alihi wa sallam- yake tsananin tsoron riya sama da Masihud dajjal?**

1. Domin fitinar Dajjal a fili take, fitinar riya kuma a boye take, kuma kubuta daga riya abu ne mai matukar wahala.
2. Domin fitinar Dajjal an kayyade ta ne da karshen zaamani, sabanin fitinar riya, fitina ce cikin kowani lokaci.

**Shirka nau'i biyu ne:**

1. ***Khafiyyun*** ( Boyayya ) Wanda yake cikin zuci kamar riya, ana kiransa: shikar boye.
2. **Jaliyyun** ( Bayyananna ), Waanda ya ke aukuwa da Magana, kamar rantsuwa da wanin Allah, ko aiki kamar dukawa ma wanin Allah.

**Riya:** Ya aikata wani aiki domin mutane su ganshi, ko su ji shi, wannan yana daga 'dabi'ar munafukai.

**Daga asalin ibada:** Yana bata ibadar.

**Ya auku cikin ibadar:** Yanada kashe kashe:

**Ya tunkude shi:** Ya aikata wajibi, ibadar ta inganta.

**Yaki tunkude shi:** Yana da kashe kashe:

**Idan farkon ibadar yanada alaka da karshenta:** Kamar sallah, dukkan ibadar ta baci.

**Idan farkon ibadar ba ya da alaka da karshenta:** kamar zakkah, kason da riyar ta shiga ciki ya baci.

**Bayan ya kare ibadar:** Ba zai yi wani tasisi cikin ibadar ba, sedai idan akwai ketare iyaka kamar gorantawa, da cutarwa bayan ya yi sadaka.

**Menene maganin Riya?**

1. Girmama Allah da koyon tauhidi da aiki da shi, domin idan mutum yasan girman Allah to ba zai damu da kowa ba.
2. Kar mutum ya bar yin aiki don tsoron riya, domin idan shaidan bai jefa ka cikin riya ba, to babu shakka zai iya jefa ka cikin tsoron wanin Allah.
3. Addu'a.
4. Mutum ya yi kokarin boye aiyukansa don tsoron aukawa cikin riya.
5. Ziyarar makabartu, ziyara ta shari'a, domin tana tunasar da mutum lahira, riya kuma tana rataya mutum da duniya.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Tafsirin ayar surat Al-Kahfi. { ***Ka ce, ni mutum ne kamar ku, anayi mini wahayi…***}. *(QS. Al-Kahfi- 110 ).*

2. Wannan lamari ne maigirma, mayar da aiki na kwwarai, idan wani abu na riya ya auka cikinsa.

3. Kuma an ambaci abin da yasa aka ki karbar aikin, shine kamalar wadatuwar Ubangiji.

4. Kuma saboda Allah Ta'ala shine mafi alkhairin masu tarayya.

5. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wa sallam- yana jin tsoron riya ga sahabbansa. (Wadanda suka biyo bayansu su su ka fi cancanta aji musu tsoron riya ).

6. Ya fassara haka da cewa: mutum zai yi sallah kuma ya kawata ta, saboda wani yana ganinsa ( Hakanan yin wata Magana ba domin Allah ba ).

## [37] BABIN YANA DAGA SHIRKA MUTUM YA NUFI DUNIYA DA AIYUKANSA

● Wannan babin yana Magana ne dangane da wanda shi ba ya nufin ayabe shi cikin ibadarsa, kuma ba ya nufin riya, a'a, yana bautar Allah da ikhlasi amma yana bukatar wani abun duniya, kamar dukiya da matsayi, da lafiya cikin jikinsa, da makamantansu, yana bukatar wani amfani a duniya da aikinsa, ya gafala daga sakamakon lahira.

● Ba a hana mutum roki ya Allah Ya azurta shi da dukiya a cikin sallarsa ba, sedai, kar yayi sallar saboda wannan, domin wannan abu ne wanda yake kaskantacce, shine mutum ya nufi duniya da aikin lahira.

● **Fadakarwa**: Wadansu mutanen yayin da suke yin Magana game da fa'idodin ibada, sai su mayar da su zuwa fa'idodi na duniya, abinda ya zama wajibi a kanmu shine kar mu sanya fa'idodin duniya su zamo asali.

● Wannan Babin yafi babin riya hadari, domin riya zata iya bijirowa a cikin sallah 'daya, amma yin aikin domin duniya hadarinsa cikin dukkan ibada ne.

### Mutane sun kasu gida biyar dangane da wannan babin:

| | |
|---|---|
| **Yana nufin duniya da aikin duniya:** | Wannan ya halatta, kamar wanda yake kasuwanci don ya sayi gida. |
| **Yana nufin lahira da aikin duniya:** | Wannan mustabbi ne, Kaman wanda yake noma don yayi sadaka. |
| **Yana nufin lahira da aikin lahira:** | Madalla da wannan mutumin, wannan itace mafi daukakar martabobin. |
| **Yana nufin duniya da lahira da aikin lahira:** | Wannan ya halatta, da sharadin ya rinjayar da lahira: [ *Ya Ubangijinmu Ka ba mu mai kyau a cikin duniya, da mai kyau a cikin lahira* ]. (QS. Al-Baqarah : 201). |
| **Yana nufin duniya da aikin lahira:** | Wannan karamar shirka ce, kamar wanda yake limanci wa mutane domin kudi. |

● Ta yaya zai fahimci cewa duniya yake nufi da aikinsa ko lahira? " idan aka ba shi sai ya yarda, idan kuma aka hana shi sai yayi fushi ".

● **Fadakarwa**: wadansu mutanen suna tsarkake ibada ga Allah a ranakun jarabawa, da zaran sakamako ya fita se su bar ibadar.

**DALILI NA FARKO:**

مَن كَانَ يُرِيدُ الْحَيَاةَ الدُّنْيَا وَزِينَتَهَا نُوَفِّ إِلَيْهِمْ أَعْمَالَهُمْ فِيهَا وَهُمْ فِيهَا لاَ يُبْخَسُونَ (١٥) أُوْلَـئِكَ الَّذِينَ لَيْسَ لَهُمْ فِي الآخِرَةِ إِلاَّ النَّارُ وَحَبِطَ مَا صَنَعُواْ فِيهَا وَبَاطِلٌ مَّا كَانُواْ يَعْمَلُونَ (١٦)

*Da fadin Allah Ta'ala: [* ***Wanda ya kasance ya yi nufin rayuwar duniya da kawarta, zamu cika musu ayyukansu zuwa gare su a cikinta, kuma su a cikinta ba za zalunce su ba, (15) wadannan ne wadanda ba su da komai a cikin lahira face wuta, kuma abin da suka aikata a cikinta -Duniya- ya baci, kuma abinda suka kasance suna aikatawa batacce ne*** *]? (QS. Huud : 15-16).*

● Wannan Ayar an kebe ta da ayar suratu isra'i:

مَّن كَانَ يُرِيدُ الْعَاجِلَةَ عَجَّلْنَا لَهُ فِيهَا مَا نَشَاء لِمَن نُّرِيدُ ثُمَّ جَعَلْنَا لَهُ جَهَنَّمَ يَصْلاهَا مَذْمُوماً مَّدْحُوراً

***[ Wanda ya kasance ya na nufin mai gaggawa sai mu gaggauta masa a cikinta abin da Mu ke so, ga wanda Mu ke nufi, sa'annan kuma mu sanya masa jahannama ya konu da ita, yana abin zargi, kuma abin tunkudewa ].*** *(QS. Al-Isra'i : 18).*

Lamarin yana komawa ne karkashin ganin damar Allah, kuma ga wanda Ya so.

**DALILI NA BIYU:**

فِي الصَّحِيحِ عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ : «تَعِسَ عَبْدُ الدِّينَارِ، تَعِسَ عَبْدُ الدِّرْهَمِ، تَعِسَ عَبْدُ الْخَمِيصَةِ، تَعِسَ عَبْدُ الْخَمِيلَةِ، إِنْ أُعْطِيَ رَضِيَ، وَإِنْ لَمْ يُعْطَ سَخِطَ، تَعِسَ وَانْتَكَسَ، وَإِذَا شِيكَ فَلَا انْتَقَشَ، طُوبَى لِعَبْدٍ آخِذٍ بِعِنَانِ فَرَسِهِ فِي سَبِيلِ اللهِ، أَشْعَثَ رَأْسُهُ، مُغْبَرَّةٍ قَدَمَاهُ، إِنْ كَانَ فِي الْحِرَاسَةِ كَانَ فِي الْحِرَاسَةِ، وَإِنْ كَانَ فِي السَّاقَةِ كَانَ فِي السَّاقَةِ، إِنِ اسْتَأْذَنَ لَمْ يُؤْذَنْ لَهُ، وَإِنْ شَفَعَ لَمْ يُشَفَّعْ».

Hadisi ya tabbata cikin Sahihul Bukhari daga Abu Hurairah Allah Ya kara yarda a gare shi- ya ce: Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallm- ya ce: " Bawan dinare ya yi asaara, bawan dirhami ya yi asara, bawan tufafi yayi asara, bawan mashinfidi ya yi asara, idan aka ba shi sai ya yarda, idan kuma aka hana shi, sai yayi fushi, yayi asara, kuma ya tabe, idan kaya ta soke shi kar ya fitar masa, madalla da bawan da ya riki linzamin dokinsa cikin hanyar Allah, wanda gashin kansa ya yamutse, kafafunsa sunyi kura, idan aka ajiye shi a wajen gadi to baya barin wajen, idan kuma yana bayan rundunar yaki, baya barin wajen, kuma idan ya nemi izini, ba a yi masa izinin, kuma idan ya nemi ceto ba a ba shi ceto ".

● تَعِسَ : Ya tabe kuma yayi asara.

● "**Bawan dinare**" : Dinare: nau'in kudi ne daga zinare, Manzon Allah ya kira shi bawan dinare ne saboda ya rataya zuciyarsa da shi irin yanda bawa yake rataya zuciyarsa da Allah, ya zamo shine baban damuwarsa, kuma ya kaddamar da shi a kan 'da'a ga Ubangijinsa Maigirma da buwaya.

● Dirhami: Kudi ni daga azirfa.

● Alkhamisah: (Taguwa mai kyawu ) - Alkhamilah: ( Shimfidi ), Babban damuwarsa, adon jikinsa da shimfidarsa.

● " Idan aka ba shi zai yarda, idan aka hana shi sai yayi fushi " : Ba ya yarda se a kan kudi -idan ya samu-, kuma ba ya fushi se idan ya rasa kudin, don haka Manzon Allah -Sallallahu alaihi wa sallam- ya kiraye shi bawan kudi.

● وَانْتَكَسَ : Lamarin ya juya a kansa da aksin burinsa, babu sauki gare shi.

● وَإِذَا شِيكَ فَلَا انْتَقَشَ : Idan wata kaya ta soke shi, kar ya iya fitar da ida.

● Wadannan jumloli uku kodai labari ne, ko kuma addu'a akan bawan dinaren.

● طُوبَى : Mafi kyawun yanayi ya kasance ga wannan mutumin, wadansu malamai suka ce: طُوبَى : wata bishiya ce a cikin Aljannah, ma'anar farkon yafi gamewa.

● " Cikin hanyar Allah ": Yana yaki don daukaka Kalmar Allah ta zamo madaukakiya, ba domin kabilanci yare ko kasa ba.

● Gashin kansa ya yamutse : Saboda jihadi don daukaka musulunci, bai damu da yanayin da yake ciki ko yanayin jikinsaba matukar wannan abu ya faru ne saboda biyayya ga Allah, kafafunsa sunyi kura saboda tafiya jihadi, duk wata alamar da faru a jikin mutum sakamakon bautar Allah matukar ba an samar da ita da niyya ba ne to za a ba shi lada a kanta; kamar yanda Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya fadi cewa: " Warin bakin mai azumi …".

● السَّاقَةِ: Yana tsayuwa a bayan rundunan mayaka, wadannan jumloli biyu na hadisin suna iya daukar ma'anoni guda biyu:

1. Shi bai damu da yanda a ka ajiye shi ba, baya neman wani matsayi samada kasantuwarsa a bayan rundunar mayaka.
2. Idan a ka sanya shi gadi, ya na ba shi hakkinsa yanda ya kamata, hakanan idan ya kasance a bayan dakarun yaki.

● " Idan ya nemi izini… " : ba shi da wani masayi ko girma a wurin mutane, amma kuma yanada matsayi a wajen Allah Maigirma da buwaya.

● Abin nufi; daga cikin mutane akwai mai bautawa duniya, yana fushi saboda ita, hadisin ya karksa mutane zuwa kaso biyu:

1. Wanda ba shi da damuwa sai duniya, kodai ya samu kudi, ko kuma ya kasance cikin yanayi mai kyau, an bautar da zuciyarsa kan duniya se ta shagaltar da shi daga barin ambaton Allah da bautarsa, sai lamarin ya juwa masa, ba ya iya kubuta daga wata cutuwa komai kashinta.
2. Lahira ce babban damuwarsa; yana matukar kokarinsa don nemanta da juriya a kan wahala da tsananin da ya ke cikin hakan.

yana jihadi domin daukaka Kalmar Allah, tare da haka yana sauke dukkan nauyin da ke kansa na wajibai, alheri ne damuwarsa da taimakom jama'a.

**MAS'ALOLIN BABIN:**

1. Mutum yakan nufi duniya da aikin lahira.
2. Tafsirin ayar suratu Hud. ( *Wanda yakasance ya na son rayuwar duniya da kawanta ......)(QS. Huud : 15).*
3. An kira mutum musulmi da bawan dinare, da dirhami, da taguwa.
4. An fassra hakan da kasancewarsa idan aka ba shi sai ya yarda, idan kuma aka hana shi sai yayi fushi.
5. Fadin Manzon Allah: " Ya tabe kuma ya yi asara ". ( ze iya daukar ma'anar labartawa kuma ze iya daukar ma'anar addu'a ce a kansa ).
6. Idan wata kaya ta soke shi ba zai iya fitarwa ba ". ( zai iya daukar ma'anar labari, kuma zai iya daukar ma'anar addu'a ce a kansa ).
7. An yabi Mujaahidi wanda aka siffanta shi da wadancan siffofin ( shine wanda ya cancanci yabo, ba ma'abota dirhami da dinarai ba, da ma'abota shinmfidu da da katifu.).

## [38] BABIN: HUKUNCIN WANDA YA YI DA'A GA MALAMAI DA SHUWAGABANNI CIKIN HARAMTA ABIN DA ALLAH YA HALATTA, KO HALATTA ABIN DA ALLAH YA HARAMTA, TO HAKIKA YA RIKE SU IYAYEN GIJI BAICIN ALLAH

**Nau'ukan bin malamai da shuwagabanni cikin sabon Allah:**

**Babban kafirci:**

Ya yi musu biyayya yana mai yarda da maganarsu, kuma yana gabatar da ita, yana mai fushi da hukuncin Allah.

Duk wanda ya ki Abinda Allah Ya saukar ya kafirta, haka nan idan ya kudurce cewa hukuncinsu daidai yake da hukuncin Allah, ko ya fi hukuncin Allah.

**Karamin kafircine maigirman hadari, wanda yake dab aukawa cikin babban kafirci:**

Ya bi su cikin hukuncinsu yana mai yarda da hukuncin Allah, kuma yana sane da cewa shine yafi zamowa daidai, kuma shi yafi dacewa da mutane da ko ina, sedai ya zabi hukuncinsu saboda son zuciya, kamar yaso wani aiki, idan ya karbi hakkin wani musulmi da shi ya zamo Azzalumi.

**Wanda Hukuncisa yake babanta, Kamar wand ya bi su da jahilci tsammaninsa hakan hukuncin Allah ne:**

1. Zai iya gane gaskiya da kansa; sai yayi sakaci wajen sanin gaskiyar; to wannan ya aikata sabo.

2. Ba masani ba ne, sannan ba zai iya koyon karatu ba, sai ya bi su da takalidanci zatonsa hakan shine gaskiya, to wannan babu komai a kansa.

**DALILI NA FARKO:**

وَقَالَ ابْنُ عَبَّاسٍ: «يُوشِكُ أَنْ تَنْزِلَ عَلَيْكُمْ حِجَارَةٌ مِنَ السَّمَاءِ، أَقُولُ: قَالَ رَسُولُ  ، وَتَقُولُونَ: قَالَ أَبُو بَكْرٍ وَعُمَرُ!».

Ibnu Abbas Abbas yace: " Ya kusata duwarwatsu su sauka a kanku daga sama, inace Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce, ku kuma kuna cewa: Abu Bakar da Umar sun ce! ".

***DALILI NA BIYU:***

وَقَالَ أَحْمَدُ بْنُ حَنْبَلٍ: «عَجِبْتُ لِقَوْمٍ عَرَفُوا الإِسْنَادَ وَصِحَّتَهُ؛ يَذْهَبُونَ إِلَى رَأْيِ سُفْيَانَ، وَاللهُ تَعَالَى يَقُولُ: ( فَلْيَحْذَرِ الَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنْ أَمْرِهِ أَن تُصِيبَهُمْ فِتْنَةٌ أَوْ يُصِيبَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ )، أَتَدْرِي مَا الْفِتْنَةُ؟ الْفِتْنَةُ الشِّرْكُ؛ لَعَلَّهُ إِذَا رَدَّ بَعْضَ قَوْلِهِ أَنْ يَقَعَ فِي قَلْبِهِ شَيْءٌ مِنَ الزَّيْغِ فَيَهْلِكَ».

Imam Ahmad bn Hanbali yace: (( ina mamakin wasu mutane wadanda suka san sanadin hadisai, kama suka san ingancinsu; se suke tafiya zuwa ga ra'ayin Sufyanu, Allah ta'ala Ya na cewa: **{ To wadanda suke saba wa umarninSa su ji tsoron kada wata fitina ta same su, ko kuwa wata azaba mai radadi ta same su** *} (QS. An Nur, 63).*

Ko kasan mecece fitinah? Fitinah itace shirka, ta yiwu ian ya mayar da sashen maganarsa wani abu na bata ta damfaru da zuciyarsa sai ya halaka ))

- Abu Bakar da umar sunce! Ba a taba sanin cewa Abubakar Umar sun saba ma wani nassi da ra'ayinsu ba.
- {*Su ke saba uamarninsa* }: Ma'ana su na juya baya wa uamarninsa, suna guje masa, kuma ba su damu da shi ba.

**Malamai sunyi sabani kan takalidanci zuwa maganganu uku:**

**Takalidanci Wajibi ne:**

Sukace: an rufe kofar ijtihadi bayan mutuwar limaman mazhabobi hudu:

( Imam Abu hanifa, Imam Malik, Imaam Shafi'i, Imam Ahmad )

**Haramun ne kai tsaye:**

Domin cikin taklidanci akwai karbar maganar wanda maganarsa ba hujjah ba ce.

**Ya halatta (wannan itace Maganar da fi inganci )**

Idan akwai laluran yin takalidancin sabo da rashin iko wajen sanin hukunce hukunce, ya halatta ya yi takalidancin wanda ya aminta da shi ya dauki maganganunsa cikin dukkan mas'aloli, kar ya rinka bibiyan rangwamin malamai.

### *DALILI NA UKU:*

عَنْ عَدِيٍّ بْنِ حَاتِمٍ؛ أَنَّهُ سَمِعَ النَّبِيَّ □ يَقْرَأُ هَذِهِ الآيَةَ: { اتَّخَذُواْ أَحْبَارَهُمْ وَرُهْبَانَهُمْ أَرْبَاباً مِّن دُونِ اللّهِ } الآيَة، قَالَ: فَقُلْتُ لَهُ: إِنَّا لَسْنَا نَعْبُدُهُمْ، قَالَ: «**أَلَيْسَ يُحَرِّمُونَ مَا أَحَلَّ اللهُ فَتُحَرِّمُونَهُ، وَيُحِلُّونَ مَا حَرَّمَ اللهُ فَتُحِلُّونَهُ؟**»، فَقُلْتُ: بَلَى، قَالَ: «**فَتِلْكَ عِبَادَتُهُمْ**»، رَوَاهُ أَحْمَدُ وَالتِّرْمِذِيُّ وَحَسَّنَهُ.

Daga Adiyy 'dan Hatim, lallai shi ya ji Manzon Allah -Sallallahu alaihi wa sallam- yana karanta wannan ayar:

*" Sun riki manyan malamansu da masu ibadansu iyayengiji baicin Allah " (QS. Al Bara'ah, 31 ),*

Se Adiyy Ya ce da shi: ( lallai ne, ba mu zamo muna bautarsu ba, sai ya ce: " ba sa haramta muku abinda Allah Ya halatta ku haramtar da shi, sannan ba su halatta muku abin da Allah Ya haramta ku halatta shi ? ", sai Adiyy ya ce: hakane, sai Manzon Allah yace: " wannan itace bautarsu " ( Imam Ahmad da Tirmizi ne suka ruwaito, Tirmizi yace: hadisi ne hasan).

- {أَحْبَارَهُمْ}: Babban malami mai yalwataccen ilimi.
- {رُهْبَانَهُمْ}: Mai yawan ibada, tare da gudun duniya.
- ( Ba mu bauta mu su ): Ba ma yin sujada, ko ruku'u a gare su, sannan ba ma yin yanka bakance dominsu, Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallam ya bayyana ma sa cewa yin 'da a yana daga ma'anonin ibada, bauta ce kayyadaddiya.

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Tafsirin ayar suratunnur { *Wadanda suke saba umarninsa -Manzon Allah- su mai da hankalinsu }" (QS. An Nur, 63).*
2. Tafsirin ayar suratu bara'ah *{ Sun riki manyan malamansu da masu ibadansu iyayengiji }"(QS. Al Bara'ah, 31).*
3. *Fadakarwa dangane da ma'anar ibada, wacce Adiyy ya musanta ta.* (yin bauta a gare su, ta hanyar yi musu 'da a ).
4. Ibn Abbas ya buga misali da Abubakar da Umar, Imam Ahmad kuma ya buga misali da Sufyan.
5. Abun mamaki, yanda lamari ya canza, ta yanda da dama daga cikin mutane suka riki bautar masu ibada daga cikinsu a matsayin mafificin ayyuka, kuma suke kiranta wilaya, kuma bautar manyan malamai ta zamo ilimi da fiqihu, sannan yanayi ya canza har a ka bauta ma wanda ma shi ba ya daga cikin salihai, aka bauta wa -da ma'ana ta biyu- wanda yake cikin jahilai.

(Wajibi ne mu mayar da hankalinmu, kuma mu sani cewa bayar da kariya da tsare addinin Allah wajibi ne a kanmu, bai halatta ba yin 'da a ga wani cikin halatta abinda Allah Ya haramta, ko haramta abinda Allah Ya halatta har Abada ).

## [39] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ يَزْعُمُونَ أَنَّهُمْ آمَنُواْ بِمَا أُنزِلَ إِلَيْكَ وَمَا أُنزِلَ مِن قَبْلِكَ يُرِيدُونَ أَن يَتَحَاكَمُواْ إِلَى الطَّاغُوتِ وَقَدْ أُمِرُواْ أَن يَكْفُرُواْ بِهِ وَيُرِيدُ الشَّيْطَانُ أَن يُضِلَّهُمْ ضَلاَلاً بَعِيداً (٦٠)

***" Shin ba ka gani ba? zuwa ga wadanda suke riyawar cewar sunyi imani da abin da aka saukar zuwa gare ka, da abin da aka saukar daga gabaninka, suna son su kai kara zuwa ga Dagutu alhali kuwa lallai ne an umarce su da su kafirce ma sa, kuma shaidan yana son ya batar da su batarwa mai nisa "***. *(QS. An Nisa, 60).*

● Wannan babin yanada alaka maikarfi da babin da ya gabata, domin wanda ya gabata bayyana hukuncin wanda ya yi 'da a ga Malamai da shuwagabanni kan halatta abinda Allah Ya haramta ko haramta abinda Allah Ya halatta, wannan babin shi kuma ya kunshi inkaari ne ga wanda ya nufi kaiwa hukunci wajen wanda ba Allah ba.

● { ***Shin ba ka gani* ba** }: Tambaya ce ta tabbatar wa tareda mamakin halin wadannan mutanen, kuma an fiskantar da wannan maganar zuwaga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam-.

● { ***Suna riyawa*** }: Bai ce: ( Wadanda sukayi imani ba ), domin su basuyi imani ba, suna raya cewar su muminai ne alhalin su makaryata ne.

● { *Kuma Shaidan yana nufin* }: Jinsin Shaidan, Shaidanun mutane da na aljanu.

● { *Ya batar da su bata mai nisa* }: Yana aukar da su cikin bata mai nisa daga gaskiya da sannu a hankali.

● { Za ka ga munafukai } : An bayyana sunan munafukai a wajen da ake sakayewa saboda fa'idodi ne guda uku:

1. Wadannan da suke raya yin imani munafukai ne.
2. Wannan dabi'a ba a samunsa wajen kowa sai munafukai; saboda muminin gaskiya baya karkacewa daga hukuncin Allah.
3. Fadakarwa; Magana idan ta zamo bisa salo guda ko da yaushe, to za a iya gafala, amma yayinda aka canza salon Magana, to se mutane su bada kula yanda ya dace.

● Shaikhul Islam Ibnu Taimiyah Allah Ya jikansa yace: (( Tabbas wadannan ayoyin zasu aiki a kan masu canza ma'anonin ayoyin sifofin Allah, da masu ta'awilinsu; saoda wadannan saboda wadannan suna fadin cewa: lallai ne su sunyi imani da Allah da manzonsa, amma idan aka ce musu: Ku tafo zuwa ga abinda Allah Ya saukar kuma ku tafo zuwa ga hukuncin Manzon Allah; sai su bijire, kuma su karkace, sai suce: mu tafi zuwaga wane da wane, idan akayi inkarin abinda sukeyi sai suce: mu na son yin ihsani ne, da daidaitawa.

Zamu hada tsakanin dalilai na hankali da na alkur'ani da Sunnah domin muyi aiki da su a lokaci guda.

***DALILI NA BIYU:***

وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ لاَ تُفْسِدُواْ فِي الأَرْضِ قَالُواْ إِنَّمَا نَحْنُ مُصْلِحُونَ (١١)

*Da fadinsa: [ **Kuma idan aka ce musu kada kuyi barna a cikin kasa sai suce iyaka dai mu masu yin gyara ne ].** (QS. Al-Baqarah : 11).*

***DALILI NA UKU:***

وَلاَ تُفْسِدُواْ فِي الأَرْضِ بَعْدَ إِصْلاَحِهَا

*Da fadinsa: [ **kuma kada kuyi barna a cikin kasa a bayan gyaruwarta** ]. (QS. Al-Aa'raf: 56).*

***DALILI NA HUDU:***

أَفَحُكْمَ الْجَاهِلِيَّةِ يَبْغُونَ وَمَنْ أَحْسَنُ مِنَ اللهِ حُكْماً لِّقَوْمٍ يُوقِنُونَ (٥٠)

*Da fadinsa: [ **Shin hukuncin jahiliyyah suke nema? Kuma wanene mafi kyawun hukunci daga Allah saboda mutane masu yakini** -tabbataccen imani-? ] (QS. Al Maidah, 50)*

● ***[ Kuma idan akace musu kar kuyi barna a cikin kasa ]***: Yin barna a cikin kasa nau'i biyu ne:

1. Barna irin wanda ake gani da ido, ko ake ji da kunne: kamar rusa gidaje ko bata hanyoyi.
2. Barna irin ta ma'ana: Wannan tana kasancewa ne ta hanyar sabon Allah; domin sabon Allah daya ne daga cikin manya manyan barna a bayan kasa.

● ***[ iyaka dai mu masu yin gyara ne ]***: Wannan da'awa ce ta karya, wadannan da suke barna a cikin kasa kuma suke da'awar cewa su masu gyara ne, hakika sune mabarnata ba wadansunsu ba.

● { ***Bayan gyaruwarta*** }: ta bangaren mutanen kirki, daga cikin wannan; tsayuwa domin kishiyantakar da'awar malamai, da da'awar magabata na kwarai, da kishiyantakar wadanda suke aiki da Shari'ar Allah.

● **{ *Shin hukuncin jahiliyyah suke nema*?}**: tambaya ce ta zargi, ma'ana: me yasa ba sa bidar wani hukunci se na Jahiliyyah? jahiliyyah tana daukar ma'anoni guda biyu: [1] Lokacin da ya rigayi Manzanci. [2] Abubuwan da aka gina su kan Jahilci.

● *{ kuma wanene mafi kyawun hukunci daga Allah?}*: Babu wani wanda yafi Allah kyawun hukunci, wannan tambayace da kunshi ma'anar kalu balanta.

***DALILI NA BIYAR:***

عَنْ عَبْدِ اللهِ بْنِ عَمْرٍو؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**لَا يُؤْمِنُ أَحَدُكُمْ حَتَّى يَكُونَ هَوَاهُ تَبَعًا لِمَا جِئْتُ بِهِ**»، قَالَ النَّوَوِيُّ: (حَدِيثٌ صَحِيحٌ، رَوَيْنَاهُ فِي «كِتَابِ الْـحُجَّةِ» بِإِسْنَادٍ صَحِيحٍ).

Daga Abdullahi dan Amru; Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Imanin dayanku ba zai cika ba har sai son zuciyarsa ya zamo biyayya ga abinda nazo da shi ", Imam Nawawi yace: (Hadisi ne ingantacce, mun rawato shi cikin: " Kitabul hujjah " da sanadi ingantacce ).

***DALILI NA SHIDA:***

وَقَالَ الشَّعْبِيُّ: كَانَ بَيْنَ رَجُلٍ مِنَ الْـمُنَافِقِينَ وَرَجُلٍ مِنَ الْيَهُودِ خُصُومَةٌ، فَقَالَ الْيَهُودِيُّ: نَتَحَاكَمُ إِلَى مُحَمَّدٍ؛ عَرَفَ أَنَّهُ لَا يَأْخُذُ الرِّشْوَةَ، وَقَالَ الْـمُنَافِقُ: نَتَحَاكَمُ إِلَى الْيَهُودِ؛ لِعِلْمِهِ أَنَّهُمْ يَأْخُذُونَ الرِّشْوَةَ، فَاتَّفَقَا أَنْ يَأْتِيَا كَاهِنًا فِي جُهَيْنَةَ؛ فَيَتَحَاكَمَا إِلَيْهِ؛ فَنَزَلَتْ: { أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ يَزْعُمُونَ أَنَّهُمْ آمَنُواْ بِمَا أُنزِلَ إِلَيْكَ وَمَا أُنزِلَ مِن قَبْلِكَ} الآيَةَ.

وَقِيلَ: نَزَلَتْ فِي رَجُلَيْنِ اخْتَصَمَا، فَقَالَ أَحَدُهُمْ: نَتَرَافَعُ إِلَى النَّبِيِّ ﷺ، وَقَالَ الآخَرُ: إِلَى كَعْبِ بْنِ الأَشْرَفِ، ثُمَّ تَرَافَعَا إِلَى عُمَرَ، فَذَكَرَ لَهُ أَحَدُهُمَا الْقِصَّةَ، فَقَالَ لِلَّذِي لَمْ يَرْضَ بِرَسُولِ اللهِ ﷺ: أَكَذَلِكَ؟ قَالَ: نَعَمْ؛ فَضَرَبَهُ بِالسَّيْفِ فَقَتَلَهُ.

Ash,sha'abi ya ce: ( Husuma ta faru tsakanin wani munafuki da wani bayahude, sai bayahuden yace: mu kai hukunci wajen Muhammad -Sallallahu alihi wasallam-, saboda yasan cewa Manzon Allah ba ya karbar rishwa, sai munafukin yace: mukai hukunci wajen yahudawa, domin yasan su suna karbar rishwa, sai sukayi ittifaki kan su je ga wani boka dan kabilar Juhainah domin yayi hukunci a tsakaninsu, sai wannan ayar ta sauka: [ Shin ba ka gani zuwa ga wadannan da suke raya cewa lallai su sunyi imani da abinda aka saukar zuwa gare ka da abinda aka saukar gabaninka ] *(QS. An Nisa, 60).*

Wasu malamai suka ce: (Ayar ta sauka ne kan wasu mutum biyu da sukayi husuma, dayansu yace: mukai hukunci ga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam-, dayan kuma yace: zuwa ga Ka'ab dan Ashraf, sai suka tafi zuwa wajen Umar, sai dayansu ya ba shi labari, sai yace ma wanda bai yarda da hukunci manzon Allah ba: hakane? Sai yace: na'am; sai ya sare shi da takwabbi ya kashe shi ). Malamai sun raunana wannan hadisin amma ma'anarsa sahihi ne.

● " Ba ya da imani " : Ma'ana: ba ya da cikakken imani, sedai idan gaba daya ba ya son abinda Manzon Allah ya zo da shi; to wannan babu imani gaba daya tare da shi.

● " Munafiki " : Shine wanda yake bayyana musulunci, ya boye kafirci.

● " Yahudawa " : Sune masu dangantuwa da addinin Annabi Musa -Alaihis salam-, an kirayesu da haka ne:

1. Saboda fadinsu: (إِنَّا هدنا إليك), Lallai mu mun komo zuwa gareka (mun tuba ).
2. Ko kuma nasaba ce zuwa ga babansu Yahuza.

● "Zuwa ga Muhammad " : sallallahu alaihi wasallam, bai siffanta shi da manzo ba saboda basuyi imani da Manzancinsa ba

● " *Rashawah* " : Kudin da ake bayarwa na -cin hanci- domin samun wata bukata.

## *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Tafsirin ayar suratun Nisa'i, da abinda ta kunsa na taimakawa wajen fahimtar ma'anar Dagut. *[ **Shin ba ka gani ba? zuwa ga wadanda suke riyawar cewar sunyi imani da abin da aka saukar zuwa gare ka, da abinda aka saukar daga gabaninka** ].*

2. Tafsirin ayar suratul-Baqarah: *[ **Kuma idan akace musu kada kuyi barna a cikin kasa** ].* (Cikinta akwai dalili kan cewa munafurci barna ce a bayan kasa, domin ayar tazo ne kan siyakin munafukai, barna ta kunshi dukkan zunubai.

3. Tafsirin ayar suratu l A'araf. *[ **kuma kada kuyi barna a cikin kasa bayan gyaruwarta** ].*

4. Tafsirin ayar: { ***Shin hukuncin jahiliyyah suke nema***?}: ( Jahiliyah itace duk wani abunda ya saba wa Shari'ah, kuma an danganta shi ne da Jahiliyyah domin a guje shi, da bayanin muninsa, kuma da bayanin cewar an gina wannan abun a kan jahilci ne da bata.

5. Sha'abi ya bayyana sababin saukar ayar da ta zo a farkon babin.

6. Banbanci tsakanin imani na gaskiya da na karya ( Imani na gaskiya shine yake lizimta cikakken jawuwa, da karba, tareda mika wuya ma hukuncin Allah da Manzonsa -Sallallahu alaihi wasallam-, imani na karya kuma shine akasin haka ).

7. Kissar sayyidina Umar tareda wannan Munafikin.

8 Kasantuwar babu wanda imaninsa zai cika har sai son zuciyarsa ta zamo biyayyya ga abinda Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya zo da shi.

## Jarabawa kashi na bakwai (Babuka 9)

**Tambaya ta farko: sanya alamar (☒) a wurin da ya dace ko ka cikita ibarar:**

1. Babi na farko a kasha na bakwai shine babin soyayya: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
2. Wadansu masu ibada suna girmama wadansu kaburbura kuma suna son su, kuma suna. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
3. Idan zuciya ta wufanta gaba daya daga son Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- wannan zuciyar : ☐ tanada tawayar imani ☐ Babu imani ckinta kwata kwata.
4. Wajibi ne son Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- fiye da son 'diya da uba da dukkanin mutane: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne .
5. Daga sabubban samun 'dan 'danon imani ayi so ☐ Domin Allah ☐ Saboda kusanci.
6. Ana 'daukar hani akan kore wa ne …………………., ko kuma akan: ……………… ……………..ko akan:………………………………………
7. Maganar Ahlus Sunnah dangane da nassoshin tsoratarwa itace………….. …… … ……………………………………………………………………………………….
Wannan yana nuni kan cewa ba zamu san ma'anarsu ba? ☐ Na'am ☐ A'a.
8. Duk wanda yake ganin yahudu da nasara suna kan addini yarjajje a wajen Allah abin karba bayan aiko Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- to wannan ya fice daga musulunci, kuma ya karyata alqur'ani ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
9. Musulmi baya algush ma kafiri, yana masa nasiha, kuma yana bayyana masa cewar shi yana kan bata, kuma ya sabawa Umarnin Annabi Musa da Isah -Alaihimas salam- ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
10. Kin abokan gaban Allah da yin adawa dasu baya nufin karmu cika musu alkawarinsu ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
11. Wani mai magana yace: (idan naga kirista sai in rufe idona domin kar naga abokin gaban Allah ) wanda ya fadi haka shine: ☐ Imam Ahmad bn Hanbali ☐ Shaikhul Islam bn Taimiyah.
12. Wani mai magana yace: ( Duk mumini mai tsoron Allah to waliyyin Allah ne ), wannan mutumin shine: ☐ Ibnu Taimiyah ☐ Ibnul Qayyim.
13. Gamammar wilalaya wacce Allah Ya baiwanta ta ga bayinsa ta game mumini da kafiri, da dukkannin halittu ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
14. Da mutum zaiyi Sallah kuma yayi azumi sannan ya jibinci abokan gaban Allah to wannan ba zai samu wilayar Allah ba. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
15. Mawallafin ya kulla babin Soyayya a bayan babin tsoro ne, domin ibada tana kaiwa da komowa ne a kansu. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

16. Mutane sun kasu bangare biyu ne da na tsakiya dangane da tsoro ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
17. Tsoro matsagaici shine wanda yake hana mutum aikata abubuwan da Allah Ya haramta, duk abinda ya karu akan wannan to lallai ne zai iya kai utum zuwa ga 'debe tsammamin daga Rahamar Allah. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
18. Duk mai taimakon alfahasha da munkari to wannan yana daga cikin waliyyan shaidan ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
19. Duk wanda yake tsoron Allah to kowa zai tsorace shi, duk wanda ya kiyaye Allah to kowa zai kiyayeshi ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
20. Abin nufi da raya masallatai shine: ( rayasu irin na: ☐ Hissi (wanda ake iya gani ) ☐ Ma'ana ☐ Duka biyun.
21. Allah Ya gwama tsakanin yin imani da Allah da imani da ranar karshe a wurare masu yawa, domin hakan zai zaburar wajen yin 'da a gareshi.
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
22. Me yasa muke son Annabi Muhammad sallallahu alaihi wasallam?
1……………………………………………….2……………………………………………….
3……………………………………………….4……………………………………………….
23. Soyayyar Annabi bayan mutuwarsa tana zamowa ne da:
1……………………………………………….2……………………………………………….
24. Ma'anar kuma ya tsayar da Sallah itace:
☐ Sallah wajiba ☐ Mustahabbiya ☐ Duka biyun.
25. Tawakali rabin addini ne ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne. Ya halatta mutum yace: ☐ Na dogara da kai ☐ Na wakilta ka ☐ Na dogara da Allah sannan na dogara da kai ☐ Ya halatta a fadi duka banda na farko.
26. Tawakali shine: ……………………………………………………………………….
Ya rabu zuwa gida: ( ☐ 3 ☐ 4 ☐ 5 ).
27. Dogara ga matattu da fakakku shirka ne: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
28. Dogaro ga wani mutumi cikin dukiyarsa da rayuwarsa dogaro ne irin na bukata ☐ Haka ne ☐ Karamar shirka ce.
29. Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallam shine shugaban masu tawakkali ga Allah, tareda haka ( ☐ Yana iya cutuwa ☐ Ba ya cutuwa ), Kuma ( ☐ Tsanani yana haduwa dashi ☐ Ba ya haduwa da wani tsanani ).
30. Me mutum zaice yayin bakin ciki? ……………………………………………………
31. Ibnu Abbas radiyallahu anhu yana ( ☐ Karbar riwaya daga banu isra'il ☐ Yana inkarin riwaya daga banu isra'il.
32. Wanda yake debe tsammani daga Rahamar Allah shine: ☐ Batacce ☐ Marashin shiriya, ☐ Dimautaccen da baisan abinda yake wajaba a kansa ba na hakkin allah ☐ Duka gaba daya.
33. Amintuwa daga makrun Allah illah ce ta janibin ☐ Tsoro ☐ Fata.

Debe tsammani daga Rahamar Allah illah ce ta janibin ☐ Tsoro ☐ Fata.

34. Manyan laifuka (☐ Sunada adadi na musamman ☐ Sunada iyaka ) Kuma suna daraja daya ne ( ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ). Karamar shirka itace mafi girman kaba'ir ( ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ). Huhuncin mai aikata babban laifi (☐ Mumini ne shi, mai tawayar imani ☐ Mumini ne da imaninsa, fasiki da babban laifinsa, ☐ mu'mini ☐ kafiri ☐ Na farko da na biyu ). Mai aikata babban laifi (☐ Ana sonsa ☐ Ana kinsa ☐ Ana sonsa gwargwadon imaninsa, kuma ana kinsa gwargwadon Fasikancinsa ). Shin ana kankare manyan laifuka da kyawawan aiyuka? ( ☐ Na'am ☐ A'a ). Shin ana iya zama tareda mai aikata babban laifi a lokacin da aikata laifin? (☐ Na'am ☐ Kuskure ne ). Tuba tana inganta daga manyan laifuka (☐ Na'am ☐ A,a).

35. Hakuri ya kasu kashi ☐ 3 ☐ 4 ☐ 5. Yana daga alamar soyayyar Allah ga bawansa jarabtarsa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

36. Mafi kololuwar nau'ukan hakuri shine hakuri daga barin sabon Allah. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

37. Daga fa'idodin haddace babin hakuri, karanta su yayin musiba, da kuma karanta su ga wanda ya fada cikin musibar. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

38. Samun ta'adodi biyu daga ta'adodin kafirci a wajen mumini suna lizimta zamowarsa kafiri ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

39. Samun ta'adodi biyu daga ta'adodin imani a wajen kafiri kamar kunya, wannan baya hukunta zamowarsa mumini. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

40. Idan kalmar kafirci (كفر) tazo nakirah -ba tareda alifun da lamun ba- (☐ tana nuni akan fita daga musulunci ☐ Bata nuni kan ficewa daga musulunci.

41. Mutane dangane da musiba sun kasu gida: ☐ 5 ☐ 4 ☐ 3 .

42. Fushi akan musiba yana iya kaiwa ga kafirci. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

43. Fushi yana kasancewa ne da: ☐ Zuci, da harshe, da gabbai ☐ Harshe da gabbai.

44. Banbanci tsakanin hakuri da yarda, cikin hukunci ne da nauyin musibar. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

45. Imanin mutun yana iya karuwa sakamakon jarabawa. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

46. Allah yana halittan sharri sabota hikima ce, wannan sharrin yakan zamo alheri ne ta fiskar abinda ya kunsa na hikimar Allah. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

47. Ankira ranar lahira da wannan sunan saboda tashin: ☐ Mutane daga kaburburansu ☐ Masu bada shaida ☐ Adalci ☐ Duka.

48. Gaggawta ukubar duniya tafi sauki samada a jinkirta masa ita zuwa ranar lahira ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

49. Sakamakon Allah ga bawa akan sukan kaya kamar sakamakon karaya ce. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

50. Wajibi ne cikin dukkan siffofin Allah ☐ A tabbatar da ita ☐ A kiyayi misalta ta da wani abu, kuma a kiyayi bayanin yanayin siffar ☐ Duka biyun.
51. *Ma'ana Suka ga nasaba shine*: ☐ Aibanta nasabar ☐ Kore nasabar ☐ Duka byun.
52. Riyah shirka ce: ( ☐ Karama ☐ Karamar shirka ce amma tana iya zamowa babbar shirka. Riya tana aukuwa ga wanda yayi aikata wani aiki domin mutane su gani, Riya bata shiga aikin wanda yayi domin mutane suji ( ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne).
53. Tuna mutuwa da magaginta daya ce daga hanyoyin magance riya.
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
54. Farin cikin mutum yayin da mutane suka san ibadarsa hakan ☐ Riya ce ☐ Ba riya ba ce.
55. Farin cikin mutum da da arsa ga Allah ☐ Riya ce ☐ Ba riya ba ce.
56. Wani mutum ya bayar da sadaka sai Allah Ya sanya sonsa da yabonsa cikin zukatan muminai ☐ Wannan mutumin mai aikata riya ne ☐ Mai ikhlasi ne.
57. Ya bayar da sadaka domin Allah da niyyar dukiyarsa ta habaka wannan mai neman ☐ Duniya ce da aikin lahira ☐ Lahira da aikinta.
58. Idan mutum yaji tsoron aukawa cikin riya to sai yabar aikata wannan ibadar ☐ Ya halatta ☐ Karamar shirka.
59. An kira shi bawan dinare ne saboda: ☐ Yana bauta wa dinaren ☐ Yardarsa da fushinsa domin dinare ne da wannan ne yazamo kamar mai bautarsa.
60. Ma'anar Kalmar: طُوبَى: ☐ Yanayi mafi dadi ya kasance ma wannan mutumin ☐ Bishiya ce a cikin Aljannah.
61. Babin nufin mutum duniya da aiyukansa yafi hadari samada babin riya ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
62. Abinda dayan mutum biyu masu husuma ya bayar wa alkali wannan abun ☐ Kautar ma'aikaci ne ☐ Rashawa ce. ☐ Duka biyun.
63. Babu banbanci tsakanin riya cikin ( La'ilaha illallahu ), da riya cikin sadaqa.
☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
64. Dirhami nauin kude ne daga ☐ Zinariya ☐ Azurfa.
65. Wanda ya cancaci yabo sune ma'abota dukiya da matsayi.
☐ Hakaen ☐ Kuskure ne.
66. Ana gane cewar mutum yana nufin duniya da aiyukansa ne idan aka bashi wani abun duniya sai ya yarda, idan aka hana shi sai yayi fushi. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
67. Malamai sune ma'abotan ☐ Lizimtawa da zartarwa ☐ Nuni da shiryarwa. Malamai sune na biyu. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
68. Ba a taba sani ba a tarihi cewar Abubakar da Umar sun saba wa nassi da ra'ayinsu. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
69. Kashe kashen da a ga malamai da shuwagabanni cikin sabon Allah:

1…………………………………………hukuncinsa………………………………………….
2…………………………………………hukuncinsa………………………………………….
3…………………………………………hukuncinsa…………………………………………
….
70. Makauniyar takalidanci, da tassubanci irin na mazhaba: ☐ Abin yabo ne ☐ Abin zargi ne.
71. Arrahib shine: ☐ Malami mai yalwar ilimi ☐ Mai ibada tareda gudun duniya. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne. Shuwagabanni sune na biyun ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
72. Cikin hadisin Adiy Allah Ya kara yarda a gareshi, Manzon Allah ya fara ne da haramta halal, saboda shine mafi tsanani samada halatta haram, kuma duk abu biyun haramunne ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
Bin malamai cikin da shuwagabanni cikin (☐ Saba ma ☐ Abinda ya dace da ☐ duka biyun ) Shariar Allah yana daga rikansu iyayen giji baicin Allah.
73. Dukkan wanda yaki abinda Allah ya saukar to wannan kafirci ne ☐ Babba ☐ Karami.
74. Kudirin halaccin yin hukunci ba da abinda Allah Ya saukar ba kafirci ne ☐ Babba☐ Karami.
75. Kudurrin cewa hukuncin wanin Allah daidai yake da hukuncin Allah, ko ma yafi kyawu samada hukuncin Allah kafirci ne ☐ Babba ☐ Karami.
76. Kudirin cewa hukuncin Allah shine mafi kyawun hukunci, sedai kiyayyarsa ga wanda yake yin hukuncin a kansa yasa shi yin hukunci ba da abinda Allah Ya saukarba to wannan.
☐ kafiri ne ☐ Azzalumi ne ☐ Fasiki ne.
77. " وَيُرِيدُ الشَّيْطَانُ " ( Shaidan yana son ), Jinsin ne, ana nufin shaidanun ☐ Mutane ☐ Aljanu ☐ Duka.
78. يَزْعُمُونَ Fadin Allah: ( Suna raya ), ma'anarsa: ☐ Yin imani alhai su makaryata ne ☐ Aiyukansu suna karyata maganganunsu ☐ duka.
79. Musiba: ☐ Ta fiskar Shari'a ce ☐ Lamari ne na duniya ☐ Duka biyun.
80. Wanda baya bin umurnin Allah da na Manzonsa wannan ☐ Mumini ☐ munafiki.
81. Mafi girman barna a bayan kasa, itace barna ta ☐ Wanda ake iya ganinta ☐ Barna ta ma'ana.
82. Barna bayan gyaruwa tafi tsanani da muni samada mutum yaci gaba da barnarsa kafin gyaruwan, koda yake abinda ake so shine gyaruwarsa bayan baci ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
83. Ma'anar Jahiliyah ☐ Kafin aiko Manzon Allah SAW ☐ Aikin Jahilcin da ba a gina shi akan ilimi ba ☐ Duka biyun.
84. Bayar da rashawa haramunne, koda kuwa saboda neman hakkinsa ne da aka hana shi, ko kuma domin ya tunkude wata barna daga samun sa: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

## [40] BABIN WANDA YA YI MUSUN WANI ABU NA SUNAYEN ALLAH KO SIFOFINSA

**Musu shine: inkari, inkari naui biyu ne:**

**Inkari na karyatawa: (Kafirci ne babu shakka)**
Duk wanda yayi inkarin wata suna daga sunayen Allah ko wata sifa daga sifofin Allah, wanda Al qur'ani da Sunnnah suka tabbatar da su, to wannan kafiri ne, da ijma,in malamai, domin karyata Allah da Manzonsa kafirci ne wanda yake fitar da mutum daga musulunci da ijma'in malamai

**Inkari na tawili:** baya muzantawa sedai yana tawilinsu zuwa wata ma'anar da saba wa hakikanin Ma'anar.

**Tawilin da bashida tushe a larabci; to wannan yana kafirta:**
Kamar yace: ma'anar Hannu: Sammai, to wannan yana kafirta, domin fassara Kalmar "Yadu " da ma'anar sammai bashida tushe a larabci, kuma ba shine hakikanin ma'anar da Shari'a take nufiba, to wannan mai inkari ne kuma makaryaci ne.

**Tawilin da yakeda tushe a larabci; to irin wannan bazai kafirtaba saboda shi, sedai yana kan hadari maigirma, sai a maida masa martani:**
kamar ya fassara fadin Allah:
(بل يداه مبسوطتان)
Yace ma'anar: " Yadu ": Niima, to wannan ba a kafirtashi; saboda Kalmar "Al-Yadu": ana iya amfani da ita a larabci da ma'anar ni'ima, sedai zamu masa raddi da cewa:

1. fassararka ta saba wa zahirin nassi, da ijma'in Salaf, kuma babu wani dalili da zai goyi bayan wannan fassarar.
2. An siffanta " Hanun " da siffofin da bazai taba yiyuwa ta dauki ma'anar ni'ima ko karfiba, Kamar: biyuntata, da Jam'inta, da Damka, da Shimfida.
3. Ubangiji Allah Ta'ala Ya goranta wa Annabi Adam da cewar Ya Halitta shi da hannunSa, to idan ma'anar " Yadu " itace ni'ima ko karfi, to lallai babu babaci tsakanin Annabi Adamu -Alaihis Salam- da sauran halittu?

● **Tauhidin Al- Asma'u was Sifat:** Shine a kadaita Allah -Maigirma da buwaya-da Sunar da Ya Rada wa kanSa, ko Sifar da Ya sifanta KanSa da ita a cikin littafinSa ko a bisa harshen manzonSa -Sallallahu alaihi wa Sallam-, a tabbatar masa da abinda Ya tabbatar wa kanSa -na Sunaye da Sifofi- kuma a kore masa abinda Ya kore wa kanSa, ba tareda an jirkita ma'anar ba, ko an kore ta ba, ko a yi bayanin yanayinta, ko a misalta ta.

**Me yasa yace: ( ba tare da an jirkita ma'anar ba) baice: ( ba tareda anyi tawili ba?)**

1. Kalmar **" Tahrifi "** itace tazo cikin Alqu'ani, bazamu canza ta da wata ba.
2. Hakan shi yafi kusa da adalci, saboda su ma'abota jirkita ma'anonin sifofin Allah ne, ba masu tawili ingantacce ba ne.
3. Domin kore mutane daga sharrinsu, saboda idan muka siffanta su da tawili sai suyi farin cikin hakan.
4. Ba dukkan tawili ne abin zargi ba, wanda dalili yayi nuni akansa to wannan sahihi ne kuma za a karbe shi, wanda kuma dalili baiyi nuni a kansa ba to wannan karya ce kuma abin jefarwa ne, amma shi **Tahrifi** gaba dayansa abin zargi ne.

**Me yasa ya kore misaltawa -Attamsil- bai kore kamantawa -Attashbih- ba?**

1. Domin misaltawa ita tazo cikin Al qur'ani, wannan abin korewa ne ga Allah, sake, sabanin tashbihi.
2. Saboda bai halatta ba kore tashbihi saki wawai, domin dukkan samammun abubuwa guda biyu to babu makawa sai an samu wani gwargwado a tsakaninsu da sukayi tarayya da kamanceceniya cikinsa, sannan kowanne ya kebanta da wadansu abubuwan da dayan bai kebanta da su ba.
3. Mutane sunyi sabani gameda ma'anar tashbihi, wadansu sun sun fahimci tabbatar da sifofin Allah da tashbihi.

**Kalmar: الإسم (suna) an tsago shi ne daga dayan kalmomi biyu:**

1. السمو ( Daukakar wani abu ), kowani maidaukaka yakan daukaka ne da sunansa, kuma ya bayyan da ita.
2. السمة ( Alama ) suna alama ce ga mai sunan.

**Banbancin suna da sifa:**

Suna: abin da Allah Ya kira kanSa dashi na sunaye, Sifa: abinda Ya siffanta dashi.

**Me yasa muke karanta tauhidin Asma'u was sifat?**

1. Domin mu tace tauhidi, mutum bazai zamo mai tauhidi ba har sai ya kadaita Allah da nau'ukan tauhidi guda uku.
2. Saboda cikin tauhidi akwai rayuwar zukata, abu mafi girma kuma mafi daraja ga rayuwar zukata shine sanin Allah .
3. Domin mu shiga Aljannah; saboda fadin Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam: "Allah Yanada sunaye tis'in da tara, duk wanda ya kiyaye su zai shiga Aljannah.
4. Wannan shine asalin da Salaf suke tafiya a kai.

5. Domin kar mu auka cikin abinda wadansu kungiyoyi na bata suka auka ciki, na misalta Allah da wani ko kore wani abun da Allah Ya sifanta kansa dashi.
6. Domin mu roki Allah da su Allah Ta'ala Ya ce:

وَلِلّهِ الأَسْمَاء الْحُسْنَى فَادْعُوهُ بِهَا

***[ Kuma Allah Yanada sunaye kyawawa sai ku roke shi da su ].*** *(QS. Al-A'araf : 180).*

**Tahrifi: Canza abinda ya wajaba a tabbatar dashi wa Allah**

**Canza Ma'anar:**
Kamar wanda yace: Ma'anar hanu itace: niima.

**Canza Lafazin:**
Kamar canza sunan Allaah daga "الله" zuwa "الله" ( daga rufu'a zuwa fataha ), misali, fadin Allah ta'alah:

وَكَلَّمَ اللّهُ مُوسَى تَكْلِيماً

" ***Kuma Allah Ya yi magana da Annabi Musa magana sosai***".
Sunyi inkarin sifar magana ga Allah saboda rayawarsu cewar Annabi Musa shine mai maganar, raddi a kansu da tambayarsu dangane da fadin Allah ta'ala:

وَكَلَّمَهُ رَبُّهُ

" ***Ubangijinsa Ya yi masa magana*** ".
Bazasu iya bada amsa ba kuma daga nan hujjojinsu zasu yanke.

**Ta'adili: Musun abinda ya wajaba wa Allah na Sunaye da Siffofinsa**

***Ta'adilun juz'i*** **( Kore wani bangare ):**
Kamar Ash'ariyya, suna tabbatar da wadansu sifofin suna kore wasu.

***Ta'adilun Kullyyun*** **( Korewa na gaba daya ):**
Kamar yanda jahamiyyah suke kore dukkan sifofin Allah Ta'alah.

**Takyifi: ana tambaya a kansa da " yaya " yana kasantuwa:**

**Da harshe ake furtashi:**
kamar ya siffanta wani abu da harshensa.

**da yatsa wajen rubutu:**
kamar ya rubuta wani abu da yatsarsa.

**Da zuci ake kaddarashi:**
kamar ya kintata wani abu da zuciyarsa.

## Nunin Suna:

**Mu'dabaqa ( Dacewa):** Nunin suna akan dukkan ma'anonin da yake gewaye dashi.

**Tadammun ( Kunsar ma'ana):** Nunin suna akan wani bangare na ma'anarsa.

**Talazum ( Lizimtawa ):** Nunin suna akan wani abu da yake wajen ma'anoninsa.

**Misali kan haka**: Sunan Allah Al-Khaliq (Maihalitta), yana nuni akan zatin Allah shi kadai ta hanyar Mudabaka -bisa dacewa da gundarin kalmar - kuma yana nuni a kan sifar halitta, ta fiskar ma'anar da Kalmar ta kunsa, sannan yana nuni a kan Ilimi da Iko na Allah ta fiskar lizimta -Kasantuwar Allah ta'ala shine Ya halicci kowa da komai wannan yana lizimta ilimi da iko na Allah- Kamar yanda Allah Yake cewa:

اللَّهُ الَّذِي خَلَقَ سَبْعَ سَمَاوَاتٍ وَمِنَ الْأَرْضِ مِثْلَهُنَّ يَتَنَزَّلُ الْأَمْرُ بَيْنَهُنَّ لِتَعْلَمُوا أَنَّ اللَّهَ عَلَى كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ وَأَنَّ اللَّهَ قَدْ أَحَاطَ بِكُلِّ شَيْءٍ عِلْماً.

*[ Allah wanda Ya halitta sammai bakwai, kasa ma suna da misalinsu, umarninSa yana sauka a tskaninsu domin kusan cewa lallai Allah mai ikone akan komai, kuma lallai Allah hakika Ya kewaye dukkan komai da sani ]* **.** *(QS. Addalaaq : 12)*

### Ta yaya zamu karanci ilimin tauhidin Al asma'u wa sifat?

1. Ilimi ibada ce, kuma wajibi ne -cikin dukkan ibada- mubi tafarkin manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- da sahabbansa -Allah Ya kara yarda a garesu-.

2. Wajibi ne manufar karatun ta zamo girmama Allah ne; don haka ne ma yayin da aka tambayi Imam Malik -Allah Ya jikansa- dangane da daidaituwar Allah akan al'arshin Allah, sai ya girgiza kansa kuma gumi ya lullube shi (saboda girmar tambayar ).

3. Ba zamuyi tambaya kan wani abunda sahabbai basuyi tambaya a kaiba.

4. Wajibi ne dalili ya rigayi kudiri, amma wadanda suka saba ma Ahlussunnah suna fara kulla kudirinsu ne kan wasu abubuwa sannan saisu nemo musu dalilai, alhali basa samar musu dalilai ingattattu, sai suyita fagauniya sannan su auka cikin bidi'oi.

5. Aiwatar da kaidar Imam Shafi'i -Allah Ya jikansa-: ( **kayi imani sai ka shiriya** ), kayi imani da Allah kuma kayi imani da abunda yazo daga wajen Allah bisa manufar Allah, sannan kayi imani da Manzon Allah -sallallahu alaihi wasallam- da abunda yazo daga wajensa kamar yanda manzon Allah yakeso.

**Wadansu abubuwan da sukeda alaqa da Sunayen Allah da SifofinSa:**

1. Sunayen Allah basuda adadi iyakantacce, dalili; fadin Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallam:

«أَوِ اسْتَأْثَرْتَ بِهِ فِي عِلْمِ الْغَيْبِ عِنْدَكَ».

"... **Ko ka kebanta da shi a wajenka cikin ilimin gaibu** ", Amma dangane da fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- "**Allah Yanada sunaye tis'in da tara** ", wannan baya nunin cewa Allah bashi da wadansu sunayen se wadannan kadai, kamar maganar wani ne: ( inada dawakai dari wadanda na tanade su domin sadaukarwa ).

2. **Sunayen Allah; Sunaye ne kuma sifofi**: ba sunaye ne tsantsa wadanda basuda ma'ana ba, Sunaye ne ta fiskar nuninsu ga zatin Allah, Sifofi ne dangane da abinda sunayen suka kunsa na sifofi, sabanin sunayenmu; sunan wani zai iya zamowa Aliyu (Wato: madaukaki ), kuma kasameshi daga mafi kaskantar mutane.

3. **Sunayen Allah abu daya ne, kuma mabanbanta ne:** Abu gudane ta fiskar nuninsu akan zatin Allah, dukkansu suna nuni ne kan abin ambato guda, (Wato Allah ), As-Sami'u, da Al-Basiru, da Al-Hakimu, da dukkaninsu suna ne da suke nuni kan wani abin Ambato guda, shine: Allah, sedai sun sha banban ta fiskar ma'anoninsu, ma'anar: Al- Hakimu ya banbanta da ma'anar As-Sami'u.

4. **Kowani suna daga sunayen Allah yana nuni akan Zatin Allah, sannan yana nuni a kan Ma'anar Sunan;** ya zamo wajibi akanmu muyi imani dashi sunane daga sunayen Allah, sannan kuma munyi imani da abinda kowani suna yake dauke dashi na sifa, kuma munyi imani da abin da wannan Sifa take nuni a kai da ta'asiri, da hukunci, idan sunane da hukuncinsa ke bayuwa zuwaga wani abun; **Misali**: sunan Allah: **Assami'u:** (**Mai ji**) munyi imani da cewa suna ne daga sunayen Allah ta'ala, kuma yana nuni a kan sifar **( Ji )**, kuma suna ne da yake da hukunci da ta'asiri, Ma'ana: Allah Yana jin komai da kowa, amma idan sunan baya zartuwa ga wani kamar: **Al-Azeem** (**Maigirma**) da: **Al-Hayyu** ( **Rayayye** ) da **Al-Jalilu** ( **Maigirma** ); Sai mu tabbatar da sunan da Sifar, babu wani hukunci dake bayuwa zuwa gareshi.

5. **Sifofin Allah sunfi yalwa samada SunayenSa:** saboda kowani suna ya kunshi Sifa, amma ba kowace Sifa ce take zamowa sunaba, ana Sifanta Allah da **Magana da Nufi**, amma ba bazamu kirashi da: **Maimagana** ko **Mai nufi** ba, a matsayin suna.

6. Duk abinda Allah Ya Sianta kansa dashi, to wannan bisa hakika ne, sedai ana tsarkake Allah daga a misalta shi ko ayi bayanin yanayin Sifar.

***DALILI NA FARKO:***

وَهُمْ يَكْفُرُونَ بِالرَّحْمَنِ

*[ **Alhali kuwa su suna kafirta da Ar-Rahman**]…(QS. Ar-Ra'ad : 30).*

● Kafiran Quraishawa sun kafirce wa sunan Allah (**Ar-Rahaman**), amma basu kafirce da mai sunan ba, suna tabbatar dashi (**Allah**).
● Cikin wannan Ayar akwai dalili kan duk wanda ya yi inkarin wata suna daga cikin sunayen Allah Ta'alah to zai iya kafirta.

***DALILI NA BIYU:***

وَفِي «صَحِيحِ الْبُخَارِيِّ»؛ قَالَ عَلِيٌّ: «حَدِّثُوا النَّاسَ بِمَا يَعْرِفُونَ، أَتُرِيدُونَ أَنْ يُكَذَّبَ اللهُ وَرَسُولُهُ؟!».

Yazo a cikin " Sahihul Buhari ", daga Aliyu ya ce: " Ku karantar da mutane gwargwadon fahimtarsu, ko ku na so a karyarta Allah da Manzonsa ne ".

● Wajibi ne akan mai da'awa ya ringa la'akari da matsayin wadanda yake kiransu zuwaga addinin Allah, sannan ya ajiye kowane mutum a wajen da yadace dashi, ya karantar da mutane gwargwadon hankalinsu, mu karantar dasu mataki mataki har su karbi wannan zancen su nutsu dashi, kar mu kiraye su zuwa ga abin da hankalinsu bazai daukaba.

***DALILI NA UKU:***

وَرَوَى عَبْدُ الرَّزَّاقِ، عَنْ مَعْمَرٍ، عَنِ ابْنِ طَاوُوسٍ، عَنْ أَبِيهِ، عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ؛ أَنَّهُ رَأَى رَجُلًا انْتَفَضَ لَـمَّا سَمِعَ حَدِيثًا عَنِ النَّبِيِّ ﷺ فِي الصِّفَاتِ؛ اسْتِنْكَارًا لِذَلِكَ، فَقَالَ: «مَا فَرَقُ هَؤُلَاءِ؟ يَجِدُونَ رِقَّةً عِنْدَ مُحْكَمِهِ، وَيَهْلِكُونَ عِنْدَ مُتَشَابِهِهِ» انْتَهَى.

Abdur Razzak ya ruwaito daga Ma'amar, daga Dawus, daga babansa, daga 'dan Abbas; cewa yaga wani mutum ya firgita yayinda yaji wani hadisi daga Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- kan sifofin Allah; domin musanta hakan, sai dan Abbas yace: ( tsoron me wadannan su ke ji, suna nutsuwa yayinda sukaji…… .

● مَا فَرَقُ:? Ma'ana tsoron me su ke wajen tabbatar da sifar Allah da aka karanta musu dalili a kanta kuma da yarensu da suke Magana ta it? Me yasa basa tabbatar da ita wa Allah kamar yanda Manzon Allah SAW ya tabbatar da ita?

**Ana siffanta Alqur'ani da:**

- **Muhkam dukkansa:** Ma'ana: wanda aka kyautata shi, matukar kyautatawa.
- **Mutashabih dukkansa:** Sashensa yana kama da sashe, kuma sashe yana gasganta sashe.
- **Cikinsa akwai muhkam, kuma akwai mutashabi**
  - **Muhkam:** Ayoyi wadanda ma'anonin Su, suka fito fili.
  - **Mutashabih:**
    - **Nisbiyyun:** Bisa qira'ar da aka sadar da ita.
    - **Mudlaq:** Bisa qira'a wacce ba a sadar da ita.

1. Ana kiran Alqur'ani da cewa shi **Muhkam ne dukkansa**: ba tare da an ambaci **Al-Mutashabih** ba, Ma'ana: Alqur'ani babu wani kuskure cikinsa, babu karya cikin labarinsa kuma babu zalunci cikin hukunce hukuncensa, Allah ta'ala Yace:

وَتَمَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ صِدْقاً وَعَدْلاً

*[ **Kuma Kalmar Ubangijinka ta cika wajen gaskiya da adalci** ]. (QS. Al-An'am 115).*

2. Kuma ana kiran Alqur'ani da cewa shi: **Mutasaabih ne gaba dayansa**, ba tareda an ambaci Al Muhkam ba, Ma'ana: sashen Alqur'ani yana kama da sashe, wajen kyawunsa da cikar kamalarsa, kuma sashensa yana kama da sashe, babu tufka da warwara cikinsa, Allah ta'ala yace:

اللَّهُ نَزَّلَ أَحْسَنَ الْحَدِيثِ كِتَاباً مُّتَشَابِهاً

*[ **Allah Ya sassaukar da mafi kyawun labari, littafi ( Alqur'ani ) Mai kama da junansa** ]. ( QS. Az-Zumar : 23).*

3. Kuma ana iya cewa cikin Alqur'ani akwai **Muhkam sannan akwai Mutashabih**, ma'anar Muhkam anan itace: wanda ma'anarsa ta fito fili kuma ta bayayana, Ma'anar Mutashabih anan itace: wanda ma'anarsa ta buya, nau'i biyu ne: (**Mudaqun da Nisbiyyun**, Wannan yana ginuwa ne akan qira'ar da ake tsayawa ( Al-Waqf ), da wacce ake sadar da ita (Al-Wasl) cikin fadin Allah ta'alah.

وَمَا يَعْلَمُ تَأْوِيلَهُ إِلاَّ اللَّهُ

*[ **Kuma babu wanda yasan tawilinsa sai Alllah** ] (QA. Al-Imran : 7).*

- **Al-Mudlaqu:** Wanda babu wanda yasan shi sai Allah shi kadai, kamar kaifiyyar sifofin Allah ( yanayinsu ), da hakikanin abubuwan da suke cikin Aljannah.
- **An-Nisbiyyu:** Malamai Matabbata cikin ilimi sun san ma'anarsa, awajen wadansunsu kuma ayoyin suna kama da juna ( Ma'anoninsi bai fito fili ba ). Babu wani abu cikin alqur'ani wanda za ace babu wanda yasan ma'anarsa cikin mutane sedai a samu kuskuren fahimta, don hakane ma Abdullahi dan Abbas yace: (Ni ina cikin malamai matabbata cikin ilimi wadanda suka san fassaransa ), dan Abbas bai fadi hakan don alfahari ba, se don mutane su san cewa babu wani abu cikin littafin Allah wanda ba a san ma'anarsaba, domin bazai taba yiyuwa ace tun daga kan Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- har karshen wannan al'ummar ace ga wani abu cikin Alqur'ani da a a san ma'anarsaba, sannan kuma suna karanata ayoyin sifa kuma alhalin basa fahimtar ma'anoinsu.

***DALILI NA HUDU:***

وَلَـمَّا سَمِعَتْ قُرَيْشٌ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَذْكُرُ الرَّحْمَنَ أَنْكَرُوا ذَلِكَ، فَأَنْزَلَ اللهُ فِيهِمْ: ( وَهُمْ يَكْفُرُونَ بِالرَّحْمَنِ)

*Yayinda quraishawa sukaji Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ambaci Arrahman se sukayi inkarin hakan, se Allah Ya saukar da fadinsa: **[Suna kafirta da Mairahama].***

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Rashin imani da wani abu na Al-Asma'u was Sifat ( Ma'ana imani yana koruwa da wannan ).

2. Fassarar ayar Surah Ar-Ra'ad *…) **[Suna kafirta da Mairahama].** (QS. Ar-Ra'ad : 30).*

3. Barin labarta wa mutum abinda yafi karfin fahimtarsa. (wajibine mu karantar da mutane gwargwadon fahimtarsu ).

4. An ambaci illar hakan, domin yana kaiwa zuwa ga karyata Allah da Manzonsa, koda mai muzantawar bai ganganta hakan ba.

5. Maganar Ibnu Abbas dangane da wanda ya muzanta wani abu na sifofi, kuma inkarinsa ya halakar dashi.

## Jarabawar kashi na takwas (Babi 1)

**Tambaya ta farko:** sanya alamar: (☒) a wurin da dace ko ka cike gurbin da babu komai.

1. Muzanta sunayen Allah da sifofinsa ya kasu kashi (☐ biyu ☐ uku ). Banbanci tsakanin suna da sifa shine: Suna shine abinda Allah Ya kira kanSa dashi, Sifa kuma abinda Ya sifantu dashi (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ).
2. Inkarin Sunaan Allah ko sifarSa wadanda suka tabbata a cikin Alqur'ani da Sunnah kafirci ne ☐ Babba ☐ Karama.
3. الإسم An cirato suna ne daga Kalmar ☐ السمو da الإرتفاع (daukaka) ☐ السمة da العلامة (alama) ☐ Duka biyun.
4. Sunayen Allah Ta'ala ☐ Sunayene tsantsa ☐ sifofi ne kadai ☐ Sunaye ne da Sifofi.
5. Sunayen bayi ☐ Sunayene tsantsa ☐ sifofi ne ☐ Sunaye ne da Sifofi.
6. Dilalar suna ta hanyar ☐ Dacewa ☐ Kunsar dukkan ma'anar ☐ Lizimtawa ☐ Duka.
7. Sunayen Allah ☐ Abu guda ne ☐ Mabanbanta ne ☐ Abu guda ne kuma Mabanbanta.
8. Sunayen Allah -ta'ala- ☐ Sunada adadi kayyadadde ☐ Basuda adadi kayyadadde.
9. Sifofin Allah sunfi sunayenSa yawa, saboda kowani suna ya kunshi sifa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
10. Allah yanada wadansu sifofi masu yawa wadanda ba su daga cikin sunayenSa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
11. Kore misalta Allah da waninSa shi yafi dacewa samada kore kamantawa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
12. Sabubban karanta tauhidin Asma'u was Sifat:
1……………………………………………….2……………………………………………..
3……………………………………………….4……………………………………………..
5………………………………………………………………………………………………..
13. Hanyoyin karatun:
1……………………………………………….2……………………………………………..
3……………………………………………….4……………………………………………..
14. Ba a isar da wani hadisi ga wadanda yafi karfin fahimtar su tareda bukatuwarsu zuwa ga ilimin ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
15. Ma'anar fadin Allah: ***[ Suna kafirta da Mairahama ]*** *(QS. Ar-Ra'd : 30)*
…………………………………………………………………………………
16. Ayoyin siffofin Allah suna daga ayoyi (Muhkam) wadanda ma'anoninsu suke a fili, (Wannan ta fiskar sanin ma'anonin ), Sannan Mutashabih ne, wadanda babu wanda yasan ma'anoninsu sai Allah' (wannan kuma ta fiskar sanin kaifiyya) ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

17. Ma'anar Muhkam idan aka ambaceshi shi kadai ☐ Wanda ma'anarsa ta bayyana ☐ Wanda babu kuskure cikinsa.
18. Makna mutashabih idan aka ambaceshi shi kadai: Wanda sashensa yake kama da sashe wajen kyawunsa da kamalarsa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
19. At-Tashabuh An-Nisbiy Shine wanda ma'anarsa ya buya ga kowa, At-Tashabuh Al-Mudlaq kuma shine wanda sanin ma'anar ya buya ga kowa ☐ Haka ne ☐ Kuskure.
20. Babu wani abunda baza a iya sanin ma'anarsa ba a cikin Alqur'ani ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
21. Wajibi ne ga duk mai da'awa ya ringa dubi zuwa ga wadanda yake musu da'awar kuma ya sanya kowa a wajenda ya dace dashi. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
22. Cikin Alqurani babu wani abinda ma'anarsa ta buya ga dukkan mutane (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ). Amma gameda hakikanin abinda Allah Ya bada labari na lamurran gaibu to wannan ma'anarsa yana buya ga ☐ Wadansu mutane ☐ Dukkan mutane.
23. Meyasa Abdullahi dan Abbasa -Allah Ya kara yarda a gareshi- yace: ( Ni ina daga matabbata a cikin ilimi wadanda suka san tawilinsa )
………………………………...........................................................................................
24. Daga mafi sharrin maganganun yan bidia fadinsu cewa babu wanda yasan ma'anar ayoyin sifofin Allah, domin cikin wannan maganar akwai jahiltar da Manzon Allah Sallallahu Alaihi wasallam, da Sahabbansa, kuma akwai karyata alqur'ani……... . ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
25. Daga alamomin yan bidia: imani da ayoyin da ma'anoninsu ya fito fili karara, inkarin ayoyin da ma'anarsu bai fito filil ba ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
26. Daga kaidodin Tauhidin Asma'u was Sifat
1……………………………………………….2………………………………………………..
3………………………………………………………………………………………………

**Tambaya ta biyu:**

Sanya daga jerin (A) abinda zai dace dashi a jerin (B)

| No | (A) | (B) |
|---|---|---|
| 1 | Tahrifi | Shine inkari, yanda nau i biyu; Karyatawa ko Tawili. |
| 2 | Ta’wili | Ana fadansa da harshe, A rubuta da hannu, A kaddarashi da zuci. |
| 3 | Ta’adili | Sashensa yana kama da sashe, wajen kyawunsa da kamalarsa, kuma sashensa yana gasgata sashe. |
| 4 | Muhkam | Canza abinda wajibi ne tabbatar dashi wa Allah, da canza lafazinsa ko ma'anarsa. |
| 5 | Mutashabih | Inkarin abinda ya wajaba ga Allah na Sunayensa ko Sifofinsa, (gaba daya ko wani bangare ). |

| | | |
|---|---|---|
| 6 | Takyif | Wanda babu wani kuskure ckinsa, babu krya cikin labarinsa, kuma babu zalunci cikin hukuncinsa. |
| 7 | Juhudi (Muzantawa) | Wanda dalili yayi nuni a kansa to ingantacce ne kuma za a karbeshi, wanda bashi ba kuma to abin jefarwa ne. |

**Na tara: Lafuzzan da akayi hani akansu, da na Shirka (Babuka 26 )**

● Wannan shine kaso mafi tsayi na littafin; domin al'adan mawallafin yakan dunkule Magana a farko sannan kuma sai yayi bayani dalla dalla.
● Ya ambaci lafuzzan da aka hana yin amfani dasu, sa'annan sai ya bayyana lafuzzan shirka, da wadansu abubuwa na shirka, kuma yafi mayar da hakali akan karamar shirka, domin ita aba ce da take boye, sannan kuma ya mayar da hankali sosai wajen Magana akan kafirce wa ni'imar Allah, saboda abu ne da ya yawaita cikin mutane.

## [41] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

**يَعْرِفُونَ نِعْمَتَ اللّهِ ثُمَّ يُنكِرُونَهَا**

***( Suna sanin ni'imar Allah sa'annan kuma suna inkarinta…)*** **(QS. An-Nahl, 83).**

**( Kafirce wa ni'imar Allah shirka ce ).**

قَالَ مُجَاهِدٌ مَا مَعْنَاهُ: «هُوَ قَوْلُ الرَّجُلِ: هَذَا مَالِي وَرِثْتُهُ عَنْ آبَائِي»، وَقَالَ عَوْنُ بْنُ عَبْدِاللهِ: «يَقُولُونَ: لَوْلَا فُلَانٌ لَمْ يَكُنْ كَذَا»، وَقَالَ ابْنُ قُتَيْبَةَ: «يَقُولُونَ: هَذَا بِشَفَاعَةِ آلِهَتِنَا».

Mujahid yace: Ma'anarsa: (( shine fadin mutum: wannan dukiya ta ce da nagada daga ubannina )), Aunu dan Abdullahi yace: (( Ma'anarsa: fadinsu: ba domin wane ba, da abu kaza bai faru ba )), Ibnu qutaiba yace: ((suna cewa: mun samu wannan ne da ceton iyayen ginjinmu -albarkacinsu- )).

● Ni'ima jarabawa ce, dalili akan haka fadin Allah Ta'ala:

وَنَبْلُوكُم بِالشَّرِّ وَالْخَيْرِ فِتْنَةً

*[ **Kuma muna jarabtarku da sharri da alheri domin fitina** ]. (QS. Al-Anbiya: 35).*
● Jingina ni'imar mahalicci zuwaga waninsa kuskure ne cikin tauhidi:
1. **Tauhidin rububiyyah;** domin ya jingina ta ne zuwaga sababi a matsayin shi ya yi wannan niimar.
2. **Ibadah;** domin yaki gode wa Allah.
●. (( Fadinsu: ba domin wane ba, da abu kaza bai faru ba )): idan ya fada ne a matsayin bada labari kuma sai labarin yadace da yanayin to babu laifi.

**Niima jarabawace, tayaya zamu kubuta daga wannan jarabawar?**

**Kafin samuwar niimar:**
wajibine neman niima a wajen Allah, kuma zuciya ta rataya da Allah, wadansu mutanen tunaninsu shine ace ga wani minister ko wani shugaba ya sansu domin ya basu wata kyauta, to kamar yanda ba a neman Aljannah wajen kowa sai Allah hakanan arziki ma ba a rokon kowa sai Allah.

**Bayan samuwarta:**
Wajibine a gode wa Allah wanda yake bada niimar, da zuciya, da harshe, da gabbai.

**Kashe kashen mutane wajen jingina Niima:**

**Ya halatta:**
Idan ya jinginata zuwaga sababi na Shari'a ko wanda ya tabbatta a al'adance, ya halatta da sharuda biyu :

**Karamar Shirka:**
Ya jinginata zuwaga sababi na zahiri, amma Shari'a da al'ada basu tabbatar da wannan sababin ba.

**Babban Shirka:**
Idan sababin yazamo boyayye ne wanda bashi da wani tasiri a kansa kwata kwata.

Kar yayi kudirin cewar wannan sababin yanada tasiri da kansa.

Kar ya mance da godiyar wanda yake bayar da niimar.

***DALILI NA BIYU:***

وَقَالَ أَبُو الْعَبَّاسِ - بَعْدَ حَدِيثِ زَيْدِ بْنِ خَالِدٍ الَّذِي فِيهِ؛ أَنَّ اللهَ تَعَالَى قَالَ: «**أَصْبَحَ مِنْ عِبَادِي مُؤْمِنٌ بِي وَكَافِرٌ...**» الْحَدِيثَ؛ وَقَدْ تَقَدَّمَ -: «وَهَذَا كَثِيرٌ فِي الْكِتَابِ وَالسُّنَّةِ يَذُمُّ سُبْحَانَهُ مَنْ يُضِيفُ إِنْعَامَهُ إِلَى غَيْرِهِ، وَيُشْرِكُ بِهِ».

قَالَ بَعْضُ السَّلَفِ: «هُوَ كَقَوْلِهِمْ: كَانَتِ الرِّيحُ طَيِّبَةً، وَالْمَلَّاحُ حَاذِقًا، وَنَحْوِ ذَلِكَ مِمَّا هُوَ جَارٍ عَلَى أَلْسِنَةِ كَثِيرٍ».

**Abul Abbas** ya yi tsokaci a bayan hadisin Zaidu dan Khalid, wanda fadin Allah Ta'ala yazo ciki: " Wani bangare na bayina sun wayi gari suna masu imani da Ni, wadansu kuma sun kafirce mi Ni " Hadisin ya gabata-: ((Wannan yazo da yawa cikin Alqur'ani da Sunnah, Allahu Subhanahu Ya zargi masu tarashi da wani wajen jingina niimarsa ga waninsa )).

Wani daga cikin magabata yace: (( Shine: cewarsu: Iskar mai dadi ne, direban jirgin ruwan haziki ne, da makamantansu na abubuwan da suke gudana a harshensu )).

**_MAS'ALOLIN BABIN:_**

1. Bayanin mecece niima da yanda ake inkarinta ( ma'ana: mutane sun sani karara cewa dukkan niimomi daga Allah suke amma kuma suna inkarin hakan ta hanyar jingina su zuwaga wanin Allah.

2. Da yawan mutane suna fadan irin wadannan lafuzzan. (musamman yayin saukarsu daga jirgi ).

3. An kirayi irin wadannan lafuzzan da inkarin niimar Allah (inkarin cewa Allah ne Ya bayar da ita, ba inkarin samuwarta ba, domin mutane suna sane da niimar da samuwarta ).

4. Haduwar kishiyoyi biyu cikin zuciya daya. (Sanin niima, da inkarinta).

**[42] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:**

فَلاَ تَجْعَلُواْ لِلّهِ أَندَاداً وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ (٢٢)

***( Saboda haka Kar ku sanya wa Allah wasu kishiyoyi, Alhali kuwa kuna sane )* (QS. Al Baqarah, 22).**

( Ma'anar kishiya ).

● Kar ku sanya wa Allah kishiyoyi cikin bauta alhali kuna sane da cewa ba shida abokan tarayya cikin Rububiyyarsa, wannan ayar cikinta akwai umarni na farko da kira zuwaga tauhidin, kuma itace ayar farko a cikin qur'ani da take hani kan shirka.

قَالَ ابْنُ عَبَّاسٍ فِي الآيَةِ: (الأَنْدَادُ؛ هُوَ الشِّرْكُ أَخْفَى مِنْ دَبِيبِ النَّمْلِ عَلَى صَفَاةٍ سَوْدَاءَ فِي ظُلْمَةِ اللَّيْلِ، وَهُوَ أَنْ تَقُولَ: وَاللهِ وَحَيَاتِكِ يَا فُلاَنَةُ، وَحَيَاتِي، وَتَقُولَ: لَوْلَا كُلَيْبَةُ هَذَا لأَتَانَا اللُّصُوصُ، وَلَوْلَا الْبَطُّ فِي الدَّارِ لأَتَى اللُّصُوصُ، وَقَوْلُ الرَّجُلِ لِصَاحِبِهِ: مَا شَاءَ اللهُ وَشِئْتَ، وَقَوْلُ الرَّجُلِ: لَوْلَا اللهُ وَفُلاَنٌ، لَا تَجْعَلْ فِيهَا فُلاَنًا، هَذَا كُلُّهُ بِهِ شِرْكٌ)، رَوَاهُ ابْنُ أَبِي حَاتِمٍ.

Abdullahi dan Abbas yace dangane da wannan ayar: (**Al-Andad: -kishiyoyi-** shirka ce, tafi tsananin buya sama da sawun tururuwa, bisa kamfan dutse baki, a duhun dare, shine kamar kace: ina rantsuwa da Allah, na rantse da rayuwarki ya wance, na rantsuwa da rayuwata, da fadinka: ba dmin wannan yar karyarba da barayi sunzo mana, ba domin agwagwan dake gidanba da barayi sun shiga, da fadin mutum wa abokinsa: Allah Yaso kaima kaso, da fadin wani: ba don Allah da wane ba, don haka kar ka sanya wa Allah abokin tarayya cikin lamurran, wannan dukkansa shirka ne ). ( Ibnu Abi Hatim ne ya rawaito ).

● **"Yafi buya samada..."** : kaiwa makura wajen buya, to idan har shirka a cikin zukatan bani Adam tafi buya daga abinda aka ambata; to babu abinda ya saura face mu roki Allah Ya taimakemu wajen kubuta daga aukawa cikin shirka..

***DALILI NA BIYU:***

وَعَنْ عُمَرَ بْنِ الْـخَطَّابِ ﭬ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «مَنْ حَلَفَ بِغَيْرِ اللهِ **فَقَدْ كَفَرَ أَوْ أَشْرَكَ**». رَوَاهُ التِّرْمِذِيُّ وَحَسَّنَهُ، وَصَحَّحَهُ الْـحَاكِمُ.

Daga Umar bn Khaddab -Allah Ya kara yarda a gareshi- Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: " Duk wanda ya rantse da wanin Allah, to hakika ya kafirta ko kuma yayi shirka ". ( Tirmizi ne ya rawaito hadisin kuma ya kyautata shi, Hakim ya inganta hadisin ).

***DALILI NA UKU:***

وَقَالَ ابْنُ مَسْعُودٍ: (لَأَنْ أَحْلِفَ بِاللهِ كَاذِبًا؛ أَحَبُّ إِلَيَّ مِنْ أَنْ أَحْلِفَ بِغَيْرِهِ صَادِقًا).

Ibn Mas ud yace: ( Na ratse da Allah a kan karya yafi soyuwa a gare ni sama da in rantse da wanin Allah akan gaskiya ).

● **"Ya kafirta ko yayi shirka"**: Babba idan ya kudurce cewa wanda aka raantse dashi din daidai yake da Allah a babin girmamawa da matsayi, amma idan bai kudurce haka ba to karamin kafirci ne ko karamar shirka.

● Ibnu Mas ud -Allah Ya kara yarda a gareshi- bayason duka biyun -nau uka biyu na rantsuwar- sedai abin nufi shine: girmar laifin shirka da muninta yafi tsanani sama da munin karya, domin shirka ba a gafarta ta.

***DALILI NA HUDU:***

وَعَنْ حُذَيْفَةَ ﭬ عَنِ النَّبِيِّ ﷺ قَالَ: «لَا تَقُولُوا: مَا شَاءَ اللهُ وَشَاءَ فُلَانٌ، وَلَكِنْ قُولُوا: مَا شَاءَ اللهُ ثُمَّ شَاءَ فُلَانٌ»، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ بِسَنَدٍ صَحِيحٍ.

Daga Huzaifa Allah -Ya kara yarda a gareshi- daga Annanbi -Sallallahu alaihi wasallam- yace: " Kar kuce: Allah Yaso, wane ma yaso, sedai, abinda za kuce shine: Allah Yaso, sa'annan wane ma ya so ". ( Abu Dawud ne ya rawaito da sanadi mai inganci ).

***DALILI NA BIYAR:***

وَجَاءَ عَنْ إِبْرَاهِيمَ النَّخَعِيِّ أَنَّهُ يَكْرَهُ أَنْ يَقُولَ الرَّجُلُ: (أَعُوذُ بِاللهِ وَبِكَ)، وَيَجُوزُ أَنْ يَقُولَ: (بِاللهِ ثُمَّ بِكَ)، قَالَ: وَيَقُولُ: (لَوْلَا اللهُ ثُمَّ فُلَانٌ)، وَلَا تَقُولُوا: (لَوْلَا اللهُ وَفُلَانٌ).

Ibrahimun Nakha'i baya son mutum yace: (Ina neman tsari da Allah, da kai ), Amma babu laifi yace: (Ina neman tsari da Allah sannan da kai ), yace: sannan babu laifi yace: (Ba don Allah ba, sannan wane ), kar kuce: (Ba don Allah da wane ba ).

● " **Sedai kuce** ": Idan shari'a ta rufe wata kofa ta haramun, sai ta bude wata kofar ta halacci, -Misali: Shari'a da haramta zina sai ta halatta aure, ta haramta riba sai ta halatta kasuwanci- domin kaurace wa haramun din yayi sauki ga mutane, sannan kuma a gane sauki da rangwami na wannan Shari'a.

## *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Tafsirin ayar Suratul Baqarah dangane da (الأنداد) **kishiyoyi.**

2. Sahabban Annabi -Allah Ya kara yarda a gare su- suna kafa hujjah da ayar da sauka a kan babban shirka, kan karamar shirka. ( domin kishiya tana iya daukar )..........................................ko cikin wasu lamurran.

3. Rantsuwa da wanin Allah shirka ce. ( Kamar fadinsu: Na rantse da rayuwarka, da rayuwata, da alkawarinka, da alkawarina, cikin alkawarina, da alkawarina, cikin wuyata, cikin gemuna, cikin fiskata, da Annabi, da matsayina, da ka'aba, da sallarka, da azuminka, da da rayurka, da taimako, ko kuma yace cikin rantsuwarsa: idan har ya aikata abu kaza, to shi bayahude ne, ko banasare, ko kafiri ).

4. Idan ya rantse da wanin Allah kan gaskiya, to laifinsa yafi girma samada rantsuwar da take nitsarwa cikin wuta. (Itace rantsuwar da zaiyi da Allah a kan karya domin ya karbi dukiyar musulmi da ita ).

5. Banbancin harafin: (و) da (ثم) wajen magana. ( Saboda harafin (و) " **Wawun** " tana hukunta tarayya ne, sabanin harafin " **Summa**" ( ثمَّ ) tana hukumta jerantuwar abubuwa tareda jinkiri, kamar fadinsu: ni da Allah, da kai nake neman taimako, Allah da kai kun isar mini, bani da kowa sai Allah da kai, na dogara ga Allah da kai, wannan daga Allah da kai ne, inada Allah a sama inada kai a kasa, ina tuba zuwaga Allah da gareka ).

## [43] BABIN ABINDA YA ZO NA HUKUNCIN WANDA BAI GAMSU BA DA RANTSUWA DA ALLAH

( Yana daga manyan laifuka **Al-Kaba'ir** )

● Mai rantsuwa ya karfafi rantsuwarsa da gimama Allah wanda ya yi rantsuwar dashi, cikin rashin gamsuwa yayin da akayi rantsuwa da Allah akwai tauye wani abu na girmar Allah, wannan yana kore kamlar tauhidi.

**DALILI NA FARKO:**

عَنِ ابْنِ عُمَرَ ؓ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**لَا تَحْلِفُوا بِآبَائِكُمْ، مَنْ حَلَفَ بِاللهِ فَلْيَصْدُقْ، وَمَنْ حُلِفَ لَهُ بِاللهِ فَلْيَرْضَ، وَمَنْ لَمْ يَرْضَ فَلَيْسَ مِنَ اللهِ**»، رَوَاهُ ابْنُ مَاجَه بِسَنَدٍ حَسَنٍ.

Daga Ibn Umar -Allah Ya kara yarda a garesu- Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yace: " kar ku rantse da Ubanninku, duk wanda zai rantse da Allah to yayi gaskiya, kuma duk wanda akayi masa rantsuwa da Allah to ya yarda, duk wanda bai yarda ba, to baya tare da Allah " ( Ibnu Majah ne ya rawaito da isnadi mai kyau ).

**Kashe kashen gamsuwa yayin rantsuwa da Allah**

**A Shari'ance:** Wajibi ne a yarda idan akayi rantsuwa da Allah, yayinda aka bukaci wanda akayi kararsa da ya rantse, sai ya rantse, bisa wajibin hukuncin Shari'a.

**A baiyane:** Wanda akayi masa rantsuwar baya fita daga dayan halaye biyar:

1. Yasan mai rantsuwar karya yake yi, to bazai gasgata shi ba.
2. Karyarsa tafi rinjaye, ba wajibi ba ne ya gasgatashi.
3. Daidaituwar zato tsakanin gaskiyarsa da karyar, wajibi a gasgata shi.
4. Gaskiyarsa tafi rinjaye, gasgata shi wajibi ne.
5. Yasan gaskiyarsa, wajibi ne ya gasgata shi.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Anyi hani kan rantsuwa da Ubanni. ( Hani ne na haramci ).

2. An umarci wanda akayi masa rantsuwa da Allah da ya yarda.

3. Narkon wanda bai yarda ba.

4. An umarci duk wanda zaiyi rantsuwa da yayi gaskiya, domin yin gaskiya wajibi ne cikin abinda ba gaskiya ba, to yaya ga rantsuwar kuma!).

## [44] BABIN CEWA: (ABINDA ALLAH YA SO KAIMA KASO

### DALILI NA FARKO:

عَنْ قُتَيْلَةَ ۞: أَنَّ يَهُودِيًّا أَتَى النَّبِيَّ ﷺ فَقَالَ: إِنَّكُمْ تُشْرِكُونَ، تَقُولُونَ: مَا شَاءَ اللهُ وَشِئْتَ، وَتَقُولُونَ: وَالْكَعْبَةِ، فَأَمَرَهُمُ النَّبِيُّ ﷺ إِذَا أَرَادُوا أَنْ يَحْلِفُوا أَنْ يَقُولُوا: وَرَبِّ الْكَعْبَةِ، وَأَنْ يَقُولُوا: مَا شَاءَ اللهُ ثُمَّ شِئْتَ، رَوَاهُ النَّسَائِيُّ وَصَحَّحَهُ.

Daga Qutailah: ( Wani bayahude ya zo ga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- sai yace: Lallai ku kuna yin shirka, kuna cewa: Allah Ya so, kaima kaso, sannan kuma kuna cewa: na rantse da Kaa'aba, sai Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya umarce su idan zasuyi rantsuwa suce: na rantse da Ubangijin Ka'aba, sannan suce: Allah Yaso, sannan kaima ka so ). ( An- Nasa'i ne ya rawaito kuma ya inganta shi ).

### DALILI NA BIYU:

وَلَهُ أَيْضًا عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ؛ أَنَّ رَجُلًا قَالَ لِلنَّبِيِّ ﷺ: مَا شَاءَ اللهُ وَشِئْتَ، فَقَالَ: «**أَجَعَلْتَنِي لِلهِ نِدًّا؟! مَا شَاءَ اللهُ وَحْدَهُ**».

Daga Imamun Nasa'i, daga Ibnu Abbas: " wani mutum ya ce wa Annabi Sallallahu alaihi wasallam: Allah Ya so kaima ka so, sai ya ce: " Shin ka sanya ni kishiya ga Allah?! Allah Ya so, shi kadai ".

- **Me yasa aka kirayi yahudu da wannan sunan?**

1. Saboda fadinsu: (هدنا إليك) Mun koma zuwa gareka.
2. Saboda sunan kakansu Yahuza dan Ya'qub Sallallahu Alaihi wasallam.

- **Hadisin farko akwai wasu fa'idodi cikinsa daga ciki:**

1. Manzon Allah -Sallallahu Alaihi wasallam- bai muzanta ma bayahuden ba saboda abind ya fada gaskiya ne, tareda cewa manufarsa shine zargin musulmai.
2. Wajibi ne komawa zuwaga gaskiya koda kuwa wanda ya fadakar a kan gaskiyar baya daga cikin masu gaskiya.
3. Yakamata idan za a canza wani abu, a canza shi da wanda yake kusa dashi.

- **Me yasa babu wanda ya fadaka da wannan kuskuren sai wannan bayahuden?** Hikimar itace: jarabtar yahudawan da suka ci gyaran musulmai tare da cewar su sunayin shirka da Allah ( Babban shirka ), amma su ba sa ganin aibinsu.

● " **Allah shi kadai Ya so** ": Manzon Allah -Sallallahu Alaihi wa sallam- ya shiryar dashi zuwaga abinda zai nusanta shi daga shirka, bai umarce shi ba da yace: " Allah Ya so, sannan ka so ", don ya yanke masa dukkan wata hanyar da zata iya kaishi zuwaga shirka komai nisanta, domin tsare shingen tauhidi, da ladabi ga Allahu -Subhanahu wa ta'ala-.

**DALILI NA UKU:**

**وَلاِبْنِ مَاجَه، عَنِ الطُّفَيْلِ -أَخِي عَائِشَةَ لِأُمِّهَا- قَالَ: رَأَيْتُ كَأَنِّي أَتَيْتُ عَلَى نَفَرٍ مِنَ الْيَهُودِ، قُلْتُ: إِنَّكُمْ لَأَنْتُمُ الْقَوْمُ لَوْلَا أَنَّكُمْ تَقُولُونَ: عُزَيْرٌ ابْنُ اللهِ، قَالُوا: وَإِنَّكُمْ لَأَنْتُمُ الْقَوْمُ لَوْلَا أَنَّكُمْ تَقُولُونَ: مَا شَاءَ اللهُ وَشَاءَ مُحَمَّدٌ، ثُمَّ مَرَرْتُ بِنَفَرٍ مِنَ النَّصَارَى، فَقُلْتُ: إِنَّكُمْ لَأَنْتُمُ الْقَوْمُ لَوْلَا أَنَّكُمْ تَقُولُونَ: الْـمَسِيحُ ابْنُ اللهِ، قَالُوا: وَإِنَّكُمْ لَأَنْتُمُ الْقَوْمُ لَوْلَا أَنَّكُمْ تَقُولُونَ: مَا شَاءَ اللهُ وَشَاءَ مُحَمَّدٌ، فَلَمَّا أَصْبَحْتُ أَخْبَرْتُ بِهَا مَنْ أَخْبَرْتُ، ثُمَّ أَتَيْتُ النَّبِيَّ ﷺ فَأَخْبَرْتُهُ، فَقَالَ: «هَلْ أَخْبَرْتَ بِهَا أَحَدًا؟»، قُلْتُ: نَعَمْ، قَالَ: فَحَمِدَ اللهَ وَأَثْنَى عَلَيْهِ، ثُمَّ قَالَ: «أَمَّا بَعْدُ؛ فَإِنَّ طُفَيْلًا رَأَى رُؤْيَا أَخْبَرَ بِهَا مَنْ أَخْبَرَ مِنْكُمْ، وَإِنَّكُمْ قُلْتُمْ كَلِمَةً كَانَ يَمْنَعُنِي كَذَا وَكَذَا أَنْ أَنْهَاكُمْ عَنْهَا، فَلَا تَقُولُوا: مَا شَاءَ اللهُ وَشَاءَ مُحَمَّدٌ، وَلَكِنْ قُولُوا: مَا شَاءَ اللهُ وَحْدَهُ».**

Daga Ibn Majah, daga Dufail, -Dan uwan Aishah ta wajen mahaifiyarta- ya ce: na ganni kamar na zo ga wadansu mutane daga yahudawa, sai nace musu: lallai ku in ba domin kuna cewa: Uaziru dan Allah ba ne, sai suma suka ce: lallai kuma mutanen … in ba domin kuna cewa: Allah Ya so, Muhammadu ma ya so, Sannan sai wuce wadansu jama'a daga Nasara, sai nace musu: ku mutane ne in ba don kuna cewa: Isah dan Allah bane, sai sukace: lallai kuma fa ba domin kuna cewa: : Allah Ya so, Muhammadu ma ya so , yayin da na wayi gari sai na bada labari ma wadanda na ba su labari, sa'annan na tafo wajen Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- sai na labarta masa, sai ya ce: "Shin ka labarta ma wani ne ?" sai nace: Na'am, sai ya gode wa Allah kuma ya yabe Shi, sannan ya ce: "Bayan haka, hakika Dufailu yayi mafarki, kuma ya labarta ma wadanda ya labarta wa, kuma hakika kuna fadin wata Maganar da kaza da kaza ne suka hana ni na hane ku daga wannan maganar, don haka kar kuce: Allah ya so, Muhammadu ma ya so, amma da kuce: Allah Ya so, Shi kadai ".

● " **Abu kaza da kaza ne suka hane ni** ": Kunya ce ta hana Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya hane su, ba kunyar inkarin abu mara kyau ba, yana kunyar yin hani akai ne ba tare da wani umarni daga Allah a kan hakan ba, kamar giya yayi shiru baice kamai akai ba se da aka haramta ta.

**Nau ukan Mafarkayya**

| Garwayayyen Mafarki. | Mafarki na hakika. | Zancen zuci. |
|---|---|---|

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Yahudawa sun san karamar Shirka.

2. Mutum yakan fahimci cewar yana kan san zuciya.

3. Fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-: “Kasanya ni kishiya ga Allah?! " to kuma yaya ga wanada yace

"يا أكرم الخلق ما لي ألوذ به سواك ..."

“Ya mafi girman halitta, bani da wanda zan fake dashi koma bayanka… ) da baituka guda biyu da suka biyo bayan wannan. (wannan kaiwa matuka ne bijirewa da zurfafawa ).

4. Wannan maganar ba babbar shirka ba ce, saboda fadinsa: " **Abu kaza da kaza ne suka hane ni** ”.

5. Mafarki na gaskiya yanki ne na wahayi.

6. Kuma yana iya zamowa sababi na Shar'anta wadansu hukunce hukuncen. (A zamanin Annabta).

## [45] BABIN WANDA YA ZAGI ZAMANI TO HAKIKA YA CUTAR DA ALLAH

● **" Hakika ya cutar da Allah"**: cutarwa ba ta lizimta cutuwa, mutum yakan iya cutuwa sakamakon jin mummunan abu, sedai qila hakan bazai iya cutar dashi ba, shiyasa Allah Ya tabbatar da cutarwa a cikin Alqur ani, amma ya kore wani wani abu ya cutar dashi.

**Kashe kashen zagin zamani:**

**Babban shirka:** Kamar ya zagi zamani yana mai imani da cewa zamani shi yake gudanar da abubuwa, shi yakae jujjuya abubuwa zuwa alheri da sharri.

**Haramun:** Ya zagi zamani ba tare da imani da cewa yana aikata wani abu ba, yayi imani da cewa Allah shine yake gudanar da komai da kowa, yana zaginsa ne kadai saboda samuwar abubuwan da yake ki cikin wannan zamanin.

**Halal:** Manufarsa itace tsantsar labartawa ba tareda zargi ba, kamar fadinsa: zafin wannan yinin ya wahalar da mu, kamar fadin Allah ta'ala: [Wannan yini ne mai wahala ] *(QS. Huud : 77).*

**DALILI NA FARKO:**

وَقَالُوا مَا هِيَ إِلَّا حَيَاتُنَا الدُّنْيَا نَمُوتُ وَنَحْيَا وَمَا يُهْلِكُنَا إِلَّا الدَّهْرُ

*{Kuma suka ce babu komai face rayuwarmu ta duniya muna mutuwa, kuma muna rayuwa, kuma babu abinda ke halaka mu face zamani }. (QS. Al-Jathiyah : 24).*

**DALILI NA BIYU:**

فِي الصَّحِيحِ عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ، عَنِ النَّبِيِّ ﷺ قَالَ: «قَالَ اللهُ تَعَالَى: يُؤْذِينِي ابْنُ آدَمَ، يَسُبُّ الدَّهْرَ، وَأَنَا الدَّهْرُ: أُقَلِّبُ اللَّيْلَ وَالنَّهَارَ»، وَفِي رِوَايَةٍ: «لَا تَسُبُّوا الدَّهْرَ؛ فَإِنَّ اللهَ هُوَ الدَّهْرُ».

Yazo cikin sahihul Bukhari daga Abu Huraira daga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- yace: " Allah ta'ala Ya ce: dan Adam yana cutar da ni, yana zagin zamani, alhali nine zamanin, Ni Nake jujjuya dare da rana" ya tabbata cikin wata riwayar: " Kar ku zagi zamani, domin Allah shine zamani ".

● *“ Rayuwarmu ta dunya” :* Ma'ana: bakomai bane zamani face samuwa da rayuwar halittu, babu wata rayuwar lahira.

● *“ Zamani ne ke halakar da mu ”:* Mutuwarmu bata zamo da umurnin Allah ko kaddarawarsa ba, iyaka, tsawon shekaru ne ga mai nisan kwana, rashin lafiya, da bakin cikin, da kuncin rayuwa ga wanda lokacinsa bashi da tsayi, zamani shi ke kashe su.

● **“ Dan Adam yana cutar da ni ” :** Ma'ana: yana riskar da cutarwa a gare Ni, wannan Sifa ta cutarwa tabbatacciya ce ga Allah, wajibine mu tabbatar da ita, domin Allah Ya tabbatar da ita wa kansa, Alllah Yafi mu sanin kansa -Da abinda ya dace dashi na sifofi- sedai sifar cutarwa ga Allah ba irin cutarwar sauran halittu ba ne.

● **“ Yana zagin zamani ”:** Ma'ana: yana zaginsa tareda munana shi, yana zarginsa, kuma yana tsine masa, **Addaharu**: shine zamani da lokaci.

● **“ Kuma nine zamani ”:** Abin nufi: wanda yake juya zamani, yake bashi umarni, kamar guguwa da wasunta.

**Shin " Addahar " ( zamani ) yana cikin sunayen Allah?**

Addaharu ba ya daga cikin sunayen Allah -Maigirma da buwaya- saboda:

1. Siyakin Ayar yana hana zamowarsa cikin sunayen Allah, da yana daga sunayen Allah da kudirin mutanen Jahiliyyah ya inganta.

2. Siyakin Hadisin shima yana mayar dashi.

3. Duk wanda ya sanya ( Addahar ) zamani shine ( Allah ), to hakika ya sanya halitta a matsayin Mahalicci.

4. Sunayen Allah dukkaninsu sun kai makura wajen kamala da kyau, kuma duka sunada ma'anoni, amma zamani ba ya sifantuwa da kyau ( A zatinsa ).

5. Sunayen Allah dukkaninsu suna kunshe ne da Sifofi, Addaharu kuma suna ne sandararre.

6. Hani yazo kan zagin dabba, da iska, da mashash, shara.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Anyi hani kan zagin zamani, (Kamar fadins: Ya tabewar zamanin, zamani mai muni, zamani mai yawan karya alkawari ”.

2. An kira hakan cutarwa ne ga Allah.

3. Abun lura cikin fadin Allah: " Lallai ne Allah Shine: Addahar -zamani- ". (Abin nufi wanda yake juya zamani kuma yake sarrafa shi).

4. Mutum zai iya zamowa mai zagi koda baiyi niyyar zagin da zuciyrsa ba.

5. Tafsirin Ayar surat Al-Jathiyah, {*Babu abinda yake halaka mu face zamani …*} *(QS. Al-Jathiyah : 24).*

## [46] BABIN KIRAN WANI: ALKALIN ALKALAI DA MAKAMACINSA (AN HANA ).

● Ma'ana: mutum ya sanya wa kanshi wannan sunan, ko kuma wani ya kira shi dashi sai ya yarda da hakan.

**Menene hukuncin kiran wani da alkalin alkalai?**

1. **Babban laifi ne**: idan manufar ta zamo sanya sunan ne kadai.

2. **Babban shirka:** idan yayi imani da cewa yafi kowa iya hukumci, har Allah, maigirma da buwaya.

3. **Halal ne:** amma barinsa shine yafi, idan aka iyakance shi da wadansu mutane, ko wani gari ko zamani.

### DALILI NA FARKO:

في الصَّحِيحِ عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ڤ، عَنِ النَّبِيِّ  قَالَ: «**إِنَّ أَخْنَعَ اسْمٍ عِنْدَ اللهِ: رَجُلٌ تَسَمَّى مَلِكَ الأَمْلاكِ**، لَا مَالِكَ إِلَّا اللهُ»، قَالَ سُفْيَانُ: مِثْلُ شَاهَانْ شَاهْ، وَفِي رِوَايَةٍ: «**أَغْيَظُ رَجُلٍ عَلَى اللهِ يَوْمَ الْقِيَامَةِ وَأَخْبَثُهُ**»، قَوْلُهُ: «أَخْنَعُ» يَعْنِي أَوْضَعُ.

Hadisi ya inganta daga Abu Hurairah Allah Ya kara yarda a gareshi, daga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " **Mafi wulakantar suna a wajen Allah: Mutumin da ake kiransa sarkin sarakuna, babu Sarki sai Allah** ", Sufyanu ya ce: (makamancinsa shine: Shahan Shah, cikin wata riwayar: " **Sunan da yafi fusata Allah, kuma mafi muni a wajansa ranar Kiyama** ". **(أخنع) (أوضع):** Mafi wulakanta.

● **أَخْنَعُ :** Anyi masa ukuba da akasin manufarsa, misalinsa shine duk wani sunan da yake nuni akan girman kai, da isa, da girma.

● **أَغْيَظُ:** Cikin wannan akwai tabbatar da sifar tsananin fushi ga Allah kamar yanda ya dace da zatinsa .

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Anyi hani kan mutum ya kira kansa, ko a kira shi: (Sarkin sarakuna).

2. Duk sunan da yake dauke da ma'anarsa to hukuncinsu daya, kamar yanda Sufyanu yace: ( Kamar: alkalin alkalai, Gwamnan gwamnoni, Sarkin sarakuna ).

3. Fadakuwa wajen kausasawa dangane da wannan sunan da makamantansa, tare da cewa zuciya bata nufin hakikanin ma'anarsa.

4. Fadakuwa kan cewa wannan hanin saboda girmama hakkin Allah ne.

## [47] BABIN GIRMAMA SUNAYEN ALLAH, DA CANZA SUNA SABODA HAKA

### Kashe Kashen Sunayen Allah

***Kebantattu*:** Sune sunayen da bai halatta a kira wani da su ba sai Allah shi kadai, idan aka sanya ma wani daya daga wadannan sunaye to wajibi ne a canza su, Misalin wadannan sunaye: **Allahu, Arrahmanu, Rabbul alamina**, da makamantansu.

***Wadanda ba kebantattu ba*:** wadanda ya halatta a kira wanin Allah da su, kamar: **Ar-Rahimu, da As-Sami'u, da Al-Basiru,** sedai idan aka hararo sifa da wannan sunar to bai halatta ba, amma idan ba a hararo sifa ba, to ya halatta a matsayin sunan yanka tsantsa.

***DALILI NA FARKO:***

عَنْ أَبِي شُرَيْحٍ: أَنَّهُ كَانَ يُكْنَى أَبَا الْـحَكَمِ، فَقَالَ لَهُ النَّبِيُّ ﷺ: «**إِنَّ اللهَ هُوَ الْـحَكَمُ، وَإِلَيْهِ الْـحُكْمُ**»، فَقَالَ: إِنَّ قَوْمِي إِذَا اخْتَلَفُوا فِي شَيْءٍ أَتَوْنِي فَحَكَمْتُ بَيْنَهُمْ، فَرَضِيَ كِلَا الْفَرِيقَيْنِ، فَقَالَ: «**مَا أَحْسَنَ هَذَا، فَمَا لَكَ مِنَ الْوَلَدِ؟**»، قُلْتُ: شُرَيْحٌ، وَمُسْلِمٌ، وَعَبْدُ اللهِ، قَالَ: «**فَمَنْ أَكْبَرُهُمْ؟**»، قُلْتُ: شُرَيْحٌ، قَالَ: «**فَأَنْتَ أَبُو شُرَيْحٍ**»، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ وَغَيْرُهُ.

Daga Abu Shuraih: ya kasance anayi masa alkunya da Abal Hakam, sai Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce masa, " Lallai Allah shine: Al-Hakam, kuma zuwa gareshi kadai hukumci yake ", sai yace: mutanena sun kasance idan suka samu sabani a tsakaninsu sukan tafo gareni sai nayi hukunci a tsakaninsu, sai dukkan bangarori biyun su yarda da hukuncin, sai Annabi ya ce: " Wannan abu ne mai matukar kyau da bankaye, me kake dashi na yara? ", sai nace: Ssuraihun, da Muslim, da Abdullahi, sai ya ce: " Wanene babbansu ? ", nace: Shuraihun, sai ya ce: " To kai Abu Shuraihin ne ". ( Abu Dawud ne da waninsa suka rawaito.)

**ALKUNYA:** Itace sunan da ta fara da: ( Baba), ko (Mama), ko (Dan uwa), ko (Baffah) ko ( Kawu), Misali: Baban wane, Maman wane, Baffan wane, wannan sunan da ake kiran wannan mutumin dashi an nufi ma'anar sifa a cikinta, wato: Alhakam, hakan se ya dace da sunan Allah, bai zamo suna tsantsa ba, sunace wanda ta ke kunshe da ma'anar sifa, da hakan sai yayi tarayya da Allah cikin hakan, saboda hakane ma Manzon Allah -Sallallahu Alaihi wasallam- ya yi masa alkunya

da abinda ya dace dashi na Alkunyar, Manzon Allah -Sallallahu Alaihi wasallam- bai umurce shi da yasake yanka abin suna ba.

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Wajibi ne a girmama Siffofin Allah da Sunayensa koda baa yin nufin wannan ma,anarba ( Ma'ana: sunayen da Allah Ya kebanta da su, ko wanda aka hararo sifa ).

2. Shar'ancin canza suna saboda haka ( Hakanan sunar da ke dauke da ma'anar da bata dace ba ).

3. Akan zabi sunan yaro na farko wajen alkunya ( Alkunya halal ne, ba a alkunya da mushiriki ).

## [48] BABIN WANDA YAYI IZGILI DA WANI ABU NA AMBATON ALLAH, KO ALQUR'ANI KO MANZON ALLAH ( SAW )

● Duk wanda yayi wargi ko izgili da Allah ko ayoyinsa, ta Kauniyya ko Shari'a, ko Manzanninsa, ya kafirta babban kafirci -wanda yake fitar da mutum daga musulunci- domin izgii yana kore imani korewa maigirma, kafurci ya kasu kashi biyu:

***Kafurci na fito na fito***: wannan nau in shine mafi girma kuma mafi tsanani, kamar kafurcin Abu Jahl da Abu Dalib.

***Kafurci na juya baya***: Ya juwa baya wa addinin Allah, bawai ta hanyar yakan addinin ba.

● Mai izgili kafiri ne kafirci na fito na fito; laifinsa yafi girma samada maisujjada ga gunki, wannan mas'alace mai hadarin gaske, dayawa wata Kalmar takan iya jefa mutum cikin bala'i da halaka ta yanda shi bai saniba, mutum yana iya Magana da wata Kalmar da zata fusata Allah wanda shi bai dauketa a bakin komaiba, zai fada tsundum cikin wuta saboda ita.

Duk wanda yayi izgili da Sallah -koda nafila ce- ko Zakkah ko Azumi, ko Hajji, to wannan ya kafirta, da ima'in musulmai, hakanan duk wanda yayi izgili da ayoyin Allah na Kauniyya ( Halitta ), kamar yace: samuwar zafi a lokacin sanyi wauta ne, ko yace: samuwar sanyi a lokacin zafi wauta neto wannan kafirci ne irin wanda yake fitar da mutum daga musulunci, domin duk Aiyukan Allahu -Subhanahu wa ta'ala- an gina su bisa hikima, wanda ba lallai ne mu riski wannan hikimar ba.

● Malamai sunyi sabani dangane da wanda ya zagi Allah, ko Manzonsa, ko littafinsa, shin za a karbi tubarsa ko baza a karba ba? Malamai sun kasu kashi biyu kan wannan mas'alar:

**Ba za a karbi tubarsa ba, ya zamo wajibi a kan Shugaba ya kasheshi:**

Sannan baza a yi masa sallah ba, kuma ba za a roka masa Rahamar Allah ba, kuma za a nesanta shi daga makabartun musulmai, ko da ya bayyana tuba, domin wannan ridda ce, lamarinta yanada girma, kuma babban laifi ne, da tuba ba zai hana a kashe shi ba.

**Ana karbar tubarsa da sharudda:**

1. A san gaskiyar tubarsa.
2. Ya yabi Allah.
3. Ya barranta daga abinda ya fada.

Wanda ya zagi Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ana karbar tubarsa ammam wajibi ne a kan shugaba ya kasheshi, saboda hakkin Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- idan aka kasheshi zamuyi masa wanka, da lifafa, sannan muyi msa sallah, a bisine shi tareda musulmai.

**DALILI NA FARKO:**

وَلَئِن سَأَلْتَهُمْ لَيَقُولُنَّ إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلْعَبُ قُلْ أَبِاللّهِ وَآيَاتِهِ وَرَسُولِهِ كُنتُمْ تَسْتَهْزِئُونَ

***[ Kuma lallai ne Idan ka tambayesu hakika zasuce abin sani kawai mun kasance muna hira ce da wasa, kace shin da Allah, da kuma AyoyiSa, da ManzonSa kuka kasance kuke izgili****?]. (QS. At-Taubah: 65).*

**DALILI NA BIYU:**

عن ابنِ عُمَرَ، ومحمَّدِ بنِ كَعْبٍ، وزيدِ بنِ أسلمَ، وقَتادةَ - دَخَلَ حَدِيثُ بَعْضِهِم في بَعْضٍ-؛ أنَّهُ قالَ رجُلٌ في غَزْوَةِ تَبوك: مَا رَأَيْنا مِثْلَ قُرَّائِنا هَؤلاءِ أرغَبَ بُطونًا، ولا أَكْذَبَ ألَسُنًا، ولا أجْبَنَ عندَ اللِّقاءِ - يَعني الرَّسُولَ ﷺ وأَصْحَابَهُ القُرَّاءَ -، فقالَ له عَوْفُ بنُ مالكٍ: كَذَبْتَ؛ ولَكِنَّكَ مُنَافِقٌ، لأُخْبِرَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ، فَذَهبَ عوْفٌ إلى رَسُولِ اللهِ ﷺ لِيُخْبِرَهُ، فَوجَدَ القُرْآنَ قَدْ سَبَقَهُ، فَجَاءَ ذَلَكَ الرَّجُلُ إلى رَسُولِ اللهِ ﷺ وَقَدْ ارْتَحَلَ، وَرَكِبَ ناقَتَهُ، فقالَ: يا رَسُولَ اللهِ! إنَّما كُنَّا نَخُوضُ ونَلْعَبُ ونَتَحَدَّثُ حَدِيثَ الرَّكْبِ، نَقْطَعُ بِهِ عَنَّا الطَّرِيقِ، قَالَ ابْنُ عُمَر: كَأَنِّي أَنْظُرُ إِلَيْهِ متعلِّقًا بِنِسْعَةِ ناقَةِ رَسولِ اللهِ ﷺ، وإِنَّ الحِجَارةَ تَنْكُبُ رِجْلَيْهِ، وَهُوَ يَقُولُ: إِنَّما كُنَّا نَخُوضُ ونَلْعَبُ، فيقولُ لَهُ رسولُ اللهِ ﷺ: ( قُلْ أَبِاللّهِ وَآيَاتِهِ وَرَسُولِهِ كُنتُمْ تَسْتَهْزِئُونَ )، مَا يَلْتَفِتُ إِليهِ، ومَا يَزِيدُهُ عَلَيْهِ.

Daga Ibnu Umar, da Muhammad dan Ka'ab, da Zaidu dan Aslam, da Qatadah, - hadisin sashensu ya shiga cikin na sashe- wani mutum ya fada a yakin Tabuk cewa: bamu taba ganin irin wadannan malaman namu ba, ga yawan cin abinci, ga ga yawan karya, ga yawan ragwantaka yayin haduwa da abokan gaba, - Yana nufin Manzon Allah Sallallahu alaihi wasallam da Sahabbansa makaranta qur'ani- se Aufu dan Malik yaace masa: kayi karya, tabbas kai Munafiki ne, kuma lallai se na labarta wa Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- se Aufu ya tafi wajen Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- don ya labarta masa, sai ya samu qur'ani ya rigayeshi, se wannan mutumin ya tafi wajen Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- bayan ya riga ya tafi, ya hau taguwarsa, sai yace: ya ma'aikin Allah! mun kasance muna kutsawa muna wasa ne da irin zancen matafiya, domin rage nisan tafiyar, Abdullahi dan Umar yace: kamar ina kallonsa yanzu haka yana rike da igiyar taguwar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-, yana tuntube da duwatsu, yana cewa: iyaka dai kutse mukeyi kuma muna wasa, Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- kuma yana cewa: [**Shun da Allah ne da AyoyinSa da ManzonSa kuke izgili** ], ba ya juyawa gareshi kuma baya karawa kan wannan maganar.

● قَرَّائِنا: Suna nufin Annabi -Sallallahu Alaihi wasallam- da Sahabbansa.

● ولَكِنَّكَ مُنَافِقٌ ( **Lallah kai dinnan munafiki ne** ): Da wannan za a fahimci cewa mai zagin Sahabban Annabi kafiri ne, domin sukan su sukan Allah ne, kuma suka ce ga AddininSa da ManzonSa ( Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi).

● بِنِسْعَةِ: Igiyar da ake daure abin hawa.

● تَنْكُبُ رِجْلَيْهِ: duwatsu na shiga kafafuwansa.

## Fa'idodi Daga Hadisin:

1. Bayani kan ilimin Allah dangane da abin da zai kasance, Allah Yasan dukkan abubuwan da suka faru, kuma yasan wadanda zasu faru a gaba.

2. Annabi Muhammad -Sallallahu alaihi wasallam- yana hukunci ne da abin da Allah Ya saukar masa.

3. Izgili da Allah da AyoyinSa, da ManzonSa yana daga mafi girman kafirci.

4. Duk mai izgili da Allah kafiri.

5. Kausasa hukunci a wajen da yadace.

6. Karbar tubar mai izgili tareda sharuddan tubar.

## Fadakarwa:

1. Wanda ya zauna cikin masu zagi hukuncinsu daya, sedai idan yayi musu inkari ko yabar wurin, Allah Ta'ala Yana cewa:

وَقَدْ نَزَّلَ عَلَيْكُمْ فِي الْكِتَابِ أَنْ إِذَا سَمِعْتُمْ آيَاتِ اللّهِ يُكَفَرُ بِهَا وَيُسْتَهْزَأُ بِهَا فَلاَ تَقْعُدُواْ مَعَهُمْ حَتَّى يَخُوضُواْ فِي حَدِيثٍ غَيْرِهِ إِنَّكُمْ إِذاً مِّثْلُهُمْ (١٤٠).

*[ **Kuma hakika -Allah- Ya sassaukar muku a cikin littafi cewa idan kunji Ayoyin Allah, ana kafirce musu, kuma ana izgili dasu to kar ku zauna tare da su, har sai sun kutsa cikin wani zancen, lallai ne ku a lokacin nan daidai kuke da su**]. (QS. An-Niisa : 140).*

2. Ka kiyayi sa mutane dariya da karantun Al'qur'ani ko Hadisi, kasance cikin taka tsantsan yayin karantasu.

3. Idan wani ya fadi maganar da take iya daukar ma'anar zagi to se mu fadakar dashi, idan ya tuba shikenan, idan yaki kuma to ya zamo mai izgili.

4. Wajibi ne mutum ya kiyayi ji ji da kai, da ruduwa da kai, domin lada kyakkyawar aiki guda takan iya shigar da mutum Aljannah kamar yanda mummunar aiki guda take iya shigar da mutum wuta, wannanan mutumin ya fita zuwa yakin Tabuk tareda Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- sannan ya aikata abin da ya jawo masa tabewa.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Mas'ala maigirma: duk wanda yayi izgili da ( Allah, ko ayoyinsa, ko Manzonsa ), to wannan kafiri ne.

2. Wannan shine tafsirin ayar kan dukkan wanda yayi izgili ko waye shi (Munafiki ko waninsa ).

3. Akwai banbanci tsakanin annamimanci da nasiha ga Allah da Manzonsa (domin manufarta; girmama Addinin Allah ).

4. Banbanci tsakanin afuwar da Allah Ya ke so ( Wanda akwai maslaha ciki ) da kausasawa ga abokan Abokan gaban Allah ( Sedai tausasawa a wasu lokutan saboda da'awa da neman hadin kan mutane abune mai kyau ).

5. Daga cikin uzuri akwai wanda ba a karbarsa. ( idan aka tabbata cewar uzurin karya ce ).

**[49] BABIN ABIN DA YA ZO NA FADIN ALLAH TA'ALA:**

وَلَئِنْ أَذَقْنَاهُ رَحْمَةً مِّنَّا مِن بَعْدِ ضَرَّاء مَسَّتْهُ لَيَقُولَنَّ هَذَا لِي

***Kuma lallai idan mun dandana masa wata Rahama daga gare Mu, bayan wata cuta da ta shafe shi, lallai zai ce wannan (ni'imar) tawa ce.*** *(QS. Fussilat:*

قالَ مُجاهِدٌ: «هٰذا بِعَمَلي، وأَنا مَحْقوقٌ بهِ»، وقالَ ابنُ عبَّاسٍ: «يريدُ من عِنْدي».

Mujahid ya fassara da cewa: ( Wannan ya samu ne da ilimina, kuma daman ni na cancanta dashi ), Ibn Abbas ya ce: (yana nufin: daga gareni ne).

● Tabbas idan mutum ya jingina wata ni'ima zuwaga aikinsa da wahalarsa, to hakika wannan wani nau,i ne na tarayya a cikin Rububiyyar Allah, amma idan ya jingina ni'imar zuwaga Allah sannan ya riya cewa dama shi ya cancanci wannan ni'imar kuma abin da Allah Ya bashi ba tsantsar falalar bace daga Allah, to wannan akwai wani nau,i na dagawa da girmankai tareda shi a janibin bautar Allah Ta'ala.

**DALILI NA BIYU:**

Fadin Allah Ta'ala:

قَالَ إِنَّمَا أُوتِيتُهُ عَلَى عِلْمٍ عِندِي

*[ **Ya ce iyaka an bani shi ne a bisa wani ilimi dake gare ni** ]. (QS. Al-Qasash : 78).*

قَالَ قَتَادَةُ: «عَلَى عِلْمٍ مِنِّي بِوجُوهِ الْمَكَاسِبِ»، وَقَالَ آخَرونَ: «عَلَـى عِلْمٍ مِنَ اللهِ أَنِّـي لَـهُ أَهْلٌ»، وَهَذَا مَعْنَى قَوْلِ مُجَاهِدٍ: «أُوتِيتُهُ عَلَى شَرَفٍ».

Qatadah ya fassara maganarsa da cewa: ( a bisa wani ilimi da na sani dangane da hanyoyin samu ), wadansu malaman kuma sukace: (bisa wani ilimi daga Allah cewa lallai ni na cancanci wannan rahamar ), wannan itace: maganar Mujahid: (an bani ne bisa wani matsayi da nake dashi ).

**DALILI UKU:**

**وَعَنْ أَبِـي هُرَيْرَةَ ﵁؛ أَنَّـهُ سمِعَ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُوْلُ: «إِنَّ ثَلَاثَـةً مِنْ بَنِـي إِسْرَائِيلَ: أَبْرَص وَأَقْرَعَ وَأَعْمَى، فَأَرَادَ اللهُ أنْ يَبْتَلِيَهُمْ، فَبَعَثَ إِلَيْهِمْ مَلَكًا، فَأَتَى الأَبْرَص، فَقَالَ: فَأيُّ شَـيءٍ أَحَبُّ إِلَيْكَ؟ قَالَ: لَوْنٌ حَسَنٌ، وَجِلْدٌ حَسَنٌ، وَيَذْهبُ عَنِّي الَّذي قَدْ قَذِرَنِي النَّاسُ بِهِ، قَالَ: فَمَسَحَهُ، فَذَهَبَ عَنْهُ قَذَرُهُ؛**

فأُعطِي لَوْنًا حسَنًا، وَجِلْدًا حسَنًا، قَالَ: فَأَيُّ الْـمَالِ أَحَبُّ إِلَيْكَ؟ قَالَ: الإبِلَ أَوِ البقَر- شَكَّ إِسْحَاقُ - فأُعطِيَ نَاقَةً عُشَرَاءَ، فقَالَ: بَارَكَ اللهُ لَكَ فِيهَا.قَالَ: فأَتَى الأَقْرَعَ، فقَالَ: أيُّ شيءٍ أَحَبُّ إِلَيْكَ؟ قَالَ: شَعَرٌ حَسَنٌ، وَيَذْهَبُ عَنِّي الَّذِي قَدْ قَذِرَنِي النَّاسُ بِهِ، فَمَسَحهُ، فَذَهَبَ عنْهُ، وَأُعطِيَ شَعْرًا حَسَنًا، قَالَ: فَأيُّ الْـمَالِ أَحَبُّ إليْكَ؟ قَالَ: البقَرُ أوِ الإبِلُ، فأُعطِيَ بقَرةً حامِلًا، قَالَ: بَارَكَ اللهُ لَكَ فِيهَا.

فأَتَى الأَعْمَى، فقَالَ: أَيُّ شَيْءٍ أَحَبُّ إِلَيْكَ؟ قَالَ: أن يَرُدَّ اللهُ إِلَيَّ بَصَرِي؛ فَأُبْصِر بِهِ النَّاسَ، فَمَسَحَهُ، فَرَدَّ اللهُ إِلَيْهِ بَصَرَهُ، قَالَ: فَأيُّ الْـمَالِ أَحَبُّ إِلَيْكَ، قَالَ: الغَنَم، وَادٍ مِنَ الغَنَمِ.

قَالَ: ثُمَّ إِنَّهُ أَتَى الأَبْرَصَ فِي صُورَتِهِ وَهَيْئَتِهِ، فَقَالَ: رَجُلٌ مِسْكِينٌ، وَابْنُ سَبِيلٍ، قَدِ انقَطَعتْ بِيَ الْحِبَالُ فِي سفَرِي هَذَا؛ فَلَا بلَاغَ لِيَ اليَوْمَ إِلَّا بِاللهِ ثُمَّ بكَ، أَسْأَلُكَ بِالَّذِي أَعْطَاكَ اللَّونَ الْـحَسَنَ، وَالْجِلْدَ الْحسَنَ، وَالْـمَالَ؛ بَعِيرًا أَتبَلَّغُ بِهِ فِي سفَرِي، فَقَالَ: الْـحُقُوقُ كَثِيرَةٌ، فَقَالَ لَـهُ: كَأَنِّي أَعْرِفُكَ! أَلَمْ تَكُنْ أبْرَص يَقْذَرُكَ النَّاسُ، فَقِيْرًا فَأَعطاكَ اللهُ الْـمَالَ؟ فَقَالَ: إِنَّمَا وَرِثْتُ هَذَا الْـمَالَ كَابِرًا عَنْ كَابِرٍ، قَالَ: إِنْ كُنْتَ كَاذِبًا؛ فَصَيَّرَكَ اللهُ إِلَى مَا كُنْتَ. قَالَ: وَأَتَى الأَقْرَعَ فِي صُورَتِهِ وَهَيْئَتِهِ، فَقَالَ لَهُ مِثْلَ مَا قَالَ لِهَذَا، وَرَدَّ عَلَيْهِ مِثْلَ مَا رَدَّ عَلَيْهِ هَذَا، فَقَالَ لَهُ: إِنْ كُنْتَ كَاذِبًا فَصَيَّرَكَ اللهُ إِلَى مَا كُنْتَ. قَالَ: وَأَتَى الأَعْمَى فِي صُورَتِهِ وَهَيْئَتِهِ، فَقَالَ: رَجُلٌ مِسْكِينٌ، وَابْنُ سَبِيلٍ، قَدِ انْقَطَعَتْ بِيَ الْحِبَالُ فِي سَفَرِي؛ فَلَا بَلَاغَ لِيَ اليَوْمَ إِلَّا بِاللهِ ثُمَّ بِكَ، أَسْأَلُكَ بِالَّذِي رَدَّ عَلَيْكَ بَصرَكَ شَاةً أَتبَلَّغُ بِهَا فِي سَفَرِي، فَقَالَ: قَدْ كُنْتُ أَعْمَى فَرَدَّ اللهُ إِلَيَّ بَصَرِي؛ فَخُذْ مَا شِئْتَ، وَدَعْ مَا شِئْتَ؛ فَوَاللهِ لَا أَجْهَدُكَ اليَوْمَ بِشَيءٍ أَخَذْتَهُ للهِ.

فَقَالَ: أَمْسِكْ مَالَكَ، فَإِنَّمَا ابْتُلِيْتُمْ فَقَدْ رَضِيَ اللهُ عَنْكَ، وَسَخِطَ عَلَى صَاحِبَيْكَ»، أَخْرَجَاهُ.

Daga Abu Hurairah -Allah Ya kara yarda a gareshi- ya ji Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi- yana cewa: (( Wadansu mutane uku cikin Banu isra'ila: kuturu, da me Koran ka, da makaho, Allah Yayi nufin Ya jarabce su, se ya tura wani Mala'iki zuwa garesu, se yaje ga makahon, yace dashi: wani abu ne yafi soyuwa zuwa gareka, sai yace: launi mai kyawu, da fata mai kyawu, kuma in rabu da wannan abin da mutane suka kyamace ni don shi, ya ce: se Mala'ikan ya shafa shi, se wannan abin kyamar nasa ta tafi, kuma aka bashi launi mai kyau, da fata maikyau, sai ya ce dashi: a cikin dukiya wanne kafi so? Sai yace: rakuma ko shanu, -Ishaq ne yayi kokwanton- se aka bashi rakuma mai ciki, yace dashi: Allah Ya sanya maka albarka cikinta.

Yace: sa'annan yaje ga me koran kayi yace dashi: wani abu ne yafi soyuwa a gareka? Sai yace: gashi maikyau, sannan in rabu da abin da mutane suka kyamace ni saboda shi, se ya shafa shi, se wannan kazamtar ta tafi, kuma aka bashi gashi mai kyau, sannan yace dashi: a cikin dukiya wanne kafi so? Yace: shanu ko rakuma, se ak bashi saniya mai ciki, sannan yace masa: Allah Ya sanya maka albarka a cikinta.

Sa'annan yaje ga makahon, sai yace dashi: me kafi so? Yace: Allah Ya dawo mini da ganina; don in ringa ganin mutane dashi, se ya shafa shi, se Allah Ya mayar masa da ganinsa, yace dashi: a cikin dukiya wanne yafi soyuwa a gareka?

Yace: awakai, se aka bashi akuya da tayi kusan aihuwa, se Rakuma da Saniyar suka hayaiyafa, akuyar ma ta hayaiyafa, sai shi na farkon ya saamu garken rakuma, na biyun kuma ya samu garken shanu, na ukun kuma garken awaki, ya ce: sannan sai Mala'aikin yaje ga kuturun a suararsa ta farko da yanayinsa sai ya ce: ni mutum ne mabukaci, kuma dan tafarki, dabaruna su kare cikin wannan tafiya tawa; banida sauran guziri a yau sai taimakon Allah, sannan da taimakonka, ina roknka don wanda Ya baka launi mai kyawu, da fata mai kyawu, da dukiya, kabani rakuma guda don samun karfin gwuiwar karasa tafiyata, sai yace: nauyi yayi yawa a kaina, sai ya ce dashi: kamar nasanka a baya! ba kaine kuturunnan da mutane ke kyamar ka ba, kuma mabukaci Allah Ya baka dukiya? Sai yace: iyakar wannan dukiyar -gadon gado ne- nayi gado ne nima a daga iyaye da kakanni, sai yace: in karya kayi to Allah Ya mayar da kai yanda kake, yace: sai ya tafi zuwaga me koran ka a cikin surarsa da yanayinsa, se ya fada masa misalin abin da wannan -kuturun- ya fada masa, shima ya mayar masa da kwatankwacin abin da wannan -kuturun- ya fada masa, sai yace dashi: idan karya kakeyi to Allah Ya mayar da kai zuwa yanda kake, yace: se ya tafi zuwaga makahon a cikin surarsa da yanayinsa, sai yace dashi: ni mutum ne mabukaci kuma dan tafarki, dabaruna su kare cikin wannan tafiyar tawa; banida sauran guziri a yau sai taimakon Allah, sannan taimakonka, ina roknka don wanda Ya maida maka da ganinka, akuya guda don samu karfin gwuiwan karasa tafiyata, sai yace: hakika na kasance makaho Allah Ya maida min ganina, ka dau abin da kaka dama kabar abin da kaga dama, na rantse da Allah ba zan >>>>> kan abin da ka dauka a yau saboda Allah ba.

Sai -Mala'ikin- yace dashi: rike dukiyarka, an jarabceku ne, <u>kuma hakika Allah Ya yarda dakai sannan yayi fushi da abokanka biyu</u> )), (Bukhari da muslim ne suka fitar dashi ).

● Cikin wannan hadisin akwai abubuwan masu yawa da yakamata a kula da su, daga ciki:

1. Ana kawo kissoshi cikin Alqur'ani da Sunnah saboda wa'azantuwa da izina.

2. Dalili kan ikon Allah wajen warkar da kuturu da maia kora da makaho, ta hanyar mala'iki gare su.

3. Mala'iku suna iya chanza kamanni da izinin Allah, suna iya zuwa cikin surar mutane.

4. Mala'iku jikkuna ne, ba kadai ruhi ne, ko ma'anoni, ko tsantsan karfi ba.

5. Maruwaitan hadisi sukan so su ruwaito hadisi da lafazinsa.

6. Baya wajaba a kan mutum yarda da abin da a ka kaddarashi, amma wajibi ne a kansa yarda da qaddara, wanda shi aikin Allah ne, a kwai banbanci tsakanin aikin Allah da abin da a ka qaddara, abubuwan da a ka kaddara sun kasu zuwa: [1] Musibun da, ba wajibi ba ne a yarda da su, [2] Hukunce hukuncen Shari'ah, wajibi ne a yarda da su.

7. Ya halatta a rataye addu'a kan wani abu.

8. Sauka daga jayayya yana halatta cikin abin da shi mai saukan bai tabbatar dashi ba, domin rufe bakin abokin hasuma da gajiyar dashi .

9. Albarkar Allah ba ta da karshe, don hakane ma aka ba ma wannan garke na rakuma.

10. Godiya kan ni'ima na kasancewa ne gwargwadon ni'imar.

11. Ya halatta mutum ya siffantu da yanayin da ba nasa ba, a hakika -saboda maslaha-.

12. jarabawa takan iya game mutane, kuma a fili, kissar tasu shahararriya ce.

13. Falalar tsantseni da zuhudu, suna iya sa mutum yayi kyakkyawan karshe, kamar wannan makahon.

14. Al'ummomin da suka gabata suna gadon junansu.

15. Daga cikin Sifofin Allah akwai Yarda, Fushi, Nufi, muna tabbatar dasu kamar yanda suka dace da Allah.

16. Ana iya amfani da Kalmar abota bisa kamanceceniya da wani abu cikin abubuwa koda babu abotan a tsakani.

17. Allah Yakan jarabci mutane cikin abin da Ya ba su.

18. Tunasarwa tana kasancewa ta hanyar; Magana, aiki, kamanni.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tafsirin ayar: *{ **Kuma lallai idan mun dandana masa wata Rahama daga gare Mu, bayan wata cuta da ta shafe shi, lallai zai ce wannan (ni'imar ) tawa ce.** …} (QS. Fussilat : 50).*

2. Menene ma'anar fadinsa: لَيَقُولَنَّ هَذَا لِي: ( Ma'ana: ni na cancance shi ).

3. Ma'anar fadinsa: { *[ **Ya ce iyaka an bani shi ne a bisa wani ilimi dake gare ni** ]. (QS. Al-Qasas: 78).*

4. Abin da ke cikin wannan qissah mai ban mamaki na wa'azi maigirma. ( daga ciki; banbancin tsakanin kuturu da me kora da makaho, domin kuturu da me kora sun muzanta ni'imar Allah bayan samuwarta garesu, tareda rashin wani ta'alluqi da Allah kafin samuwar ni'imar, amma shi makahon ya tabbatar da Ni'imar Allah a kansa bayan samuwar ni'imar, sannan kuma ya rataya da Allah kafinta, Imam ibul Qayyim yace: Mutum ya kiyayi ketare iyaka matuka, na kalmar: ( nine, nawane, inada ), domin da wadannan kalmomin aka jarabci Iblis, da Fir,auna, da Karuna, kalmar: (na fishi alheri ) ta Iblis ce, ( mulkin Misra tawa ce ) wannan kuma ta Fir auna ce, ( iyaka an bani ne a bisa wani ilimi da nakeda shi ) wannan kuma ta Karuna ce, mafi kyawun wajen da aka sanya kamar ( ni ), cikin fadin bawa maizunubi, mai kuskure, mai neman gafara wanda yake furuci da gazawarsa da makamancinsa, sannan kalmar ( tawa ce ), fadin bawa: inada zunubi da laifi iri kaza, matalauci, mabukaci, makaskanci, sannan kalmar ( tare dani ) cikin fadin bawa: ( ya Allah Ka gafarta min ) …………..da kuskurena, da gangancina, duk wadannan suna tare dani " ).

## [50] **BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:**

فَلَمَّا آتَاهُمَا صَالِحاً جَعَلاَ لَهُ شُرَكَاء فِيمَا آتَاهُمَ

***[ To a lokacin da ya basu abin kwarai, sai suka sanya masa abokan tarayya a cikin abin da Ya ba su ]****. (QS. Al-A'araf : 190).*

**Nau'in shirkar da ake nufi cikin ayar:**

**Babban shirka:** Idan wani ya kudirce cewar wani waliyyi ne ya bashi aihuwa da makamancin wannan, saboda ya jingina halitta zuwaga wanin Allah.

**Karamar shika:** ingina amintuwar yaron da kubutarsa zuwaga likitoci da amkamantansu, saboda ya jingina ni'ima zuwaga sababi ya mance da wanda ya halicci sababin, (Shine All).

**Karamar shika:** cikin bauta, kamar gabatar da soyayyar yaron akan soyayyar Allah, ko ya shagaltar dashi daga yi masa 'da a, ta yaya ze sanya wannan yaron kini wa Allah a cikin soyayya?.

**DALILI NA BIYU:**

قَالَ ابْنُ حَزْمٍ: «اتَّفَقُوا عَلَى تَحْرِيمِ كُلِّ اسْمٍ مُعَبَّدٍ لِغَيْرِ اللهِ؛ كَعَبْدِ عَمْرٍو، وَعَبْدِ الْكَعْبَةِ، وَمَا أَشْبَهَ ذَلِكَ؛ حَاشَا عَبْدَ الْمُطَّلِبِ».

Ibnu Hazm: ya ce: ( Malamai su hadu a kan haramcin dukkan sunan da aka bautar ga wanin Allah, Kamar: bawan Amru, bawan Ka'aba, da makamantansu, banda Abdul Muddalib ).

● Baya halatta a bautar da wani suna ga wanin Allah, duk wanda ya kafa dalili da fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-: (( **Ni dan Abdul-Muddalib ne** )), zamu bashi amsa kamar haka:

1. Wannan yana daga hadisai mutashabihah (hadisan da ma'anoninsu basu fito fili ba ), munada nassoshi bayyanannu wadanda suka haramta hakan .

2. Wannan hadisin yana shiga babin labari ne, ba farawa ko tabbatarwaba.

3. Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- bai sanya irin wannan sunan ma wani ba, kuma baiyi izini ga daya daga sahabbansa dashi ba, kuma bai tabbatar dashi ba.

4. Sunsan Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- da wannan sunan, da wani zai kira Annabi da ( Ibn Abdullahi ) da babu wanda zai san cewa shi ake nufi .

5. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yana Magana ne kan abin da ya gabata, domin Abdul Muddalib ya riga ya mutu.

6. Abdul Muddalib ba suna bane, lakabi ne, sunansa: Shaibatul - hamd, babansa: Hashim, ya tura shi Madinah yana karami, zuwaga kawunansa a kabilar banu Annajar, don yazauna a wajensu saannan ya koyi muhimman abubuwa a yayinda baffansa Al-muddalib ya tafi zuwa Madinah sai ya dauko Shaibatul-hamd, yayinda ya isa dashi Makkah se launinsa ya chanza saboda tsawon tafiya, se wadansu sukace: wannan bawan fa? Sai sukace: Abdul-Muddalib - bawan Muddalib- ( bauta irinta Ubangida da yaron gida wannan babu matsala ), daganan ne se wannan lakabin ya bishi.

**DALILI NA UKU:**

وَعَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ فِي الآيَةِ قَالَ: «لَـمَّا تَغَشَّاهَا آدَمُ حَمَلَتْ، فَأَتَاهُمَا إِبْلِيسُ، فَقَالَ: إِنِّي صَاحِبُكُمَا الَّذِي أَخْرَجْتُكُمَا مِنَ الْجَنَّةِ؛ لَتُطِيعُنِّي أَوْ لأَجْعَلَنَّ لَهُ قَرْنَيْ أَيِّلٍ، فَيَخْرُجَ مِنْ بَطْنِكِ فَيَشُقَّهُ، وَلأَفْعَلَنَّ وَلأَفْعَلَنَّ؛ يُخَوِّفُهُمَا، سَمِّيَاهُ عَبْدَ الْحَارِثِ، فَأَبَيَا أَنْ يُطِيعَاهُ، فَخَرَجَ مَيِّتًا، ثُمَّ حَمَلَتْ فَأَتَاهُمَا، فَقَالَ مِثْلَ قَوْلِهِ؛ فَأَبَيَا أَنْ يُطِيعَاهُ، فَخَرَجَ مَيِّتًا، ثُمَّ حَمَلَتْ فَأَتَاهُمَا فَذَكَرَ لَهُمَا، فَأَدْرَكَهُمَا حُبُّ الْوَلَدِ، فَسَمَّيَاهُ عَبْدَ الْحَارِثِ، فَذَلِكَ قَوْلُهُ تَعَالَى: ( جَعَلاَ لَهُ شُرَكَاءَ فِيمَا آتَاهُمَ )، رَوَاهُ ابْنُ أَبِي حَاتِمٍ.

Ibnu Abbas ya ce dangane da tafsirin ayar: ( Yayinda -Adamu -Alaihis salam- ya rufeta; Hauwa'u- se ta yi ciki, sa'annan Iblis ya zo musu, yace: nine abokinku da na fitar da ku daga aljannah; kodai kuyi mini 'da a ko kuma in sanya masa kafo biyu na barewa wanda zai tsaga cikinki ya fice, kuma lallai ne se na aikata, wallahi se na aikata; ya tsoratar dasu, don haka ku rada masa suna: Abdul Harith, se suka ki suyi masa 'da a, se ta haife shi matacce, sannan ta sake yin ciki se ya sake zuwa musu, ya fada musu irin abin da ya fada musu a farko; suka ki siyi masa 'da a, se ta sake aihuwarsa macacce, sannan ta sake yin ciki ya sake zuwa musu, kuma ya sake ambata musu irin wancan maganar, se aka jarrabe su da son 'da, sai suka kiraye shu da Abdul-Harith, wannan shine ma'anar fadin Allah Ta'ala: [**... sun sanya masa abokan tarayya cikin abin da Ya basu** ]. *(QS. Al'araf: 190).* ( Ibnu Abi Hatim ne ya rawaito ).

وَلَهُ بِسَنَدٍ صَحِيحٍ عَنْ قَتَادَةَ قَالَ: «شُرَكَاءَ فِي طَاعَتِهِ، وَلَمْ يَكُنْ فِي عِبَادَتِهِ».

Daga ibnu Abbas da isnadi maikyau zuwaga Qatadah ya ce: (... -Sun sanya masa- abokan tarayya cikin 'da a ba bauta ba ).

وَلَهُ بِسَنَدٍ صَحِيحٍ عَنْ مُجَاهِدٍ فِي قَوْلِهِ: ( لَئِنْ آتَيْتَنَا صَالِحاً ) قَالَ: «أَشْفَقَا أَنْ لَا يَكُونَ إِنْسَانًا»، وَذَكَرَ مَعْنَاهُ عَنِ الْحَسَنِ، وَسَعِيدٍ، وَغَيْرِهِمَا.

Daga Ibn Abbas -Allah Ya kara yarda a gareshi- da isnadi sahihi daga Mujahid dangane da fadinsa: ( Wallahi idan har ya ba mu na kwarai..), ya ce: (( Sun ji tsoron kar a basu wani halitta wanda ba mutum ba )), ya ambaci ma'anarsa daga Hassan, da Sa'id, da wadansunsu.

● **قَرْنَيْ أَيِّلٍ :** Kafo biyu na namijin barewa.

● **Abdul Haarith:** Shaidan ya zabi wannan sunan saboda sunansa ne, don haka yaso su bautar dashi, a gareshi.

● **Wannan kissar karyace ta fiskoki masu yawa:**

1. Babu wata ingatacciyar riwaya daga Annabi -Sallallahu alihi wasaallama- dangane da wannan kissar, Ibn Hazm ya ce: ( Kissar karya ce, kirkirarta a kayi ).

2. Sunnar Allah ce idan ya ambaci kuskuren wani Annabi, yakan ambaci tubarsa .

3. Annabawa ts划rarru ne daga aikata shirka, bisa ittifaqin malamai.

4. Mutane zasu je ga Annabi Adam -Alaihis Salam- ranar tashin alkiyama, sai yabada hanzari da sabonsa na cin itaciyar da aka hanasu kusantanta, da sun aikata shirka, da gabatar da hankari a kanta shi yafi karfi da chanchanta.

5. Fadin Shaidan a garesu: ( nine ma'abocinku ), wanda yakeson ya batar da wani bazai fadi hakaba .

6. Bazai taba yiyuwa ba su gasgata Shaidan kan cewa zai sanya wa dansu kafo biyu na barewa, domin gasgatshi kan haka shirka ce cikin Rububyyah .

7. Fadin Allah -Ta'ala- cikin ayar: (يشركون), aka kawo shi da lamirin jama'a, da Adamu da Hauwa'u ake nufi da yace: (يشركان), lamirin mutum biyu.

8. Saboda haka, tafsirin ayar yana komawa ne zuwaga banu Adama wadanda sukayi shirka ta hakika, cikinsu akwai masu shirka da Allah, sannan daga cikinsu akwai masu kadaita Allah.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Haramunne duk sunan da aka bautar ga wanin Allah ( har Abdul-Muddalib ).

2. Tafsirin ayar ***[ To a lokacin da ya basu abin kwarai, sai suka sanya masa abokan tarayya a cikin abin da Ya ba su ]***. *(QS. Al-Aa'raf : 190).*

3. Wannan shirkar cikin cikin sunane kadai ba hakikanin shirkarba ( Abin da yake daidai shine: shirka ce ta hakika, shirkar da ta auku cikin banu Adam, ba daga Adamu da Hauwa'u ba ).

4. Baiwar Allah ga mutum da 'ya mace madaidaiciya yana daga cikin ni'imar Allah ( Saboda wadansu mutane sun daka cewa baiwar diya mace jarabawa ce, kamar yanda baiwar 'da namiji madaidaici shima yana daga ni'imomin Allah ).

5. Magabata sun banbance tsakanin shirka cikin 'daa da shirka cikin ibada ( domin Adam da Hauwa'u -Alaihimas Salam- sun yi biyayya ne ga shaidan basu bautata masa ba, wannan a bisa cewa in har kissar ta inganta ne ).

## [51] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

وَلِلّهِ الأَسْمَاء الْحُسْنَى فَادْعُوهُ بِهَا وَذَرُواْ الَّذِينَ يُلْحِدُونَ فِي أَسْمَآئِهِ

**(KUMA ALLAH YANADA SUNAYE MASU KYAU SAI KU ROKESHI DA SU, KU KYALE WADANDA SUKE YIN ILHADI A CIKIN SUNAYENSA *... )* (QS. Al-A'araf, 180).**

ذَكَرَ ابنُ أَبِي حَاتِمٍ عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ ( يُلْحِدُونَ فِي أَسْمَآئِهِ ): «يُشْرِكُونَ»، وَعَنْهُ: «سَمَّوُا اللَّاتَ مِنَ الإِلَهِ، وَالْعُزَّى مِنَ الْعَزِيزِ»، وَعَنِ الأَعْمَشِ: «يُدْخِلُونَ فِيهَا مَا لَيْسَ مِنْهَا».

Ibnu Abi Hatim ya ambaci riwaya daga Ibnu Abbas dangane da tafsirin: (Sukeyin ilhadi cikin sunayenSa ), ma'ana: ( Sukeyin shirka -cikin sunayensa- ), daga Ibn Abbas yace: (( sun cirato sunan Laata daga sunan Allah: Al-Ilah, Uzza kuma da Al-Aziz )) an rawaito daga Al-Aamash: (( Suna shigarwa a cikinsu abubuwan da basa cikinsu )).

● Cikin wannan babin akwai martani ga wanda yace: Kitabut tauhid kadai Tauhhidin Uluhiyyah ya kunsa.

● { وَلِلّهِ }: Tafarkin tauhidi a nan, gabatar da labarinsa, domin gabatar da abin da yakaata a jinkirtar dashi yana nuni akan iyakance wannan abun ta takaitashi kan labarin.

● { الْحُسْنَى }: Ma'ana: Sunkai matuka wajen kyawu, Masu cikan kamala ta kowace fiska, babu tawaya tattare dasu.

● { *Ku kiraye Shi da su* }: rokon Allah da sunayensa nada ma'anoni biyu:

**Du'au Ibadah ( Addu'ar bauta ):** Ka bauta wa Allah gwargwadon Ma'anin wadannan sunayen, Misali: sunan Allah: Al-Basiru, yana hukunta ka bauta wa Allah da hukuncin wannan ganin, kar Allah Yaga wani aikin da bayaso daga gareka.

**Du'au Mas'alah (Addu'ar roko):** Ka gabatar da sunayen Allah yayin addu'ar, kana mai tawassali da su zuwaga Allah; kamar kace: ( Ya Allah Kayi min gafara, wata gafara daga gareka, kuma kayi mini rahama, lallai kai Maigafara ne kuma Mai jinkai) .

**ILHADI:** Karkatar dasu -Sunayen Allah- daga abin da ya wajaba ayi imani dashi cikinsu, ilhadi ya kasu zuwa:

**Ilhadi cikin Sunayen Allah da SiffofinSa:**

**Yanada nau'uka kamar haka:**

1. Inkarin Sunayen Allah dukkansu, ko sashensu, kamar mazhabin Jahamiyyah .
2. Ya tabbatar da suna amma yana inkarin Sifa, kamar cewarsu, Allah Mai ji ne ba tareda ji ba, Mazhabin Mu'utazilawa.
3. Ya kamantata da halitta, AL Mumassilah.
4. Ya cirato wa gumaka sunaye daga sunayen Allah, kamar Al-Uzzah daga Al Aziz.
5. Ya sanya wa Allah sunan da bai kira kansa dashiba, kamar masu cewa: Allah na ukun abubuwa uku ne, ko shi Mai ikone akan kagan wani abu.

**Ilhadi cikin AyoyinSa:**

1. **Shar'iah**: Kamar masu cewa: Alqur'ani halitta ne .

2. **Kauniyyah**: kamar masu cewa: 'dabi'a ce take halittan abubuwa ba Allah ba.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tabbatar da sunaye ( wa Allah Ta'ala, sabanin Jahamiyyah da wadanda suka zurfafa daga Mu'utazilawa)

2. Kasantuwar sunayen Allah sunkai Makura wajen kyawu ( ma'ana: Sunayen Allah sun kai makura wajen cikan kamala ).

3. Anyi umurni da a roki Allah da su ( Addu'a ta bauta da kuma ta roko, cikin duk biyun anyi umurni da a kirayi Allah da sunayensa ).

4. Barin -hanyar- wanda yayi fito na fito da su daga Jahilai da mulhidai ( Ma'ana a rabu da hanyarsu, ba a na nufin kar mu kirayesu mu bayyana musu gaskiya ba, wannan ayar har wayau ta kunshi ma'anar: tsoratarwa ) .

5. Bayanin ma'anar: ilhadi.

6. Narkon wanda yayi ilhadi ( cikin Sunayen Allah ko SifofinSa ).

## Jarabawar farko, Kashi na tara ( Babuka 11 ).

**Tambaya ta farko:** Sanya alamar (☒) a wurin da ya dace ko ka cika gurbin:

1. Kashi na tara shine kaso mafi tsayi na littafin . ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
2. Mawallafin ya mayar da hankali sosai kan karamar shirka saboda buyarta ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
3. نِعْمَةَ اللَّهِ ( Ni'imar Allah) ☐ Lafazi ne dake nuni kan ni'ima guda, amma jam'i ake nufi ( Ni'imomi ) ☐ Ni'ima guda .
4. Ni'ima tana tabbatuwa ne da ☐ Janyo abin so ☐ Daguwar abin ki ☐ Duka.
5. ثُمَّ يُنكِرُونَهَا ( Suna inkarin Ni'imar Allah ):
☐ Suna inkarin samuwar ni'imar ☐ Suna inkarin jingina Ni'imar zuwaga Allah.
6. Yin tafi yayin saukar jirgin sama domin gidiya ga direban jirgin ☐ Halal ne ☐ Bai halatta ba.
7. Jingina ni'ima ga wanin Allah kafirci ne ☐ Babba ☐ Karami.
8. Shirka a zukatan banu Adam ☐ Yafi buya samada alamar tafiyar tururuwa akan kamfan dutsi baki, a duhun dare ☐ A fili take karara.
9. Rantsuwa da Allah a kan karya: ☐ Karamar shirka ce ☐ Babban laifi ne ☐ Haramun ne ☐ Hukunci yana karkasuwa.
10. Rantsuwa da wanin Allah bisa gaskiya: ☐ Karamar Shirka ce ☐ Babban shirka ☐ Haram ☐ Yana bukatan dalla dalla.
11. Allah ba Ya gafarta shirka koda karama ce ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
12. Rantsuwa da Allah kan karya yafi sauki wajen Abdullahi dan Mas'ud bisa rantsuwa da wanin Allah kan gaskiya ( ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ). Ibnu Mas’ud bayason duka biyun ( ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ).
13. Fadin dame zan rantse maka don ka gasgata ni: ☐ Halal ne ☐ Bai halatta ba.
14. Fadin: (Allaf Ya so wane ma ya so ), idan yayi imani da cewa wannan mutumin yafi Allah ko kuma yana dai dai da Allah to wannan mushiriki ne ( ☐ Babba ☐ Karama ). Amma idan ya kudurce cewa wanda ya rantse dashi din kasa yake da Allah to wannan shirka ce ( ☐ Babba ☐ Karama ).
15. Fadin: (Amana a kanka ), ko: amaanah ( ☐ Karamar shirka ce ☐ Babban laifi ne ☐ Ya halatta ).
16. Wajibi ne sanin shirka don tsoron aukawa cikinsa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
17. Sahabbai Allah Ya kara yarda a gare su, sun kasance suna fassara ayar da ta sauka kan babban shirka a kan karamar shirka.

☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

18. Rantuwa mai dulmiyarwa cikin wuta itace: ☐ Rantsuwa da Allah kan karya ☐ Ya yanke dukiyar musulmi da rantsuwar karya.

19. Harafin: الواو ( Wawun ) tana hukunta: ( ☐ Jerantawa ☐ Daidaitawa ), hukuncinta: ☐ Shirka ce ☐ Halal.

20. Idan wanda ya rantse da Allah ba amintacce ne wanda za a gasgatashi ba, (☐ Ya halatta kaki yarda da rantsuwarsa ☐ Bai halatta ba ).

21. Rantsuwa da Annabi Muhammad -Sallallahu alaihi wasallal-, ko da rayuwar mahaifiya, ko da alkawari, ko da wuyana, ko da matsayi ☐ Abu ne da ya zama ruwan dare ☐ Karamar shirka ce.

22. Ma'anar fadin Annabi: " Kaza da kaza ne suka hana ni ": …………………………...
……………………………………………………………………………………………

23. Me yasa babu wanda ya fadakar a kan mas'alar rantsuwa sai bayahude?..............
……………………………………………………………………………………………

24. Bayahude shine yake nasabtuwa zuwaga Shari'ar (☐ Annabi Isa Alaihis salam ☐ Annabi Musa Alaihis Salam ), Sababin nasabar shine: (☐ Fadinsu: إنا هدنا إليك -mun koma zuwa gareka- ☐ Nasaba ce zuwaga kakansu Yahuza ☐ Duka ).

25. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya kafa hujjah da babban shirka a kan karamar shirka cikin " **Shin zaka sanya ni kishiya wa Allah**? " (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne). Ya shiryar dashi zuwaga ( ☐ Nisantar duk wata hanyar da zata kaishi zuwaga shirka komai nisanta ☐ Barin Shirka ).

26. Idan wani ya duka maka yayin gaisuwa (☐ Wajibi ne ka yi inkarin hakan ☐ Babu laifi ☐ Idan kunya ya hanaka yin inkarin to babu laifi ), Idan bakayi inkari ba to lallai kai dinnan ( ☐ Dagutu ne ☐ Mumini ).

27. Girmama Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- da lafazin da yake daidaita shi Allah ☐ Shirka ce ☐ Wannan ya na komawa zuwaga niyyar mutumin ne, idan manufarsa itace: girmama Annabi to babu laifi.

28. Yahudawa sunada manyan laifuka, Alqur'an ya kebance maganarsu: {Uzair dan Allah ne }, Saboda itace mafi girma kuma mafi shahara a wajensu: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

29. " Kaza da kaza ne suka hanani: ☐ Kunyar inkarin laifi ☐ Kunyar hani a kai ba tare da wani umarni daga Allah ba.

30. Maganar gaskiya ☐ Ana fara kafa daliline sannan kuduri ☐ Ya yi imani da wani abu sannan ya kafa dalili.

31. Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- Ya daukaka ne da kasantuwarsa ☐ Bawan Allah kuma manzonsa ☐ Muhammad dan Abdullah.

32. Mafarki na gari shine: ☐ Ya kunshi abu mai kyau ☐ Yana zuwa cikin tsari ☐ Duka biyun.

33. Duk mafarkin da ba shi da kan gado, to wannan garwayayyen mafarki ne ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
34. Mafarki mara kyau daga Shaidan nee? (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ), Sunna ne ☐ Ya labarta ma wanda zai fassara masa ☐ Yayi tofi ta gefen hagunansa so uku sannan ya nemi tsarin Allah daga Shaidan ).
35. Duk mafarkin da yasaba wa Shari'ar Allah ☐ Ana la'akari dashi ☐ Ba ya da kima.
36. Idan mutum yace wa matarsa: (Mafi muni rana a gareni shine ranar aurenmu ) ☐ Halal ne ☐ Bai halattaba.
37. Maganar gaskiya: ☐ Cutarwa bata lizimta cutuwa ☐ Tana lizimtawa.
38. Sunayen Allah dukkansu kyawawa ne makurar kyawu, **Addaharu** sunane sandararre wanda bai kunshi wata ma'ana ba, face shi suna ne na lokuta kadai: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne. Ma'anar nine Zamani: …………………………………………
39. Fadin cewa: " Zamanin mayaudari ne " ☐ Haramun ☐ Ya halatta saboda yana shiga babin labari ne.
40. Fadin cewa: " An haifi wane a shekarar yunwa " ☐ Haramun ☐ Halal ne, saboda yana shiga babin labari ne.
41. Fadin cewa: " Ya ke kasa, ki kiyaye wanda yake kanki ☐ Wannan shirka ce, domin rokon wanin Allah ne ☐ Ya halatta domin babin labari ne.
42. Nauoin zagin zamani:
1…………………………………………..hukuncinsa…………………………………………..
2………………………………………….hukuncinsa…………………………………………..
3………………………………………….hukuncinsa…………………………………………..
43. Fadin cewa: " Dabi'ar duniya tanada sirri da ababen mamaki " ko " wannan yana daga aiyukan dabi'a " ☐ Ya halatta ☐ Bai halatta ba.
44. Al-Kali shine wanda ya siffantu fatawa tareda lizimtawa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
45. Fadin: " Alkalin alkalan karni na bakwai " ☐ Ya halatta ☐ Barinsa shi yafi.
46. Ma'anar Shaikul islam: ☐ Cikakken malamin da musulunci yake komawa zuwa gareshi ☐ Mujaddadi, wanda yakeda tasiri mai yawa wajen bada kariya wa musulunci .
47. (☐ Ya dace ☐ Bai dace ba ) A kula da janibin wanda aka bashi wata sifa domin kar ya rudu ko yayi ji ji da kai.
48. Sunan da yafi soyuwa a wajen Allah shine wanda yayi nuni kan kankan da kai, misalin: (☐ Sarkin sarakuna ☐ Abdur Rahman ). Mafi wulakantar suna a wajen Allah shine wanda yake nuni kan: ☐ girman kai ☐ Iko ☐ Girmamawa ☐ Duka). Don haka aka masa sakaiya da akasin manufarsa, aka wulakantashi (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ).
49. Kiran wani da Sarkin sarakuna ko alkalin alkalai ☐ Halal ☐ haram ☐ Kabirah.

50. Alkunya na farawa ne da: ( Baban ) ko ( Maman ) ko (Dan' uwan ) ko ( Baffan ) ko ( Kawun ) takan iya zamowa: ☐ Yabo ☐ Zargi ☐ Abota da wani abu da lizimtarsa ☐ Suna tsantsa ☐ Duka.

51. Daga cikin Sahabbai akwai mai suna Al-Hakim da Al-Hakam, Manzon Allah - Sallallahu alaihi wasallam- bai canza masa suna ba saboda suna ce tsantsa (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ) Abinda akayi hani akai na sunayen Allah ☐ Wanda ya kebanta da Allah ☐ Wanda aka hararo sifa ☐ Duka biyun ).

52. Sanya alkunya ☐ Halal ne ☐ Mustahabbi.

53. (Wanda yayi izgili da Allah, ko Alqur'ani ko Manzo ), Abin da ake nufi da Manzo shine: ☐ Annabi Muhammad Sallallahu alaihi wasallam ☐ Dukkan Manzanni.

54. Koruwar imani da izgili abu ne maigirma, abun mamaki ne musulmi baisan hakanba ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

55. Sharuddan tuban mai izgili:

1……………………………………………….2…………………………………………………..

3………………………………………………………………………………………………….

56. Wajibi ne yin hukunci mai tsauri a babin izgili da Addinin Allah ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

57. Wadansu suna bada kariya ga wanda ya zagi Allah, da su aka zaga ko Uwarsu bazasu iya hakuri ba. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

58. Wajibi ne a bayyana wa mutane hadarin wannan babin, domin izgili da addini kafirci ne dake fitar da mutum daga addinin musulunci, bazamu jira har sai zagin ko izgilin ya auku ba ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

59. Wadansu suna da fahimtar cewa har sai an tambayi mai zagin ko mai izgilin cewa zagin yake nufi ko kuwa, wannan? ☐ Kuskure ne ☐ Daidai ne.

60.Yana daga girmama hakkin mahaluki a kan hakkin Allah: karban uzurin mai zagin Allah da yin fushi dashi, amma ba a karbar uzurin wanda ya zagi shugaban kasa ko Uba ko, ya sace kudin al'umma ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

61. Daukan mataki mai tsauri a wannan babin yayi amfani a wadansu kasashen godiya ta tabbata ga Allah, amma sakaci da a kayi a wadansu kasashen kuma ya janyo manya da yara ma zagin sukeyi ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

62. Mai izgili yafi girman laifi samada mai sujada wa gumaka ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne .

63. Qila ba zaka taba jin wani bayahude ko banasare yana zagin Allah, ko zagin Annabi Musa ko Annabi Isah ba, amma ka iya samu cikin masu daawar musulunci ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

64. Musulmin gaskiya shine wanda idan yaji karatun Al'qurani ko hadisi sai tsoro ya kamashi kuma imaninsa ya karu, Munafuki kuma shine yake izgili da wargi, da maganar da zai ba da dariya wa mutane: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

65. Shin zaka yada faifayin da ake zagin mahaifiyarka cikinsa, ko kuma zaka saurari karatun mai zaginta? To ina kuma ga wanda yake zagin uwar muminai? (Aishatu Radiyallahu anha?) ☐ Na'am ☐ A'a.
66. Wajibi ne a kanmu yayin da muka samu wani faifai da ya kunshi zagi: ☐ Mu saurare shi, sannan mu yada shi ☐ Mu gogeshi ba wata wata.
67. Tara faya fayen da suka kunshi zagi da izgili hanyar ☐ Magabata ce ☐ Munafukai ne.
68. Yin ridda sanadiyyar zagi da izgili lamari ne maigiran gaske, daga cikin malamai akwai wanda yace: tuba baza tayi amfani ba, wajibi ne shugaba ya kashe shi, baza ayi masa sallah ba, ba za a roka masa Rahama ba, ba za a birne shi tareda musulmai ba ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
69. Idan mai zagi ya baiyana tubarsa sannan ya sake komawa ga zagin wannan dalili ne akan karyarsa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
70. Idan munafuki yayi zagi, sannan yace: ba zagi nake nufi ba, Magana ce kawai a baka ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
71. Abinda yake nuni a kan gaskiyar tubar mai izgili: ya baiyana cewa zagi da izgili kafirci ne, kuma ya baranta zuwaga Allah. ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
72. Duk wanda yaji wani yana zagin ko yana izgili amma baiyi inkari baa, ko ya karkatar da hukuncin to kamar mai izgilin ne ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
73. Shaidan yana iya bude kofofin alhairi domin ya auka ka cikin kafirci, kamar yanda ya faru da wannan mutumin a yakin Tabuk ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
74. Zamu iya fahimtar kafircin mai zagin Sahabbai daga hadisin wannan mai izgilin (☐ Haka ne ☐ Kuskure ne ) Domin sukan Sahabban Annabi sukan: ( ☐ Allah ne ☐ Sukan Manzon Allah ne -Sallallahu alaihi wasallam- ☐ Addini ne ☐ Sahabbai ne ☐ Duka ).
75. Duk wanda yin afuwarsa ta zamo barna ba gyara ba, to lallai ☐ Yayi laifi ☐ Baiyi laifi ba.
76. Idan mutum ya jingina Ni'ima zuwaga iliminsa da aikinsa; to wannan yayi tarayya cikin: (☐ Rububiyyah ☐ Bauta ), Amma idan ya jinginata ga Allah sannan ya raya cewa shi dinnan daman ya cancanci wannan niimar do akwai wani nau i na dagawa da girman kai tattare da shi ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
77. Yarda da kaddarar Allah (☐ wajibi ne ☐ Ba wajibi ba ne ), Idan abinda Allah Ya kaddara musiba ce to ba wajibi ba ne a yara da ita ba ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
78. Babu banbanci tsakanin makahon da maikoran da kuturun dangane rokonsu ga Mala'ikan ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
79. Sunan Abdul Muddallib ☐ Halal ne ☐ Bai halatta ba.
80 Kiran wani nau i na fulawa da bawan rana ☐ Halal ne ☐ Bai halatta ba.

81. Kewaye ko kaja layi karkashin sunan da bai halatta a kira wani mutum da shi ba: ( Abdul Muddalib, Abdul Ka'bah, Abdu Manaf, Abdul Husain, Abdun Nabi, Abdul Haris, Fir'aun, Khinzab, Asiyah, Sarkin sarakuna, Shugaban mutane, Bawan Ali, Rabdul Alamin, Abdur Rahman, Al-Khalik, Abdus Sattar, Abdun Nur, Bitrus, Jeorge, Sayyidus Saadaat, Sittun nisa, Abdun Nasir ).

82. Daga cikin abubuwan da suka yi naso a cikin musulmai na wuce iyakan yan shi'a, Rafidah wanda suke nufin bauta da shine kamar fadinsu: (Ghulamu Ali ) ma'ana: ( Bawan Ali ) to wannan nasabta bauta ga wanin Allah ne, kuma shirka ne ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

83. Fadin wanda ba ya da ikon zartar da wani abu cikin dukiyan wani: (Ni bawane, wanda ake bashi umurni ) ☐ Ya halatta ☐ Bai halatta ba.

84. Kissar Adamu da Huwau -Alaihimas Salam- ☐ Ya inganta ☐ Karya ce.

85. Shaidan ya zabi sunan Abdul Harith: ☐ Saboda sunansa kenan ☐ Wannan ba gaskiya ba ce, domin Al-Harith shine mafi gaskiyan sunaye.

86. Sanya ma wani suna Al-Haarits ☐ Halal ne ☐ Bai halatta ba.

87. Annabawa kubutattu ne daga shirka bisa ijma'in malamai, duk wanda ya fadi mummunar Magana a kansu ko yayi kwakwaf dangane da wasu abubuwan da suka faru dasu to wannan ☐ Munafiki ne ☐ Mumini ne.

88. Rokon Allah da sunayensa, addu'a ce irinta: ☐ Ibadah ☐ Mas'alah ☐ Duka.

89. Kitabut Tauhid: ☐ Ya kunshi nau ukan tahidi uku ☐ Kadai tauhidin ibada ne.

90. Ilhadi cikin sunayen Allah yana kasuwa zuwa: ☐ Kaso biyu ☐ Kaso biyar.

91. Fadin Allah: [ Ku kyale wadanda suke ilhadi cikin sunayensa ], Ma'ana: ☐ Kar mu kira su zuwaga gaskiya, ko bayaninsa gare su ☐ Mu fita sha'aninsu.

92. Ilhadi cikin Sunayen Allah da Sifofinsa ya kasu zuwa: 1………………………...
2…………………………………………….….3……………………………………………..
4……………………………………………..…5……………………………………………..

## [52] **BABIN BA YA HALARTA ACE: ASSALAMU ALAL LAHI (Haram)**

**Menene dalilin haramcin?**

Saboda hakan ya saba ma hakika, domin Allah shine wanda ake rokonsa komai, ba a roka masa, saboda shi Mawadaci ne, sannan wajibi ne yabon Allah Ta'ala da Siffofinsa masu cikan Kamala.

Kuma saaboda irin wannan addu'ar ta na bayuwa zuwaga tunanin wata tawaya cikin hakkin Allah, domin duk wanda aka roka masa aminci daga wata tawaya to lallai zai iya siffantuwa da tawayar, Allah kuma Ya tsarkaka daga dukkan tawaya.

**DALILI NA FARKO:**

فِي الصَّحِيحِ عَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ ؓ قَالَ: كُنَّا إِذَا كُنَّا مَعَ النَّبِيِّ ﷺ فِي الصَّلَاةِ؛ قُلْنَا: السَّلَامُ عَلَى اللهِ مِنْ عِبَادِهِ، السَّلَامُ عَلَى فُلَانٍ وَفُلَانٍ، فَقَالَ النَّبِيُّ ﷺ: «**لَا تَقُولُوا: السَّلَامُ عَلَى اللهِ؛ فَإِنَّ اللهَ هُوَ السَّلَامُ**».

Hadisi ya tabbata cikin Sahihul Bukhari daga Ibn Mas'ud -Allah Ya kara yarda a gareshi- yace: mun kasance idan muna sallah tare da Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- muna cewa: Aminci ya tabbata ga Allah daga bayinsa, aminci ya tabbata ga wane da wane, se Annabi Sallallahu alaihi wasallam yace: " **Kar kuce aminci ya tabbata ga Allah, domin Allah Shine: Aminci** ".

● As-Salam: Sunane tabbatacce, Maikoruwa, ma'ana: kore dukkan wata tawaya ko aibu, wanda hankali zai iya tunaninsa, wata tawaya bata shafar Zatin Allah, ko Siffofinsa, ko Aiyukansa ko Hukunce hukuncensa, **Thubutiyyun:** ma'anarsa shine: tabbatar wannan sunan ga Allah, sannan tabbatar da siffar da sunnan ya kunsa: **Assalamah**.

● As-Salam: yanada ma'anoni masu yawa:

| | | |
|---|---|---|
| **Attahiyah**: Gaisuwa, kamar yanda ake cewa gaisuwa ta tabbata ga wane. | **Amintuwa daga tawaya daga aibu,** kamar fadinmu: (Amincin Allah Ya tabbata a gareka ya Annabin Allah ). | **As-Salam** Suna ne daga sunayen Allah ta'ala. |

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tafsirin kalamar As-salam. ( Sunan Allah ne, Maigirma da Buwaya, ma'anansa: wanda ya kubuta daga dukkan aibu ).

2. As-Salam, ya kunshi ma'anar gaisuwa.

3. Bai halatta ayi sallama wa Allah ba ( Haramun ne ).

4. An baiyana dalilin haramcin (Saboda Allah shine: As-Salam ).

5. Annabi ya koyar da Sahabai irin gaisuwar da ta dace da Allah ( cikin tahiyar sallah, ba za muce ma wani mahluki: dadadan gaisuwata a garekaba ).

## [53] BABIN CEWA: YA ALLAH KA GAFARTA MIN IDAN KASO. ( HARAMUN NE A SANYA SHARADI WA ALLAH CIKIN ADDU'A)

● Wannan babin yana bayani ne akan cikar Ikon Allah maigirma da buwaya da Baiwarsa, da Falalarsa, dalilin yasa aka hana sanya sharadin shine:

| | | |
|---|---|---|
| Tana nuni kan cewa kamar akwai wani wanda zai tilasta Allah, kuma lamarin ba haka yake ba. | Tana nuni kan girman wannan kan girman wannan lamarin da nauyinsa, da gagararsa a wajen Allah, wanda lamarin kuma ba haka yake ba. | Tana nuni kan wadatuwar mutum daga Allah, wannan kuma abu ne wanda bai dace ba, wannan baya cikin ladabi. |

**DALILI NA FARKO:**

في الصَّحِيحِ عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «لَا يَقُلْ أَحَدُكُمْ: اللَّهُمَّ اغْفِرْ لِي إِنْ شِئْتَ، اللَّهُمَّ ارْحَمنِي إِنْ شِئْتَ، لِيَعْزِمِ الْمَسْأَلَةَ؛ فَإِنَّ اللهَ لَا مُكْرِهَ لَهُ».

وَلِمُسْلِمٍ: «وَلْيُعَظِّمِ الرَّغْبَةَ؛ فَإِنَّ اللهَ لا يَتَعَاظَمُهُ شَيْءٌ أعْطَاهُ».

Hadisi ya tabbata cikin Sahihul Bukhari daga Abu Huraira -Allah Ya kara Yarda a gareshi- Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yace: " Kar dayanku yace: Ya Allah ka gafarta min idan Ka so, Allah Ka yi mini Rahama in Ka so, lallai ne ya muhimmanta rokon nasa; domin babu wanda yake tilasta Allah ". a riwayar Muslim kuma: " Ya girmama kwadayin nasa; domin babu wani abun da bayar dashi zai gagari Allah ".

● Neman zabi a wajen Allah cikin addu'ar istikhara wannan ba sharadi ba ne cikin mashi ar Allah, iyakanta: tana nuni ne wani lamarine da na jahilta, ban sani ba shin wannan abun alkhairi ne gare ni ko ba alkahaii ba? Hakanan ma dangane da hadisin

أَحْيِنِي مَا كَانَتِ الْحَيَاةُ خَيْرًا لِي:

" Ya Allah Ka Raya ni idan rayuwar ita tafi alkhairi gare ni "

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Anyi hani kan sanya sharadi ma Allah cikin addu'a.

2. An baiyana dalilin hanin.

3. Fadin Annabi: " Lallai ne ya girmama mas'alar " ( Idan zakayi addu'a sai ka muhimmata lamarin, kar kayi taraddudi ).

4. Girmama kwadayinsa a wajen Allah ( Ma'ana: mutum yaroki abinda yakeso, babu wani abinda zai gagari Allah ).

5.Anyi bayanin dalilin hakan ( [1] Domin bayanin daukaka da matsayin Shari'a. [2] Karin nutsuwa cikin zuciyar bawa. [3] Kiyasi, idan rokon ta zamo cikin hukunce hukunce ne ).

## [54] BABIN BA YA HALATTA MUTUM YACE: ( BAWANA, KO BAIWATA )

Hukuncin: fadin: bawana, ko baiwata

**Ya jingina shi zuwaga kansa:** wannan yanada sura biyu:

**Ya jingina shi zuwaga waninsa: kamar yace:** ( Bawan wane ) ko ( Baiwar wane ), wannan ya halatta

**Ya zamo da sigar labari:** kamar fadin: (Na ciyar da bawana ) ko (Na 'yanta bawana ), wannan ya kasu biyu:

**Ya zamo da sigar kira:** kamar fadin: (Ya bawana), wanan anyi hani akai.

Idan ya fadi hakan a bayan idon bawan nasa ko baiwar, to wannan ya halatta.

Idan ya fadi hakan akan idon bawan, ko baiwar, se mu duba mugani, idan babu wata barnar da zata ratayu da bawan ko shugaban, idan aka hararo wata barna to bai haalatta ba, amma idan ba a hararo wata barna ba to ya halatta.

**DALILI NA FARKO:**

**في الصَّحيحِ عَنْ أَبي هُرَيْرَةَ ڤ؛ أنَّ رَسُولَ اللهِ  قَالَ: «لَا يقُلْ أَحَدُكُمْ: أَطْعِمْ رَبَّكَ، وضِّئْ ربَّكَ، وَلْيَقُلْ: سَيِّدِي وَمَوْلاي، وَلَا يَقُلْ أحَدُكُم: عَبدِي وَأَمَتي، وَلْيَقُلْ: فَتَايَ وفَتَاتِي وَغُلَامِي».**

Hadisi ya tabbata cikin Sahihul Bukhari daga Abu Huraira -Radiyallahu anhu- Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Kar dayanku yace: ciyar da ubangijinka, kawo ma ubangijinka abin alwala, ya ce: maigidana, shugabana, kuma kar dayanku yace: bawana, ko baiwata, yace: Yaron gidana, kuyangata, karamin yarona ".

● “ **Kar dayanku yace: ciyar da ubangijinka, kawo abin alwala wa ubangijinka**: Saboda akwai ketare iyakar Rububiyya cikin hakan.

● **“ Ya ce: maigidana, shugabana":** Wannan maganar ana fiskantar da itace ga bawan, bawai umarni ne na wajibi ba, shiryar da shi ne zuwaga halaccin amfani da wannan lafazin, domin abinda malamai sukace shine: " idan umarni yazo bayan to yana nuni kan halacci ne ", kamar fadin Allah Ta'ala:

وَإِذَا حَلَلْتُمْ فَاصْطَادُواْ

[**idan kuka fita daga cikin ihrami to sai kuyi farauta** ].

● “ **Kuma kar dayanku yace** ”: Wannan hani ne na haramci ko makruhi, anyi hanin ne saboda kar lafazin yayi kama da bauta irin wacce ake nufin Allah - Maigirma da buwaya- shi kadai da ita, (( **Bawana** )): Ma yaron, (( **Baiwata** )) Ma yarinyar.

● “ **Yace**: Yaron gidana, kuyangata, **karamin yarona** ”: Wannan maganar zuwaga shugaban ne, wannan yana nuni kan cewa: idan Shari'a ta rufe kofar haramci se ta bude kofar halacci, sannan akwai fadakarwa cikin wannan kan wajabcin tace Tauhidi har a cikin lafuzza.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Anyi hani kan lafazin: ( Bawana, ko baiwata ).
2. Kar bawa yace: (ubangijina), kuma kar ace masa: (Ciyar da ubangijinka ).
3. Karantar da shi na farkon -Ubangidan- lafazin: (Yaron gidana, kuyangata, karamin yarona ).
4. Karantar da shi na biyun -yaron gidan- lafazin: ( Maigidana, shugabana ).
5. fadakuwa dangane da hikimar hanin, itace tace Tauhihidi har cikin lafuzza.

## [55] BABIN BA A HANA WANDA YA TAMBAYI WANI ABU DA SUNAN ALLAH (Haramun ne ko Makruhi )

Kashe kashen tambayar wani abu da Sunan Allah:

**Tambaya da Sunan Allah, da sigar:** kamar yace: ina rokon ka don Allah, -ina rokonka da ssunar Allah, ina gamaka da Allah-.

**Tambayar abu Shari'ar Allah:** Ma'ana: ya roki wani abunda Shari'a ta halatta; kamar wani mabukaci ya roki wata sadaka.

**Shin ya halatta mutum ya roki wani abu da Sunan Allah ko kuwa?**

Roko a karan kansa makruhi ne ko haramun, se idan har akwai bukatar rokon ko kuma idan ya zamo dole, Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yayi muba'aya wa sahabbansa kan cewa kar su roki mutane wani abu, dangane da amsawa ga wanda ya tambayi wani abu, mai tambaya baya fita daga dayan biyu:

**Rokon Zalla:** Kamar wani yace maka: (wane bani abu kaza ), idan Shari'a ta halatta abinda ya roka din, to se ka bashi (idan kanada shi ).

**Roko da sunan Allah:** wannan zaka bashi abinda ya roka koda bai cancanci a bashi ba, saboda yayi tambayar da sunan Allah maigirma, amsa masa girmama Allah ne, amma idan ya tambayi wani abinda bai halatta ba, ko kuma bashi wannan abun akwai cutarwa a ciki to ba za a amsa masa ba.

**DALILI NA FARKO:**

**عَنِ ابْنِ عُمَرَ ﭬ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «مَنِ اسْتَعَاذَ بِاللهِ فَأَعِيذُوهُ، وَمَنْ سَأَلَ بِاللهِ فَأَعْطُوهُ، وَمَنْ دَعَاكُمْ فَأَجِيبُوهُ، وَمَنْ صَنَعَ إِلَيْكُمْ مَعْرُوفًا فَكَافِئُوهُ، فَإِنْ لَمْ تَجِدُوا مَا تُكَافِئُوهُ فَادْعُوا لَهُ، حَتَّى تَرَوْا أَنَّكُمْ قَدْ كَافَأْتُمُوهُ». رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ وَالنَّسَائِيُّ بِسَنَدٍ صَحِيحٍ.**

Daga Abdullahi Ibn Umar -Allah ya kara yarda a garesu- yace: Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam yace-: " Wanda duk ya nemi tsari da Allah

To kubshi kariya, **kuma duk wanda ya rokeku da sunan Allah, to ku bashi,** kuma duk wanda ya kirayeku to ku amsa kiransa, kuma duk wanda ya aikata abu mai kyau a gareku to sai ku saka masa, idaan baku samu abinda zaku saka masa dashi ba, to sai kuyi masa addu'a, har kuji cewa kun saka masa ". Abu Dawu ne da Nasa'i suka rawaito da isnadi mai kyau.

● **" Ku bashi kariya "**: Sedai idan yanemi tsari daga wani abinda wajibi ne a kansa, ko kuma kan wani laifi da ketare iyaka -to wannan ba za a ba shi ba-.

● Shin amsa gaiyatar wani hakkin Allah ne ko hakkin dan Adam ? hakkin wanda yayi gaiyatan ne, shiyasa ma idan ka nemi wanda ya gaiyaceka da ya yafe maka sai ya amince to babu komai a kanka idan baka amsa gaiyatarba, amsar gaiyatar wajibi ne da umarnin Allah, amma idan ya yafe maka saboda kunyarka ba har cikin ransa ba, to bai kamata ba kaki amsa gaiyatarsa.

● **"Ku amsa masa"** : Ma'anar gayyata irinta karramawa, ba kiran sunan mutum ba, mafi yawan malamai sun tafi a kan cewa mustabbai ne amsa gayyata sedai idan na aure ne to wannan wajibi ne da sharudda masu zuwa:

1. Wanda yayi gaiyatar ya zamo baya daga cikin wadanda a ka wajabta kaurace musu ko aka Sunnanta.
2. Babu wani munkari a wajen da akayi gaiyatar, amma idan akwai munkari a wajen kuma zai iya gusar da munkari to wajibi ne a kansa ya halarta, domin amsa gaiyata da kawar da wannan munkarin.
3. Kasantuwar mai gaiyatar musulmi ne, idan ba musulmi ba ne to ba wajibi ba ne amsa gaiyatar.
4. Mai gaiyatar ya zamo yana neman kudi ta hanyar da ta halatta.
5. Kar amsa gaiyatar ta saryar da wani wajibi, ko taci karo da wajibin da ya fita karfi.
6. kar ya zamo akwai wata cutarwa kan wanda aka gaiyata, kamar yin bulaguro, ko rabuwa da iyalansa da suke bukatuwa zuwa gareshi a lokacin.

● **Shin katin gaiyaata ( invitation card ) da ake rabawa yana daidai da gaiyatar fada da baka?** idan a kasan, ko kuma zato maikarfi cewa an aika da katin gaiyatar musamman ga wani sanannen mutum, to hakika wanan yana daidai da gaiyatar fada da baka ne.

● **" To sai ku saka masa "**: Sakaiya tanada faidodi guda biyu:

1. Karfafa guiwar mutanen kirki wajen aikata alherin.
2. Hakika da wannan sakaiyar mutum zai tsira daga kaskancin da zai iya haduwa dashi wajen wannan da ya yi masa alherin.

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. A bada tsaro ga wanda ya nemi tsari da sunan Allah. ( Duk wanda ya nemi tsari da sunan Allah to wajibi ne a bashi tsaron, sedai idan ya nemi tsarin ne daga wani abun da wajibi ne a kansa aikata shi, ko barinsa, to wannan ba za a ba shi tsaro ba ).

2. Kar a hana mutumin da ya tambayi wani abu da sunan Allah.

3. Wajibi ne amsa gaiyata ( tareda kula da sharuddanta ).

4. A sakanta ma wanda yayi aikin alheri (ga wanda ya kyautata maka ).

5. Addu'a tana daidai da yin sakaiya ga wanda ba ya da abin da zai saka dashi (Sakaiya ne cikin hakan, kuma sakaiya ce ga wanda a al'adance ba a bayarda sakamako ma irinsa idan yayi wani alheri -Kamar sarki ko gwamna- ).

6. Fadinsa: " **Har sai kunji a jikinku cewa kun saka masa** " (Kar mutum yayi koro wajen addu'a, yayi ta addu'ar har sai ya gamsu cewa ya saka masa ).

## [56] BABIN BA A ROKON KOMAI DA FISKAR ALLAH SAI ALJANNAH

Ma'anar Tarjamar Babin:

Ma'ana: kar ka tambayi wani abu wajen halittu da fiskar Allah, domin halittu basu da ikon bayar da Aljannah.

ko kuma: idan har zaka roki wani abu da fiskar Aljannah, to sai ka roki Aljannah, kar ka roki wani abu daga lamurran duniya.

Cikin wannan akwai girmama Fiskar Allah, ta yanda bai halatta ba rokon wani abu da Fiskar Allah Maigirma face Aljannah kadai, ko abin da ze iya kaiwa gareta.

**DALILI NA FARKO:**

عَنْ جَابِرٍ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «**لَا يُسْأَلُ بِوَجْهِ اللهِ إِلَّا الْجَنَّةُ**»، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ.

Daga Jabir yace: Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yace: " **Ba a roko da fiskar Allah se Aljannah** " (Abu Daud ya rawaito).

- " **Da Fiskar Allah** " Cikin wannan hadisin akwai tabbatar wa Allah da sifar fiska, kamar yanda ya tabbata cikin Alqur'ani da Sunnah da Ijma'i, Fiska ce ta hakika wacce ba ta kama da fiskokin halittu.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Anyi hanin kan rokon wani abu da fiskar Allah sai makurar abun roko ( Domin yana daga cikan ladabi kar a tambayi wani abu da fiskar Allah se abin da ke alaka da lahira: Rabauta da Aljannah, ko tsira daga wuta ).
2. Tabbatar da sifar fiska ga Allah.

**HUKUNCIN ROKON SIFA:**

Rokon sifa baya halatta, kamar cewar wasu: Ya Rahamar Allah, ya Fiskar Allah, ya Buwayar Allah, wannan adduar bidi'a ce, bata tabbata ba cikin nassoshin shari'a, kuma bata tabbata ba daga Salaf, Shaikhul Islam ibn Taimiyyah Allah Ya jikansa ya ce: (rokon sifa kafirci ne).

## [57] BABIN ABIN DA YAZO CIKIN LAFAZIN (LAU)
## Ma'ana: ( BA DON ABU KAZA BA, TO DA KAZA...

Kashe kashen amfani da lafazin لو (Lau) tare da Ambaton hukuncinsu:

| | |
|---|---|
| **Haramun zai iya kaiwa ga kafirci:** idan akayi amfani ita wajen fito na fito da muzantawa ga Shari'a. | Fadin Munafukai: [ **Da munada wani abu daga al'amarin da ba a kashemu ba a nan** ]: Munafukai sunyi fito na fito da shari'ar Maanzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- sukace -dangane da wadanda aka kashe a Uhud-: da sunyi mana 'da a suka koma kamar yanda muka koma, da ba a kashe su ba, ma'ana: ra'ayinsu shine yafi alheri smada shari'ar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-. |
| **Haramun:** idan akayi amfani da ita domin fito na fito da kaddara. | Da fadin Munafukai: [ **Da sunyi mana da'a da ba a kashe su ba** ]: Ma'ana: da sun zauna basu fita yakin ba to da ba a kashe su ba, suna fito na fito d bore ga Shari'ar Allah. |
| **Haramun:** idan akayi amfani da ita domin nadama da bacin rai da bakin ciki. | ((**Da na aikata abu kaza da abu kaza ya kasance**)): Saboda yin nadama kan wani abu yana gadar wa rai da bacin rai da kunci, Allah kuma Yanaso mu zamo cikin yalwan zuci da annashawa. |
| **Haramun:** idan akayi akayi amfani da ita domin kafa hujja da kaddara a kan sabon Allah. | Fadin Mushirikai: [ **Da Allah Yaso da bamuyi shirka ba** ]: wannan karya ce, sedai ya halatta a kafa hujja da kaddara kan masiba, ba laifi ba, ana gane hakan ne ta hanyar tubar bawa da tubuwa daga sabon Allah. |
| **Idan akayi amfani da ita cikin alheri, to alherine, cikin sharri kuma sharri ne:** kamar amfani da ita wajen burace burace. | Kamar mutum yace: (( **Da inada dukiya da na aikata irin aiyukan wane -aikin alheri-** )), to wannan yayi fatan alheri, Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: ((**Shi yanada kwatankwacin niyyarsa, ladansu daya ne** )), Manzon Allah kuma yace dangane da wanda ya yi fatan sharri: ((**Shi yanada kwatankwacin niyyarsa to zunubinsu iri daya ne** )). |

**Halal:** idan akayi amfani da ita domin bada labari kadai.

Kamar fadin Annabi -Sallallahu alaihi waallam- " **Da zan dawo da baya gaba to da ban koro Hadaya ba** ": wannan labari ne, saboda Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- baya fatan wani abun da Allah Ya kaddara sabaninsa, kamar fadin wani: ( Da na halarci darasin da na fa'idantu ).

**DALILI NA FARKO:**

Da fadin Allah Ta'ala:

يَقُولُونَ لَوْ كَانَ لَنَا مِنَ الأَمْرِ شَيْءٌ مَّا قُتِلْنَا هَاهُنَا

[ **Suna cewa: da munada wani abu daga al'amarin da ba a kasha mu ba a nan** ]:. *(QS. Ali-Imran : 154)*.

**DALILI NA BIYU:**

Da fadin Allah Ta'ala

الَّذِينَ قَالُواْ لإِخْوَانِهِمْ وَقَعَدُواْ لَوْ أَطَاعُونَا مَا قُتِلُوا

***{ Wadanda suka ce ma yan'uwansu alhalin kuma sun zauna, da sun yi mana da'a da ba a kashe su ba… }****. (QS. Ali-Imran : 168).*

**DALILI NA UKU:**

**[٣] فِي الصَّحِيحِ عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ؓ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «احْرِصْ عَلَى مَا يَنْفَعُكَ، وَاسْتَعِنْ بِاللهِ، وَلَا تَعْجَزَنْ، وَإِنْ أَصَابَكَ شَيْءٌ فَلَا تَقُلْ: لَوْ أَنِّي فَعَلْتُ كَذَا لَكَانَ كَذَا وَكَذَا؛ وَلَكِنْ قُلْ: قَدَّرَ اللهُ، وَمَا شَاءَ فَعَلَ، فَإِنَّ لَوْ تَفْتَحُ عَمَلَ الشَّيْطَانِ».**

Hadisi yazo cikin Sahihul Bukhari daga Abu Huraira -Allah Ya kara yarda a gareshi- Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yace: " **Kayi kwadayi wajen abin da zai amfaneka, kuma ka nemi taimakon Allah, karka gajiya, idan wani abu yasameka kar kace: ai da na aikata abu kaza da abu kaza da kaza, sedai, kace: Allah Ya kadara, kuma Yana aikata duk abin da Yaso, domin LAU -Ba domin kaza ba da kaza- yana bude aiyukan shaidan** ".

● [ **Suna cewa:** **da munada wani abu al'amarin da ba a kasha mu ba a nan** ]: wannan daga fito na fiton munafukai a kan shari'ar Allah, domin su sun zargi Manzon Allah ne -Sallallahu alaihi wasallam- saboda yafita batareda amincewarsu ba.

● Kuma zai iya zamowa fito na fito ne da kaddarar Allah da ma'anar: ( Ba mu fita domin a kashe mu ba ).

● *{ Wadanda suka ce ma yan'uwansu alhalin kuma sun zauna, da sun yi mana da'a da ba a kashe su ba… }*: Cikin wannan magana tasu akwai fito na fito da muminai, sannan da kaddarar Allah da hukuncinsa, da ragontakar barin jihadi.

● Duk wanda yayi fito na fito da kaddarar Allah to wannan bai yarda da cewa Allah Shine Ubangiji ba, kuma bai tabbatar da tauhidin Rububiyyah ba.

● Wannan Hadisi ya kunshi:

1. Kwadayi wajen abin da zai amfani mutum, da barin abin da zai cutar da shi.
2. Neman taimako da Allah.
3. Himmatuwa wajen zartar da lamari mai muhimmanci, da cigaba cikinsa, babu tsayawa, wannan matakai ne da yakamata ka kula dasu.
4. Idan aka samu sabanin abin da mutum yakeso, to wannan ba daga gareka ba ne, iyaka da kaddarar Allah ce, don haka, ka mika dukkan lamurra ga Allah.

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Fassarar ayoyi biyu cikin Suratu Al-Imrana ( Ta farko: danganeda fito na fito da shari'ar Allah, ta biyu, dangane da fito na fito da kaddarar Allah ).

2. Anyi hani karara dangane da fdin: ( Da ni ), yayinda wani abu ya sameka.

3. An bayyana dalilin hanin da cewa: hakan yana bude aiyukan shaidan ( wanda ke saka mutum yin nadama da bacin rai ).

4. An shiryar damu zuwaga Magana maikyau, ("Allah ya riga Ya kaddara, kuma Yana aikata abin da Yaso " ).

5. Anyi umarni zuwaga abin da zai amfani mutum, tareda neman taimako da Allah.

6. Anyi hani kan kishiyan hakan, shine gajiyawa ( da sakaci ko kasala wajen aikata wani abu; domin hakan shine gwargwadon abinda mutum zai iya ).

## [58] BABIN HANI KAN ZAGIN ISKA (YARDA DA KADDARA)

**DALILI NA FARKO:**

عَنْ أُبَيِّ بْنِ كَعْبٍ ؓ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ □ قَالَ: «لَا تَسُبُّوا الرِّيحَ؛ فَإِذَا رَأَيْتُمْ مَا تَكْرَهُونَ فَقُولُوا:

اللَّهُمَّ إِنَّا نَسْأَلُكَ مِنْ خَيْرِ هَذِهِ الرِّيحِ، وَخَيْرِ مَا فِيهَا، وَخَيْرِ مَا أُمِرَتْ بِهِ، وَنَعُوذُ بِكَ مِنْ شَرِّ هَذِهِ الرِّيحِ، وَشَرِّ مَا فِيهَا، وَشَرِّ مَا أُمِرَتْ بِهِ»، صَحَّحَهُ التِّرْمِذِيُّ.

Daga Ubaiyu dan Ka'ab -Allah Ya kara yarda a gareshi- lallai Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " **Kar ku zagi iska; idan kukaga abin da ba ku so, sai kuce: ya Allah muna rokonka alherin wannan iskar, da alherin dake cikinta, da alherin da ka umarceta dashi, kuma muna neman tsarinka daga sharrin wannan iskar da sharrin abin da ke cikinta, da sharin da ka umarceta dashi** " ( Tirmzi ya inganta shi ).

● Zagin iska yanada kashe kashe kamar yanda ya gabata dangane da zagin zamani, mawallafin ya ware masa wannan babin ne saboda yawan aukuwarsa, kuma lallai ne anyi hani kan tsinuwa da zagi gaba daya, Manzon Allah -Sallallahu alaihi waallam- yace:

«لَيْسَ الْمُؤْمِنُ بِالطَّعَّانِ وَلَا اللَّعَّانِ وَلَا الْفَاحِشِ وَلَا الْبَذِيءِ»

" Mumini bai kasance mai yawan suka ba, kuma bai zamo mai yawan tsinuwa ba, ba mai alfahasha ba ne, kuma ba mai batsa ba ne ".

«لَا يَكُونُ اللَّعَّانُونَ شُفَعَاءَ وَلَا شُهَدَاءَ يَوْمَ الْقِيَامَةِ».

" **Masu yawan tsinuwa bazasu zamo masu ceto ko shaida ba a Ranar alkiyama** ".

● Gameda zagin mumini Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce:

سِبَابُ الْمُسْلِمِ فُسُوقٌ، وَقِتَالُهُ كُفْرٌ

" **Zagin musulmi fasikanci ne, yakarsa kuma kafirci ne** ".

● Gameda zagin matattu Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce:

لَا تَسُبُّوا الْأَمْوَاتَ؛ فَإِنَّهُمْ قَدْ أَفْضَوْا إِلَى مَا قَدَّمُوا

" **Kar ku zagi matattu, domin lallai ne su sun tafi zuwa ga abin da suka gabatar** ".

● Gameda zagin dabbobi, Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: لَا تُصَاحِبْنَا نَاقَةٌ عَلَيْهَا لَعْنَةٌ

“ **Duk rakumar da aka tsine mata, to baza ta bimu ba** ”.

● Gameda zagin mashashara, Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: لَا تَسُبُّوا الْحُمَّى

“ **Kar ku zagi mashashshara** ”.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Anyi hani kan zagin iska ( Wannan hani ne na haamci, domin zagin iska zagin wanda ya halicceta ne kuma ya aikota ).

2. An shiryar da mu zuwaga Magana mai amfanarwa yayinda wani yaga abin da ba ya so ( Ddaga cikinta mutum yace: Ya Allah ina rokonka…, sannan yayi riko da sabubba na zahiri, kamar ya kiyaye kansa daga sharrinta da katanga).

3. An shiryar da mu cewar ita wannan iskar umarni ba ta.

4. Lallai ne ana iya umartarta da alheri, kuma ana iya umartarta da sharri.

( Abin nufi: wajibi ne a an mutum kar yayi fito na fito da kaddarar Allah, da hukuncinsa kuma kar ya zagi wani abu daga ciki, ya kasance mai mika wuya ga lamurran da Allah Ya kaddara, kamar yanda ya wajaba a kansa mika wuya ga abubuwan da Allah Ya shar'anta, domin wadannan halittu basa mallakan aikata wani abu a karan kansu sai da umurnin Allah.

## [59] BABIN FADIN ALLAH TA'ALA:

يَظُنُّونَ بِاللَّهِ غَيْرَ الْحَقِّ ظَنَّ الْجَاهِلِيَّةِ يَقُولُونَ هَل لَّنَا مِنَ الأَمْرِ مِن شَيْءٍ قُلْ إِنَّ الأَمْرَ كُلَّهُ لله

*[ SUNA ZATON ABIN DA BA SHI NE GAKIYA BA A GAME DA ALLAH, IRIN ZATON JAHILIYYAH, SUNA CEWA: SHIN KO A KWAI WANI ABU A GARE MU DAI DAGA LAMARIN?, KA CE LALLE NE AL'AMARIN DUKKANSA NA ALLAH NE…](QS. Al`-Imran : 154).*

● **" Suna zato ga Allah "**: ( Munafukai ), Zato irin na addinin jahiliyyah wanda mai zato bai san matsayin Allah da girmarsaba a cikinta, zatone na karya wanda aka ginashi a kan jahilci, zato ga Allah ya kasu iri biyu:

1. **Kyautata zaton alhairi ga Allah**, wannan yanada rassa biyu:

a. Wanda yakeda alaka da aiyukan Allah cikin halittunsa; wajibine ka kyautata zato wa Allah cikin wannan.

b. wanda yakeda alaka da yanda Allah zaiyi da kai; wajibene kayi zato mafi kyawu ga Allah, da sharadin samuwar abin da yake wajabta kyakkyawar zaton a wajenka, sune: yin ikhlasi cikin bauta, da biyayya ga Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- cikin dukkan ibada.

2. **Munana zato ga Allah:** kamar yayi zaton cewa akwai wauta da zalunci cikin aiyukan Allah ko makamancin hakan, wannan yana daga manyan abubuwan da aka haramta, kuma yana cikin zunubai mafi muni, kamar yanda munafukai da wadansunsu sukayi zaton abinda ba gaskiyaba ga Allah.

**DALILI NA BIYU:**

الظَّانِّينَ بِاللَّهِ ظَنَّ السَّوْءِ عَلَيْهِمْ دَائِرَةُ السَّوْءِ

*Masu zaton mugun zato game da Allah, mugunyar masifa mai kewayewa ta tabbata a kansu (QS. Al-Fath : 6).*

● Abin nufi da wadannan: sune munafukai da mushrikai, alhalin sune wadanda munana suka gewaye su ta kowani janibi.

قَالَ ابْنُ الْقَيِّمِ فِي الآيَةِ الْأُولَى: «فُسِّرَ هَذَا الظَّنُّ بِأَنَّهُ سُبْحَانَهُ لَا يَنْصُرُ رَسُولَهُ، وَأَنَّ أَمْرَهُ سَيَضْمَحِلُّ، وَفُسِّرَ بِأَنَّ مَا أَصَابَهُ لَمْ يَكُنْ بِقَدَرِ اللهِ وَحِكْمَتِهِ. فَفُسِّرَ بِإِنْكَارِ الْحِكْمَةِ وَإِنْكَارِ الْقَدَرِ وَإِنْكَارِ أَنْ يُتِمَّ أَمْرَ

رَسُولِهِ، وَأَنْ يُظْهِرَهُ عَلَى الدِّينِ كُلِّهِ، وَهَذَا هُوَ ظَنُّ السَّوْءِ، الَّذِي ظَنَّ الْمُنَافِقُونَ وَالْمُشْرِكُونَ فِي سُورَةِ الْفَتْحِ. وَإِنَّمَا كَانَ هَذَا ظَنَّ السَّوْءِ؛ لِأَنَّهُ ظَنُّ غَيْرِ مَا يَلِيقُ بِهِ سُبْحَانَهُ، وَمَا يَلِيقُ بِحِكْمَتِهِ وَحَمْدِهِ وَوَعْدِهِ الصَّادِقِ. فَمَنْ ظَنَّ أَنَّهُ يُدِيلُ الْبَاطِلَ عَلَى الْحَقِّ إِدَالَةً مُسْتَقِرَّةً يَضْمَحِلُّ مَعَهَا الْحَقُّ، أَوْ أَنْكَرَ أَنْ يَكُونَ مَا جَرَى: بِقَضَائِهِ وَقَدَرِهِ، أَوْ أَنْكَرَ أَنْ يَكُونَ قَدَّرَهُ لِحِكْمَةٍ بَالِغَةٍ يَسْتَحِقُّ عَلَيْهَا الْحَمْدَ، بَلْ زَعَمَ أَنَّ ذَلِكَ لِمَشِيئَةٍ مُجَرَّدَةٍ، فَذَلِكَ ظَنُّ الَّذِينَ كَفَرُوا، فَوَيْلٌ لِلَّذِينَ كَفَرُوا مِنَ النَّارِ. وَأَكْثَرُ النَّاسِ يَظُنُّونَ بِاللهِ ظَنَّ السَّوْءِ فِيمَا يَخْتَصُّ بِهِمْ، وَفِيمَا يَفْعَلُهُ بِغَيْرِهِمْ، وَلَا يَسْلَمُ مِنْ ذَلِكَ إِلَّا مَنْ عَرَفَ اللهَ وَأَسْمَاءَهُ وَصِفَاتِهِ، وَمُوجِبَ حِكْمَتِهِ وَحَمْدِهِ. فَلْيَعْتَنِ اللَّبِيبُ النَّاصِحُ لِنَفْسِهِ بِهَذَا، وَلْيَتُبْ إِلَى اللهِ، وَيَسْتَغْفِرْهُ مِنْ ظَنِّهِ بِرَبِّهِ ظَنَّ السَّوْءِ. وَلَوْ فَتَّشْتَ مَنْ فَتَّشْتَ؛ لَرَأَيْتَ عِنْدَهُ تَعَنُّتًا عَلَى الْقَدَرِ وَمَلَامَةً لَهُ، وَأَنَّهُ كَانَ يَنْبَغِي أَنْ يَكُونَ كَذَا وَكَذَا، فَمُسْتَقِلٌّ وَمُسْتَكْثِرٌ، وَفَتِّشْ نَفْسَكَ هَلْ أَنْتَ سَالِمٌ؟ (فَإِنْ تَنْجُ مِنْهَا تَنْجُ مِنْ ذِي عَظِيمَةٍ وَإِلَّا فَإِنِّي لَا إِخَالُكَ نَاجِيًا)».

Imam Ibnul Qayyim ya ce, gameda ayar farko: (( An fassara wannan zaton da cewara Allah Subhanahu bazai taimaki Annabinsa ba, kuma lamarinsa zai lalace, kuma an fassara da cewar abinda ya sameshi bai zamo da kaddarawar Allah da hikimarsa ba, wato an fassara da inkarin hikimar Allah da kaddararsa, da inkarin cewar lamarin Manzon Allah bazai cika ba, kuma Allah bazai daukaka shi bisa dukkan addinai ba, wannan shine munana zato da munafukai sukayi, wanda aka labarta a cikin Suratul Fathi, kuma yazamo mummunar zato ne saboda zatone da bai dace da Allah Maitsarki ba, kuma bai dace da hikimarsa ba, bai dace da gidiyarsa ba, kuma bai dace ba da alakrinsa na gaskiya, duk wanda yazaci cewar Allah zai dora karya a kan gaskiya dorawa ta har abada, wacce zata kawar da gaskiya gaba daya, to ko kuma ya muzanta cewa: abubuwan da suke gudana ba da hukuncin Allah da kaddarawarsa ba ne, ko yayi inkarin cewar: bai hukunta wani abu da hikimarsa to wacce takai matuka ba, wanda Ya cancanci a gode maSa a kai ba, A'a, kawai shi ya riya cewar duk abubuwan da suke gudana suna gudan ne bisa kanin damar Allah zalla wanda bai da alaka da wata hikima, wannan zatone na wadanda suka kafirce wa Allah, Azabar wuta ta tabbata ga kafirai, kuma mafi yawan mutane suna munana zato ga Allah cikin lamurransu, da yanda Allah zai aikata dasu, babu wanda yake kubuta daga wannan sai wanda yasan Allah, da sunayensa da sifofinsa, sannan yasan wajabcin hikimar allah da godiyarSa, don haka, mutum maihankali, mai nasiha wa kansa sai ya kula da wannan, sannan ya tuba zuwaga Allah, kuma ya nemi gafararSa daga mummunar zaton da yayi wa Allah, da zaka binciki duk wanda ka samu damar bincikarSa; to da kaga ta'annuti a kan kaddara da zargi gareta, da ganin cewa da abu kaza da kaza ne yakamata ba kaza ba, tsakani mai takaita hakan da mai yawaitawa, don haka kabinciki kanka, shin ka kubuta daga wannan?

فَإِنْ تَنْجُ مِنْهَا تَنْجُ مِنْ ذِي عظيمَةٍ ... وَإِلّا فَإِنِّي لَا إِخَالُكَ نَاجِيًا

**((( Idan ka kubuta daga wannan to lallai ka kubuta daga abu maigirma idan ba hakaba kuma to bana zaton zaka tsira )))**

● Ibnul Qayyim Allah Ya jikansa ya ambaci wannan maganarce a cikin littafinsa: ((Zadul Ma'ad)) a karshen magana kan yakin Uhud, karkashin Magana kan hikimomin Allah kyawawa wadanda suka kasance cikin wannan yakin.

**Takaitattun abubuwan da ya ambata kan munana zato:**

1. Zaton cewar Allah zai taimaki karya ya dorata a kan gaskiya, har abada.
2. Inkarin cewa abubuwan da suka faru ba da kaddarar Allah, da hukuntawarSaa ba ne, ta yaya wani abu zai faru cikin Mulkin Allah wanda bai kaddara faruwarsa ba?.
3. Ya muzanta cewa: abubuwan da Allah Ya kaddara su, saboda hikima ce wacce takai matuka, wanda ya cancanci godiya a kayi.

**● Takaitattun abubuwan da ya ambata wajen magance munana zato ga Allah:**

1. Sanin Sunayen Allah da SifofinSa, sani na gaskiya, ba sani irin na karkatar da ma'anoninsu ta tawilinsu ba.
2. Himmatuwar duk mai hankali da wannan lamari, har ya ringa kyauta zato wa Allah zaton gaskiya, ba munana zato irin na jahiliyya ba.
3. Komawa ga Allah da tuba daga zunubbai zuwaga 'da'a da neman gafara .
4. Ka ringa zargin kanka, saboda mutum yana sifantuwa da tawaya da mummuna.

*MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Tafsirin Suratu Ali-Imran (***Suna zaton abinda ba gaskiya ba game da Allah***). Lamirin zancen yana komawa kan Munafukai ne.

2. Tafsirin ayar Surat Al-Fath (***Masu zaton mugun zato game da Allah, mugunyar masifa mai kewayewa ta tabbata a kansu***). Lamirin zancen yana komawa kan Munafukai ne.

3. An bada labarin cewa munana zato yanada nau'uka masu yawa ( Hakikaninsa shine ayi wa Allah zaton abinda bai dace dashi ba).

4. Babu wanda zai kubuta daga wannan sai wanda yasan Sunayen Allah da SifofinSa, kuma yasan kanSa ( ya binciketa, domin lallai mutum yanada sifar tawaya da munanawa, amma Ubangiji -Maigirma da buwaya- Shi Mai cikakkiyar Kamala ce, wanda ya tsarkaka daga dukkan tawaya ta kowace irin fiska ).

## [60] BABIN ABINDA YAZO NA HUKUNCIN MASU MUSUN KADDARA
### ( Babban kafirci ne )

● Al-Qadar ( Kaddara ): Sirrin Allah ne cikin halittunsa, ba ma saninta se bayan aukuwarta, kaddara tanada alaqa da Tauhidin Rububiyyah a kebe, kuma tanada alaqa da Tauhidin Asma'u was-Sifat, mutane dangane da qaddara sun kasu bangare Uku:

1. **Kungiyar Jabariyyah:** sun tabbatar da qaddara tareda wuce gona da iri, har suka tabbatar da cewa: bawa bayada zabi ko iko cikin aiyukansa.
2. **Kungiyar Qadariyah Almu'tazilah:** sun tabbatar wa bawa da zabi, da iko cikin aiyukansa, har suka wuce iyaka wajen tabbatar da hakan, har suka kore ganin daman Allah cikin aiyukan bawa, kuma sukace: Allah bai halicci aiyukan bayiba.
3. **Ahlu Sunnah Waljama'ah:** Sun tattaro dukkan dalilan babin sannan suka bi tafarkin mafificin addini, sukayi imani da qaddarar Allah, sun tabbatar wa bawa iko da zabi wanda suke rataye da ganin damar Allah.

**CIKIN IMANI DA QADDARA AKWAI FAIDODI MASU YAWA DAGA CIKI:**

1. Imani da kaddara yana daga cikan Tauhidur Rububiyyah .
2. Yana wajabta gaskiyar dogaro ga Allah.
3. Yana wajabta wa zuciya da natsuwa, idan kasan cewa duk abin da ya sameka to bai zamo abin da zai kubuce maka ba, kuma duk abin da ya kubuce maka, to bai zamo abn da zai sameka ba, kana samun natsuwa kan duk abin da ya same ka bayan ka aikata dukkan sabubban da suka dace.
4. Imani da qaddara yana hana mutum ruduwa da iliminsa, yayinda ake gode masa bisa wani aiki da ya aikata, saboda yasan cewa Allah ne Ya yi masa baiwar wannan ilmin.
5. Bawa bazaiyi bakin cikiba kan duk abun da ya same shi, domin yasan cewa daga Allah ne, ya faru ne daga Rahamar Allah da Hikimarsa.
6. Lallai mutum yana yin riko da sabubba, saboda imaninsa da Hikimar Allah, kuma yasan cewa Allah baya qaddara abubuwa sai Ya gwama su da sabubbansu.

**DALILI NA FARKO:**

وَقَالَ ابنُ عُمرَ: وَالَّذِي نَفْسُ ابْنِ عُمَرَ بِيَدِهِ، لَوْ كَانَ لَأَحَدِهِم مِثْلُ أُحُدٍ ذَهَبًا، ثُمَّ أَنْفَقَهُ فِي سَبيلِ اللهِ؛ مَا قَبِلَهُ اللهُ مِنْهُ، حتَّى يُؤمِنَ بِالقَدَرِ، ثمَّ استَدَلَّ بِقَوْلِ النَّبيِّ ﷺ: «**الْإِيمَانُ: أَنْ تُؤْمِنَ بِاللهِ وَمَلائِكَتِهِ وَكُتُبِهِ وَرُسُلِهِ وَاليَومِ الآخِرِ، وَتُؤمِنَ بِالقَدَرِ خَيْرِهِ وَشَرِّهِ**» رَوَاهُ مُسْلِمٌ.

Ibnu Umar -Allah Ya kara yarda dashi-: ya ce: ( ina rantsuwa da wanda rayuwar Ibnu yake hanunsa, da dayansu zai mallaki kwatankwacin dutsin Uhud na zinare, sannan ya ciyar dashi a hanyar Allah, Allah bazai karbi ciyarwarsa ba har sai yayi imani da qaddara, ya kafa hujja kan haka da fadin Annabi -Sallallahu alaihi wasallam-: " **IMANI: shine: kayi imani da Allah, da Mala'ikunsa, da Litattafansa, da Manzanninsa, da Ranar Lahira, da Qaddara mai kyau da mummuna** ") ( Muslim ne ya rawaaito ).

Imani: Magana ce da harshe, da kudirin zuci, da aiki da gabbai, yana karuwa da aiyukan 'da a, kuma yana raguwa da sabon Allah, yanada rukunnai shida:

- Imani da Allah.
- Imani da Mala'ikun Sa.
- Imani da Litattafan Sa.
- Imani da Manzanni nSa.
- Imani da ranar Lahira.
- Imani da Qaddara, alhairi da sharri.

● " **Kayi imani da Allah** ", imani da Allah ya kunshi abubuwa hudu:

- Imani da samuwar Allah, na tabbatuwa da:
- Tauhidur Rububiyyah
- Tauhidul Uluhiyyah
- Tauhidul Asma'u was-Sifat

**Hankali:** baya taba tunanin samuwar wata halitta ba tareda wanda yayi halittan ba [ **Shin an halitta su ne daga ba daga kome ba, ko kuwa su ne masu yin halitta** ].

**Zahiri:** mutum yakan samu kansa cikin bakin ciki, da tsanani, sannan ya roki Allah, sai Allah Ya Yaye masa wannan bakin cikin, kamar yanda Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- yayi addu'a a yakin Uhud.

**Fidrah:** Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " **ko wani yaro ana aihuwar sa ne a kan fidrah, Iyayensa biyu su suke mayar dashi bayahude ko banasare...** ".

**Shari'a:** Imam Ibnul Qayim -Allah Ya jikansa- ya ce: (babu wata cikin alqur'ani face akwai dalilin Tauhidi a cikinta ).

● **" Da Mala'ikunsa ":**

Malaiku halittu ne boyayyu, Alllah Ya halittasu daga haske, sunayin 'da a ga Allah ba sa saba masa, sunada rayuka, Allah Ta'ala Ya ce:

قُلْ نَزَّلَهُ رُوحُ الْقُدُسِ مِن رَّبِّكَ بِالْحَقِّ

***" Kace, Ruhul Qudusi (Jibril) ne ya sassaukar da shi -Al Qur'ani- daga Ubangijinka da gaskiya ".***

Kuma sunada jiki, Allah Ta'ala Yace:

جَاعِلِ الْمَلَائِكَةِ رُسُلاً أُولِي أَجْنِحَةٍ مَّثْنَى وَثُلَاثَ وَرُبَاعَ يَزِيدُ فِي الْخَلْقِ مَا يَشَاءُ

***[ Mai sanya Mala'iku manzanni ma'abota fukafukai, bibbiyu, da uku uku, da hurhudu, yana karawar abin da ya ke so a cikin halittar ].***

Kuma sunada hankula da zukata, Allah Ta'ala Ya ce:

حَتَّى إِذَا فُزِّعَ عَن قُلُوبِهِمْ قَالُوا مَاذَا قَالَ رَبُّكُمْ

***[ Har a lokacin da aka yaye tsoro daga zukatansu sai suce menene Ubangijinku Ya ce?].***

Munyi imani da su, da abin da Allah Ya sanar da mu na sunayensu, (kamar: Jibrilu, da Mika'ilu, da Isra'filu ), kuma munyi imani da sifofinsu, Allah Ta'ala Ya ce:

لَا يَعْصُونَ اللَّهَ مَا أَمَرَهُمْ وَيَفْعَلُونَ مَا يُؤْمَرُونَ

***[ Ba su saba wa Allah kan abin da Ya umarce su, kuma suna aikata abinda ake umurnin su ]."***

Kuma munyi imani da aiyukansu, (Misali: daga cikinsu akwai: wadanda suke dauke da Al'arshin Allah), sannan munyi imani da dukkan abin da Allah da Manzanninsa suka labarta mana dangane da su.

● **" Da Litattafansa ":**

Wajibi ne muyi imani da cewa litattafan da Allah Ya saukar dukkaninsu maganar Allah bisa hakika ba majazi ba, kuma saukakku ne daga Allah ba halitta ba ne, kuma Allah Ya saukar ma kowani Manzo littafi, munyi imani da su, da abin da Allah Ya labarta mana na sunayensu, da labaransu, da hukunce hukuncensu, a dunkule kuma a rarrabe, matukar ba a shafe hukuncinsu ba, kuma munyi imani da cewa Alqur'ni ya shafe dukkan Litattafan da a ka saukar

Gabaninsa, sune: At- Taurat, Injil, Zabur, Suhuf Ibrahim, da Suhuf Musa (Alaihimus Salam ).

● **" Da Manzanninsa ":**

Wajibi ne muyi imani da cewa su mutane ne, basu mallakar wani abu daga kebantattaun Rububiyyah, kuma su bayi ne, ba a bauta musu, kuma aallah Ya auko su sannan Ya saukar musu da wahayi, kuma Ya karfafe su da ayoyi, sannan hakika sun sauke isar da amanar da Allah Ya daura mu su, kuma sun yi nasiha wa al'umma, sun isar da sako, sunyi jihadi a hanyar Allah hakikanin jihadi, munyi imani da su, da abin da Allah Ya sanar da mu na sunayensnu, da Sifofinsu, da labaransu, kuma Annabin farko shine: Annabi Adamu -Alaihis salam- kuma Annabi Nuhu -Alaihis Salam- shine: farkon Manzanni, Annabi Muhammad -Sallallahu alaihi wasallam- shine cika makon Annabawa da Manzanni, kuma hakika Shari'ar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ta share dukkan shari'oin baya, Kuma Ulul Azmi su biyar ne, ambatonsu yazo cikin Surat Ash, shura da Ahzab, sune: ( Muhammad, Nuh, Ibrahim, Musa, Isah -Alaihimus Salam- ).

● **" Da Ranar karshe ":**

Imani da ranan qiyama ya kunshi imani da dukkan abin da Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya bada labari dashi na abubuwan da zasu kasance bayan mutuwa, kamar: fitinar kabari, da busa cikin kaho, da tashin mutane daga kaburburansu, da Mizani, da bada takardun aiyuka wa bayi, da Siradi, da Tafkin ruwa (Al-Haud), da Ceto, da Aljannah, da Wuta, da ganin muminai Ubangijinsu, a filin qiyama da cikin Aljannah, da wasunsu na lamurran gaibu.

● **" Kuma kayi imani da Qaddara ":**

Ya maimata Kalmar ( Kayi imani ), saboda imani da kaddara yanada matukar muhimanci, sannan imani da qaddara yanada matakai guda hudu:

عِلْمٌ، كِتَابَةٌ مولَانَا، مَشِيْئَتُه        وَخَلْقُهُ وَهُو إِيْجَادٌ وَتَكْوِيْنُ

*Ilimin Ubangiji, da rubutunSa, sannan Mashi'arSa*

*HalittarSa, shine: samar da halittu daga rashi zuwa samuwa.*

**Ilimin Allah:** Yin imani da cewa Allah Yasan komai a dunkule kuma yasan shi filla filla, dalili fadin Allah Ta'ala: [ **Yana sanin abin da ke a gaba garesu da abin da ke a bayansu**]. *(QS. Al-Baqarah: 255).*

**RubutunSa:** imani da cewa Allah Ya rubuta kaddarar komai har zuwa ranar tashin alqiyamah, dalili kan haka fadin Allah Ta'ala: [ **Kuma babu wata mai boyuwa a cikin sama da kasa face tana a cikin littafi bayyananne** ]. *(QS. An-Naml: 75).*

**Mashi'arSa:** imani da cewa duk abin da Allah Yaso kasantuwarsa, to zai kasance, babu makawa, kuma abin da Allah baiso kasantuwarsa ba to bazai kasance ba, kuma bawa yanada zabi wanda yake karkashin ganin daman Allah [ **Kuma ba za ku so ba, sai Allah Yaso** ] *(QS. Al-Insan: 30).*

**HalittarSa:** babu wani abu cikin abubuwa face Allah ne Ya halicce shi, kuma shi Yake jujjuya shi, Sannan shine Mai cikkakken iko a kansa, har aiyukan da bawa yake aikatawa Allah ne Ya halicce shi: [ **Alhali Allah ne Ya halitta ku da abin da kuke aikatawa** ]. *( As-Sa'fa'at: 96).*

**DALILI NA BIYU:**

وَعَنْ عُبَادَةَ بْنِ الصَّامِتِ؛ أَنَّه قَالَ لِابْنِهِ: يَا بُنيَّ ؛ إِنَّكَ لَنْ تجِدَ طَعْمَ الْإِيْمَانِ حَتَّى تَعْلَمَ أَنَّ مَا أَصَابَكَ لَمْ يَكُنْ لِيُخْطِئَكَ، وَمَا أَخْطَأَكَ لَمْ يكُنْ لِيُصِيبَكَ، سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُولُ: «**إِنَّ أَوَّلَ مَا خَلَقَ اللهُ الْقَلَمُ، فَقَالَ لَهُ: اكْتُبْ، فَقَالَ: رَبِّ! وَمَاذَا أَكْتُبُ؟ قَالَ: اكْتُبْ مَقَادِيرَ كُلِّ شَيْءٍ حَتَّى تَقُوْمَ السَّاعَةُ**»، يا بُنَيَّ سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ ﷺ يقولُ: «**مَنْ مَاتَ عَلَى غَيْرِ هَذَا فَلَيْسَ مِنِّي**»، وَفِي رِوَايَةٍ لِأَحْمَدَ: «**إِنَّ أَوَّلَ مَا خَلَقَ اللهُ تَعَالَى الْقَلَمُ، فَقَالَ لَهُ: اكْتُبْ، فَجَرَى فِي تِلَكَ السَّاعَةِ بِمَا هُوَ كَائِنٌ إِلَى يَوْمِ الْقِيَامَةِ**».

Daga Ubadah bn Samit; ya ce wa dansa: ya kai dana; Lallai kai bazaka samun dandanon imani ba har sai kasan cewa duk abin da ya sameka to bazai kubuce maka ba, kuma duk abin da ya kubuce maka, to bai zamo wanda zai sameka ba, naji Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yana cewa " **Farkon abin da Allah Ya halitta shine Alkalami, sai yace masa: ka yi rubutu, sai ya ce: ya Ubangiji! me zan rubuta? sai ya ce: rubuta kaddarorin komai har qiyama ta tsaya** ", ya kai dana naji Manzon Allah -Sallallahu alihi wasallam- yana cewa: " **Duk wanda ya mutu ba akan wannan ba, to ba ya tare da ni** ",

A cikin wata riwayar ta Al-Imam Ahmad: " Lallai farkon abin da Allah Ta'ala Ya fara halitta shine Alkalami, sai yace dashi: Rubuta, sai ya rubuta a wannan lokacin duk abin da zai faru har zuwa tashin Alqiyama ".

**DALILI NA UKU:**

وَفِي رِوَايَةٍ لِابْنِ وَهْبٍ: قَالَ رَسُولُ اللهُ ﷺ: «فَمَنْ لَمْ يُؤمِنْ بِالقَدَرِ خَيرِهِ وشرِّهِ؛ أَحْرَقَهُ اللهُ بِالنَّارِ».

A cikin wata riwayar ta Ibn Wahab, Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: " Duk wanda baiyi imani da Qaddara ba, alhairinsa da mummunarsa, sai Allah Ya kona shi da wuta ".

**DALILI NA HUDU:**

وَفِي «الْمُسْنَدِ» وَ«السُّنَنِ» عَنِ ابْنِ الدَّيْلَمِيِّ؛ قَالَ: أَتَيْتُ أُبَيَّ بنَ كعْبٍ، فَقُلْتُ: فِي نَفْسِي شَيْءٌ مِنَ القَدَرِ، فَحَدِّثْنِي بِشَيءٍ لَعَلَّ اللهَ يُذْهِبُهُ مِنْ قَلْبِي، فَقَالَ: «لَوْ أنفقْتَ مِثْلَ أُحُدٍ ذَهبًا، مَا قَبِلَهُ اللهُ مِنْكَ؛ حَتَّى تُؤمِنَ بِالقَدَرِ، وَتَعْلَمَ أَنَّ مَا أَصَابَكَ لَمْ يَكُنْ لِيُخْطِئَكَ، وَمَا أَخْطَأَكَ لَمْ يَكُنْ لِيُصِيبَكَ، وَلَوْ مِتَّ عَلَى غَيْرِ هَذَا لَكُنْتَ مِنْ أَهْلِ النَّارِ، قَالَ: فَأَتَيْتُ عَبْدَ اللهِ بْنَ مَسْعُودٍ، وَحُذَيفةَ بْنَ الْيَمَانِ، وَزَيْدَ بْنَ ثَابِتٍ؛ فَكُلُّهُمْ حَدَّثَنِي بِمِثْلِ ذَلِكَ عَنِ النَّبِيِّ ﷺ»، حَدِيثٌ صَحِيحٌ، رَواهُ الحَاكِمُ فِي «صَحِيحِهِ».

Hadisi yazo cikin littafin: " Musnad " da " Assunan " daga Ibn Addailami; yace: nazo wajen Ubaiyu bn Ka'ab, se nace dashi: a cikin raina akwai wani abu na kokwanto dangane da qadara, don haka kabani labarin wani abu mai yuyuwa Allah Ya tafiyar dashi daga zuciyata, sai yace: (( Da zaka ciyar da kwatankwacin dutsin Uhud na zinari, Allah ba zai karba ba daga gareka har sai kayi imani da qaddara, kuma har sai kasan cewa duk abin da ya sameka bazai kubuce maka ba, kuma duk abin da ya kubuce maka, to bazai sameka, da zaka mutu a kan wanin wannan to lallai da ka zamo cikin yan'wuta, ya ce: sai nazo wajen Abdullahi dan Mas'ud, da Huzaiftu dan Al Yaman, da Zaid dan thabit sai dukkaninsu suka labarta min kwatankwacin wannan daga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- )). Hadisi ne Sahihi, Hakim ne ya rawaito shi cikin (( Sahinhinsa )).

● **" Har sai kasan "**: Allah Ta'ala Ya yi ishara zuwaga wannan ma'anar cikin fadinSa:

مَا أَصَابَ مِن مُّصِيبَةٍ فِي الْأَرْضِ وَلَا فِي أَنفُسِكُمْ إِلَّا فِي كِتَابٍ مِّن قَبْلِ أَن نَّبْرَأَهَا إِنَّ ذَلِكَ عَلَى اللَّهِ يَسِيرٌ (٢٢) لِكَيْلَا تَأْسَوْا عَلَى مَا فَاتَكُمْ وَلَا تَفْرَحُوا بِمَا آتَاكُمْ وَاللَّهُ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ (٢٣)

**[ Wata musiba ba zata auku ba sameka a cikin kasa, ko cikin rayuwanku face tana a cikin littafi tun tun gabanin mu halitta ta, lallai wannan**

**Ga Allah mai sauki ne.(22) Domin kar ku yi bakin ciki kan abin da ya kubuce muku, kuma kar kuyi alfahari da abin da Ya baku, Allah ba Ya son dukkan wani maitakama mai fariya** ].

*. (QS. Al-Hadid 22-23).*

● **" Ya kai dana "** : Cikin wannan akwai tausasawa ma 'ya'ya wajen wa'azi, kuma lallai yakamata a karantar da 'ya'ya hukunce hukunce da dalilansu: [1] Domin ka sabar wa danka da bin dalilan Shari'a. [2] Sannan ka tarbiyyantar dashi bisa son Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-.

● **" Wani abu cikin raina "**: abin da ya auku cikin ran Dailami dalili ne akan hadarin zama da 'yan bidi'a wadanda suke shakka cikin Qaddara, ana tunkude shubuha ne da dalilin Shari'a sai ya kawar da ita, ba da hankali ba, sai ya kara girmar shubuhar.

● الْقَلَمُ: Alkalami, akwai riwayoyi biyu tabbatattu: Domma الْقَلَمُ da Fatha الْقَلَمَ:

1. **Domma:** Ma'anar zata zamo cewa: Alkalami shine abin da Allah Ya fara halitta dangane da abubuwan da muke iya ganinsu kadai na halittu, Kaman Sammai da Kassai, Imam ibnul Qayyim Rahimahullahu ya ce:

Mutane sunyi sabani dangane da alqalamin da<br>
Aka rubuda Qaddara dashi daga Allah (Mai sakamako)<br>
Shin Alkalamin aka fara halitta ko Al'arshi ne farko<br>
Akwai maganganu biyu wajen Abul ‘Ala Al-Hamazani<br>
Maganar gaskiya hahlittar Al'arshi ta rigaya domin<br>
Tun kafin **rubutu Al'arshi yana nan a yanda yake**

2. **Nasba:** Sai ma'anar ta zamo cewa: Allah Ya umarci Alkalami da yayi rubutu yayin farkon halittarsa.

## *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Bayani kan cewa imani da Qaddara farilla ce cikin Farillai.
2. Bayanin sifar imani da Qaddara ( wajibi ne muyi imani da martabobi hudu, Ilimi, Rubutu, Mashi'a, Halitta ).
3. Lalacewar aiyukan wanda baiyi imani da qaddara ba ( Kafiri ne babbar kafirci ).
4. An bada labarin cewa babu mai samun dandanon imani sai wanda yayi imani da kaddara.
5. An bada labarin abin da Allah Ya fara halitta ( babu shakka halittan Alkalami ya biyo bayan halittan Al'arshi ne, Alkalami shine farkon halitta dangane da abubuwan da muke iya ganinsu , halittansa ya rigayi halittan sammai da kassai, kan haka, farkon takar halittar alkalami ya kebanci abubuwan da ake gani ne ).
6. Alkalami ya rubuta abubuwan da Allah Ya qaddara faruwarsu tun daga wannan lokacin har zuwa tashin Alkiyama ( ciki akwai dalili kan cewa Allah

Yana Magana da abubuwan da basuda rai, kuma suna hankaltar umarnin Allah, domin Allah Ya fiskantar da Magana zuwa ga Alkalami kuma yaji maganar Allah sannan ya amsa masa ).

7. Barrantar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- daga duk wanda baiyi imani da qaddara ba ( kafiri ne irin kafircinda yake fitar da mutum daga musulunci ).

8. Al'adar Magabata wajen kawar da Shubuha itace: tambayar malamai ( wannan yana nuni kan halaccin tambayar samada malami daya domin samun tabbaci kan hukunci ba domi bibiyar rangwami ba ).

9. Hakika Malamai sun amsa masa da abin da zai kawar da shubuha, saboda sun jingina Maganarsu ne zuwaga Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- shi kadai ( da hakane kuma dukka wata shubuha take gushewa daga mumini, babu laifi a kafa hujjah da dalilai na hankali da na zahiri domin gamsar da abokin husuma, da kuma Kara samun yakini ga wanda yayi imani, sannan kuma, akwai dalili na hudu a ciki shine dalili na Fidirah ).

## [61] BABI NA ABINDA YAZO NA HUKUNCIN MASU DAUKAR HOTO ( NARKO MAI TSANANI ).

1. Cikin yin hoto akwai kwaikwayon halitta da kagar wani abu, da wannan ne shi mai yin hoton yake tarayya da Allah cikin halitta da kirkira.
2. Farkon shirka da ta auku a bayan kasa cikin cikin mutanen Annanbi Nuhu -Alaihs Salam- ta auku ne sanadiyyar hotuna da mutum mutumi.

**DALILI NA FARKO:**

عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ڤ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «قَالَ اللهُ تَعَالَى: وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنْ ذَهَبَ يَخْلُقُ كَخَلْقِي، فَلْيَخْلُقُوا ذَرَّةً، أَوْ لِيَخْلُقُوا حَبَّةً، أَوْ لِيَخْلُقُوا شَعِيرَةً»، أَخْرَجَاهُ.

Daga Abu Hurairah -Allah Ya kara yarda a gare shi-" ya ce: Manzon Allah -Sallallahu Alaihi wasallam- yace: " Allah Ta'ala Ya ce: Wa yafi zalunci samada wanda ya tafi yake halitta irin halittata, to su halicci zarrah, ko kwaya, ko su halicci Sha'air ". ( Bukhari da Muslim suka rawaito ).

**DALILI NA BIYU:**

وَلَهُمَا عَنْ عَائِشَةَ ڤ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «أَشَدُّ النَّاسِ عَذَابًا يَوْمَ الْقِيَامَةِ: الَّذِينَ يُضَاهِئُونَ بِخَلْقِ اللهِ».

Daga Bukhari da Muslim, daga Aisha -Allah Ya kara yarda a gareta- tace: Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam ya ce-: " **Mafi tsananin azabar mutane ranar tashin kiyama, wadanda suke kwaikwayon halittar Allah** ".

**DALILI NA UKU:**

وَلَهُمَا عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ: سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُولُ: «كُلُّ مُصَوِّرٍ فِي النَّارِ؛ يُجْعَلُ لَهُ بِكُلِّ صُورَةٍ صَوَّرَهَا نَفْسٌ يُعَذَّبُ بِهَا فِي جَهَنَّمَ».

Daga Bukhari da Muslim, daga Ibn Abbas ya ce: ( Naji Manzon Allah -Sallallahu alaihi waallam- yana cewa: " **dukkan maiyin hoto yana cikin wuta; za'a sanya masa bisa kowani hoto da yayi wata rai, za'a azabtar da shi da ita a cikin wutan jahannama** ".

**DALILI NA HUDU:**

وَلَهُمَا عَنْهُ مَرْفُوعًا: «مَنْ صَوَّرَ صُورَةً فِي الدُّنْيَا؛ كُلِّفَ أَنْ يَنْفُخَ فِيهَا الرُّوحَ، وَلَيْسَ بِنَافِخٍ».

Daga Bukhari da Muslim kuma, daga Ibn Abbas daga Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- " **Duk wanda ya suranta wani hoto a duniya, to za a tilasta shi da ya busa masa rai -a Lahira- kuma bazai taba iya ba** ".

**DALILI NA BIYAR:**

وَلِـمُسْلِمٍ عَنْ أَبِي الْهَيَّاجِ؛ قَالَ: قَالَ لِي عَلِيٌّ: (أَلَا أَبْعَثُكَ عَلَى مَا بَعَثَنِي عَلَيْهِ رَسُولُ اللهِ ﷺ؟: «أَنْ لَا تَدَعَ صُورَةً إِلَّا طَمَسْتَهَا، وَلَا قَبْرًا مُشْرِفًا إِلَّا سَوَّيْتَهُ»).

Imam Muslim ya rawaito daga Abul Hayyaj; yace: Aliyu ya ce dani: ba na aike ka kan irin abin da Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya aike ni a kai ba? " **Kar kabar wani hoto face sai ka gogeshi, sannan kar kabar wani kabari mai tudu face sai ka daidaita shi** " ).

● **<u>Ukubar maiyin hoto</u>:** [1] Shine mafi tsananin azaba cikin mutane ko kuma yana daga cikinsu. [2] Tsinanne ne. [3] Allah zai sanya masa bisa duk wani hoton da yayi wata rai, za ayi masa azaba da ita a wutan jahannama. [4] Shi dan wuta ne. [5] Za a tilasta shi da busa rai ma wannan hoton kuma bazai iyaba. [6] Babu wanda yakaishi zalunci a wannan babin, ko kuma yakai kololuwa wajen zalunci.

● **<u>طَمَسْتَهَا</u> ( ka goge shi ):** idan mai kala ne to yasanya wani launin na dabam domin ya gusarda alamar hotunanan, idan kuma mutum mutumi ne -mai jiki- to sai a yanke kayinsa, idan kuma hotunan zanasu akayi to se a lalata fiskar domin batarda alamar, goge hoto yanada yanayi mabanbanta, kuma zahirin hadisin na nuni kacewar hotone da ake bauta masa baicin Allah, ko ma wanda ba a bauta masa.

● **مُشْرِفًا :** Maitudu.

● **سَوَّيْتَهُ ( Sai ka daidaita shi)** : yanada ma'anoni biyu:

1. Ka kyautata shi yanda zai dace da Sharia.
2. Ka daidata shi da kaburburan da suke gewaye da shi.

**Kashe kashen ajiye hotuna da hukuncinsu:**

1. **<u>Domin girmama wanda yake cikin hoton</u>**: wannan haramun ne babu wani kokwanto; saboda girmama masu matsayi ta hanyar ajiye hotunansu aibi ne cikin rububiyyah, sannan girmama ma'abota ibada ta hanyar ajiye hotunansu kuskure ne a janibin Uluhiyyah.
2. **<u>Domin jindadin</u>** kallo da dubi zuwaga hoton, wannan haramun ne saboda fitinar dake cikin hakan.
3. **<u>Sabaoda tarihi da tausayin wadanda suke cikin hoton</u>** kamar wadanda suke daukan hoton kananun yaransu, wannan shima haramun ne.
4. **<u>Lalura ko bukatuwa zuwaga ajiyewan;</u>** kamar hotunan da suke jikin kudi da ko katin 'dan kasa, I D card, wannan babu laifi a cikinsa, domin baza a iya kubuta daga gareshi ba,

5. **<u>Kasantuwar hoton a jikin wani kayan amfanin mutane</u>** bai ajiye hoton don yanaso ba: kamar hotunan da suke jikin jaridu, majallu, to wannan babu laifi, amma idan zai iya goge hoton ba tareda wata damuwa ba, ko wahala, to wannan shine abin da yafi dacewa.

6. **<u>Abin wulakantawa</u>** wanda aka jefar dashi a kwandon shara, ko aka shimfida shi ko take shi to wannan babu laifi, hotunan da suke jikin tufafi bazasu shiga cikn wannan ba ( ma'ana akwai laifi ).

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Kausasawa mai tsanani dangane da masu yin hoto.

2. Bayani kan dalilin kausasawan, rashin ladabi ne wa Allah, saboda fadinsa: [**Wa yafi zalunci samada wanda ya tafi yake kwaikwayon halittata** ] ( wannan ya munana ladabi tareda Allah, Kaman wanda ya kishiyanci Allah ne cikin Shari'arsa, babu wanda yafi zalunci samada wannan ).

3. Fadakarwa kan ikon Allah, da gajiyawar bayinsa saboda fadinsa: [**To su halicci kwaya mana ko Sha'ir** ] ( Hakika Allah Ya halicci abin da yafi wadannan girma, a yayinda suka kasa halittar zarrah ko sha'ir ).

4. Anyi bayani karara cewa sune mafi sananin azaba daga mutane.

5. Allah yana halitta wata rai tareda kowani hoto wanda ake mata azaba cikin wutan jahannama sakamakon wannan hoton.

6. Za'a tilasta shi ya busa rai ma wannan hoton ( wannan yana daga mafi wahalar ukuba ).

7. Umarni yazo kan share hoton idan aka sameshi ( wannan yana nuni kan haduwar fitinar mutum mutumi da fitinar kaburbura; domin kowannensu hanya ce dake iya kaiwa ga shirka, da tabbatuwar azaba ranar lahira, kuma sakamako yana daga jinsin aiki ne, sannan kallafa wa mutum yin abin da bazai iya ba a Lahira wannan naui ne na ukuba ).

## [62] BABIN ABIN DA YAZO KAN YAWAN RANTSUWA (NA NARKO, SABODA GIRMAMA ALLAH ).

**DALILI NA FARKO:**

Da fadin Allah Ta'ala:

وَاحْفَظُوا أَيْمَانَكُمْ

*“ **Ku kiyaye rantsuwowinku** …” (QS. Al Maidah, 89).*

**Darajojin kiyaye rantsuwa:**

| | | | |
|---|---|---|---|
| **Kiyaye ta a asali:** kar ya yawaita yin rantsuwa. | **Kiyaye ta a tsakiya:** da rashin komawa daga gareta, sedai wanda ya togace. | **Kiyaye ta a karshe:** ya fitar da kaffara idan har ya janye rantsuwar. | **Kar ya rantse da komai se da Allah shi kadai.** |

**DALILI NA BIYU:**

عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ؓ قَالَ: سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُولُ: «**الْحَلِفُ مَنْفَقَةٌ لِلسِّلْعَةِ، مَمْحَقَةٌ لِلْكَسْبِ**»، أَخْرَجَاهُ.

Abu Hurairah -Allah Ya kara yarda a gareshi- ya ce: naji manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: “ …” ( Bukhari da Muslim ).

**DALILI NA UKU:**

وَعَنْ سَلْمَانَ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**ثَلَاثَةٌ لَا يُكَلِّمُهُمُ اللهُ، وَلَا يُزَكِّيهِمْ، وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ: أُشَيْمِطٌ زَانٍ، وَعَائِلٌ مُسْتَكْبِرٌ، وَرَجُلٌ جَعَلَ اللهَ بِضَاعَتَهُ؛ لَا يَشْتَرِي إِلَّا بِيَمِينِهِ، وَلَا يَبِيعُ إِلَّا بِيَمِينِهِ**»، رَوَاهُ الطَّبَرَانِيُّ بِسَنَدٍ صَحِيحٍ.

Daga Salman; Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: Mutane uku Allah ba zai yi musu Magana ba, kuma ba zai tsarkake su ba, kuma sunada wata azaba mai radadi, tsoho mazinaci, da talaka maigirman kai, da mutumin da ya sanya Allah sila wajen saye da sayarwa…... baya sayan wani abu se da rantsuwa kuma baya sayar da wani abu se da rantsuwa ( Dabarani ya rawaito da sanadi ingantacce ).

## DALILI NA HUDU:

وَفِي الصَّحِيحِ عَنْ عِمْرَانَ بْنِ حُصَيْنٍ ﭬ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «**خَيْرُ أُمَّتِي قَرْنِي، ثُمَّ الَّذِينَ يَلُونَهُمْ، ثُمَّ الَّذِينَ يَلُونَهُمْ** - قَالَ عِمْرَانُ: فَلَا أَدْرِي أَذَكَرَ بَعْدَ قَرْنِهِ مَرَّتَيْنِ أَوْ ثَلَاثًا! -، **ثُمَّ إِنَّ بَعْدَكُمْ قَوْمًا يَشْهَدُونَ وَلَا يُسْتَشْهَدُونَ، وَيَخُونُونَ وَلَا يُؤْتَمَنُونَ، وَيَنْذُرُونَ وَلَا يُوفُونَ، وَيَظْهَرُ فِيهِمُ السِّمَنُ**».

Hadisi ya inganta daga Imran dan Husain -Allah Ya kara yarda a gare shi- yace: Manzon Allah -Sallallahu Alaihi wasallam- yace: " Mafi alhairin al'ummata karnina, sa'annan wadanda suka biye musu, sa'annan wadanda suka biye musu, -Imran ya ce: bansaniba, shin so biyu ya ambata a bayan karninsa ko so uku!-, sannan za a samu wadansu mutane a bayanku suna bayar da shaida ba a nemi su bada shaidan ba, suna ha'inci kuma ba a aminta da su, sunayin bakance kuma ba sa cikawa, kuma kiba yana baiyana gare su ".

## DALILI NA BIYAR:

وَفِيهِ عَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ؛ أَنَّ رَسُولَ اللهِ ﷺ قَالَ: «**خَيْرُ النَّاسِ قَرْنِي، ثُمَّ الَّذِينَ يَلُونَهُمْ، ثُمَّ الَّذِينَ يَلُونَهُمْ، ثُمَّ يَجِيءُ قَوْمٌ تَسْبِقُ شَهَادَةُ أَحَدِهِمْ يَمِينَهُ، وَيَمِينُهُ شَهَادَتَهُ**».

Daga Ibn Mas'ud, Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: "Mafi alhairin mutane sune karnina, sa'annan wadanda suka biye musu, sa'annan wadanda suka biye musu, sa'annan sai wadansu mutane su zo, wadanda shaidar dayansu tana rigayar rantsuwarsa, kuma rantsuwarsa tana rigayar shaidarsa ".

## DALILI NA SHIDA:

قَالَ إِبْرَاهِيمُ: «كَانُوا يَضْرِبُونَنَا عَلَى الشَّهَادَةِ وَالْعَهْدِ وَنَحْنُ صِغَارٌ».

Ibrahim (An-Nakha'i): “ Sun kasance -Magabatansu- suna dukanmu akan rantsuwa, da daukan alkawari ”.

- **مَنْفَقَةٌ:** rantsuwa sababi ne na karewar kayan sayarwa **ممحقة:** tana tafiyar da albarkar nema.
- **وَلَا يُزَكِّيهِمْ ( Kuma ba zai tsarkake su ba ),** ba zai amintar da su ba a ranar Lahira, kuma ba zai yi musu shaida da imani ba.
- **أُشَيْمِطٌ :** wanda bakin gashin kansa ya garwaya da farin saboda shekarunsa, da raunin sha'awarsa.
- **عَائِلٌ:** talaka.
- **مُسْتَكْبِرٌ:** maigirman kai wajen karban gaskiya, kuma maigirman kai wa mutane.
- “ **Baya saya ko sayar da wani abu sai yayi rantsuwa** ”: yawan rantsuwarsa tana nuni kan yanda yake wulakanta rantsuwa da rashin daukanta a bakin komaiba.

shaidar, ko kuma saboda suna shaidar karya.

● " **Shaidar dayarsu tana riga rantsuwarsa** ":

[1] Saboda karancin amintuwar mutane da su, ba sa yin Shaida se da rantsuwa.

[2] Ko kuma kinaya ce kan kasancewarsu basu damu da yin shaida da rantsuwar ba.

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Anyi wasiyci da kiyaye rantsuwa.

2. Annabi Sallallahu alaihi wasallam ya bayar da labarin cewar rantsuwa tana sa kayan sayarwa ya kare, tana tafiyar da albarkar nema.

3. Narko maitsanani kan wanda ba ya sayar da wani abu ko saya sai da rantsuwa.

4. Fadakarwa kan cewa zunubi yakan girmama yayin rashin sababin da zaisa a yi zunubin.

5. An zargi wadanda sukeyin rantsuwa ba a nemi suyi rantsuwar ( se in da bukata, ko kuma idan maslaha ta hukunta hakan ).

6. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya yabi karnoni uku ko hudu, sannan Manzon Allah ya bada labarin abinda zai auku a bayansu.

7. An zargi wadanda suke bayar da shida ba a nemi suyi shaidar ba ( suke ha'inci kuma ba a amincewa da su, suna yin bakance ba sa cikawa, suna aikata abubuwan da zasu sanya su kiba da girman jiki amma kuma suna gafala daga gyarar zuci da imani da ilimi ).

8. Magabata sun kasance suna dukan kananun yara kan shaida da alkawali ( domin girmama lamarin alkawali da shaida, da kuma kulawarsu ta musamman wajen tarbiyyar yaransu, dukan yara yanada sharudda kamar haka:

1. Yaron ya kai matakin karbar ladabtarwa, ba a dukan wanda baisan hikimar da ta saka aka bugeshiba.
2. Wanda zai ladabtar din ya zamo yanada wilaya (iko) akan yaron.
3. Kar ya wuce iyaka wajen yanayin dukan da yawanta, ko nauinta, ko wurin da zaiyi bugun da sauransu.
4. Yaron ya aikata abun da ya cancanci horo da ladabtarwa a kai.
5. Manufar ta zamo ladabtarwa ce ba huce haushin ba, idan ba hakaba to ya zamo mai taimakon kansa ba mai ladabtarwa ba.

## [63] BABIN ABIN DA YAZO DANGANE DA ZIMMAR ALLAH DA ZIMMAR ANNABINSA ( IKHLASI DA MUTA'BA A )

Rashin cika alkawarin Allah tawaya ce cikin hakin Allah wannan kuma tawaya ce ga tauhidi, wajabi ne a girmama Allah cikin mua'malla da mutane koda kuwa kafirai ne, kuma koda cikin mafi wahalar yanayi ne, shine jihadi domin daukaka Kalmar Alla, wajibi ne mutum yayi aiki da Shari'ar Allah kuma ya girmama alkawarin Allah da alkawarin Annabinsa -Sallallahu alaihi wasallam-.

**DALILI NA FARKO:**

Da fadin Allah Ta'ala:

{وَأَوْفُواْ بِعَهْدِ اللهِ إِذَا عَاهَدتُّمْ وَلاَ تَنقُضُواْ الأَيْمَانَ بَعْدَ تَوْكِيدِهَا } الآيَةَ

***[ Kuma ku cika alkawarin Allah idan kun dau alkawari, karku warware rantsuwoyinku a bayan karfafa su…]*** *(QS. An-Nahl : 91).*

**DALILI NA BIYU:**

وَعَنْ بُرَيْدَةَ قَالَ: كَانَ رَسُولُ اللهِ ﷺ إِذَا أَمَّرَ أَمِيرًا عَلَى جَيْشٍ أَوْ سَرِيَّةٍ أَوْصَاهُ فِي خَاصَّتِهِ بِتَقْوَى اللهِ، وَبِمَنْ مَعَهُ مِنَ الْمُسْلِمِينَ خَيْرًا، فَقَالَ: «**اغْزُوا بِاسْمِ اللهِ، قَاتِلُوا فِي سَبِيلِ اللهِ مَنْ كَفَرَ بِاللهِ، اغْزُوا وَلَا تَغُلُّوا، وَلَا تَغْدِرُوا، وَلَا تُمَثِّلُوا، وَلَا تَقْتُلُوا وَلِيدًا، وَإِذَا لَقِيتَ عَدُوَّكَ مِنَ الْمُشْرِكِينَ فَادْعُهُمْ إِلَى ثَلَاثِ خِصَالٍ – أَوْ: خِلَالٍ - فَأَيَّتَهُنَّ أَجَابُوكَ فَاقْبَلْ مِنْهُمْ، وَكُفَّ عَنْهُمْ، ثُمَّ ادْعُهُمْ إِلَى الإِسْلَامِ، فَإِنْ أَجَابُوكَ فَاقْبَلْ مِنْهُمْ، ثُمَّ ادْعُهُمْ إِلَى التَّحَوُّلِ مِنْ دَارِهِمْ إِلَى دَارِ الْمُهَاجِرِينَ، وَأَخْبِرْهُم أَنَّهُمْ إِنْ فَعَلُوا ذَلِكَ فَلَهُمْ مَا لِلْمُهَاجِرِينَ، وَعَلَيْهِمْ مَا عَلَى الْمُهَاجِرِينَ، فَإِنْ أَبَوْا أَنْ يَتَحَوَّلُوا مِنْهَا؛ فَأَخْبِرْهُمْ أَنَّهُمْ يَكُونُونَ كَأَعْرَابِ الْمُسْلِمِينَ، يَجْرِي عَلَيْهِمْ حُكْمُ اللهِ تَعَالَى، وَلَا يَكُونُ لَهُمْ فِي الْغَنِيمَةِ وَالْفَيْءِ شَيْءٌ؛ إِلَّا أَنْ يُجَاهِدُوا مَعَ الْمُسْلِمِينَ، فَإِنْ هُمْ أَبَوْا فَاسْأَلْهُمُ الْجِزْيَةَ، فَإِنْ هُمْ أَجَابُوكَ فَاقْبَلْ مِنْهُمْ وَكُفَّ عَنْهُمْ، فَإِنْ هُمْ أَبَوْا فَاسْتَعِنْ بِاللهِ وَقَاتِلْهُمْ، وَإِذَا حَاصَرْتَ أَهْلَ حِصْنٍ فَأَرَادُوكَ أَنْ تَجْعَلَ لَهُمْ ذِمَّةَ اللهِ وَذِمَّةَ نَبِيِّهِ؛ فَلَا تَجْعَلْ لَهُمْ ذِمَّةَ اللهِ وَذِمَّةَ نَبِيِّهِ، وَلَكِنِ اجْعَلْ لَهُمْ ذِمَّتَكَ وَذِمَّةَ أَصْحَابِكَ، فَإِنَّكُمْ إِنْ تُخْفِرُوا ذِمَمَكُمْ وَذِمَّةَ أَصْحَابِكُمْ؛ أَهْوَنُ مِنْ أَنْ تُخْفِرُوا ذِمَّةَ اللهِ وَذِمَّةَ نَبِيِّهِ، وَإِذَا حَاصَرْتَ أَهْلَ حِصْنٍ فَأَرَادُوكَ أَنْ تُنْزِلَهُمْ عَلَى حُكْمِ اللهِ؛ فَلَا تُنْزِلْهُمْ عَلَى حُكْمِ اللهِ، وَلَكِنْ أَنْزِلْهُمْ عَلَى حُكْمِكَ؛ فَإِنَّكَ لَا تَدْرِي أَتُصِيبُ حُكْمَ اللهِ فِيهِمْ أَمْ لَا**»، رَوَاهُ مُسْلِمٌ.

Daga Buraidah -Radiyallahu anhu- ya ce: Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi- ya kasance idan ya nada wani shugaba a kan rundunar mayaka yakan yi masa wasiyci a kebe da tsoron Allah, sannan ya kyautata ga wadanda suke tareda shi daga musulmai, sai ya ce: **" Ku tafi kuyi yaki da sunan Allah, kuyaki -cikin hanyar Allah- duk wanda ya kafirce wa Allah, kuyi yaki kuma kar ku saci kayan ganima kafin a raba, kuma kar ku yi yaudara, kuma kar ku kacancana gawan wanada kuka kashe, kuma kar ku kashe karamin yaro, idan ka hadu da abokin gabanka daga mushrikai, to sai ka kiraye su zuwaga ta'adodi uku -Abubuwa uku- duk wanda suka amsa maka daga ciki to ka karba daga gare su, kuma ka kame hannunka daga yakarsu, sannan ka kiraye su zuwaga musulunci, idan suka amsa maka to ka karba daga gare su, sannan ka neme su da su yi kaura daga garuruwansu zuwa garin mahajirun, sannan kabasu labarin cewa idan suka aikata haka to sunada kwatankwacin abin da muhajirun suke dashi, sanna yana kansu irin abin da yake kan muhajirun, idan suka ki barin garuruwansu, to ka basu labarin cewa lallai ne zasu kasance daga kamar kauyawan larabawa daga musulmai, hukuncin Allah ta'ala yana gudana cikinsu kuma basuda wani abu na kaso daga ganima ko fai'u, face se idan sunyi jihadi tareda musulmai, idan kuma suka ki, to ka tambaye su su bayar da jizya, idan sun yi maka biyayya to ka karba daga garesu sannan ka kame hannunka daga yakarsu, idan kuma suka ki, to sai ka nemi taimakon Allah ka yake su, <u>sannan idan ka keweye ma'abota ganuwa a ganuwarsu sai suka bukaci kasanya musu alkawarin Allah da alkawwarin Annabinsa, to kar kasanya musu alkarin Allah da alkawarin Annabinsa,</u> sedai ka sanya musu alkawarinka da alkawarin sahabbanka, domin lallai ku warware alkawarinku da alkawarin sahabbanku shi yafi sauuki sama da ku warware Alkawarin Allah da Alkawarin annanbinsa, kuma idan ka keweye ma'abota ganuwa a ganuwarsu sai suka bukaci ka saukar da su bisa hukuncin Allah to kar ka saukar da su kan hukuncin Allah, kaidai saukar da su bisa hukuncinka, domin tabbas kai baka saniba shin zaka dace da hukuncin Allah cikinsu ko ba zaka dace ba " ( Muslim ya rawaito ).**

- جَيْشٍ : **Al-Jaish**: sune mutanen da suka haura ma dari hudu 400 na mayaka.
- سَرِيَّةٍ : **Sariyyah** wadanda basukai mutum dari hudu ba 400.
- **"Kuyi yaki da sunan Allah "**: [1] Kuna masu neman taimako da Allah [2] Ku fara yakin da Sunan Allah.
- **" A hanyar Allah "** : Ya game niyya da aiki.
- **" Duk wanda ya kafirce "**: Kar ku yaki mutane don ta'assubannci ko kabilanci, ku yake su domin maslaha, itace tsamar da su daga wuta, kafirci yana gewaya ne kan abubuwa biyu: musu da girman kai.

- **وَلَا تَغُلّوا :** Ghululi: boye wani abu na ganima domin ya kebance kansa dashi.
- **وَلَا تَغْدِرُوا :** Kar kuyi ha'inci bayan kunyi alkawari, **yaudarar abokan** yaki in babu alkawari ya halatta, saboda yaki dan yaudara na.
- **وَلَا تُمَثِّلُوا :** Kacancana macacce ta hanyar yanke wani bangare na gabbansa ba tare da wata bukata ba, domin hakan ramuwar gayya ce a wajen da bai dace ba, sedai idan su suka fara yi mana hakan to babu laifi mu rama.
- **وَلِيدًا :** Ba za mu kashe kananan yara ba, ko mata ko tsofaffi, ko masu ibada ko marasa lafiya, sedai in sun dau makami suka yake mu, ko suka zaburar da wadansu wajen yakarmu, ko sunada ra'ayi kan yakin.
- **عَدُوَّكَ (makiyinka):** Ana zaburar dasu kan yakan abokan gaba, makiyin yana kyamatarka kuma yana nisantarka, sannan ketare iyaka a kanka.
- **"Ghanimah":** Shine Abin da aka karba na dukiyar kafirai ta hanyar yaki ko abin da aka riskar dashi.
- **الْفَيْءِ:** Shine Abin da ake karkartar dashi zuwaga baitul mali, kamar khumusin khumusi na ghanimah, ko haraji, ko jizyah.
- **" Sai har in sunyi jihadi ":** Idan sun musulunta, kuma sukayi jihadi, to sunada irin abin da musulmai suke dashi na ghanima da fai'u.
- **" Jizyah ":** Dukiya ce da ake karba daga wajen wanda ba musulmi ba, a maimakon tsaro da ake bashi da zamarsa a garin musulmai, ciki a kwai dalili na karbar jizyah wajen wanda ba bayahude ba ba nasara ba kuma bamajuse ba.

**Yanda zamu mu'amalanci kafirai Al-Mua'hadun.**

Wajibi ne mu cika musu alkawari matukakar sun kiyaye alkawalin: Allah Ya ce: ***[ To matukar sun tsaya sosai gare ku, sai ku tsayu sosai gare su ]*** *(QS. At-Taubah: 7).*

Idan suka warware alkawarin da sukayi, shikenan alkawarin zaman lafiya tare dasu ya saraya: Allah Ya ce: ***[ Kuma idan suka warware rantsuwoyinsu daga bayan alkawrinsu*** *….](QS. At-Taubah : 12).*

Idan mukayi kokwanto wajen alkawari da su, sai mu mayar musu: Allah Ya ce: ***[ kuma in kaji tsoron wata yaudara daga wasu mutane, to ka jefar -da alkawarin-zuwa garesu ]*** *(QS. Al-Anfaal : 58).*

| Abbubuwan da musulmai su ka aikatawa yayin jihadinsu da kafirai: | Abubuwan da kafirai suk aikatawa yayin jihadinsu da musulmai: |
|---|---|
| Haramun ne kashe kananun yara, da mata da masu ibada, da marasa lafiya. | Suna kashe kananun yara, da mata da masu ibada, da marasa lafiya. |
| Yaki saboda maslahar kafiran (tsamar da su daga wuta). | Yaki saboda duniya. |
| Suna cika wa kafirai alkawarinsu. | Suna yawan warware alkawari. |
| Idan kafirai suka warware alkawari musulmai sukan fadakar da su cewa: yanzu babu wani alkawri a tsakaninsu. | Ba sa fadakar da musulmai idan wani abu ya faru daga bangaren musulmai. |
| Ba sa ha'inci bayan anyi alkawari. | Suna ha'inci bayan anyi alkawari. |
| Basa kacancana gawan matattun kafirai, sedai idan kafiran su suka fara yi. | Suna kacancana gawawwakin musulmai, ba tare da musulmai sun kacancana nasu ba. |
| Ba sa fara yakar su se bayan sun ba su zabi tasakanin musuluntа ko jizyah ko yaki. | Asali su ba su yin da'awa. |
| Sunayin adalci wajen hukunci basa zalunci. | Suna gina hukunce hukuncensu ne bisa zalunci. |
| Yawan wadanda aka kashe tun aiko manzon Allah SAW har mutuwarsa basu wuce dubu ba a dukkan yakukuwan. | |
| Ba a taba kashe karamin yaro ko mace ko tsoho ba.<br>Sau daya Manzon Allah SAW ya kashe wani. | |

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Banbanci tsakanin alkawarin Allah da alkawarin Annabinsa, da alkawarin Musulmai.

2. Shiryarda mutane zuwaga abu mafi karancin hadari daga abubuwa biyu.

3. Fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- " **ku tafi kuyi yaki da sunan Allah kuma a hanyar Allah** " (Wajabcin yin yaki tareda neman taimakon Allah, da yin Ikhlasi, da wanzuwa bisa Shari'arsa.

4. Fdinsa: " **Ku yaki wanda ya kafirce wa Allah** " ( kafirci shine dalilin yakarsu ).

5. Fadinsa: " **Ka nemi taimako da Allah sannan ka yake su** " (kar mutum ya dogara a kan dabararsa ko karfinsa).

6. Banbaci tsakanin hukuncin Allah da hukunci malamai.

7. Sahabin Annabi SAW yakanyi hukunci da hukuncinsa ( ijtihadinsa ) yayin bukata, amma bai saniba shin ya dace da hukuncin Allah ko bai dace ba?. (Wannan bai takaita kadai kan wannan Sahabinba, ya game har wadanda zasu zo a bayansu ).

## [64] BABIN ABINDA YAZO NA YIN RANTSUWA WA ALLAH (RANTSUWA NA SHISH,SHIGI WA ALLAH -cewa zaiyi kaza ko bazaiyi ba- )

Duk wanda yayi **rantsuwa wa Allah** to hakika ya munana ladabi tareda Allah kuma ya kuntata Falalar Allah kuma ya munana zato wa Allah, duk wannan abu ne da ke kore kamalar tauhidi, kuma yana iya kore asalin tauhidin, rantsuwa **rantsuwa kan duk wani** maigirma, tawaya ce ga matsayinsa.

### Kashe kashen rantsuwa wa Allah ( Maigirma da buwaya)

**Halal:** Ya rantse kan abinda Allah da Manzonsa suka labarta, na korewa ko tabbatarwa, wanda ciki akwai dalilinsa na yakini kan abin da yayi rantsuwar; kamar yace: ( Wallahi, Allah zaiba wa Annabinsa ceto ranar qiyamah).

**Halal:** Ya rantse da UbangijinSa saboda krfin tsammani da kyautata zato ga Allah, da sharadin kasantuwarsa a kan aiyuka na gari; kamar yanda ya tabbata cikin qissas Anas bin An-Nathir RTA .

**Haram, yana kusa da bata aiyukan mutum:** Abin da ya kai shi ga yin rantsuwar shine ji ji da kansa, da kuntata Falalar Allah, da munana zato ga Allah Ta'ala.

### DALILI NA FARKO:

عَنْ جُنْدُبِ بْنِ عَبْدِ اللهِ ۏ قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ □ : «قَالَ رَجُلٌ: وَاللهِ لَا يَغْفِرُ اللهُ لِفُلَانٍ، فَقَالَ اللهُ ۵: **مَنْ ذَا الَّذِي يَتَأَلَّى عَلَيَّ أَنْ لَا أَغْفِرَ لِفُلَانٍ؟ إِنِّي قَدْ غَفَرْتُ لَهُ، وَأَحْبَطْتُ عَمَلَكَ**»، رَوَاهُ مُسْلِمٌ،

Daga Jundub dan Abdullahi -Allah Ya kara yarda a gareshi- ya ce: Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi- ya bada labarin cewa: " **Wani mutum yace: Wallahi Allah ba zai gafarta ma wane ba, sai Allah - Migirma da buwaya- Ya ce: Wanene wannan da ke rantsuwa kaina cewa bazan gafarta ma wane ba? To hakika na gafarta masa, kai kuma na rusa aiyukanka** ", ( Muslim ne ya rawaito ).

### DALILI NA BIYU:

وَفِي حَدِيثِ أَبِي هُرَيْرَةَ: أَنَّ الْقَائِلَ رَجُلٌ عَابِدٌ، قَالَ أَبُو هُرَيْرَةَ: «تَكَلَّمَ بِكَلِمَةٍ أَوْبَقَتْ دُنْيَاهُ وَآخِرَتَهُ».

Yazo cikin hadisin Abu Hurairah: cewa wanda ya yi wannan rantsuwar wani mutum ne mai yawan ibada, Abu Hurairah ya ce: (( ya fadi maganar da ta halakar masa da duniyarsa da lahirarsa )). ( Ahmad da Abu Dawud suka rawaito).

● Cewarsa: "**Allah ba zai gafarta ma wane ba**": yana nuni a kan debe tsammani daga Rahamar Allah, da raina bayin Allah, da ji ji da kansa.

● يَتَأَلَّى عَلَيَّ : Yake kuntata Falalata da Ni'imata, ceawar bazan gafarta ma wanda ya munana daga bayina ba.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tsoratarwa dangane da rantasuwa kan Allah.

2. Kasantuwar Wuta tafi kusanci zuwaga daya daga cikinmu daga hancin takalminsa.

3. Aljannah ma kamar hakane.

4. Cikin hadisin akwai dalili kan haka, fadinsa: "Lallai mutum zai fadi wata maganar da ya raina ta….. " zuwa karshen hadisin.

5. Allah Yana iya gafarta wa mutum da wani sababi cikin abubuwan da yafi kinsu.

## [65] BABIN BA A NEMAN CETO DA ALLAH A WAJEN HALITTUNSA (SABODA CIKAR KAMALARSA).

Neman ceton Allah wajen halittunsa tawaya ce ga Allah, saboda hakan yana hukunta sanya maysayin Allah kasa da matsayin wanda za a nemi ceton a wajensa.

### DALILI NA FARKO:

عَنْ جُبَيْرِ بْنِ مُطْعِمٍ قَالَ: جَاءَ أَعْرَابِيٌّ إِلَى النَّبِيِّ ﷺ فَقَالَ: يَا رَسُولَ اللهِ نُهِكَتِ الأَنْفُسُ، وَجَاعَ الْعِيَالُ، وَهَلَكَتِ الأَمْوَالُ، فَاسْتَسْقِ لَنَا رَبَّكَ، فَإِنَّا نَسْتَشْفِعُ بِاللهِ عَلَيْكَ، وَبِكَ عَلَى اللهِ، فَقَالَ النَّبِيُّ ﷺ: «**سُبْحَانَ اللهِ!، سُبْحَانَ اللهِ!**»، فَمَا زَالَ يُسَبِّحُ حَتَّى عُرِفَ ذَلِكَ فِي وُجُوهِ أَصْحَابِهِ، ثُمَّ قَالَ: «**وَيْحَكَ أَتَدْرِي مَا اللهُ؟ إِنَّ شَأْنَ اللهِ أَعْظَمُ مِنْ ذَلِكَ، إِنَّهُ لَا يُسْتَشْفَعُ بِاللهِ عَلَى أَحَدٍ...**»، وَذَكَرَ الْحَدِيثَ، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ.

Daga Jubair dan Mud'im ya ce: ( wani balaraben kauye yazo wajen Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- sai ya ce: ya Manzon Allah rayuka sun raunana, iyalai kuma sun yunwata, dukiyoyi sun halaka, ka roka mana Ubangijinka Ya shayar damu ruwan sama, lallai mu, muna neman ceton Allah a wajenka, kuma muna neman cetonka a wajen Allah, se Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: (( Subhanallah!, Subhanallah! )), bai gushe ba yana ta tsarkake Allah se da aka gane hakan a fiskokin Sahabbansa, sannan ya ce: (( Kaitonka shin kasan wanene Allah? Sha'anin Allah yafi karfin haka, ba a neman ceton da Allah a wajen wani… )). ( Abu Dawud ne ya rawaito shi ) .

- **نُهِكَتِ:** Sun raunana. • **"Dukiya sun halaka"**: Saboda karancin ruwan sama da kuma karancin abinci.
- **"فاستسق":** Ka roka mana Allah ya shayar da mu ruwa, wannan ya halatta a nema a wajen duk wanda a ke fatan idan yayi addu'a Allah zai karba, ba tareda nuna bukatuwa zuwa gareshi ba.
- **نَسْتَشْفِعُ بِاللهِ عَلَيْكَ:** Muna neman ceton Allah a wajenka, ma'ana: mun sanya Allah a matsayin tsani tsakaninmu da kai, ka roka mana shi, wannan yana hukunta ya sanya matsayin Allah kasa da matsayin Manzon Allah SAW, munkari.
- **سبحان الله!، سبحان الله!:** Saboda girman wannan maganar, da yi masa inkari, da tsarkake Allah Ta'ala.
- **((ويحك))** Ina matukar jin tausayinka.

### *MAS'ALOLIN BABIN:*

1. Inkarin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ga mutumin da yace: " muna neman ceton Allah a wurinka ".

2. Canzawar yanayin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yayin da yaji wannan maganar ta balaraben kauyen, Sahabbai sun fahimci hakan a fiskansa.

3. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- bai yi masa inkarin fadinsa: " muna neman cetonka a wurin Allah ".

4. Fadakarwa dangane da Fassarar Fadinsa: ( Subhanallah ).

5. Musulmai sun kasance suna tambaayar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- da ya roka musu Allah Ya shayar dasu ruwa ( A halin rayuwarsa ).

(wannan yana nuni kan halaccin mutum ya gabatar da wasu kalmomin da za su lizimta a ji tusayinsa yayinda yake neman wani abu ).

## [66] BABIN ABIN DA YAZO NA KARIYAR MANZON ALLAH -SALLAHU ALAIHI WASALLAM- WA SHINGEN TAUHIDI DA TOSHEWARSA HANYOYIN SHIRKA. ( Har a cikin Lafuzza).

### DALILI NA FARKO:

عَنْ عَبْدِ اللهِ بْنِ الشِّخِّيرِ قَالَ: انْطَلَقْتُ فِي وَفْدِ بَنِي عَامِرٍ إِلَى النَّبِيِّ ، فَقُلْنَا: أَنْتَ سَيِّدُنَا، فَقَالَ: «**السَّيِّدُ اللهُ تَبَارَكَ وَتَعَالَى**»، قُلْنَا: وَأَفْضَلُنَا فَضْلًا، وَأَعْظَمُنَا طَوْلًا، فَقَالَ: «**قُولُوا بِقَوْلِكُمْ، أَوْ بَعْضِ قَوْلِكُمْ، وَلَا يَسْتَجْرِيَنَّكُمُ الشَّيْطَانُ**»، رَوَاهُ أَبُو دَاوُدَ بِسَنَدٍ جَيِّدٍ.

Daga Abdullah bin As-Shikhkhiir, ya ce: na tafi a cikin tawagar banu Amir zuwaga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- sai muka ce da shi: Kai ne shugabanmu , Sai ya ce: " **Allah ne Shugaba, Madaukaki wanda alhairinsa ya yawaita** " muka ce: kuma kaine Mafificinmu ta fiskar falala, kuma mafi girmanmu ga wadata, sai yace: " **Ku dai ku fadi maganarku ko sashen maganarku, kar Shaidan ya hallakar da ku** ", ( Abu Dawud ne ya rawaito da sanadi maikyau ).

### DALILI NA BIYU:

وَعَنْ أَنَسٍ؛ أَنَّ نَاسًا قَالُوا: يَا رَسُولَ اللهِ، يَا خَيْرَنَا، وَابْنَ خَيْرِنَا، وَسَيِّدَنَا، وَابْنَ سَيِّدِنَا، فَقَالَ: «**يَا أَيُّهَا النَّاسُ؛ قُولُوا بِقَوْلِكُمْ، وَلَا يَسْتَهْوِيَنَّكُمُ الشَّيْطَانُ، أَنَا مُحَمَّدٌ عَبْدُ اللهِ وَرَسُولُهُ، مَا أُحِبُّ أَنْ تَرْفَعُونِي فَوْقَ مَنْزِلَتِي الَّتِي أَنْزَلَنِي اللهُ ٥**»، رَوَاهُ النَّسَائِيُّ بِسَنَدٍ جَيِّدٍ.

Daga Anas; cewa wadansu mutane suka ce: ya Maanzon Allah, ya mafi alherinmu, dan mafi alherinmu, ya shugabanmu, dan shugabanmu, sai yace: " **Ya ku mutane; ku dai ku fadi maganarku ba wannan ba, kar Shaidan ya hallakar daku, nine Muhammadu, bawan Allah kuma Manzonsa, ba na son ku daukaka ni samada matsayina da Allah -Maigirma da buwaya- Ya saukar da ni a kai** ", (Al-imam An-Nasa'i ne ya rawaito da sanadi mai yawu ).

- **السَّيِّدُ اللهُ (As-Sayyid shine Allah):** As-Sayyid sunane daga sunayen Allah, daya ne daga ma'anoni na As-Samada, yayi hanin ne don kar shaidan ya karkatar daku daga ba ni matsayin shugabanci kebantacciya zuwa gamammiya, wacce ba ta da kaidi, wannan kuma ta Allah ce shi kadai.
- **وَلَا يَسْتَجْرِيَنَّكُمُ الشَّيْطَانُ :** kar shaidan ya batar daku har ku fadi wata mummunar Magana, sai ya shiryar dasu zuwaga abin da ya halatta su fada, sannan yayi musu hani daga abin da bai halatta su fada ba domin kare tauhidi daga tawaya ko bata shi.

● يَا خَيْرَنَا **( Ya fiyayyenmu )**: ga nasaba da matsayi da halaiya.

● وَابْنَ خَيْرِنَا **(Kuma dan fiyayyenmu )**: ga nasaba.

● وَلَا يَسْتَهْوِيَنَّكُمُ الشَّيْطَانُ: kar shaidan ya karkatar daku bare ku so shi sannan kubi hanyoyinsa wanda zasu kaiku ga wuce iyaka.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tsawatar wa mutane dangane da ghuluwwi.

2. Abin da ya kamata mutumin da akace masa " Kai ne shugabanmu ) ya fada: (sai yace: Allah shine shugaba, fasiki ko munafuki ko kafiri, namiji ne shi ko mace ).

3. Fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- (( kar shaidan ya karkatar da ku)), tareda cewa abin da suka fada din gaskiya ne.

4. Fadin Manzon Allah " **Ba na son ku daga ni samada matsayina** ". ( Bawan Allah kuma Manzonsa ).

## [67] NAGOMA: CIKITAWA
## ( BABI GUDA)

Mawallafin ya cikita littafin ne da wannan babin -wallahu A'alam- domin:
1. Kar mu zamo Kaman mushrikai wadanda basu girmama Allah ba.
2. Kar mu rudu da ilminmu, akwai gazawa cikin aiyukan mutum babu makawa, to wannan zaisa bawa ya kankan da kansa ga Allah tareda tawali'u.
3. Koyi da Imamul Bukhari -Rahimahullah- wajen cikita hadisan littafinsa da hadisin: " **ثقيلتان في الميزان** ", kamar rokon Allah yakeyi da ya nauyaya mizaninsa da wannan littafin kamar yanda Ya nauyaya wadannan halittu, kuma Yana nema gafarar Allah kan kura kurensa.

### [67] BABIN: FADIN ALLAH TA'ALA:

{ وَمَا قَدَرُوا اللَّهَ حَقَّ قَدْرِهِ وَالْأَرْضُ جَمِيعاً قَبْضَتُهُ يَوْمَ الْقِيَامَةِ وَالسَّماوَاتُ مَطْوِيَّاتٌ بِيَمِينِهِ سُبْحَانَهُ وَتَعَالَى عَمَّا يُشْرِكُونَ}

[ **Kuma ba su girmama Allah ba hakikanin girmanSa, kasa gaba daya damkarSa ce a Ranar tashin qiyama, sammai kuma suna ninkewa ne a DamanSa, tsarki ya tabbata a gare Shi, kuma Ya daukaka, ga barin abin da suke tara Shi da shi** ]. *(QS. Az-Zumar : 67).*

● Lamirin zancen yana komawane kan mushrikai, ba su girmama Allah hakikanin girmanSa ba, ta yanda suka tara Shi cikin bauta da halittunSa, alhalin Allah Ya tsarkaka daga dukkan tawaya da aibu, wajibine a tsarkake Shi daga dukkan kishiyoyi, da sun girmama Allah hakikanin girmamanSa da basu bautata ko waninSa, ko suyi masa 'da a ba.

### DALILI NA BIYU:

عَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ ﭬ قَالَ: جَاءَ حِـبْرٌ مِنَ الأَحْبَارِ إِلَى رَسُولِ اللهِ ﷺ، فَقَالَ: يَا مُحَمَّدُ، إِنَّا نَجِدُ أَنَّ اللهَ يَجْعَلُ السَّمَوَاتِ عَلَى إِصْبَعٍ، وَالْأَرَضِينَ عَلَى إِصْبَعٍ، وَالشَّجَرَ عَلَى إِصْبَعٍ، وَالْـمَاءَ عَلَى إِصْبَعٍ، وَالثَّرَى عَلَى إِصْبَعٍ، وَسَائِرَ الْـخَلْقِ عَلَى إِصْبَعٍ، فَيَقُولُ: أَنَا الْـمَلِكُ، فَضَحِكَ النَّبِيُّ ﷺ حَتَّى بَدَتْ نَوَاجِذُهُ؛ تَصْدِيقًا

لِقَوْلِ الْحِـبْرِ، ثُمَّ قَرَأَ: (وَمَا قَدَرُوا اللَّهَ حَقَّ قَدْرِهِ وَالْأَرْضُ جَمِيعاً قَبْضَتُهُ يَوْمَ الْقِيَامَةِ ) الآيَـةَ، وَفِـي رِوَايَـةٍ لِـمُسْلِمٍ: «**وَالْجِبَالَ وَالشَّجَرَ عَلَى إِصْبَعٍ، ثُمَّ يَهُزُّهُنَّ فَيَقُولُ: أَنَا الْـمَلِكُ، أَنَا اللهُ**»، وَفِـي رِوَايَـةٍ لِلْبُخَـارِيِّ: «**يَجْعَلُ السَّمَوَاتِ عَلَى إِصْبَعٍ، وَالْـمَاءَ وَالثَّرَى عَلَى إِصْبَعٍ، وَسَائِرَ الْـخَلْقِ عَلَى إِصْبَعٍ**»، أَخْرَجَاهُ.

Daga Ibnu Mas'ud -Allah Ya kara yarda dashi- ya ce: wani malami daga cikin malaman Yahudawa yazo wajen Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- sai ya ce: ya Muhammad, lallai mu mun samu -a cikin Attaurah- cewa Allah Zai sanya sammai -bakwai- a kan yatsa daya, Kassai -bakwai- a kan yatsa daya, bishiyoyi a kan yatsa daya, Tekuna a kan yatsa daya, kasa a kan yatsa daya, sauran halittu a kan yatsa daya, sa'annan Ya ce: Ni -kadai ne- Mai mulki, ina sarakunan duniya, se manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yayi dariya har saida hakwaransa suka bayyana; saboda gasgata maganar wancan bayahuden, sa'annan ya karanta fadin Allah Ta'ala: [ **Ba su girmama Allah ba hakikanin girmanSa, kasa gaba daya damkarSa ne a Ranar Alqiyamah** ], A cikin wata riwayar ta Imam Muslim: (( **Da duwatsu da bishiyoyi a kan yatsa daya, sannan ya girgizasu kuma ya ce: Nine Mamallaki, Nine Allah** )), a wata riwayar kuma ta Imamul Bukhari: (( **Zai sanya Sammai a kan yatsa daya, da ruwa da fadin kasa a kan yatsa daya, sauran halittu kuma a kan yatsa daya** )), ( Bukhari da Muslim ne suka fitar dashi ).

- **حِـبْرٌ:** Malami mai yawan sani, ana kiransa kuma da: **بَحْرٌ:** kogin ilimi.
- **إِنَّا نَجِدُ ( Hakika mu, mun samu ):** ma'ana a cikin Attaurah.
- Cikin hadisin akwai tabbatar da sifar yatsu ga Allah Ta'ala bisa hakika, kamar yanda suka dace da Shi, kamar yanda yakeda hannu na hakika, kamar yanda yadace da Shi.

**DALILI NA UKU:**

وَلِـمُـسْلِمٍ عَنِ ابْنِ عُمَرَ مَرْفُوعًا: «**يَطْوِي اللهُ السَّمَوَاتِ يَوْمَ الْقِيَامَةِ، ثُمَّ يَأْخُذُهُنَّ بِيَدِهِ الْيُمْنَى، ثُمَّ يَقُولُ: أَنَا الْـمَلِكُ، أَيْنَ الْـجَبَّارُونَ؟ أَيْنَ الْـمُتَكَبِّرُونَ؟ ثُمَّ يَطْوِي الْأَرَضِينَ السَّبْعَ، ثُمَّ يَأْخُذُهُنَّ بِشِمَالِهِ، ثُمَّ يَقُولُ: أَنَا الْـمَلِكُ، أَيْنَ الْـجَبَّارُونَ؟ أَيْنَ الْـمُتَكَبِّرُونَ؟**».

A riwayar Imam Muslim kuma daga Ibn Umar, hadisi marfu'i zuwaga Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: (( **Allah zai nade Sammai -bakwai- Ranar tashin Alkiyama, Sa'annan Ya damke su da hanunsa na dama, sannan yace: Nine Mamallaki, ina azzalumai? ina masu girman kai? sannan ya ninke kassai bakwai, sannan ya rike su da HagunanSa, sannan Yace: Nine Mamallaki, ina azzalumai? ina masu girman kai?** )).

**DALILI NA HUDU:**

وَرُوِيَ عَنِ ابْنِ عَبَّاسٍ قَالَ: «مَا السَّمَوَاتُ السَّبْعُ وَالأَرَضُونَ السَّبْعُ فِي كَفِّ الرَّحْمَنِ؛ إِلَّا كَخَرْدَلَةٍ فِي يَدِ أَحَدِكُمْ»

An rawaito daga dan Abbas, ya ce: (( **Sammai bakwai ba komai ba ne ba, haka kassai bakwai suma ba komai ne ba, a Tafin Allah face kamar kwayar komayya ce a hannun dayanku** )).

**DALILI NA BIYAR:**

وَقَالَ ابْنُ جَرِيرٍ: حَدَّثَنِي يُونُسُ، أَنْبَأَنَا ابْنُ وَهْبٍ، قَالَ: قَالَ ابْنُ زَيْدٍ: حَدَّثَنِي أَبِي قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «**مَا السَّمَوَاتُ السَّبْعُ فِي الْكُرْسِيِّ؛ إِلَّا كَدَرَاهِمَ سَبْعَةٍ أُلْقِيَتْ فِي تُرْسٍ**»، وَقَالَ: قَالَ أَبُو ذَرٍّ ﵁: سَمِعْتُ رَسُولَ اللهِ ﷺ يَقُولُ: «**مَا الْكُرْسِيُّ فِي الْعَرْشِ إِلَّا كَحَلْقَةٍ مِنْ حَدِيدٍ، أُلْقِيَتْ بَيْنَ ظَهْرَيْ فَلَاةٍ مِنَ الأَرْضِ**».

Ibnu Jarir ya ce: Yunus ya bani labarin cewa Ibn Wahab ya labarta musu, cewa Ibn Zaid ya ce: babana ya fada mini cewa: Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- ya ce: " **Sammai bakwai ba komai ba ne a cikin Al'arshi, face Kaman dirhamai ne guda bakwai da aka jefa su a cikin dan wani jaka na fata** ", yace: Abu Zarrin Allah Ya kara yarda a gare shi yace: naji Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yana cewa: (( **Kursiyyu ba komai bane idan an kwatanta shi da Al'arshi face kamar wani zobe ne na karfe da aka jefa shi a filin sahara.** )).

● " **Nine Mamallaki** ": Nine wanda Na ke da gamammen mulkin da ba shi da kaidi- da cikakken ikon da babu wani mai jayaiya da ni cikinsu.

● " **Ina azzalumai?** ": tambaya ce ta kalu bale, ma'ana ina masu mulki a gidan duniya? masu iko, da zalunci, masu girman kai ga bayin Allah? Za a tayar da su a wannan lokacin misalin kwayakin zarrah, mutane suna takasu da kafafuwasnsu.

● " **Da Hagunansa** " wannan riwayar ta saba ma riwayar da tafita inganci, idan kuma muka kaddara cewa riwayace da aka kiyayeta to ma'anarta zai zamo: (dayan Hannun), babu cin karo tsakaninta da riwayar: (( **Dukkan hannayensa biyu dama ce** )); ba kamar hagunan halittu ba, wacce takeda tawaya a kan damansu.

● **كَخَرْدَلَةٍ**: Kwayace irin ta tsiro karama sosai, wannan yana nuni akan matukar girman Allah, kuma hakika babu wani abun da ya isa ya gewaye Allah da sani.

● "**الْكُرْسِيِّ**": Wajen ajiye kafafu biyu na Allah Maigirma da buwaya.

● **تُرْسٍ** : Abun da akayi da fata ko itace wanda ake ɗauka yayin yaƙi a matsayin garkuwa daga takubba, mashi, da makamantansu.

● **الْعَرْشِ** : Halitta ce maigirma wanda Allah Mai Rahama Ya daidaita a kansa, babu wanda yasan hakikanin girmansa se Allah.

● Wannan hadisi yana nuni akan matukar girmar Allah -Maigirma da buwaya-, kuma ya dace da tafsirin ayar ga tarjamar babin.

**DALILI NA SHIDA:**

وَعَنِ ابْنِ مَسْعُودٍ قَالَ: «بَيْنَ السَّمَاءِ الدُّنْيَا وَالَّتِي تَلِيهَا خَمْسُمِائَةِ عَامٍ، وَبَيْنَ كُلِّ سَمَاءٍ خَمْسُمِائَةِ عَامٍ، وَبَيْنَ السَّمَاءِ السَّابِعَةِ وَالْكُرْسِيِّ خَمْسُمِائَةِ عَامٍ، وَبَيْنَ الْكُرْسِيِّ وَالْمَاءِ خَمْسُمِائَةِ عَامٍ، وَالْعَرْشُ فَوْقَ الْمَاءِ، وَاللهُ فَوْقَ الْعَرْشِ، لَا يَخْفَى عَلَيْهِ شَيْءٌ مِنْ أَعْمَالِكُمْ»، أَخْرَجَهُ ابْنُ مَهْدِيٍّ عَنْ حَمَّادِ بْنِ سَلَمَةَ، عَنْ عَاصِمٍ، عَنْ زِرٍّ، عَنْ عَبْدِ اللهِ، وَرَوَاهُ بِنَحْوِهِ الْمَسْعُودِيُّ، عَنْ عَاصِمٍ، عَنْ أَبِي وَائِلٍ، عَنْ عَبْدِ اللهِ؛ قَالَهُ الْحَافِظُ الذَّهَبِيُّ $ تَعَالَى، قَالَ: «وَلَهُ طُرُقٌ».

An karbo daga Abdullahi dan Mas'ud ya ce: ((Tsakanin sama ta duniya da wacce take binta tafiyar shekara dari biyar ne, tsakanin kowace sama da wacce take biye da ita tafiyar shekara dari biyar ne, tsakanin sama ta bakwai da Kursiyyu tafiyar shekra dari biyar, tsakanin Kursiyyu da ruwa tafiyar shekara dari biyar ne, Al'arshin Allah yana saman ruwa, Allah kuma Yana saman Al'arshi, babu wani abun da yake buya gareshi na aiyukanku )), Ibnu Mahdi ne ya fitar dashi daga Hammad bn Salamah, daga Asim, daga Abi wa'il, daga Abdullahi, Hafiz Zahabi -Allah Ya jikansa- ya ce: (Hadisin yanada hanyoyi ).

**DALILI NA BAKWAI:**

**وَعَنِ الْعَبَّاسِ بْنِ عَبْدِ الْمُطَّلِبِ ڤ، قَالَ: قَالَ رَسُولُ اللهِ ﷺ: «هَلْ تَدْرُونَ كَمْ بَيْنَ السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ؟»، قُلْنَا: اللهُ وَرَسُولُهُ أَعْلَمُ، قَالَ: «بَيْنَهُمَا مَسِيرَةُ خَمْسِمِائَةِ سَنَةٍ، وَبَيْنَ كُلِّ سَمَاءٍ إِلَى سَمَاءٍ مَسِيرَةُ خَمْسِمِائَةِ سَنَةٍ، وَكِثَفُ كُلِّ سَمَاءٍ مَسِيرَةُ خَمْسِمِائَةِ سَنَةٍ، وَبَيْنَ السَّمَاءِ السَّابِعَةِ وَالْعَرْشِ بَحْرٌ بَيْنَ أَسْفَلِهِ وَأَعْلَاهُ كَمَا بَيْنَ السَّمَاءِ وَالْأَرْضِ، وَاللهُ تَعَالَى فَوْقَ ذَلِكَ، وَلَيْسَ يَخْفَى عَلَيْهِ شَيْءٌ مِنْ أَعْمَالِ بَنِي آدَمَ»**، أَخْرَجَهُ أَبُو دَاوُدَ وَغَيْرُهُ.

Daga Abbas dan Abdul Mudallib -Allah Ya kara yada a gareshi- yaa ce: Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya ce: (( Shin ko kunsan ratan dake tsakanin Sama da Kasa?)), muka ce Allah da Manzonsa su suka fi sani, ya ce: ((tsakaninsu tafiyar shekara dari biyar ne, tsakani kowace sama zuwa wata samar tafiyar shekara dari biyar ne, kaurin kowace sama tafiyar shekara dari biyar ne, tsakanin Sama ta bakwai da Al'arshi akwai kogi, tsakanin kasansa da samansa kamar tsakanin Sama da Kasa ne, Allah Ta'ala Yana saman wannan, babu wani abu da yake buya masa na aiyukan Bani Adam )), ( Abu Dawud da waninsa suka fitar ).

● " **Allah Yana saman Al'arshi** ": Wannan nassi ne karara kan daukakar Allah Ta'ala, daukakar zati da kuma Sifofi.

● " **Babu abun da yake buya masa na aiyukanku** ": Aiyukan zukata da na gabbai, wadanda ake ganinsu, ko jinsu, saboda fadin ilminSa da yalwansa, mawallafin ya kawo wannan ne bayan ambaton daukakarSa don bayanin cewa daukakarSa baya hana IliminSa kan dukkan aiyukanmu, wannan kuma ishara ce karara kan daukakar ZatinSa, Madaukakin Sarki.

● ( هَلْ ): Alamar tambayace, tana nuni kan abubuwa biyu:

1. Kwadaitarwa ka abin da za,a fada.
2. Fadakarwa dangane da abin da zai karanta musu.

da damu. ● " **Allah da ManzonSa ne sukafi sani** ": Ana fada ne a:

[1] Lokacin rayuwar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam-.
[2] Da kuma al'amurra na Shari'a wadanda aka sanar dashi.

● Cikin wannan a kwai grmama Allah tare da tsoratrwa kan saba masa; saboda Yana samanmu, Ya daukaka akanmu gaba daya, IliminSa yana gewaye damu.

***MAS'ALOLIN BABIN:***

1. Tafsirin fadin Allah Ta'ala: [ *Kasa gaba daya damkarsa ne ranar tashin Alkiyama]. (QS. Az-Zumar : 67).*

2. Yahudawan da suka rayu a zamanin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- sun sa wannan ilmi kan Sifofin Allah, shiyasa basuyi inkari ba, kuma basuyi tawilinnsu ba, ( Kaman dai mawallafin yana ishara ne da cewa yahudawan sunfi alhairi samada wadanda suka canza ma'anonin sifofin, s ).

3. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya gasgata wannan bayahuden yayinda ya fada masa wannan maganar, Sannan Allah ayar qur'ani ta saka tabbatar da hakan.

4. Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- yayi dariya mai yawa lokacin da wannan malami bayahuden wannan muhimmin ilimin.

5. An tabbatar da Sifar hannaye guda biyu karara, Sammai bakwai suna hanun dama, kassai bakwai kuma suna daya hannun ( Alqur'ani da Sunnah sun tabbatar wa Allah da Hannaye guda biyu bisa ijma'in Salaf ).

6. Riwayar da ta bayyana cewa Allah Yanada hanun haguna ( Wannan riwaya ce da saba wa riwayar da ta fita inganci ).

7. Ya ambaci Azzalumai da masu girman kai.

8. Fadin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ((Kamar kwayar komaiya a tafin dayanku )).

9. Girman Kursiyyu idan an kwatanta shi da Sammai ( Kaman dirhamai ne guda bakwai wanda aka jefa a cikin ….. ).

10. Girman Al'arshi dangane da Alkursiyyu ( kamar zobe ne da aka jefa a fili fallau ).

11. Banbanci tsakanin Al'arshi da Alkursiyyu.

12. Nawane ratan dake tsakanin kowace sama da wacce take biye da ita?( tafiyar shekara dari biyar ).

13. Nawane ratan dake tsakanin sama ta bakwai da Kursiyyu? ( tafiyar shekara dari biyar ).

14. Nawane ratan dake sakanin Kursiyyu da Ruwa? (tafiyar shekara dari biyar).

15. Al-Arshin Allah yana saman ruwa.

16. Allah Yana saman Al'arshi.

17. Menene rattan dake tsakanin sama da kasa?. ( tafiyar shekaru dari biyar ).

18. Kaurin kowace sama kimanin tafiyar shekaru dari biyar.

19. Kogin dake saman sammai bakwai tsakanin samansa da kasansa tafiyar shekara dari biyar ne. Allah ne mafi sani ( Faidoji daga hadisan babin:

[1] Tsoratarwa kan saba ma Allah.

[2] Babu wani abu wanda yake buya ma Allah daga aiyukan Bani Adam ).

والله أعلم، والحمد لله ربِّ العالمين، وصلَّى الله وسلَّم على نبيِّنا مُحمَّدٍ ﷺ، وأسأل الله أن يختم لنا ولكم بالتَّوحيد؛ آمين.

## Jarabawar ragowar kaso na tara da cikitawa ( Babuka 16 )

Tambayar farko: sanya alamar (☒) a wajen da ya dace, ko kacika gurbin da komai:

1. Hukuncin fadain " Assalamu alallah " ☐ Makruhi ☐ Haram ☐ Halal.
2. As-Salam sunan Allah ne ☐ Na tabbattarwa ☐ Na korewa ☐ Duka biyun, Allah Ta'ala ☐ Ana rokonSa ne ☐ Ba a roka maSa.
3. Ba a roka ma wani da amintuwa daga wani abu se har idan halatta ya siffantu da hakan ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
4. Hukuncin fadin: " Ya Allah ka gafarta min in kaga dama "? ☐ Makruhi ☐ Haram ☐ Halal.
5. Ya halatta yin togaciya cikin addu'a -Kaman mutum yace: ya Allah kayi min abu kaza in kaga dama- ☐ Haka ne kuskure ne, togaciya cikin addu'a shine sanya sharadi ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
6. Babu laifi mutum yayi kokwanto wajen addu'a, kuma babu laifi ya rataye addu'ar ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
7. Idan mutum zaiyi addu'a to babu laifi ya roki Allah duk abin da yake so, domin babu wani abun da zai gagari Allah ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
8. Fadin mutum:

اللَّهمَّ إنِّي أسألك أن أكون بوَّابًا عند باب الجنَّة

" Ya Allah ina rokonka ka sanya ni nazamto maigadin kofar Aljannah ".
☐ Ya halatta ☐ Bai halatta ba.
9. Fadin mutum:

اللَّهمَّ إنِّي لا أسألك ردَّ القضاء ولكن أسألك اللُّطف فيه

" Ya Allah bana rokonka da Ka mayar da abin da Ka kaddara, sedai ina rokon tausayawarKa cikinsa " ☐ Ya halatta ☐ Bai halatta ba.
10. Shin wanne ya halatta bawa ya roki Allah?
☐ Aljannah ☐ Aljannar Firdaus, mafi daukaka cikin aljannoni.
11. Addu'ar istikharah (☐ Cikinta akwai ☐ Babu a cikinta ) rataye addu'a.
12. Fadin: " Bawan wane ko baiwar wane ", hukuncin fadan hakan: ☐ Halal ne ☐ Haram ne.
13. Fadin shugaba ga bawansa: " Ya kai bawana kawo min abu kaza " hukuncinsa. ☐ Ya halatta ☐ Bai halatta ba.
14. Anyi hani kan fadin " Yaron gidana, kuyangata " domin tabbatar da tauhidi ne, hatta cikin lafuzza ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
15. Roko haram ne, ko makruhi, se in akwai bukata ko lalura ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

16. Wanda ya rokeka kudi da sunan Allah domin yasayi wani abin da aka haramta dashi kamar giya ☐ Za a amsa masa ☐ ba za a amsa masa ba.
17. Hukuncin amsa ma wanda ya roki wani abu da sunan Allah:
☐ Mustahabi ☐ Wajibi.
18. Ya zo cikin hadisi cewa: " Duk wanda ya kiraye ku to ku amsa masa ", Abin nufi shsine: ☐ Gaiyata domin karramawa ☐ Kira.
19. Amsa gayyata ☐ Wajibi ne a sake ☐ Mustahabbi ne, sedai idan gaiyatar ta walimar aure ne to wannan wajibi ne.
20. Wanda ya nemi tsari daga wani abin da aikatashi ko barinsa wajibi ne to wannan ☐ Za a bashi tsaro ☐ Ba za a tsare shi ba.
21. Hadisin: " .. **To kuyi masa addu'a har sai kun ga cewa kun saka masa** "
ma'ana: ☐ Addu'a guda daya ☐ Kar kuyi kasa a guiwa wajen yi masa addu'ar .
22. Hadisin: " **Ba a tambaya wani abu da fiskar Allah se Aljannah** " ma'ana:
☐ Kar ka tambayi wani cikin mutane da fiskar Allah.
☐ Kar ka tambayi Allah da fiskarSa face Aljannah ☐ Duka amsa biyun.
23. Sifar fiska ga Allah ta tabbata ne da ☐ Alqur'ani ☐ Sunah ☐ ijma'i ☐ Duka.
24. Fadin:

اللَّهمَّ إنِّي أسألك بوجهك الكريم أن توفِّقني لحفظ القرآن

Ya Allah ina rokonKa -tawassuli- da fiskarKa Maigirma da Ka datar dani wajen haddace Alqur'ani ☐ Haram ☐ Halal ne, Hakanan cewa:

اللَّهمَّ إنِّي اعوذ بوجهك من النَّار

Ya Allah ina neman tsari da fiskarka daga wuta, hukuncinsa: ☐ Halal ☐ Haram.
25. Fadin:

اللَّهمَّ إنِّي أسألك بوجهك أن ترزقني أثاثًا جميلًا

Ya Allah ina rokonKa -Tawassuli- da fiskarKa Ka azurta ni da kayan gida masu kyawu.
☐ Halal ☐ Haram.
26. Hukuncin fadin: ( da kayi mini biyayya bakayi tafiyarba da baka hadu da wani hadariba ): ☐ Halal ☐ haram.
27. Hukuncin fadin: (da baniyi tafiyarba da ribar bata tsere mini ba ) ☐ Halal ☐ haram.
28. Hukuncin fadin: (da Allah Ya ga dama da banyi karyaba ) ☐ Halal ☐ haram.
29. Hukunci fadan: (da inada irin dukiyar wane da nayi sadaka dashi ): ☐ Halal ☐ mustahabbi ☐ haram.
30. Hukuncin cewa: ( da na halarci darasin da na faidantu ): ☐ Halal ☐ haram.
31. (☐ Yakamata ☐ Baikamata ba ga mai hankali ya tafiyar da rayuwarsa cikin abinda bazai amfaneshi ba.
32. Duk abin da mutum ba ya da iko akansa to (☐ya halatta a gareshi ☐ bai halattaba a gareshi ) ya kafa hujja a kansa da kaddara.

33. Ya halatta a kafa hujja da kaddara a kan ☐ Musiba ba zunubbai ba ☐ Akasinsa.
34. Zagin iska ☐ haram ne ☐ makruhi. Fadin: " wannan iskar cike take da ruwan sama " ☐ Halal ☐ haram.
35. Fadin: "Ubangijina yana sona " ga wanda ya samu wata ni'ima, halal ne ☐ Na'am ☐ kuskure ne.
36. Fadin wanda yaga wani fasiki mawadataci: (wannan bai cancanci wannan dukiyarba ): ☐ Ya halatta ☐ haram ne.
37. Mutum mai sakaci wajen aikata wajibai, Mai aikata abubuwan da Allah Ya haramta, kuma tareda haka sai ya kyautata zato wa Allah, to wannan yana daga (☐ munana ☐ kyautata ) zato ga Allah.
38. Zaton wani kan cewa koda ya roki Allah akan fiskar da ta dace da shari'a to lallai Allah bazai amsa masaba, to wannan: ☐ munana zato ne ☐ kyautata zato.
39. Fadin cewa: ( Allah zai iya azabtar da mai yi masa da a, ya bada lada wa mai saba masa ), zato ne ☐ maimuni ☐ maikyau.
40. Fadin wani: (Ni nafi cncantar matsayin sama da wane ) ☐ mai muni ☐ maikyau.
41. Fadinsa ga maras lafiya: ( Miskini ), ( ciwon bai dace da kai ba ), (da lamarin a hanuna yake da bai sameka ba ) wannan zato ne ☐ mai muni ☐ mai kyau.
42. Hukuncin fadin: (da lamarin a hannuna yake da na sanya wane a matsayin Mufti ) ☐ halal ☐ haram.
43. Fadin: ( hanyar kubuta ) daga munana zato yake ☐ haka ne ☐ kuskure ne.
44. Fadin: ( bai dace cututtuka su same mu ba, kuma ya kamata a yalwata mana arzikinmu ) wannan zato ne ☐ mai muni ☐ maikyau.
45. Dole mutum ya wa kansa zato (☐ Mummuna ☐ Maikyau ).
46. Wajibi ne mutum ya ringa munana zato wa kansa har ya gyarata da kansa ☐ haka ne ☐ kuskure ne.
47. Rai itace matattaran dukkan munanan abubuwa na rowa da zalunci ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
48. Matakan AlQada wal Qadar : ☐ Hudu ☐ Biyar ☐ Uku.
49. Hukuncin wanda yayi musun AlQada wal Qadar ☐ Ya fita daga musulunci ☐ Bai fita daga musulunci ba.
50. Fadin wani: (cikin zuciyata akwai wani abu na inkarin Qaddar ): ☐ ma'ana: akwai kokwanto rashin natsuwa ☐ Inkari da musantawa.
51. "Cikin zuciyata akwai wani abu na Qaddar " Ma'ana:……………………………., Shin zai iya kafirta da wannan?........................................................................................
52. Al-Qalami shine ☐ Farkon abin da Allah Ya halitta daga dukkan halittu ☐ Farkon halitta dangane da abubuwan da muke iya ganinsu.
53. Al'adar Salaf wajen kawar da shubuha da tambayar ☐ Malamai ☐ Masu ibadah.
54. Tambayar sama da malami daya ya halatta idan tambayar ta zamo ☐ domin samun tabbaci ne ☐ domin bibiyar sassauci ☐ Duka biyun.

55. Shubuha tana kawuwa gaba dayan idan aka jingina lamarin zuwaga ☐ Allah da Manzonsa ☐ Malamai.
56. Abin da ya zamo wajibi shine mutum ya nisanci jin shubuha domin zata damfaruwa da zuciyarsa ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
57. Yawancin mutane suna saba umarnin Annabi -Sallallahu alaihi wasallam- ta hanyar jin shubuha da yada ta: ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
58. Karanta Attaura da Injila baya halatta, rashin halaccin karanta wasunsu shi yafi dacewa ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
59. kulla ( babin abin da yazo dangane da hukuncin masu hoto ) kuskure ne daga wadansu cikin masu marubuta littafin saboda wannan babin ba shi da alaqa da tauhidi alaqarsa da babin fiqh ne ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
60. Ukubar mai yin hoto sun kai guda: ☐ biyar ☐ Hudu ☐ Uku.
61. Cikin yin hoto akwai kirkira da halitta wanda duk mai yin hoto yake tarayya da Allah a cikinsu ☐ Haka ne ☐ kuskurene.
62. Yin hoto kabirah ce (Babban laifi ) saboda: ( ☐ kamanceceniya da kafirai ☐ Yana cikin almubazzaranci ☐ Kwaikwayon halittan Allah ne ).
63. Yin hoton bishiya, da koguna, da duwatsu, da koramu ☐ halal ne ☐ haram.
64. Ana goge hoto ne da: ☐ Sanya wani launin na dabam wanda zai batarda alamar hoton ☐ yanke kayin mutum mutumin ☐ Idan wanda aka zana ne se a goge fiskar ☐ Duka, gwargwadon hali.
65. Kabari maitudu shine wanda a kansa akwai: ☐ Tuta ☐ Gini ☐ Launuka ☐ Wanda aka banbanceshi da waninsa da dutsi, da kasa ☐ Duka.
66. Daidaita kabari yana kasancewa ne da: ☐ Ayi su bisa karantarwar Sunnah ☐ daidaita su da kaburburan da suke gewaye da su ☐ duka biyun.
67. Ajiye hotuna domin girmama masu hotunan ☐ halal ne ☐ baya halatta.
68. Mai yawan rantsuwa ☐ yana girmam Allah ☐ ba ya girmama Allah.
69. Duk rantsuwa tanada farko da tsakiya da karshe ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.
70. Kibar da mutum yayi ba tareda zabinsa ba ☐ Abun zargi ne ☐ ba abun zargi bane.
71. Zunubi yakan girmama idan sababin yin zunubin ya karanta ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.
72. Yin rantsuwa idan akwai bukatuwa zuwa gareshi ko maslaha: ☐ Ya halatta ☐ Bai halatta ba.
73. Dukan karamin yaro ☐ Ya halatta kaitsaye ☐ Ya halatta da sharudda.
74. Allah Yayi alkawari bayinsa cewa: ☐ Su bautata masa kar su hada Shi da komai ☐ Allah bazai azabtar da wanda bai hada Shi da komai ba.
75. Al-Jaish -rundunar mayaka- shine abin da ya karu a kan (☐ mayaka 400 ☐ Mayaka 1000 ), Sariyyah kuma akasin haka.

76. Aikin da za a yi fi sabililillahi: ☐ Ta kebanci niyya ne ☐ Ta kebanci aiki ne ☐ Ta kunshi niyyah da aiki.

77. Muna yakar kafirai ne saboda maslaharsu, don tsamar da su daga wuta ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

78. Al-Ghulul: Shine boye wani abu na ganima don ya kebanta dashi (☐ Haka ne ☐ kuskure ne ). Hukuncin ghululi ☐ Halal ☐ haram ☐ Babban laifi.

79. Ba ya halatta -a yaki- kashe; kananun yaran kafirai, da mata, da masu ibada: ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

80. Kacancana gawan wadanda aka kashe a yaki, da boye wani abu na ganima, da ha inci, da kashe karamin yaro -a yaki- ☐ halal ne ☐ haram ne.

81. Ana karbar Jizyah ne daga: ☐ Yahudu, Nasara da Majus ☐ Dukkanin kafirai.

82. Hukuncin fadin: " Allah ba zai karbi tubarka ba ": ☐ Halal ☐ Babban laifi.

83. Hukuncin fadin: " Wallahi Allah ba zai gafarta ma wanda yayi shirka dashi ba " ☐ Haram ☐ Babban laifi.

84. Yin taka tsan tsan wajen subut da baka da sauke hukunci kan mutane ☐ Mubah ☐ Halal ☐ Wajibi.

85. Hani kan fadin: ( Allah ba zai gafarta ma wane ba, alhali wannan mutumin yana raye ) ☐ Wannan ya kebanci musulmi mai sabo ne ☐ Ya game musulmi da kafiri.

86. Abin da Shari'a tayi inkari shine fadin: نستشفع ( Muna neman ceton …): ☐ Allah a wajenka ☐ Cetonka a wajen Allah.

87. Ma'nar: نَسْتَشْفِعُ بِاللهِ عَلَيْكَ ……………………………………………………………………

88. Babin abin da yazo na tsarewar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- (☐ babi ne me cin gashin kansa ☐ Maimaici ne ) cikinsa akwai kariyar da Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya bayar wa Tauhidi cikin ☐ Aiyuka ☐ Lafuzza.

89. السيد ( As-Sayyid ): ☐ Yana cikn sunayen Allah ☐ Baya cikin sunayen Allah.

90. As-Sayyid daya ne daga ma'anonin As-Samad ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

91. Kebantacciyar Shugabanci tana halatta ga wani cikin halittu sabanin gamammiyar shugabanci: ☐ Haka ne ☐ Kuskure ne.

92. Mafi kyawun sifar Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- kuma mafi kaiwa makura: ☐ Bawan Allah kuma Manzonsa ☐ Muhammad dan Abdullahi.

93. Bayahude yafi alhairi a wannan babin, kuma yafi sanin Allah samada wanda yake musanta Sifofin Allah, kuma yake tawilinsu. ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

94. Ma'anar Al'arshi: ……………………………………………………………………..
Ma'anar Al-Kursiyyu: ……………………………………………………………………

95. A karshen Kitabuttauhid, kamar mawallafin ya roki Allah da ya nauyaya Mizaninsa da wannan littafin kamar yanda Sammai da Al'arshi, da Al'kursiy suka nauyaya? ☐ Haka ne ☐ kuskure ne.

96. Malamai masu yawa cikin magabata sun kira ingantacciyar aqida da sunaye masu yawa daga ciki a kwai: ☐ As-Sunnah ☐ Ash-Shari'ah ☐ At Tauhid ☐ Alfiqhul akbar (fikihu mafi girma ) ☐ Dukkan abin da aka amabata.

## Abubuwan dake cikin Littafin:


**Shimfida**…………….....…………………………………………………………………..3

**Babukan Kitab Attauhid a takaice ( Babuka 67)**……….…………………….....…….. 4

**Na farko: Gabatarwa ( Babuka 5 )**… ….……………………………………...……………. 12

[1] Babin wajabcin Tauhid……………………………………………………………..13

[2] Babin falalar Tauhidi da abinda yake kankarewa na zunubi…...……………………..22

[3] Babin wanda ya tace Tauhidi zai shiga Aljannah ba tareda hisabi ba ………………27

[4] Babin tsoro daga shirka……..…………………………………………………..33

[5] Babin kira zuwaga Shahadatu an La ilaha illallah…………….………………...……..38

Jarabawan kashi na farko ( Babuka 5 )…...…………………………………………...43

**Na biyu: tafsirin Tauhidi ( Babuka 9 )** …..………………………………………………...51

[6] Babin Tafsirin Tauhidi da Shahadatu an la ilaha illallah……..……………..…………51

[7] Babin yana daga shirka rataya kambu ko zare da makamantansu domin dage bala'i ko tunkude shi ……………………………………………………………………...55

[8] Babin abinda ya zo dangane da Ruqyah da Layu …………………...……...…………60

[9] Babin wanda yayi tabarruki da wata bishiya ko dutsi da mkamantansu …………..64

[10] Babin abinda yazo na yanka domin wanin Allah…………………………………..68

[11] Babin ba a yin yanka wa Allah a wurin da ake yanka don wanin Allah …………72

[12] Babin yana daga shirka yin bakance ma wanin Allah………………………………...76

[13] Babin yana daga shirka neman tsari da wanin Allah………………………………78

[14] Babin yana daga shirga neman agaji a wajen wani Allah, ko rokon waninSa …….80

Jarabawan kashi na biyu ( Babuka 9 ) ……………………………………….……...……..83

**Na biyu: Bacin bautar wanda ba Allah ba ( Babuka 4 )**…... ……….…….…………..…88

[15] Babin fadin Allah Ta'ala: ( **Shin suna shirka da Abinda baya halittar komai, kuma sune ake halittawa, kuma basa iya bayarda taimako garesu** )………....88

[16] Babin fadin Allah Ta'ala: ( ***Har a lokacin da aka kuranye tsoro daga zukatansu sai su ce: Menene Ubangijinku ya ce? Suka ce Gaskiya, kuma Shine Madaukaki, Maigirma*** )………………………………………..…………………………93

[17] Babin ceto ……..………………………………………………………………98

[18] Babin fadin Allah Ta'ala: ( ***Lallai ne kai ba ka shityar da wanda ka so*** )….103

Jarabawan kashi na Uku ( Babuka 4 )……………………...……………………………107

**Na hudu: Sababin kafircin banu Adam ( Babuka 4 )**……..……………………………110

[19] Babin abinda ya zo dangane da kafircin banu Adama da barin addininsu, shine: wuce iyaka cikin salihan bayi……………………………………..……………………...110

[20] Babin abinda yazo na kausasawa kan wanda ya bautata wa Allah a wurin kabarin wani salihi, to yaya kuma idan yabauta masa? …………………………………115

[21] Babin abinda yazo na cewa wuce iyaka cikin kaburburan salihai yana iya mayar dasu gumaka wadanda ake bautata musu baicin Allah …………………..…………...120

[22] Babin abin da yazo na tsarewar Manzon Allah SAW janabin Tauhidi, da toshe duk wata hanyar da zata kai zuwaga shirka……………………………………………..124

**Na biyar: Lalata hujjar wanda yace: shirka ba zata taba aukuwa cikin wannan al'ummar ba, hakanan a yankin larabawa -Jazira- ( Babi daya )**…………………....126

[23] Babin abinda yazo na cewa sashen wannan al'ummah zai bauta wa gumaka….126

Jarabawar kashi na hudu da na biyar ( Babuka 5 )……………………………………134

**Na shida: Aiyukan Shaidanci ( Babuka 7 )**……………………………………...…...138

[24] Babin abinda da yazo kan Sihiri……...…………………………………………138

[25] Babin bayanin wasu nau 'ukan Sihiri……………..………………………………..143

[26] Babin abinda yazo na hukuncin bokaye da makamantansu………………...………146

[27] Babin abinda yazo kan An-Nushrah (warware Sihiri)…………………………...…...151

[28] Babin abinda yazo kan campi )………………………………………….………154

[29] Babin abinda yazo dangane da aiki da taurari (Astrology)……………..…………161

[30] Babin anda yazo na neman shayarwa da taurari……………..……………………..165

Jarabawar kashi na shida ( Babuka 7 )……………………..……………...………………170

**Aiyukan zukata ( Babuka 9 )**………………………………………...…………………176

[31] Babin Fadin Allah Ta'ala: " ***Kuma akwai daga mutane wanda yake rikon kishiyoyi baicin Allah suna son su kamar son Allah*** "Al'ayah …………………176

[32] Babin Fadin Allah Ta'ala: "***Iyaka wancan Shaidan ne yake tsoratar da ku masoyansa, To kar kuji tsoronsu, ku ji tsoroNa idan kun kasance masu imani*** " ……………………………………………………………………………………….182

[33] Babin Fadin Allah Ta'ala: ( ***Kuma ga Allah kadai sai ku dogara idan kun kasance muminai*** )…………………………………………………...…………....……186

[34] Babin Fadin Allah Ta'ala: (**Shin yanzu sun amince wa Makrun Allah, To babu mai amincewa wa makrun Allah sai mutane masu hasara** )…....….190

[35] Babin yana daga imani da Allah hakuri kan kaddara……………..………………192

[36] Babin abinda yazo dangane da Riya………..……………………..…..…………196

[37] Babin yana daga shirka mutum ya nufi duniya da aiyukansa……..………………199

[38] Babin wanda yayi biyayya ga malamai da shuwagabanni cikin haramta halal....203

[39] Babin Fadin Allah Ta'ala: "***Shin, baka gani ba, zuwaga wadanda suke riya cewar sunyi imani da abinda aka saukar zuwa gareka*** "Al'ayat ….......……. 207

Jarabawar kashi na bakwai ( Babuka 9)……………..…………………………………… 212

**Tauhidin Asma'u was-Sifat: ( Babi daya )** ……………………………………...……218

[40] Babin wanda yayi musun wani abu na sunayen Allah da SifofinSa……..……218

Jarabawar kashi na takwas ( Babi daya )..…………………………………………..…….226

**Na tara: Lafuzzan da aka hana amfani dasu na shirka ( Babuka 26 )** …...……228

[41] Babin Fadin Allah Ta'ala: (***Suna sanin ni'imar Allah, sa'annan kuma suna musunta*** ) *Al'ayah*……..………………………...……………………………………...228

[42] Babin Fadin Allah Ta'ala: ( ***Saboda haka Kada ku sanya wa Allah wasu kishiyoyi alhali kuwa kuna sane*** ) …………………………………….…….………………….231

[43] Babin abinda yazo game da wanda bai gamsu da rantsuwa da Allah ba….. 234

[44] Babin hukuncin cewa: (Abinda Allah Yaso, kaima kaso )……….……………………236

[45] Babin wanda ya zagi zamani hakika ya cutar da Allah…………….……………………..239

[46] Babin kiran wani da alkalin alkalai da makamancinsa…….…………………………241

[47] Babin girmama sunayen Allah Ta'ala da canza suna saboda hakan ……………242

[48] Babin hukuncin wanda yayi izgili da wani abu na ambaton Allah, ko Alqur'ani ko Manzon Allah (Sallallahu alaihi wasallam) ………………………………………………244

[49] Babin abinda yazo na Fadin Alah Ta'ala: ( **Kuma lallai idan Mun dandana masa wata rahama daga garemu** ) Al'ayah ……………………………...…………..248

[50] Babin Fadin Allah Ta'ala: ( **To a lokacin da Ya ba su abin kwarai, sai suka sanya Masa abokan tarayya a cikin abin da Ya ba su** ) Al'ayah ……………..253

[51] Babin Fadin Allah Ta'ala: ( ***Kuma Allah Yana da sunaye masu matukar kyau*** ) Al'ayah ……………………………………………………………………………..………257

Jarabawar farko, kashi na tara ( Babuka 11 ).…………..………………………………..259

[52] Babin bai halatta ba ace: (Assalamu alallah ) (Haram)……….……………….…………265

[53] Babin hukuncin cewa: ( Allah ka gafarta min in kaso ) ( Haramcin sharadi cikin addu'a)……………………………………………………………………….……………....267

[54] Babin kar mutum yace ma wani: (Bawana, baiwata) ………..……………………269

[55] Babin haramun ne ko makaruhi a hana wanda ya roki wani abu da sunan Allah………………………………………………………………………….....………...271

[56] Babin ba a rokon wani abu da fiskar Allah sai Aljannah ……….………..274

[57] Babin abinda yazo gameda lafazin (لو) (Ba don abu kaza ba da kaza ya kasance) ( hukuncin yana kasuwa )…...……………………………………………………..….275

[58] Babin an hana zagin guguwa (Yarda da kaddara)………..………………………..278

[59] Babin Fadin Allah Ta'ala: ( **Suna zaton abin da ba shi ne gaskiya ba, a game da Allah, irin zaton jahiliyya** )Al'ayah ………………………….……..……...280

[60] Babin abinda yazo na hukuncin mai inkarin kaddarar (Babban kafirci)……..….283

[61] Babin abinda yazo kan masu yin hoto ( Narko mai tsanani )……………………...292

[62] Babin abinda yazo kan yawan rantsuwa (Na narko don girmama Allah )………. 294

[63] Babin abinda yazo na Alkawarin Allah, da Alkawarin Annabinsa ( Ikhlasi da koyi da Manzon Allah ) ………………………………………………………….... …..297

[64] Babin Abinda yazo na rantsuwar shigege wa Allah (Katsalanda wa Allah)…..301

[65] Babin ba a neman ceto da Allah a kan bayinsa (Saboda kamalarSa)…...………303

[66] Babin abinda yazo na bayanin Manzon Allah -Sallallahu alaihi wasallam- ya tsare shingen Tauhidi, kuma ya toshe hanyoyin shirka…………………………..….305

**Na goma: Cikitawa**………………..………..…………………………………….…….307

**[67]** Babin Abinda yazo dangane da Fadin Allah Ta'ala:

Jarabawar ragowar kaso na tara da cikitawa ( Babuka 16 )……………...……..…….313

**Faharasan abubwan da ke cikin littafin………………………………………………317**